[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI🌱

Writing by Amnah el yaqoub

1

Aguje na shigo gida, koda wasa bana kallan gabana, ko ina sa kafata nakeyi ,mama na tarar a tsakar gida tana tankadan garin tuwo, da saurinta ta daga kai ta kalleni kawai ta girgiza kai tare da fadin "Allah ya shiryeki,
" kafin taci gaba da abinda take anty na husna ta shigo Aguje itama, tanata faman haki, kasan cewarta me Dan jiki, mama tace" husna menene?" Kafin ta Koro Mata bayani saida ta wankeni da mari, aikuwa atake nasa kuka tare da bibbiga kafafuna,
" mama kin ganta ko" harara mama ta watsamin, husna tace" mama tsokanata tayi, har yaushe zanci gaba da fada Mata cewa niba sa'arta bace, Amma taqi ji"
mama tace "ubangiji Allah ya shiryeku"
Ta dubeni tasake cewa "ke kuma jiki magayi,"
ta maida hankalinta Zuwa ga husna, "ina Aiken dana muka?"
Sai asannan husna ta kalli ledar hannunta sannan tabawa mama tattasanta, nide cike da haushi nayi cikin daki ina harare harare.

Ma'u kenan koda wasa batasan raini, akwaita da San girma inde kana so ku shirya toka girmamata, wnda nikuma bazan yi wannan ba, inde Fannin tsokana ne to bada ga nanba, kasan cewarta me jiki shiyasa nake tsokanarta da suna lakekiya, kokuma Ma'u, ita kuma abnda bata so kenan, tafisan husna, nikuma inde inasan wani Abu awajanta to anan zakaga ruwan biyayya, anty husna kamr abakina aka radata

Asalin labari
Garin zaria gari ne me cike da dunbin albarka, mahaifinmu malam mu'az (principal) Dan Garin ne, unguwar kofar doka jikin gidan firzin, iyayensa sun Dade da rasuwa, su biyu suka bari shida kaninsa hassan suma su biyu ne yayinda hussainin yarasu awajan haihuwar su, Ammu hassan baida aure yanade karatu ne ynxu, muna kiransa da Ammu ne kasan cewarsa qani awajan mahaifinmu

Mama kuma sun hadu da Abba ne amakaranta inda aka turashi teaching practice daga zaria Zuwa kano anan suka qulla soyaiya harta kaisu ga aure har aka samemu, ita din haifaffiyar kano ce, kuma bafulatanar asali, haihuwar mama ta farko ta haifi yan biyunta Mata hassana da hussaina, hassana ta rasu awajan qyanda saikuma hussaina ayanxu wadda nake kira da anty husna, saikuma ni danaci sunan kakata ta wajan uba Nafeesa, Amma Ana kirana da FEENAH

Mrs usman ce🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

3

Anty maimuna ita tayimin komai muka shiga hostel ina ganin mutane da robobinsu Amma kala ta banbanta suna tafiya Hall na amsar abinci, lebira yana binmu da kayana akansa, har mukaje wani hostel inda naga ansa P.T.A HOUSE, wata yar tsohuwa muka gani fara da ita, ashe itace me kula damu, naji anty maimuna tace mama yar yalwa ina wuni nima na gaida ta, anbani kwana da komai nashirya kayana wasu kuma nasaka su cikin loka, daga nanfa nafada tunanin gida, Allah sarki mama kome take yi yanzu? Dumin danaji a fuskata shiya tabbatar min dacewa kuka nake, ga wani Abu danakeji a maqogarona, "sannu" naji anfada, wata matashiya ce medan jiki na kalleta tacemin "kema new Comer ce? Nace" eh tace sunana Rabi'atu idan bazaki damuba zanso mu zama qawaye ni nazo ne daga Hadejia, kefa?"

Uhm nayi ajiyar zuciya nace Mata" daga Zaria nake, "

😳Ido ta zaro tace" gaskiya daga nesa kike," ta sake cewa" kiyi hakuri kidena kuka ahankali zaki saba muma da haka muka saba, kinga ni tun daga js 1nafara", Ido na zaro cike da mamaki, nace "bazan iyaba," tacemin "dande ba'a kawokin bane, wanne bangare zakiyi karatun"?

"  Arabic"

murmushi tayimin tace" gaskiya ni ina S.T.Q ne (Senior Tahfizul Qur'an) ss1,amma kirki damu akwai qawata Zainab da take S.A.S (Senior Arabic School) zan hadaki da ita, batada matsala, saiku dinga tafiya tare harkisan kan school din,"

godia nayi Mata, tace" ga gadona nan Opposite din naki idan kina buqatar wani Abu,"

nace Mata" to. "

Ta Mike Zata tafi sannan tacemin" baki fadamin sunanki ba,"

NAFEESA MU'AZ Amma FEENAH ake kirana, tayi murmushi "nice name"

" shukhran" nafada Mata,

Tace " iyeeee gaskiya ne kaji yan Arabic,"

murmushi na maida Mata, ni shaf na manta da larabci nafada Mata, kuma hakan yasamo asali ne da musun da mukeyi nida husna agida, tayimin turanci in maida Mata da larabci, duk wanda baijiba munyiwa kanmu, 😃😃hawaye ne suka zubomin Allah sarki anty husna qawata yayata abokiyar fadana

** *** **

"Wai bazakici abincin nanba tun dazu kinsa kwano agaba Babu abinda kike sai tunani"

husna tace "mama wallahi nafisa nake tunani Allah sarki ko yaya take yanzu"
mama tace "toya za'ai husna, jinake jiya jiyan nan kika Gama cewa garama ta tattara yanata yanata tatafi," husna tace "to ai mama itace take tsokanata,"

"haka de kuka iya, inji mama, yi sauri ni kici kizo ki doramin kunun gyada babanku yakusa dawowa, banaso ya tadda ba'ayiba yafara fada, daga kai husna tayi, tana goge qwallar idonta, kallanta mama tayi, ita kanta daurewa kawai take Dan wani Abu takeji aranta kamar ta fashe da kuka, toya za'ayi, nafeesa kwata kwata bataji, tafiyarta school din shine kwanciyar hankalinsu.

** *** **

Cikin wata daya na goge, nasaba da mkrnta, saide kewar su mama danake kwana da ita nake tashi, kwanciyar hankali na shine ina tare da Zainab da kuma Rabi'atu, kokari na da kuma yawan surutu danake dashi shiyasa nayi jama'ah duk inda nabi zakaji Ana Feenah Feenah ba junior ba, ba senior ba, anty maimuna tunda na bata dubu dayan nan nace inji Ammu shikkenan kullum saita yabeshi, babanku yanada kirki Feenah gashi Dan kyakykyawa, nide kawai jinta nake ina Mata dariyar yaqe, to wanne kirki mutumin dayayi sanadin rabani dasu mama.

** *** **

Nayi suna sosai amakaranta har club nashiga na larabci wato Arabic Club, kuma hakan yaqara temakamin wajan sanin larabci na, haka kuma suna ji Dani da suka fahinci inajin larabci sosai yawan fitar da za'ayi kokuma wata drama to Dani aciki.
Ranar wata jama'ah muna dakinsu Zainab sani, nida Rabi'atu kaina Akan acinyar Zainab tanamin tsifa,tace" Feenah kanki badai gashi ba, infada miki wani sirri?"

Nace Mata" fadi,"

tace" wallahi har darura nake kicemin inyi miki kitso sbd kan naki yayi tsawo", kallanta nayi nace" lalle bakisan me tsawon gashi ba, tacemin "kamar ya" , nace wlh da kinga na husna bazakice inada gashi ba, tafini gashi, Ido ta zaro tacemin "a hakan" nace" yes, "tace" kai Feenah kinga fa gashinki"

nace" baby bazaki yarda ba sai kin ganta tukunta," haka sukai ta mamaki, muna firar club dinmu ne Atu tace "nifa Feenah wlh idan kina larabci har birgeni kike, bari kiji inde kikasa abaya kikai Rolling ko hmm kede kawai qawata "mafi kalam" (ba magana)" daria mukayi Gaba dayanmu" wlh Atu Allah ya shiryeki,"
daga karshe muka tafi yawonmu kasancewar juma'ah ce Babu abinda ake, saida muka tsaya awani bohol dayake gaban Dakin su Zeey wato Gumel house muka qaraci wasan ruwanmu sannan muka tafi, mune Arewa house, su Hadejia house da kano house, kasan cewar duk muna da friends acan sai wajan magrib muka tafi dakinmu nida Atu.

Mrs Usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

2

Babu abnda nabari daga kamannin mama tamkar photo copy, yayinda anty husna tayi kama da abbanmu, ayanda mama take bamu labari itama hassanar anty husna suna kama da juna Sam bazaka gane suba.
Nikam kamar maman nadauko Hali nede ya banbanta fara ce ni tas da dogon hancina, inada yalwar gashin gira tare dana ido, ayayinda Dan qaramin bakina yake da taushi me launin ja, inada gashi dede misali Amma na anty husna yafi nawa yawa
Gaba daya na fitini yaran unguwa banda wasu qawaye na kirki sai marasa ji irina, ni kenan kullum cikin yawo tare dasu, qawata ta arziqi daya ce Amina yarinyar maqocinmu.
Shekara ta goma sha hadu matakin karatuna ynxu ne magana junior, ayayinda anty husna take 17years yanxu ne take shirin yin candy, ganin yanda na fitini yaran unguwa da jawa iyayena magana hakan yasa Ammu yace akaini boarding school ko suma sa huta da wannan abin fadar danake rabawa.
Hakan ce ta kasance da'aka tashi sai aka rabani dama jihar Gaba daya akai nesa Dani izuwa jigawa, bording school ta BABURA, kasan cewar tun muna yara nafi karfi ta bangaren Arabic, husna boko shiyasa tayi science nikuma nake Arabic school, inada kokari dede misali

musanman ta Fannin larabci, kokadan bana maida hankali sosai Akan boko kawai nide larabcin Nan nasa agaba, ayayinda husna kuma ko ta'al bata saniba saide ta tambayeni itama tafisan bokonta.
Bamusha wahalaba Akan hanya kasancewar Ammu yasan jigawa kadan, hakan yasa muna Zuwa babura muka dau hanyar dazata sadamu da school din, mun danyi tafiya kadan sannan muka je gate din makarantar, dayake Ana kawowa dalibai shiyasa muma muna Zuwa aka Bude mana gate din muka shiga, akwai tafiya medan nisa kafin muka shigo cikin makarantar, muna Zuwa Aria class nafara gani sai kuma bishiyoyi dayawa, wadanda basuda cikar ganye, ina juyawa hannun hagu na na hango wani gate din na daban, wasu yanmata nagani guda biyu suna dosowa inda muke sukazo zasu wuce ta gabanmu, daya daga cikinsu ce take magana da yar'uwarta, muyi sauri muje hostel kar abusa karbar lunch mu makara adakemu, anan nagane kenan gate din hostel ne, Ammu ne yamusu tambaya su nuna mana office din da ake karbar sababbin dalibai, Babu musu suka nuna mana wani office, Nan muka nufa, tagaban wani class muka wuce naga ansa J.A.S 3B muka wuce mukaje office aka gamamin komai, hatta roba da kofi sun bani sbd karbar abinci, anan malamin yahadani da wata prifet sbd ta nunamin inda zan zauna da class dinmu, sunanta maimuna, Ammu yabani kudi yace indinga amfani dashi kafin suzomin visit, yabani  1k yace inbawa maimuna ,yaqara da cewar bazai min fadaba idan na musu laifi zasuci ubanane yaqara Gaba, daga nanfa idona yarena fata, ba uwa ba uba Babu yar'uwata mai sona husna.

Mrs Usman ce🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to Mrs Abdallah

4
Watana biyu mama Abba husna da Ammu sukazo ganina, nayi murna kamar ba gobe, kowa sai nan nan yake Dani, Ammu kuwa fuskar nan ahade "ke baki iya gaisuwa bane" nace" sannu Ammu ina wuni?" Bai amsaba

naje nakira musu qawayena harda anty maimuna suka gaisa, ina kallanta tana satar kallansa shima haka, nan kuwa basusan uwar yan sa'ido tana hankalce dasuba,🤣 husna ta taboni tace" autar mama nakusa candy fa,"

fari nayi da idona nace" wlh fadi ki qara nice farko nice qarshe," hararata tayi tace" a a kece qarshen de yarinya", nace" ina lissafawa fa tare zakuyi candy da anty na," tace
" wace antynki bayan ni," nace "aike ta dabance, anty maimuna nake nufi,"

"Ok" tace,kallan su mama tayi taga hankalinsu baya kanmu tace" ke wannan boss dinfa naga suna kallan kallo shida ita, koda wata aqasa ne? "
Nace" nima haka nagani," dariya tayi tace" intayi tsami maji," dariya mukasa harda tafawa, kallanmu mama tayi, aranta tace" me Hali baya fasa abinsa. "
Dazasu tafi kuka nasa musu, ina kallan Ammu tagefen idona yana harara ta, niko ko ajikina, Abba yayimin fadan karatu da fatan alkhairi, yayinda mama tayimin fada Akan cin abinci, tace" nafeesa gashinan baki rasa komai ba, Amma duk kinbi kin rame saikace yar gidan kamaye awun igiya, kinyi firit dake sai wani uban kwankwaso", dukanmu maganar mama tabamu dariya bnda Abba da Ammu da hankalinsu baya kanmu, haka suka tafi inaji ina gani, sai kuma kewarsu tadawomin sabuwa fil, Amma dana tuna saura befi wata dayaba muyi hutu sai naji sauqi.
Haka muka Gama term din bayan munyi jarabawa nazo ta biyar, cike da murna nadawo gida, kowa yayi farin ciki da dawowa ta, haka kuma su mama sunga canji atare Dani, mun baje afalo ina tabawa husna labarin bording, Ammu yayi sallama take muka shiga taitayinmu, muna gaisawa nabashi report dina, murmushi yayi yace yayi kyau saiki qara dagewa, "insha Allah" nace, yasakai zai fita mama tace "ga abinci fa,"
yace "yana dawowa."
Allah sarki sai gashi ya dawo da leda ahannunsa ya miqo min, nakarba tare da fadin "nagode,"

"gashinan kyaci duk kin rame sai uban qashin wuya" mama tace" kaima de kafada nafeesa batasan cin abinci. "

Araina nace" ai kaine ka ziga akaini school din," shide ya dauki abincinsa yayi waje, yana fita muka Bude ledar, kaza ce babba sai maiqo take, kai nida husna munyi party ranar mama tace" kamar Baku taba cin kazaba," husna a kace ai mama kazar Ammu daban take," tace "wato kun raina babanku hmm zaku hadu dashi ai, jiki magayi."

Dazai fitane bayan yagama cin abinci yacemin "ya gajiyar hanya ya qawayen naki?" Nace "suna nan kalau anty maimuna ma tace na gaida ka,"
be cemin komai ba yafice, aikuwa mukasa daria, nace" anaso Ana kaiwa kasuwa, "husna tace" hmm damafa ita yakesan tambaya, shine aka wayance "ya qawayen naki" tafada tana kwaikwayon maganar sa, dariya muka qara sawa.
Haka naci Gaba da karatuna a jigawa cikin kwanciyar hankali, Dan nalura da jihar akwai zaman lafiya, a term dinmu na karshe su anty maimuna sukayi candy, nayi kuka harna godewa Allah, tabani address dinta hade da number waya, nima nabata nawa, nayi kuka na rashin ta, danma da qawayena yan Amana zeey da atu

Mrs usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to Mrs Abdallah

5...
Rayuwa na tafia lokaci na sauyawa, harna shiga  ss 3,yayinda husna tasamu gurbin karatu a A. B. U zaria,tana karan tar "lab" a wannan lokacin kam, komai nawa yasake futowa, nazama yanmata boobs dina dede misali yayinda hips dina suke acike, naqara haske nutsuwa tazomin nikaina idan nayi kwalliya tsayawa nake ina kallan fuskata musamman idan naga nayi murmushi kumatuna sun lotsa, (dimple), nida husna bazaka ce yaya da qanwa bane danna tarota komai, nan kuwa tabani shekaru masu yawa kafin a haifeni shiyasa batasan raini.

"Zeey wai kukan nan be isabane, tun dazufa kike ta faman yi,"
"feenah Dan Allah kudena kuka,"
tafada tana goge kwalla itama, rabuwa kenan Babu dadi, anhadu daga gari mabanbanta gashi ynxu za'a rabu, munyi alkawarin ko bayan mun rabu zamu dinga zumunci, haka muka rabu kowa rai Babu dadi, munyi exchange din numbers tare da address, daga karshe akazo daukar kowa muka rabu cikeda kewa
Ammu ne yazo daukana shida wani abokinsa banma sanshi ba acikin abokan Ammu, muna tafiya suna firarsu, munzo wani gari suka tmbyeni nafeesa inane nan, nace musu STK ne (sule tankarkar) haka sukai ta tambayata garuruwa ina fada musu su Gumel dasu layin dazaka shiga Dan zomo,, su gagarawa, munzo round na wani gari gujungu anan bacci yafara fizgata, bansan kuma me suke tattaunawaba.

 **   ***    ***

Kwance yake Akan bed dinsa qirar Italy, Dakin na kalla komai pink and blue ne, banga fuskar wanda yake kwancen ba kasan cewar yarufe duka har fuskarsa da wani farin tattausan blanket,yaya! Yaya!! Yaya!!! Tafada da karfi, dakyar ya Bude Zara zaran gashin idonsa, yasaukesu Akan ta, "Saudat yaushe zaki bar mutum ya huta ne,"

Dan turo baki tayi, tace" yaya momy tace infadama break fast is ready"
"naji" shine kawai abinda yace yajuya yaci Gaba da baccinsa, sai wajan eleven yatashi, dama haka yake, kasan cewar Babu abinda yake yi, bayan yayi wanka saida yagama shafe shafensa kamar wani mace sannan yafuto, iyayansa yasamu a main falo bayan ya gaida su ne momy tafara fadan data saba wato Akan rashin cin abinci da wuri, shafa kansa yayi cike da shagwaba

yace "momy zan dinga cifa"
, yan biyu ne sukasa daria Muslim yace "yaya na shagwaba kamar mu" , bukhari yace "ai shima namiji ne shiyasa yake yi, dama maza ne sukeyi ko momy," hararарsa tayi tace" ai sakarci ne yasa sukeyi din ba komai ba, "
Muslim yace" yaya wai hakane? ", dalla kuyiwa mutane shiru kamar dasu ake magana," momy bari inyi sauri inci abinci akwai inda zanje, abincin sa yakeci cike da nutsuwa dady yafuto da shirin office bayan ya tsugunna ya gaida shine, yace " my son idan kagama abinda kakeyi kuje ka raka saudat Zata duba exam dinta jiya tayimin magana nace tabari Zuwa Yau mugani, kadaure kakaita banaso tana driving da kanta ne" , amsawa yayi cike da ladabi, bayan yagama ne saudat ta futo sanye da atamfa Riga da sket, dinkin ya karbi jikin ta kasancewar ta fara, suka yiwa momy sallama suka tafi.
Iyalan sanata muhd marzuq kenan, matansa biyu yana zaune a unguwar sharada, marzuq farid Dan kasar masar ne balarabe ne na asali yana kasuwancin saida motoci daga masar Zuwa Nigeria, kuma sosai harkar ta karbeshi, yana yawan zama a Nigeria da matarsa saudat balarabiyar masar suna Nigeria Allah yabasu ciki suka reneshi a Nigeria har lkcin haihuwarsa yayi suka samu muhd, bayan haihuwarsa da shekara ashirin ta rasu, haka marzuq yayi ta renon muhd haryakai minzalin aure, bayan yaga hankalin dansa ya kwanta shine ya sake aure ya auri wata balarabiyar mai suna bara'ah, Amma ita tafisan zaman masar tace bazata iya nesa da iyayenta ba, shiyasa shima marzuq din zamansa yafi yawa a masar, shikuma muhd yace yafi San Nigeria inda yagama karatunsa yafada harkar siyasa har yakai matsayin sanata, saide suje masar ziyara shida iyalansa, matarsa ta farko hajiya hafsat tanada yara hudu Ahmad shine babba sai saudat dataci sunan kakarta wadda ta rasu, sai kuma yan biyu bukhari da Muslim, sai mamy hakima, tanada yara biyu mabaruka da maryam, gidan Ana shimfida zaman lpy Babu tashin hankali, haka kuma basa nuna banbanci Akan yaransu saide Akan Ahmad, mahaifinsa yana mutukar sansa, ya shagwaba shi duk abinda yake so yi masa yake, kodan shine babban dansa oho.
Yana wadaqa da kudi San ransa, haka iyayensa agaban kowa nuna masa kauna suke, Yau shine wannan mota gobe waccan, saide baya neman Mata haka kuma Babu ruwansa dasu shaye shaye na zamani kamili ne na gske haka kuma yatsaya Akan qannansa Babu wasa sosai yake kula dasu.
Ahmad yahadu qarshe ne wajan kyau Gaba daya shiya dauke kamar kakansa marzuq saide kawai launin fatarsa ne yadau na momy wankan tarwada ne, yanada doguwar fuska gashin idonsa gazar gazar masu tsawo tare da dogon hanci idan yayi murmushi gefen kumatunsa daya yana lotsawa yayinda yake Dan karamin lips masu laushi, ba shida jiki sosai, haka kuma Shiba ramamme bane, yanada tsawo daidai misali, Ahmad yahadu karshen haduwa gashida gayu, kuma sai gayun nasa yahadu da kudi, Dan haka yake facakarsa San ransa, duk kannansa farare ne bnda maryam shida itane kawai fatarsu take da Dan duhu Amma daka gansu kasan hutu yazauna musu, baya shiga sabgar yanmata shiyasa har Yau baida wata budurwa, shekarar sa 27 yanzu, yagama degree dinsa a masar wajan kakansa, yakaranci bangaren kasuwanci (business administration)

** *** **

Kinsan Allah feenah idan bakiyi sauri ba zamu tafi mu barki, turo bakina nayi nace kai sister ynxu fa zan Gama, tsaki tayi "haba mutum kullum baya gajiya da shafe shafe" wayarta ce tayi ringing ta amsa tace" hello sister aysha gamu nan fa ahanya", husna ce ta zare wayar tace" karyata ke aysha kinganta nan tana abinda ta iya, shiru tayi sannan naji tace karki damu ai Yau sai kwanan kano insha Allah, OK bye sai mun zo. "

Mrs Usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to Mrs Abdallah

7

"Sister Dan shirya ki rakani gidan su khadijaty mana, tun shekaran jiya take ta damuna awaya inje, naqi Zuwa, shine Yau nace Mata gani nan ahanya tare da autar mama" ,nace
"khadijatyn ki qawarki ta Amana,"
tace "yes kinsan ni banasan kwashe kwashen qawayen nan kamar ki"
, dariya nayi nace "Allah  sarki ni, aina kusa denawa insha Allah nima ina shiga babbar makaranta shikenan,"

tace "nikuwa ina qawayen ki su Zeey,"

"dazu ma munyi waya kalau suke"

"OK,"

Munje gidan su khadijaty yarinya me hankali tayi mana tarba ta mutunci, Babu ruwan ta, saida suka Gama firar rakinsu sannan mukadau hanyar gida.
Munzo daidai layin gidanmu mukaji Ana mana horn abayanmu, Babu wadda tajuya acikin mu, "haba yanmata inata muku magana kamar bakwa jina" juya manyan idanuna nayi nace "ayya ai kasan dayake ba jinsinmu daya da motor ba shiyasa mukayi tunanin da yar'uwarta kake," murmushi yayi yaga alama tanada zafin kai, husna ya kalla yace" to kuyi hakuri, nayi laifi nide sunana auwal kuma ina zaunane a kaduna, naga sister dinki kuma tayimin wlh ina kaunar ta Dan Allah ko zaku bani dama nasaukeku agida ta yanda zanga gidan namu?"

Husna Ikci daya tayaba da hankalinsa Babu ruwansa da tarkacan nan irinsu tara suma na samarin zamani, tace" karka damu, acan baya kadan muke ai munkusa qarasawa, "
Yace" a a anty kode bakwasan shiga ne, Baku yarda daniba, "

tace" masa shknn, sis mushiga",

muna hanya yake tmbya ta number ta, nace masa" bnda waya," yacewa husna" wai haka ne anty, "murmushi tayi tace" karka damu zan baka"

, inajinsu yana tambayarta tanata bashi amsa akaina, daga karshe ta bashi Number ta, muna Zuwa kofar gidan, gabana yabada damm ganin Abba da Ammu atsaye, sum sum muka futo daga motor mukayi gida.
Juya motar yayi, shima ya futo su Abba suna tsaye suna kallan ikon Allah, yatako yazo har wajansu, har qasa ya tsugunna yagaidasu ya gabatar musu da kansa, sosai su Abba sun yaba da hankalinsa, "yaro daga ganinka naji hankali na ya kwanta dakai inde nafeesa kake so ka nemi soyaiyar ta, idan kun dedeta atsakaninku shknn ni bnda damuwa, Amma yanzu de makaranta Zata tafi, bazan iya yi musu auren dole ba Amma inde kun dedeta banda matsala," godia auwal yayi yana farin cikin Jin kalaman wannan bawan Allah, yatashi yatafi.
" kai wallahi bakiji gabanaba yanda ya yanke yafadi, husna tace" gabanki ko gabana nida na zaqe harda shiga gaban motar, 🤣"

" hmm Allah de yarufamana asiri, nikam gaskiya be minba",

" kai sister nikuwa kinga nayaba da hankalinsa shiyasa ma nayarda har muka shiga,"

nace" haba anty husna kinganshi fa, wani babba dashi, nikam ina bana sanshi, "
kallona tayi tace" wato ke sai yan zamani ko masu ajiye suma suna tafe suna kakkade takalmi da handkerchief"🤣
, nace" a a dede misali de, "

" auta kinga ki shiga hankalin ki da irin samarin nan, ni basa birgeni,"

" kai anty husna kuma de daga magana"

" to sai kiyi tayi ai kuma wlh saina ziga Ammu anbaki shi, inyaso ki mutu,"

aikuwa kan kace me na fara kuka ni wlh bana sanshi, haka kawai za'a min auren dole, ganin ina kuka kuma sai jikinta yayi sanyi, dafa kafadata tayi tace" feenah wasafa nake miki, haba keda kike auta waye zai miki dole bayan mama ma tana ji dake, "

dago kaina nayi ina murmushi Dan nikam inaso inji Ana zugani awajan mama, tace" yauwa kokefa,  share hawayanki in baki wani labari, kawai rannan basai naga wannan maimunan taku ba,"

nace" wai anty maimuna"
tace "yes ita, wlh mun futo daga lecture kawai naji ance husna, ina juyawa naganta, ni mantawa ma nayi ban fada mikiba, tace kuma in baki hakuri wlh tarasa paper din data rubuta Number ki da address din gidan nan da tuni ta nemeki, harfa number mukai exchange tace ma inbawa Ammu number,"

😳 ido na zaro nace" sanshi fa take",

"aida gani sanshi take, shekara da shekaru takasa mantawa dashi, tace yanzu bari idan yashigo yana mana muzurai kawai zan bashi number shknn mun rufe bakinsa,"

"aikuwa haka za'a yi," dariya mukasa hade da tafawa.
"kun dawo ne? Mama yanzu muka dawo auta nake rarrashi yanzu ma wai Dan tayi miki suruki nace zamusha biki shine take kuka,"
murmushi mama tayi tace "Allah ya kyauta."

Da daddaren kuwa Ammu yashigo husna ta bashi Num. Kamar bayaso ya karba, nan kuwa wani sanyi yaji aransa, nikuwa sai washe gari nakirata mukasha firar yaushe gamo.
Kwance nake a dakinmu ina karanta novel a wattpad husna tace" ansamu wattpad anmanta da littafi yanzu andawo online, "
" dariya nayi nace wlh banyi tunanin karatun online zai kai na littafi dadiba ada nafijin dadi in rike novel ahannu na ina karantawa Amma yanzu inaaaa sai wattpad," husna tace" ai shine abinda nake fada miki kinki yarda, ya kikaji hafsatul ikhram, wannan yana so wannan anaso ahadasu ashe duk cikima Babu me dauka, pilot zaizo ya dauke abarsa, nace "wannan shi ake kira da rashin sani."
Da daddare saiga kira da wata new number nadauka, bayan mun gaisa yake sanar Dani auwal ne, tsaki nayi araina nace DANA SANI daban amsaba, anan yake sanar Dani yanda sukai dasu Abba, yaqara tabbatar min da cewa zai rikeni Amana idan na amince dashi hakade yayi ta yimin surutu nide nawa eh a a shikkenan, ahaka nace masa saida safe zan kwanta.

** *** **

Haka auwal yake ta kokarin kirana a koda yaushe wataran in daga wataran inqi,haka rayuwa tayi ta tafiya har Ikcin bada admission yayi.
Ammu shine yayi duk wani shige da fice yasama min, muna zaune yazo yake sanar Dani cewa nima nasamu admission a legal, mama tayi murna, nikuwa araina nace shknn nazama yar jigawa," to Ammu nagode yaushe zan tafi jigawan?" Yace '' me zakiyi a jigawa, haba nafisa dama abinda yasa nakaiki nesan saboda rashin jinki ne, Amma yanzu legal ta kano nake nufi, bansan Ikcin danayi murmushi ba, sbd dangin mama dasuke kano.

** *** **

Agajiye ya dawo gida, yana sanye cikin qananun kaya bakin wando tare da jar Riga, kan nan

yasha gyara, sai sheqi yake, yana sanye da agogo Gucci, fadawa yayi cikin daya daga cikin kujerun falon, "wash Allah, yafada" ,walaya ce tazo da sauri yallabai sannu da Zuwa, bai amsa bataba tajuya takawo masa ruwa mai sanyi, ta sake juyawa kenan taji yace kiramin sauda, to yallabai angama angama, ta Juya, wayarsa ce tayi qara akasalance yadaga guy ya akayi, bansan me a kace daga daya bangaren ba, yace tahir Babu wata Abuja da zamu je kawai ka share ta haba yrinya karama Tanata juyaka, kawani nace Mata, ba inda zani, naji naji ni karkamin kuka, Allah yakaimu jibin sai muje Amma gsky saide mubi flight bazan iya tuqi ba OK, right ya wullar da wayar Akan kujera ya lumshe idonsa, yagaji wallahi daga office din dady yake yagaji, gashi daga can ya wuce yadubowa saudat admission latter dinsu daya futo.
Yaya gani, sai sannan yabude idonsa, yafada Mata dalilin Kiran, yeeeee tasaki tsallan murna ta rungumeshi, bigeta yayi waike saudat yaushe zakiyi hankali ne, karkayi tunanin cikin zafi yake maganar a a da sanyinsa yake yi shi ala dole fada yake Mata, dariya tayi tace yaya murna ce fa, fari tayi da idonta shknn nakusa yin friends, inshiga lecture, idan kun kirani in daga ince yaya ka kirani alokacin muna lecture, ganin shirman nata bazai qare ba ne yasashi girgiza kansa yajuya yayi part dinsa, ita kuwa ta daga kai sama Tanata Zuba batasan ya silale yabar falon ba, tace indinga shiga motata, ina Zuwa siyan shawarma daga nan indawo gida koba hakaba ya...
Ganin wajan tayi wayam lalle ma yaya hmm zamu hadu ne saina qarasama wallahi

Mrs usman ce🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

8

Tunda na fara karatu na tsaida hankali na waje daya, banda wasu qawaye, kawai abin gabana nake, banda burin daya wuce yanda na fara karatuna da Arabic in qarasa dashi, kuma sai nayi sa'ah suka bani faculty of Arabic din, kullum daga gidan kaka rabi nake tafiya, aysha tayi tayi in koma gidansu Amma naqi, nace sai na gaji da gidan kaka sannan zan dawo nasun.
Sanye nake cikin doguwar Riga me sauqin kudi, nayi rolling da farin mayafi, tafiya nake hankalina kwance kasancewar akwai sauran minti talatin kafin mu shiga lecture, "guy kaga cikar danake fadama, yarinyar tayi bala'in tafiya da imanina"

" haba salman karka bani kunya mana, kaida Mata ke rububi, suke burin ka kulasu Amma wannan abar kakasa tun kurarta haba salman karka bada gayu mana,"

cike da takaici salman yace da abokinsa "kaga yaks karka qara kiranta da wata aba, babyn nawa zaka kalla kakira da wata aba,"

dafa kafadarsa yaks yayi yace "haba abokina menene abin zafi kuma naji sorry"

"karka sake nafadama karka sake,"

"haba salman wannan yawane kawai komai ya wuce kabasar kawai, yanzu de jeka karka bada gayu,"

"kuma fa haka ne"

yafada tare da saukowa daga kan motor
Kaina aqasa ina tafiya kawai sai ganin mutum nayi agabana "Malam lafiya?" miye haka? Ko bakaga tafiya nake ba? Duk maganar datake kawai Dan qaramin bakinta pink color yake kalla yanda take sarrafa lips dinta, "Malam ko da kurma nake magana ne, bakajina?"
Murmushi yayi yace" salman, salman guy kenan, wannan shine sunana, tun ranar dana fara ganinki naji kinmin, so abinda nakeso dake shine kiyimin biyayya, ban taba son mace tace bata sonaba, kinyi sa'ah da nazo dakaina nace ina sonki, surarki tamin Gaba daya idan ina tunanin ki kasa bacci nake, ki amince Dani kiga harka yanmata"

, bakinsa na kalla yanda kasan nayi amai, Gaba dayansa mashayi ne ga dukkan alamu, kakarin amai na fara, cike da hanzari yace "baby menene"
nace" Malam zakasani amai, Dan Allah ka matsa daga kusa Dani kar mutane su ganmu tare ace nima na fara shaye shaye kamar ka,"

"kut"
Jin yafara zagi yasa nayi Gaba abina, yasake shan gabana, ya daga hannu zai mareni nace" karka fara, "

"ke har kin isa kifadamin magana nine ma mashayin?"

Nace "to waye zaiyi abinda kayi inba mashayi ba, kuma da kake cewa baka taba San mace taqi kaba, to kazo inda za'a qika, idan ko wacce budurwa tana sanka Toni bana sanka, kayimin kazanta, inyi soyaiya dakai,"
Mari yasake kaimin akaro na biyu, na bige hannun sa nayi Gaba, ihu wasu daga cikin dalibai sukasa, ashe wai har taruwa akai Ana kallanmu.

" kekuwa baiwar Allah meya kaiki yin rikici da namiji, namijin ma irin wannan? Bayan daga ganinsa kinsan baida mutunci, ko bakya tsoro amatsayinki na mace?"

Kallanta nayi daga sama har qasa, daga ganin kayan jikinta kasan nera ta zauna, kyakykyawa ce ajin farko, daga ganinta kasan ta hada jinsi da larabawa, abinda zan nuna Mata wajan kyau kadan ne.
Ganin yanda nake kallan ta yasa tacemin" karki damu, tun ranar dana fara ganinki naji

nutsuwarki ta birgeni, bakida kule kule irin na qawayen banza, kuma koba niba duk wani wanda yake faculty din nan zai yabeki Akan tarbiyar ki, idan bazaki damu ba, zanso mu qulla qawance, "

tafada tana murmushi,tareda miqomin hannu  sunana" SAUDAT MUHD MARZUQ"

hannun nima nabata nace "NAFEESA MU'AZ (FEENAH)"

"nice name" tace, mukayi murmushi atare.

Daga wannan lokacin muka qulla qawance nida saudat, tanada kirki sosai, haka kuma tanada sauqin kai, kokadan bata bani hanya nagane cewa itadin yar wani ceba, saboda bata daukar kanta a komai, nunawa take itama mutum ce kamar kowa, duk inda ka ganni zakaga sauda, munzama kamar wasu taurari, duk inda mukai sai mun haska.

** *** **

Agajiye na dawo gida Yau, kaka rabi a kace" sannu, "

nace" yawwa tsohuwa,"

" ga abinci," nace" haba kaka, saikace azamaninku, aikya bari inyi wanka ko, "

tabe baki tayi, tace" 'ya'yan zamani iyayinku bai isheku ba, "

nace  "eh munji,"
bayan nagama komai nahuta nazauna na fara assignment din da aka bamu tun ranar Monday kuma jibi alhamis ne yakesan karba,bayan nagama ne nahau chting bansan ma bacci ya daukeni ba, sai Jin muryar kaka nayi tana cewa "nafi, ke nafi ki tashi kiyi sallah yanzu haka nasan qila kina nan kina watsar, (whatsapp) koba watsar ba, nasan in kika maqa daki aka jiki shiru to shi kikeyi," 🤣

nide ko kulata banyi ba, hammam (toilet) na wuce nayi wanka Dan naji karfin jikina sannan nadauro alwala domin gabatar da sallar magrib.
Washe gari, bayan na shiga school ina tare da saudat, "qawata wlh na gaji da school din nan, harma Garin, Gaba daya nayi kewar su mama, da sis husna,"
sauda tace "haka ne, dole zakiyi missing dinsu Amma yazakiyi hakuri zakiyi, gashi keba wani yawo kikeba bare kiji Dan sauqi, Dan Allah Yau kizo muje yawo da motata Babu me kulamu, kinga ni yaya bazai yimin fadaba idan yaji da qawata zan fita yasan bazanyi shirme ba, zai barni, kema kuma kina yiwa kaka bayani shikkenan, "

nace" sauda bazaki ganeba, wlh bansan yawo kokadan Amma ki bari wani lkc zaki ganni har

gida nace miki nazo ne mu fita yawo,"

dariya tayi tace" tab bade wannan feenan ba,"

nace" shikkenan sister zanyi miki "mufaja'ah"(surprise) tace "shknn nide kisani su momy da twins har damuna suke Akan yaushe zan kaiki,"

nace "karki damu zanzo"

tace" to Allah yasa "

" amin "
Bayan wasu mintina tace" nifa banyi assignment din lacturer nan ba, "

" meyasa?"

Tace" wallahi yaya ne yasani aiki kuma kinsan shidin ba wasa wlh bazaiga girmana ba, tsaf zansha na jaki,"🤣

murmushi nayi nace" aikin kenan kede koda yaushe complain din ki, yaya yaya, bansan yaushe zaki sauyaba, ki fada masa idan yasake sakaki aiki toya tabbatar ya karbi "bahas" (assignment) dinki yayi miki, inba hakaba kozan baki nawa saikin koyamin larabci sannan nima zan baki,"

😳ido ta zaro cike da mamaki tace
" yayan zan fadawa haka? "

Nace" to miye? "

Tace" na gwammace inyi ta koya miki larabcin bakisan yaya bane"

Mrs Usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to Mrs Abdallah

6

Husna tayi gaba, nagama kwalliya nakalli kaina amadubi, gskyr Zeey ne datace idan nayi wata shigar ta larabawa bazaka taba cewa ni din jinin hausawa ceba, kamar yanda kuka gani a bangon littafi na.
Kalatinmu ce ta tahaihu zamuje wajan taron suna, (muna kiranta da kala ne kasan cewarta qanwa awajan mama kuma duk nice silar fada musu wannan sunayen) kowa yagama abinda yake ni kadai suke jira, dana futo kowa ya miqe "masha Allah" mama tace aranta , Abba yayi waje da Ammu mukuma muka rufe gidan, munje kano mun sauka gidan kaka Rabi dake hotoro, mama de bata tsayaba tawuce gidan suna, nida husna da aysha cousin dinmu muna zaune agidan kaka muna mata shaqiyanci, "a'i tashi ku tafi gidan sunan kinji kun zauna sai zancen makaranta kuke, ke usena naga Babu ruwanki jasu ku tafi Nafi tashi,"

"gsky kaka ki dena cemin nafi, haba saikace azamaninku,"
daquwa tamin, "ke nafi nafiki rashin mutunci wlh nafi zance, su nade guda daya a dinga yanyankashi saikace albasa haba"

, kyaleta mukai tana ta sababinta mukuwa dariyar mu muke.
Sai yamma muka tafi gidan kala yaro yaci sunan sultan, agidan muka kwana mama kuma gidan kaka rabi, sai washe gari muka dawo gida muna yiwa aysha murnar samun qani, Amma da ita kadai qwal.

** *** **

Bayan sati daya muna zaune afalo dukanmu muna kallan shirin gari ya waye atashar Arewa 24, Ammu ne yashigo bayan mun gaida shine yake tambayata exam dinmu yafuto na duba ne?
Nace "ai ban San ta futoba ba,"
"yacemin aikuwa wani abokina yacemin takai kusan sati da futowa, number ta yakarba yace bari yaje yadubomin, husna tace" Ammu zanje"

"me zakiyi"

" Dan Allah Ammu ai harda feenah ma,"

toshkn kawai yace muka shirya muka tafi.
Result dina yayi kyau sosai, nan muka dau hanyar gida, Ammu kuma yayi wani wajan, muna tafiya a hanya muka ga mai balangu husna tace" wlh yabani sha'awa"

nace" nima haka," anan de aka yanke shawarar siya Dan akwai wata guntuwar dari ukunmu, bayan mun siya husna tace" gsky wannan naman kamata yayi sai mun Gama abinda muke munyi wanka idan zamu kwanta saimu ci, "

nace" hakane kam" ina tura tsokar naman daya abakina, muka dawo gida bamu bi takan

mamaba kasancewar tana Dakin Abba, muka wuce dakinmu da nama husna ce mai cewa inboye mana, nikuma banyi wata wata ba na tura nama qasan gado, muka dawo falo muna Dan fira kafin mama ta futo, husna ta shiga wanka Abba yafuto da buta ahannun sa, anan na bashi results din nawa, "masha Allah uwata sakamako yayi kyau, insha Allah dazaran anfara bada admission kema sai anema miki" , nace "to Abba"
Bayan nima nayi wanka muna falo nida mama kaina yana kan cinyarta" feenah! Feenah!! Feenah!!! Husna ce take qwala min kira, kafin na amsa tacemin ina yake?" Nace "Mata me?"

Tacemin" abinda muka siya nabaki ki ajiye", tuni nagano ta, mama tace" menene? "Mukai shiru, nace" ki duba yana kasan gado, ta duba can tasake cemin "na duba baya nan,"

nace" a a sake dubawa de, "🤣

Tasake cemin" na duba banga komai ba, Amma de nagano wata takarda acan karshen gado", ai inajin haka bansan yaushe na sauka daga cinyar mama ba, nayi daki, nakarbi fitilar hannun husna kasancewar Babu wuta, haskawar da zanyi saina gano takardar balangu akarshen gado,🤣🤣" ita ce, wallahi itace anty husna," daqyar dai mukasa Abu muka janyo takardar balangu, anan mukaga takarda ayaiyage nama sai tsoka uku, 😱atare muka hada baki wajan fadin kaiiii, "bera ya cinye" mukaji maganar mama a kanmu, tai juyawarta falo tana ta dariya, aida ku nan din nama ne aka siyo za'a yi qurmusu, wlh wannan bera ya kyau tamin tafada tanaci Gaba da dariya, meqomin sauran in bashi ya cinye inji mama, na kalli anty husna data rike sauran takardar nama ahannun ta, nice nayi karfin halin cewa garama ni naci tsoka daya, husna sai Ikcin aka samu bakin magana a kace" shege wlh bamu yafeba, "munaji muna gani haka muka hakura

** *** **

" Momy wai yanzu yarinyar nan dady yadage saitaci Gaba da karatu, me saudat ta nema tarasa Momy," hmm numfashi hajiya hafsat taja, tace" kaima kasan de halin alhaji idan yafada din nan bazai fasaba, Amma kai kayi masa magana may be yajika, "toshkn Momy,"

da daddare bayan sun Gama dinner ahmad yasamu dadynsa da zancen karatun saudat, dady yace "wato ahmad saudat bata rasa komai ba, Amma inaso in inganta Mata rayuwarta banaso ta dogara Dani, sannan koda ace batayi aiki ba, bamusan me gobe Zata haifar ba, Yau mune gobe bamu bane, to gara de tayi karatun ko yaya ne, kuma wannan karatun bawani dadewa zatayi ba diploma ce zatayi, kuma nasan saudat Zata riqe mutunci ta, "

"hakane dady to Allah yasa hakanne yafi zama alkhairi" amin my son.

** *** **

Muna zaune afalo nida husna muna kallan film din india atashar bollywood, "nace sister kinsan me, wlh soyaiyar yan India tana birgeni,"

tabe baki husna tayi tace" nikuwa banga abin birgewa ba, kiss hug shknn aikinsu", nace" hmm anty bakisan soyaiya ba, shiyasa nifa nake San Korean film Babu tashin hankali sosai aciki sai zallar "hub" (so)"

" malama kawai kice aure kikeso shiyasa kike fakewa kina cewa wai soyaiya kede kawai kice kina kallan "qubla"( kiss) koba haka kika ce sunan kiss da larabci ba,"

murmushi nayi nace" su anty husna anji larabci"

fari tayi da ido tace "to ya ranki, nafi San soyaiyar bahaushe mutum ya rike mutuncinsa sai yayi aure" , nace "sis hakan yanada kyau Amma fa suma wannan din bawani Abu ne yake faruwa ba bayan wannan din" , tace "wasunsu ba,"

nace" to Allah yaqara kare mu"

tace "amin."

Mrs Usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

9

Murmushi nayi nace" aikuwa kya koyamin din,saboda rashin kirki irin naki kinajin larabci kakanki balarabe Amma bakyasan yimin larabci nikuma inaso saboda ina girmama abinda nake karanta, "
tace" toshkn aikuwa zan dinga yi miki,  yanzu de sister Tuba nake bani inyi, "
bayan tagama mukaje mukai submitting, mun Gama abinda zamuyi zamu fita tadau waya ta kira driver yace hajiya ta aikeshi Amma yayansu yace zaizo yadauketa, OK kawai tace, tayi dialing number ahmad, saide kuma baturiyar nan tafada Mata cewa batada kati," bani aron wayarki sister zan kira yaya, tawa kudin sun qare,"

bayan nabata takirashi, Amma no answer, tunawa tayi da baya daga sabuwar number, saita tura masa da text cewar saudat ce yakirata, sai bayan kusan minti biyar sannan yakira, alokacin wayar na hannu na, bansan number sa bace  zuciya daya nadaga tare da fadin " hello,"
sake kara wayar yayi akunnansa saboda Jin wata irin zazzaqar murya ta daki dodon kunnansa, " hello, hello! Wai waye ne?"
Saudat ce takarbi wayar tace "kode yayane?" Tana dubawa kuwa taga shine, dasauri tace "hello yaya,"

dasauri yadauke wayar daga kunnansa Jin muryar saudat na shirin fasa masa dodon kunne,😃
 "saudat gani nan Zuwa 2 minutes"

"OK yaya," takashe wayar, araina nace wannan yayan nata Dan renin wayo ne wato shine ina masa magana ya shareni sai ihu nake da waya akunne hmm. 🤣

Munzo gate nace "sis zan hau adede ta, sai mun sake haduwa,"
"haba sister Dan Allah ki tsaya ku gaisa da yayana, Baku taba haduwa bafa,"
nace "karki damu "Marra jay" (next time) zamu gaisa insha Allah,"

 tace" ke bazai iyuba sai kin tsaya,"🤣
nikuma nace" bafa zan tsaya ba, ki bari da week end sai nazo gidan, "
tace" a a, muna wannan musun wata hadaddiyar mota ta tsaya agabanmu kirar Mercedes-cls63, saudat tayi sauri ta Bude gaban motor, "

yaya tare nake da qawata ko zamu sauketa kafin mu qarasa gida,"

"ok" kawai yace tajuyo tace "sister muje,"

tashiga Gaba nikuma na Bude gidan baya nashiga, ina shiga naji wani sanyi ya dakeni na "mukayyab" (ac) hadeda wani daddadan qamshi, bansan lokacin dana lumshe idona ba, haduwar gashin idona waje daya, sai hakan yaqara yimin kyau, daidai wannan lokacin shima ya kalloni
ta glass din gaban motor,yanaso yaga wacece wannan dabazata iya gaidashi ba, hankali na yanakan wayata idona aqasa, nadago da niyyar ince masa ina wuni, karaf idanunmu suka hadu, yana sanye da farin yadi, farar hula da agogo qirar Gucci yayi kyau sosai, subhanallah yace aransa, anya wannan kuwa mutum ce? Ya tambayi kansa,
Qarar da waya ta ta dauka shiya dawo dashi daga tunanin daya afka, wata yar "kulliyarmu" ce (faculty) daukar wayar nayi tare da cikakkiyar sallama, magana takemin tana neman saudat, Zata bata book dinta, sai a kace Mata mun shiga mota tare, kuma takira saudat din wayarta akashe, shine take so nahadasu, kafin nabata amsa wayar ta katse, still wani Kiran yaqara shigowa nadago nace saudat, da zazzaqar murya ta, "ittasil biki fittal fon" (Ana kiranki awaya) Ahmad najin haka aransa yace no wonder ashe balarabiya ce shiyasa bata gaishe niba, ashe batajin hausa, 😃
kafin yagama tunan sa yaji nace masa " ina wuni," kallo na yayi ta madubi, yakasa dauke

idonsa akaina, nice na fara janye nawa idon, qiiiii kakeji yaja wani wawan birki, saudat dasauri tace "subhanallah yaya me kake tunani saura kadan kabige me wancan motor,"
saida yaseta kansa sannan muka ci Gaba da tafiya, har layin unguwarmu suka kawoni, na leqo ta window nacewa saudat "nagode sister, yayan sister nagode,"

lalle ma wato yayan sister, baikai matsayin dazata kira sunan saba 🙄

Bayan sunje gida suka zube afalo cikin gajiya, saudat Zata fara surutun nata taga hankalinsa yanakan aminiyar tasa wato waya, saita yunqura Zata tafi daki taji yace" sauda", juyowa tayi tare da fadin "na'am yaya,"

"wacece wannan?" Kasan cewar hankalinsa nakan waya yasa tayi tunanin wata yake nuna Mata, ta leqo fuskar wayar tana so taga wayake nufi, Amma bataga komai ba
"qawarki nake nufi "
"yaya feenah cefa qawata danake Baku labarin ta kullum, wannan yar zariyan," alama yayi Mata da hannu alamun tatafi kawai, tabe bakinsa yayi bayan wucewarta shide baisan wata feenah ba, tunda ba sabgar labarin qawayanta yake shigaba, tashi yayi daga falon yayi banqarensa.

** *** **

" Kaka ingaya miki saura kadan Yau muyi hatsari,"

dafe qirjin ta tayi tana fadin "subhanallahi ni badawiyya, Garin yaya? shiyasa banasan kina hawa adedetan yara masu ji da karfin balaga,🤣 yanzu saisu nemi halakaka,"

🤦🏻‍♀️dafe kaina nayi da hannu na, "haba kaka tun bakiji komai ba harkin fara sharhi, nifa a mota nazo,"
"waye yakawo ki a mota,"

"yayan saudat nefa wannan qawar tawa,"

"oh naji naji, to Garin yaya zaku fadi a mota," nace "wlh tsautsayi kaka,"
rike haba tayi tace" to Allah ya kiyaye Gaba, nan Gaba karki sake shiga motarsa bazai halakaki yabarmu da koke koke ba, "🤣

nace" kaka baki ganshi ba me kyau wallahi," daquwa tayimin da hannu nide nayi daki ina dariya.

Mrs Usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to yar'uwa rabin jiki, mabaruka

10

Fadawa kan gado yayi tare da lumshe idonsa, itan dai yake gani, alokacin data rufe idanuwanta, bacci yake so yayi Amma yakasa banda juyi Babu abinda yake yi, wayarsa ya janyo da niyyar Kiran tahir yafada masa halinda yake ciki, tsawon sati biyu, sai kuma yafasa, yaga shima macen ce take wahalar dashi

Yayi ajiyar zuciya dole de yakawo qarshan wannan matsalar bazai iyaba, ina da sake, shida Bama kula matan yake ba, tayaya wata tunanin ta zaiyi ta wahalar dashi, shida ake sansa, ya mutsa sumar kansa yayi sai sheqi take (ahmad abinda kayi...)
Dayaga dai tunanin Babu inda zai kaishi saiya tashi yayi shirin masallaci.

** ***

"Kaka na gaji, na gaji da wannan karatun wallahi, so nake naganni kusa da iyayena,"

"a a to yar nan waya riqeki"🤣

"haba kaka ni kenan koda yaushe saboda karatu ace baza kaga yan'uwan kaba,"
nafadi haka tare da turo bakina, "to ai sai kiyi tayi nafi" cewar kaka, "ni kaka ki dena cemin nafi"

"aikuwa nafisa nasani haka zan fada, nafisa uwar ma'azu "🤣

dafe kaina nayi da hannu na" haba kaka kuma abin harda 'bankaro sunan mahaifi,"🤣

"to ai nafada miki saboda kisan itace sa'ar yina,😃"

"hmm kaka kenan, kinga ni Yau banajin rikici kiyi tayi, ni kinga tafiya ta,"

nayi cikin daki na kwanta,

Zeey nakira itada Atu, mukasha fira, inda take cemin itama tana legal ta jigawa, Atu kuma bikinta za'a yi, anan de mukasha fira
"Nafi! Nafi!!"
Kaka ce take kwalamin kira, nace "na'am kaka ya akayi" , tace "namanta ban fada miki ba, dazu aisha tazo bakya nan, tace inkin dawo ki kirata, ita ta nemeki bata sameki ba, in kuma bakida kati ki nemeta a watsar (whatsApp)" jijjiga kai nayi wannan matar bazata sauyaba

Kwanci tashi Babu wuya awajan Allah gashi har muna shirin Gama semester farko, karatu nake Babu kama hannun yaro, musamman damuka samu interval nayin karatu, saiya kasance bana Zuwa ko'ina koda yaushe ina karatu na

Mun futo daga "imtihan" (exam) ta karshe, sauda ta dubeni tace "yanzu sisi har semester ta qare bakije gidanmu ba,"
nace "sister kemafa baki je gidan kakaba,"
tace "haba feenah karki manta bakuda yawa dagake sai kaka, nikumafa qanne na koda yaushe suna tambayata yaushe anty feenah zatazo, bini bini suna tambayarki aike kuwa kodan wannan yaran kyaje,"
nace "shknn yanzu de insha Allah nayi miki alqawarin idan Allah ya aramin lokaci idan na dawo daga hutu zanzo," tace "shikkenan idan kinje ki gaida su mama, nace" zasu ji, "
haka muka rabu cike da kaunar Juna, ita tahau saman gada, tana jiran driver nikuma nahau adedeta nayi gidan kaka

** *** **

Kaka Yau sai gida insha Allah,"

"to nafi yanzu tafiya zakiyi ki barni,"
haba kaka ta ai kamar yaune na dawo, "
tace" shikkenan, Amma ai kyaje gidan uwar taku kiyi Mata sallama ko," nace" to kaka bari intafi,"

bayan nagama shiryawa tsaf nahada kayana, sannan nayi gidansu aysha, munsha fira sosai, anan take fadamin tasamu admission na scholarship babanta ya nema Mata, kuma tayi sa'ah tasamu, yanzu haka next month Zata tafi Uganda, Amma kafin tatafi zataje zaria nace Mata ai dole, bayan mun rabu nazo gidan kaka nadau kayana, nahau adedeta yakaini tasha, Allah sarki kaka harda yar qwallarta. 🤣

** *** **

Zaune yake a part dinsa, yana falo, yazubawa katuwar plaxmar falon nasa ido, saika rantse kallan yake, Amma Gaba daya hankalinsa da tunanin sa baya tare dashi, yana tare da ita.
Ya lumshe idonsa ya Bude itande yake gani "oh ya rabbi, wannan wacce irin masifa ce" yafada abaiyane, Ace kullum yarinya ta hanani aikata komai, banda aikin tunanin ta bana tsinana komai,shiru yayi kamar wani zautacce ya zubawa p.o.p din Dakin ido

Momy tayi tambayar harta gaji, saide ya zauna a Dakin shi kadai yana faman tunanin ta, wai yanzu shida baya shiga sabgar yanmata shine soyaiya take wahalar wa haka
"ya rabbi, ukrijni fi hazihil mishkila ya Allah (ya Allah kafitar Dani daga wannan matsala) ya fada abaiyane
Wayarsa ya janyo yashiga inbox dinsa, text din da saudat ta turo masa da number ta yake nema, kasancewar akwai massages din yanmata dasuke turo masa dayawa, dakyar de yagano number, tuni yayi saving dinta,
Sake kallan Number yayi, yana murmushi dialing Number yayi, saikuma ya katse,
To ai dole ya katse, idan ya kirata meze fada Mata,? nine Ahmad sanki nake?
Gani nayi ya shafa fuskar wayarsa yana murmushi ina leqawa sainaga ansa FEENAH TAH

Wani tunanin yayi kawai sai naga yasaki murmushi, "yes haka za'ayi"
Yafada abaiyane

Mrs usman ce🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

11

Sati na daya agida, muna dakinmu nida husna, datake karatu, dayake tana shirin shiga final year ne yanzu, waya nake nida auwal, yana qara jaddada min yanda yake sona, nide ina jinsa, araina nace dama ace yanda auwal yake sona yakasance kamanninsa kamar yayan saudat ne,🤣 danaji dadi, da Babu abinda zaisa naqi shi, saide kuma shi yayansu saudat din ne, naga alamun zaiyi dagun kai, maganar auwal ce tadawo Dani daga tunanin dana fada,
"Nafeesa kina jina kuwa?"

"Eh inaji, am Dan Allah kagane, wlh nadan gaji ne, inaso in Dan huta, mayi waya "ba'aden" (latter) "

" OK to to my heart, rabin raina, gaskiya kam gara ki huta din, nima ai zanso ki huta dakyau,"

nace" ok bye,"

banjira amsarsa ba nakashe wayar.
Husna kallo na tayi gamida girgiza kai, dariya namata, nace" wallahi girgiza kanki dakyau, bana sansa yanzu har Sai kinyi aure sannan nima zai samu kaina, har in aure shi, Amma yanzu kam, ban shirya ba,"

sake girgiza kai tayi batare datace komai ba

Chatting nahau, ina fira da fan's dina, ta whatsApp, naga new number tayimin magana, sallama akamin, araina nace yanzu haka irin samarin nan ne masu Jan magana, zanyi maganin ku, nafada araina, larabci zanyiwa koma waye, bayan na amsa sallama nace "man?" (waye?)

Murmushi yayi, yarinyar nan yaga alama tanasan larabci
"ma'aki Ahmad "(kina tare da Ahmad)
Gaba nane yafadi, Ahmad, Ahmad kuma, dp natafi na duba Babu pic din mutum sai na flawer, sunansa na duba still naga ansa, hammad, nace to waye kuwa wannan tambayarsa nasake yi"

" Aiyi ahmad "? (wanne ahmad)

"AHMAD MUHD MARZUQ"

😳zaro idanuna nayi, ahmad yayan saudat fa, tome zemin me yake faruwa ne?
Tuni nakoma hausa, nace "au ashe kaine, yakake, yagida?"

Yanake, wato bazata iya cemin ina wuni Bama, to Amma ya zanyi tunda ni nake nema 🤣

" lafiya "

shine kawai abinda yace
Nakalli text din dana tura masa, Amma amsata kawai itace lafiya 🤣

Nace "masa yasu saudat da momy"

" kowa lafiya "

Nace "Ok"

Daga nan kuma kowa shiru, shi yarasa me zai ce Mata, ita kuma tana jiran taji dalilin maganar, Ya Salam yafada aransa, yarinyar nan datasan halin dayake ciki da itace zatake yin maganar nan, yanzu haka yana kwance agadonsa Amma fillo ya janyo yarike yana kare fuskar sa dashi,

kai kace itace agabansa🤣
Feenah dataga shirun yayi yawa, karshe de tace,

"
Allah yasa de lafiya?

"lafiya "

shima yabata amsa
Araina nace kaji mutum, kana yimin magana kamar namaka dole, nida bansa ka kamin magana ba

Can har Zata sauka taji ya turo Mata text

"ya labari?"

Nace masa "yana wajanku"

" mu kuma suwa "

Nace masa "ina nufin ku samari
Kokuma kai bakada labarin yacemin

" inada "

Nace" ok, "
feenah shiru shiru tanajiran taji labari, harde ta hakura Zata sauka tace masa" saida safe
Ka gaida su saudat,"

yace" tun yanzu? "nace masa" eh aina Gama abinda nake. "

yacemin " to ai nikuma banajin bacci yanzu"
Nace masa "to Allah yakawo ma"

Shi kansa saida yafada yakejin wani iri, to bayajin bacci yazata masa, kawai de saiya share,

Kujimin mutum toda tare nake kwana dakai dazaka cemin wani kai bakajin bacci yanzu hmm

"yanzu sauka zakiyi"?

Nace "meze hana koda wani Abu? "

Yace "a a"

Yasake cewa "kona hadaki da qawarki naga ni kamar bakisan magana Dani"

Nace masa "a a kyaleta dazu munyi waya ai, kabarta ta huta"

Yacemin "wanne hutu ai ba abinda take"

Nace masa "a a kyaleta de, ko gyaran Dakin da ake sasu ai yaci ace mutum ya huta, kullum mutum yana cikin gyara"

Murmushi yayi, wato saudat tabata labari kenan, yace "bawani gajiya"

Nace "yakamata de ka dinga barinta tana hutawa kodan tasamu sukunin yin assignment"

"haka kike so? "

Nace "eh"

"angama gimbiya "

Juya idanuna nayi kamar yana yana ganina afili na furta gimbiya kuma

Husna ta juyo ta kalleni," Ana luv dinne yar luv," nace "a a," tabe baki tayi taci Gaba da karatu abinta

Nikuma nace masa " to saida safe bye,"

" ki kulamin da kanki,pls "

Araina nace wannan gayen ba kalau yake ba

Nide nace masa" ok"

Wait yace, natura masa da alamar quation mark "?"
Yacemin ni bazaki cemin in kula miki da kaina ba?

Mrs usman ce🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

12

Dafe kaina nayi da hannu na, 🤦🏻‍♀️kai wannan man din akwai damu, "toka kula da kanka,"

"no haka zaki ce inkula miki da kaina "

" saudat tacemin kai Dan gatan mom ne, nasan cewa Zata kula dakai"

"no mom daban ke daban "

Oh" ya rajil "(man) nafada araina

" Toka kulamin da kanka,"

banjira amsar saba nakashe data na, nasauka

Shi kam mutumin ku, murmushi ne saman fuskar sa, ya maimaita chting din nan yafi sau biyar, kissing din chting din yayi, yanayin back, mezai gani?
Text ne rututu akayi ta turo masa, shi bema luraba, shide yasan yanajin qaran shigowar text din Dayawa daga cikin text din na yanmata ne, kowa yana tururuwar yimasa magana, wai Yau shine online, abinda ba wani hawa yake ba
Tabe bakinsa yayi gamida kashe datarsa, yayi addu'ah ya kwanta, ba tare daya duba saqon nin da aka turo masaba

** *** **

Dariya suke sosai, kaida ganinsu kasan sunajin dadin firar tasu"
Wallahi hajiya ingaya miki haka mukai da ita,"

mamy hakima tace" ai wallahi kin kyauta, kinsan hajiya Asma'u akwai ta da wayo "

Falon ya shigo fuskar sa dauke da murmushi, shi kansa Yau yana jinsa asama, tun jiya saide kaga shi kadai yana sakin murmushi, kamar sabon kamu, 🤣kuma duk ta dalilin ta ne, yadubi step mom dinsa," mamy ina abinci na?"

Hada ido sukai itada momy, Yau ahmad ne mai neman abinci?
Momy ce ta bashi amsa, "da mu muke tashi muje mu dauko ma? Bakasan dining dinba ne?"

Murmushi yasaki, dimple dinsa suka lotsa, yana susar kai yayi hanyar dining
Mamy hakima kuwa kasa yin shiru tayi, saida ta tanka

"Dan mamy kode kode? "
Juyowa yayi "mamy kode me?"

" kode surukar tamu ta amince ne mu tura"? Irin wannan walwala haka

Sosa kai yayi, cike da shagwaba kamar wani qaramin yaro yace "kai mamy abinda bata sona ma?"
Zaro ido momy tayi😳," wai da gske ne abinda kunnuwa na, sukeji hajiya?
Wacece?
Gaskiya kakawo mana ita mu ganta"

Mamy hakima tace" Gaskiya kam, yakamata mu ganta, Amma wannan yarinya ko wayece tayi sa'ah "

"wayyo mamy, yayi wuf hanyar dining "

Awannan ranar ahmad yahau chatting kusan sau shida, Amma abin mamaki banda text na group dana yanmata Babu abinda yake, wanda shi kuma baida lokacin su
Harya gaji yana tunanin ma bazata hau ba kawai saiya ganta online alokacin kusan goma na dare
" yes" yafada da karfi kamar wani tababbe, shi kansa yana mamakin kansa, wai shine yake San mace har haka, abinda bai taba faruwa dashi ba, murmushi yasaki, daya hangosu a idon zuciyar sa, gasunan awani waje harda yaransu, kai Gaskiya dole ya seta kansa awajan yarinyar nan, saboda yanajin Santa aransa, a koda yaushe qaruwa Santa yake aransa, kamar yadda yake shaqar numfashi, haka Santa yake qaruwa aransa

Yauma a chting din bai barta ta hutaba, saida ya isheta, kullum hakane yake kasancewa, atsakanin su, har yanajin Yau idan bai ganta ba bayajin zai samu nutsuwa aransa

Da yamma, ya shirya cikin wani yadi light blue, yasaka hula baqa, takalmi baqi gamida baqin agogo kirar Rolex, falo yasauko sai zuba kamshin turaren Ahlamul Arab yake, duk ya Bude Falon da qamshi,

Saudat yasamu afalo sai rabon fada take tsakanin maryam da bukhari da Muslim, Akan game, yana saukowa aka fara kawo masa qara, yace" ku banda lokacin ku, akwai inda zani,"
maryam yaja gefe yayi Mata rada akunne, aikuwa tuni ta saki murmushi ga hawaye shabe

shabe a fuskar, tayi sama da gudu abinta

" Ke tashi ki rakani,"

yafadawa saudat, to yaya, mayafi ta janyo ta yafa, saida suka futo harabar gidan taga de ba shida niyyar fada Mata inda zasuje, tace "yaya ina zamu ne?

Yace" aike zan tambaya,"
tace" kamar ya? "

Yace" to nima ina nasan wajan, gidansu wannan yarinyar zaki rakani, "🙈

Tace." oh wai binta, Allah sarki, jiyama saida tazo nemanka, Allah sarki yaya ashe kun dedeta,😃 wallahi dama nasan mahakurci mawadaci, ta Dade tana sanka baiwar Allah, ashe wannan ranar zatazo 🤣"

Cike da tsawa wadda ita kanta tayi mamaki, yace "ke dallah kiyiwa mutane shiru kinbi kin wani cikawa mutane kunne da wata binta binta"

"Wannan yarinyar qawar kin nan, mene sunanta?"

Saudat tace "oh wai feenah?"

"eh" yabata amsa kamar bayaso,
"To ai yaya dare yayi,"

Yace "dare yayi "kaif ya'ani" (kamar yaya) "

" To yanzu yaya karfe hudu ne da rabi, tayaya zamu dau hanyar zaria? Yaushe mukaje muka dawo? "

Kallanta yayi sosai yace" zaria kamar yaya? "

" Yaya feenah yar zaria ce, nan din agidan kakarsu take, kuma tun da mukai hutu aranar tatafi gida hutu, ai nan kawai karatu take, Amma da munyi hutu can take tafiya, "

"ok" kawai yace,

Ita kuma tayi gida, ta dinga dariya, oh su yaya, da anci kwalliya za'a je zance, ko ya yake yi idan yaje zancen, wannan baqin rai nasa, hmm wallahi sister zan gamu dake, ashe soyaiyarku kukeyi a gefe, bansani ba, ko tayaya suka hadu oho musu!

Mrs usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

13

"Yasalam,"

shine kawai abinda ahmad ya furta, wayarsa ya janyo yakira tahir, number busy
Mtw tsaki yaja, yanzu haka yana can yana waya da wannan yarinyar ya wani liqe Mata kamar gam,
Yana tunanin yankewa kanshi mafita, yaji Kiran tahir din,

"yakai, kana gida ne?"

"Yes ina nan, ya akayi?"

"No gani nan Zuwa kawai,"

"OK" inji tahir

** *** **

"Abokina yade naganka cikin damuwa, waya tabamin kai ne?" Dagowa yayi ya zubawa abokin nasa ido, shi dinma duk yafada, yara me,

"tahir me yake damunka? "
"soyaiya

iklima tanamin yawo da hankali, narasa gane kanta, ga ummi koda yaushe tanamin magana Akan aure, tace min tana so taga yan dagwai dagwai suna yawo agabanta,"

ahmad kwashewa yayi da dariya, "wai yan dagwai dagwai, to kai kayi auren mana, kawai kazabi wata acikin babies din da suke binka, kufa likitoci Ana sanku, yanda yan Mata suke rububinku," yafada cikeda zola ya, tahir yakai masa duka ya kauce

"Kai bance yanmata suna binka ba saini, ni ai zuciyata nariga na yiwa iklima kyautarta,"

"Gaskiya ne" inji ahmad "kaji masoya"

"No bazaka ganeba ahmad dande Babu wadda tayi sa'ah ka budewa zuciyarka ta shiga shiyasa zaka ce haka"

"Hmm tahir kenan, da kasani, Amma ita wannan bata nemi iznina Bama ta Bude zuciyar ta shiga ciki tayi bake bake," 🤣

tahir yace "serious ahmad"

"Serious abokina, wlh ban taba Jin so yamin mugun kamu kamar yanda na yarinyar nan yakamani ba"

Tahir yace," pls abokina wacece Dan Allah"

"Zinariya," inji ahmad,

" kamar ya, haka ne sunanta?"

Ahmad yace "inaaa ina nufin Zinariya acikin Mata, yarinyar tayi, akwai sura me kyau wallahi, saide Amma fa yarinya ce Gaskiya, bansani ba ko Zata iya daukar nauyina, sa'ar saudat ce, kuma qawarta"

Tahir dayayi sakare yana kallan abokin nasa, yace" kuma sa'ar saudat dince yarinya?"

" Emana to nima shekara nawa nabawa saudat din? "
Tahir yace" karka ce haka, ai Mata bahaka suke ba, sai kaga kana renasu wallahi sun baka mamaki a karshe "

" to ai shknn "inji ahmad, sannan yasake cewa

" Allah yabani ke my feenah "

" Gaskiya abokina ka shiga dayawa,"

" wallahi sosai," inji ahmad

" Am kagane tahir, kawai kayi hakuri da halin iklima, wataran komai zai wuce, kuyi magana da ita ta fahimta, idan batayi kawai kasamu wata, idan kuma tana yi dakai, kawai ta ajiye wani Jan aji, tabada kai bori yahau, ko muma masamu yan dagwai dagwai"

Tahir dariya yasaki "wato nabaka sara ko? Hmm qilama kai saika rigani samun su, tunda naga da gske kakesan wannan yarinyar"

Ahmad yace "gsky kam, aini kasan ba jira, tana Zuwa Zata samu"

Zaro ido 😳tahir yayi, "Zata samu me?"

** *** **

Washe gari sunacin abinci, kowa yayi shiru kawai abincin su, sukeci, ahmad yadubi saudat yace Mata," yaushe zaku koma school,?"
Kafin ta bashi amsa, Muslim yace,
"yaya tun rannan kake tambayar ta kode kaima school dinsu zaka shiga?"

Maryam ce tace, "yauwa yaya na tuno, infada?"

Shi ahmad shaf Yama manta yayi wani magana da yarinyar,kai tsaye yace" auta fadi mana,"

tace" yaya kace zaka kaini wajan anty tun waccan ranar Amma har yanzu baka kaini ba,"

bukhari yace" haba?" Wai haka yaya? Wallahi muma sai munje ko Muslim,"

"eh wlh" inji Muslim daya cika bakinsa da chips 🤣

Cikin tsawa yace musu" wai ba anhanaku yin surutu idan Kuna cin abinci ba? "🤣

Tsit kakeji kowa yadawo taitayinsa

Saudat ce a hankali tace" saura kwana biyar, wai ita nan babba, 🤣

itama da harara yabita
Su kuwa su momy mamaki suke, kayi tambaya anbaka amsa, Amma kana ta harara,🤣 shide daddy yanajinsu yana murmushi bai sa musu bakiba

Shima gogan naku, shiru yayi, saide yayi alkawarin yadena sirri da Maryam,🤒 haka yatashi yadau tissue yana goge bakinsa, ya fita yanata faman harare harare😊

** *** **

Akwana atashi gashi har mun dawo hutu, munci Gaba da karatu cikin nasara, aranar da muka

fara "muhadara" (lecture)  saudat tayimin tas
"Yanzu dama sister soyaiya kuke keda yaya, Amma shine ko naji labari?"

"Soyaiya,? soyaiya fa kika ce sauda
Shine yafada miki muna soyaiya?"

"a a ni bai fadamin Ba alama nagani kawai "

"Nace Mata to nide wlh bamuyi wannan mgnr ba," saudat ta cika da mamaki tace "Amma fa koda yaushe tambayata yake yaushe zamu dawo hutu yaushe zamu dawo?"

Dariya nayi nace "wlh Bama wata soyaiya kawai de muna gaisawa a chting, shima bansan waya bashi number naba"

Saudat tace "harfa cewa yayi inrakashi gidanku"

Zaro ido feenah tayi tace" gidanmu? Wlh da baba aure zaimin shikkenan, 🤣dama ga auwal shima yadameni "

Tace" to koma de menene idan tayi tsami maji, "
nace" hmm sauda kenan, Babu abinda zaki ji sai.... Kafin na qarasa tayi karaf tace "sai soyaiya"

Nace "saudat banda abinki, inani ina yayanki, Dan gayu yafi karfina, sannan ni bamu taba haduwa dashi Bama fa"

Saudat hararata tayi tace," wlh nikuma kinga ban taba ganin wadanda suka dace da junaba kamar ku, kuma kina cewa Baku taba haduwa ba, ranar da muka kaiki gida fa
Ina kallan ku ai, sai wani kallan Juna kuke Kuna basarwa
Har kikasa Dan bawan Allah yakusa zubar damu
Wlh feenah yaya yana sonki, pls idan yazo miki da maganar karkiyi rejecting dinsa, feenah ina sanki a family din MARZUQ
Duk fa yan gida sunsan yaya yafara soyaiya, ke karshe ma har cewa yayi zai kawo miki auta "
Anan tabani labarin baran baramar da Maryam tayi masa,
ni abin ma saiya bani dariya🤣

Ahaka de muka rabu, muna masu farinciki

** *** **

Da daddare bayan nagama komai, ina chting nida husna, tana bani labarin practical dinsu da aka turasu, kuma Ana turo musu manyan doctors suna qara yi musu bayani da wayar musu da

kai Akan wasu ciwukan
Anan nake qara Mata qwarin gwiwa takara dagewa, Allah kuma yabasu sa'ah

Shigowar text din ahmad dana gani ne yasa nasaki murmushi, ni kaina Zuwa yanzu nasan cewa ahmad yatafi da tunani na, inajin sansa araina sosai

Sallama yayimin na'amsa masa, "feenah"

"Na'am yaya"

"Ashe bakiyi bacci ba,"

nace masa "um, banajin bacci,"

"to ko inzo intayaki fira?"

Nace " nabaka dama yaya"

yace "are u serious?"

Nace "eh,"

"to idan nazo me zaki bani?"

Gabana ne yafadi nace me ahmad yake nufi?
Kawai sai nace bari naga gudun ruwansa, sainace masa, "duk abinda kake so,"
saiyace "um um fa, abinda nakeso babba ne" , nace "kamar me kenan?" Gabana yana ci Gaba da faduwa

Yace " idan nafada kinyi alkawarin zaki bani?"

Nace masa "insha Allah"

Yace "I LUV YOU FEENAH
inaso ki mallakamin zuciyarki"

Zaro ido nayi 😳gabana yana faduwa.

(nide nace to feenah, gashi de kinyi alkawari)

Mrs usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

14

Karfe goma sha biyu na dare, yana kwance adakinsa, haka itama daga bangarenta, suna maqale da waya akunnan su.
"Kinga nide ba qaramin yaro bane, yakamata mu tsaida magana daya atsakanin mu, kema kinsan nadade ina kaunar ki, tun lokacin dana fara dora idanuna akanki, koda yaushe banada nutsuwa kullum cikin tunanin ki nake, zuciyata ta nesanta da abinda take so, ki temaka ki kasance agareni tun kafin zuciyata taqara afkawa acikin damuwa,
Aduk lokacin dana zauna adaki ni kadai ina tunani Akan soyaiyar mu,  saina dinga hasashen cewa dama ace inada fiffike tamkar tsuntsu, ta yanda zan iya daukarki inkai ki qayatacciyar fadar datake can babban birnin masoya, domin sada ki da kujerar alfarma, ta muqamin sarauniyar yanmatan duniya, dana Dade da baki,
Wallahi soyaiyar ki, tana neman ta zautani, pls pls maimuna yakamata ki bani dama inturo magaba tana domin ayi maganar auren mu "

Gaba daya yagama kashe Mata jiki da kalamansa, yaushe zatayi sakaci ta rasa Ammu, yanda yake Mata wannan soyaiya, idanun ta a lumshe, tace "nabaka"

"Me kenan maimuna?"

"Nabaka dama ka turo, iyayena sun Dade da sanar Dani cewa idan nasamu mijin daya kwantamin zan iya turoshi domin suyi bincike akansa,"

"Da gaske kike farin cikina?"

"Serious abin alfahrina"

"Gaskiya naji dadi nagode, zanyiwa yaya magana Yau, duk yanda mukai dashi zakiji,"
haka sukaci Gaba da firarsu ta masoya.

Asuba tagari maimunan Ammu.

** *** **

Dif takashe datar ta, Ahmad yana jiran amsa yaji shirun yayi yawa, kawai yana dubawa yaga wayam Babu feenah Babu alamarta, kansa ne yasara, badai yarinyar nan bata sansa ba, innalillahi, yanzu ya zaiyi, dama hakane yanzu shida yake qin wasu shine, shima ake gudunsa, bai Gama tunanin saba yaji dumi akumatunsa, hannunsa yakai wajan

"hawaye?"

Shine abinda ya furta da bakinsa, shi wallahi ko durqusa mata sai yayi, inde Zata so shin, Agogo yakalla yaga 12:45 bai tsaya shawara da zuciyarsa ba, kawai ya kirata, saide kuma harta gama ringing bata amsaba,
Shikkenan hasashe na yazama Gaskiya,

"Nafeesa bata sona,"

yafada abaiyane,
Dama nasan tana kulani ne saboda qawarta saudat
Kwallar idonsa ya share,

"wallahi saina sake kira"🤣
yasake fada abaiyane, shi kadai adaki sai sunbatu yake

Acan bangarenta kuwa duk ta rikice, tayaya wannan Dan gayun zaice yana Santa ta yarda, anya kuwa ahmad ba yaudarar ta yake ba? Amma ace mutum mai aji, da kudi da gayu kamarsa har yana kiranta bayan kuma taga abinda yace, yanzu menene mafita, yaya zatayi dashi?
Wani bangare na zuciyarta yana masa kwadayinsa sbd ahmad yayi Babu qarya, saide wani sashen kuma yana fada Mata yafi karfinta karta jawa kanta abinda yafi karfinta itada iyayenta
Saide maganar da saudat tafada Mata data tuna da ita sai taji bazata iya kyale ahmad dinba
Amma dole zai bata lokaci tayi tunani

Wayar tasa aqasan fillo, tayi addu'ah ta kwanta, saide tana rufe idonta qarar wayarta yasake tashin ta
Hannu tasa ta dauko, tana dubawa kuwa ahmad ne, samun kanta tayi da amsawa tunda tariga ta yankewa kanta mafita,

"feenaaah"

ya kirata gamida Jan sunan nata

"Na'am yaya,"
kayi hakuri naga kiranka bana kusa da wayar ne

"a a feenah, ban yarda ba"

"feenah "
yasake Kiran sunana, na amsa

" feenah bakya sonako? "
Nace "a a"

" to meyasa kika sauka a chatting Babu amsa Babu sallama bayan ba haka kika sabar min ba?"

Nide nayi shiru inajinsa yana magana a hankali cikin nutsuwa badan dare neba nima nasan ba lalle naji komai ba
Nace "yaya bahaka bane kayi hakuri"

"Shikkenan anyi miki afwa, Amma pls yanzu fadamin yaya kike jina a zuciyarki?"

Saida nayi Jim sannan nace "kamar yanda nakejin saudat mana,"

yace "um um, niba wannan nake nufi ba, kema kinsan me nake nufi,
"Feenaaah" yasake Kiran sunana
"Na'am yaya,"

"Feenah kinaso namiki kuka?"
Nace "kuka kuma yaya,?"

"Emana tunda bakya sonaba, nafeesa tunda nake bantajin nakamu dasan wata yarinya lokaci dayaba sai akanki, pls kisoni feenah Dan Allah kinji
Yaqarasa maganar cike da shagwaba ni sai yabani mamaki ma," ganin yanda yake magana cike da shagwaba
Nace "yaya to kabani lokaci zanyi tunani,"
Yace" nide um um yanzu nakeso naji, "

nace" yaya.....

Yayi saurin tarar numfashi na "pls karki ce komai haba feenah ki yarda Dani, kinji, zan kasance mai rike miki amanar soyaiyar mu, "alaikillah quli anti tuhibbuni" (Dan Allah kice kina sona) "

Kinji feenah ta pls, yafada kamar zaiyi kuka, nace masa" Shikkenan yaya na amince, "

" Alhmdlh to fadamin"

"ina sonka"

Lokacin datace tana sansa baisan lokacin daya lumshe idonsa ba, "nima ina sanki matata

Murmushi nayi kawai," yaushe zaki kwanta?"
Nace" yanzu"

, "to da fatan de kinyi addu'ah muradina,"

“nayi mana, "

" Toshiknn nikam banyi ba, ko zakizo kimin, "

rufe idona nayi da hannu na, nace" Toshiknn kasa aranka nice nake yima yaya "

" OK baby toki kulamin da kanki kinji "

" Insha Allah yaya."

" Oya to rufe idonki pls karki kashe, "

" Narufe yaya"

saukar kiss naji Akan kunne na Dif ya kashe wayar
Yabarni da waya a hannu, wayar nabi da kallo tamkar yana gabana karshe na rufe idona cikeda nishadi, sai alokacin na farga da lokaci 1:28, tuni nasake addu'ah na kwanta.

"Oh ni rabi'atu yaran zamani saiku kwanta da wuta qwal akanku bazaku kashe ba, ke nafi nafi, dake nakefa, inajinta nayi shiru, cande nayi juyi nace" kaka menene kuma,"
" sallah zanyi naga wutar taki akunne, ke bakya tsoron kwana da jinnu ne", nace "haba kaka fadi alkhairi kokai shiru, haka a kace,"

"to naji kinga tafiyata, gara inyi sallah indanyi lazimi tun karfe tara inata zuba bacci," nima wutar na kashe na kwanta

** *** **

Bayan sati daya, kwance suke adaki suna firar duniya, ya kalleta yace" maman yara yakamata fa a yiwa auta qani, ko qanwa, "
Murmushi tayi" haba Abban husna, yanzu duk tsawon wannan shekarun ai yakamata ace mun hakura "

" A a maman nafeesa karki sake fadar haka, ai bawa baya yankewa kansa rahmar Allah, nide har gobe inde yara daga wajanki ne to ina maraba dasu, saide inkece bakya maraba Dani "

" Haba Abban husna kaimafa cewa kayi auta, to tayaya za'a yi Mata qani "

" Kinga wannan duk maganr ku ce hausawa nide nariga nafada miki inason yara "

Mrs usman ce🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

15

"To kayi hakuri Abban husna, ai abin bana zafi bane, duk ka daga hankalin ka"

" to ai kedin ce naga alama nema kike ki sande,"
"to alhaji Allah yabamu nagari,"

"yauwa kokefa."

** *** **

After 2 months, a wannan lkcin soyaiyar ahmad tayimin mugun kamu, har banajin zan iya auren wani bayan shi, banga abinda zai nema in hanashi ba inde ban sabawa addini naba, koda yaushe muna liqe awaya, haka a chting dinma ba banza ba, sosai ya koyamin yanda zan soshi, ta yanda bazan iya mai musu ba, haka shima idan muna waya tamkar bawana yake zama.

** *** **

Wayarta ce tayi ringing, tana kallan wayar, wannan ne kira na hudu, dakyar de ta amsa, tana wani yauqi, iklima Kenan 'ya awajan mai bawa gwamnan katsina shawara🤣, kai tsaye tace "doctor ya akayi,"

"Haba iklima sau nawa ina kiranki, baki amsaba, meyasa ke bakya bani time dinane, kamar kin manta da soyaiyar da mukayi, iklima kema kinsan irin soyaiyar danake miki, a school fa har sha'awarmu ake"

" dakata doctor tahir, yanzu menene laifi na saboda ban amsa wayarka ba,? So kake infatse abubuwan dasuke gabana inqare akanka?
Sannan Bama wannan ba, iklimar da daban ta yanzu daban, a yanda nake jina kam, na wuce ajin doctor, saide matar governor, rayuwar school dakake magana, kawai nasoka ne saboda ka taimakamin kuma kagama, Dan haka banda case dakai, dif takashe wayar ta"

Daskarewa doctor tahir yayi awajan, baisan lokacin da wayar ta fadi qasa ba, nan take ta tarwatse.

** *** **

"My feenah yaushe zaki bani dama inzo inga wannan kyakykyawar fuskar taki ne?"

"Karka damu my ahmad nabaka dama koda yaushe zaka iya Zuwa"

"serious?"

"My ahmad kenan da gske nake"

"Toshikkenan zaki ganni very soon,"
sukai sallama

Number tahir yake kira Amma akashe, to me yake damun wannan gayen shida baya rufe waya, cigaba yayi da nemansa ganin yakasa samun sa saiya yanke shawarar Zuwa office din nasa, domin yafada masa yazama ready zai kai shi su gaisa da gimbiyarsa feenah.

Asbitin tahir din yanufa, dayake yanada hospital nasa nakansa, halinda yatarar da abokin nasa aciki yayi bala'in daga masa hankali, tahir yagani kwance shame shame Babu alamar numfashi atare dashi
Acan cikin asbitin kuwa marasa lafiya suna ta jiransa wanda shi zai dubasu da kansa
duk suna tunanin yana wani uzirinne, shiyasa bai futo ba, ahmad Gaba daya ya rude Yama rasa ya zaiyi, fita yayi daga office din, saura kadan suyi Karo shida wata nurse, anan yayi Mata bayani ta kira wani likitan aka kai shi wani Dakin, aka fara bashi temakon gaggawa

Bayan wani lokaci ya farfado, ruwan da aka qara masa ya kallah, yajuya ya kalli ahmad dake zaune agefensa, ya share qwallar idonsa, "ahmad shikkenan iklima ta gujeni bansan Mena mataba ta gujeni, iklima tacemin bazata iya aure naba, shikkenan yanzu burin hajiya bazai cikaba, bazata ga jikokinta ba,
Haba, haba iklima Mena miki meyasa zaki gujeni alokacin da ni nafi buqatar ki a kusa Dani, Mena miki iklima,"
yana magana yana hawaye abin tausayi

Ganin abin nasa zai zama kamar sambatu ahmad yatashi yakira wani doctor yazo yayi masa allurar bacci, yana fita daga Dakin, office din tahir ya nufa, Yau saide ayi abinda za'a yi, Amma saiyaci mutuncin iklima, saita gane kuranta, saide yana Zuwa office din yaga wayar a tarwatse, haka ya hakura Dan kansa yace Allah yasaka Maka abokina, insha Allah, Ubangiji zaiyima zabi da mafi alkhairi wadda tafi iklima

Dakin yakoma ya zauna yana jiran farfadowar tahir
Yakusa awa daya yana zaman jiransa, sannan yafarka, saide ba magana yana kallan silin Dakin, yayi shiru, ahmad ne ya dinga kwantar masa da hankali da dadadan kalamai,
"man bazaka ganeba, ni tun farko nayi tunanin wannan Zata kasance, dole nasan iklima akwai abinda ta taka shiyasa take wulakanta ni, Amma Babu komai Dan kanta, rayuwa ce, ba governor ba, ta auri shugaban qasa ma,🤣 ahmad baisan sanda ya kwashe da dariya ba yace" baba buhari fa kenan"

"yes" inji tahir

"Ahmad kaga idan bazaka bani hakuri ba Dan Allah ka tashi katafi kabarni da abinda nakeji araina," ganin serious yake maganar hakan yasa ahmad ya daina dariyar yace," yanzu menene mafita?"

Tahir yace" damuwa ta dayace ahmad ummi ta matsa insami mace inyi aure, Sanin kanka ne ni kadai suka mallaka, yanzu haka jiyan suka zaunar Dani Akan inyiwa yarinyar danace musu inaso magana, zasu tura ayi maganar auren mu, yanzu ya zanyi? Yaya take so nayi Dan Allah, meyasa tun farko bazata fadamin Ba? "

"Ahmad yaja dogon numfashi yace" karka damu abokina nasan yanda za'a yi, matso kaji, "

Tahir ya matsa, ahmad yayi masa rada akunne, dagowa yayi,
" Kana ganin hakan zai iyu?"

" Mai zai hana, ta so muje wajan ummin ni zanyi Mata bayanin komai. "

Mrs Usman ce 🖊️

🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

16

"Oh ni rabi'atu, yar nan tun dazu kike ta kwalliya kamar zakije wajan zabar  sarauniya,"

"hmm kaka kenan, ai wannan ba kwalliya nakeba, kawai gyaran fuska nake,"

kaka tace "ahakan?" "Emana kaka,"

"To yanzu nafi ina zakije,"
"Kaka baqi fa zanyi,"

"au to to to, to jikanane ne zaizo?"
"Kai kaka yan makarantar mu nefa zasuzo,"
"Bawani nan munafuka, ai zanji zan gani, kinga mayafina ma nadauka zani unguwa, Amma nafasa sai naga qwaqwaf," 🤣

"Ke kaka ashe kin koma sa'ido bansaniba?"

"Tun yaushe, tun yaushe nafi, ainajima a wannan halin
Tunda ki kazo gidan nan baki taba irin wannan caba adoba, tayaya Yau zakiyi, sannan kicemin wai qawanki ne zasuzo nayarda, kema kinsan ba wannan mgnr nafi"

Fari nayi da idona, nace" to kaka zauna wallahi, inkin gaji da kanki zaki tafi, zakice nabaki labari"

"Aiba inda zanima nafi"

** *** **

Ahmad na hango ya rike tahir suna tafiya dakyar, tahir ya dora kansa Akan kafadar ahmad suna tafe dakyar, me gadi yana ganinsu, ya matso "sannu alhaji, sannu, ba shida lafiya ne?"

"Eh"
kawai ahmad yace suka qaraso cikin qayataccen falon gidan, wanda yaji kujeru na alfarma, ummi na hango a zaune ta zubawa TV ido tana kallah hankalinta kwance

Bayan sunje wajan ummi ahmad ne yayi Mata bayani, da yanda yasa meshi a office dinsa, da kuma dokar likita na adena takura masa Akan tunani, (duk wannan shirin ahmad ne) haka ta dinga sababi, wai wata shegiya zatayi Mata sanadin ran danta, daga karshe de tace zatayi masa addu'ah Allah yabashi mace ta gari, ta San da iklima dinma ya aura bazata haifi da mai idoba, shi tahir kawai yana jinta ne Amma baya tunanin zai qara San wata yarinya kamar yanda yaso iklima

Daga karshe tace "to Allah yasawaqe kamashi, ahmad kuje daki,"
tahir kuwa sake langabewa yayi, saida tataso da kanta ta rike hannu a kaje da kinsa aka kwantar dashi
Dakin yayi kyau komai neat, black and white komai, sosai Dakin ya yi kyau
Saida ahmad yaqara Jan kunnansa Akan yarage tunani sannan yatafi

Tafiya yake yana so yaje gida ya shirya, yana so yaje yaga babynsa tunda shide tahir Zuwa bazai iyu dashi ba
Wani super market yashiga yana so ya siya Mata koda ice-cream da chocolate ne
Shigarsa keda wuya kawai daga siyan chocolate saiya wuce wajan perfumes

Wani turare yagani mai kyau na Mata aqallah kudin sa zaiyi 50k yakai hannu zai dauka itama ta dora nata hannun, dasauri ya janye hannun sa, ya kalleta, mace ce aqallah zatayi 28 year's,

murmushi tayi masa tace "sorry fa,"

"no problem" yace
Yabar Mata turaren aikuwa tasa hannu tadau ka, memakon taga yadauki yadauki wani irinsa kawai sai taga yadauki Dan 95k yasa akwando yayi Gaba ko a jikinsa

Murmushi tasaki tabbas nasamu wanda ya dace da rayuwa ta, yana gama abinda yake yaje yabada ATM dinsa suka cire kudin su yayi gaba
Motorsa yashiga ya dau hanyar gida

Har gate man ya Bude masa, tana kallansa harya shige sannan tasake sakin wani murmushin tayi rebus Takoma gida

Wanka yadauka yayi shigar manyan kaya, yadi yasaka fari mai ratsin ash color, sosai yayi kyau bema shiga ta wajan su momy ba kawai wucewa yayi

Yana tafiya amota suna waya, shida ita, saida yazo har kofar gidan sannan yace ta futo, mayafi ta yafa ta fice, kaka ta bita da kallo, tun kafin taqaraso ya zuba Mata shanyaiyun idanunsa, yana cikin mota,
Saida ta qaraso sannan yabude ya futo wani qamshi ya bugeta, ta lumshe idonta, shikuwa yasamu abin kallo yayi shiru yana kallanta, firgigit ta dago kanta aikuwa suka hada ido
Tayi murmushi ta sunkuyar da idonta
"my feenah yakike ya missing dina?"

"Bayan tun dazu inata jiran ka shine ka shanyani,"
"sorry feenah abokinane baida lafiya, aina fada miki da tare dashi zamuzo tahir, Amma kuma hakan bai samu ba,"
nace" ayya to Allah ya bashi lafiya "
Yace" amin
Danma likita ne yasan yanda zai kula da kansa," nace" au doctor ne?"

Yace" babba ma kuwa,"

" Allah yabashi lpy, "

" amin my feenah"

"Muje kimin iso na gaida kakarmu ko"

"ok"

kawai nace
Gaba nashiga, yana Bina abaya, Gaba daya ya shagala da kallan yanda nake tafiya, duk natafi

da imaninsa
Kawar da wannan tunanin yayi sbd agaskiya baida burin daya wuce suyi aure ba tare da komai ya gifta ta tsakanin suba, yaqi jinin zina haka yana Allah wadai da masu aikatata

Kaka Ana zaune akujera yar tsugunno sai ganinsu tayi, kallan mamaki take masa, saida ya tsugunna har qasa ya gaisheta sannan tace" Dan nan ban wayekaba,"
yayi murmushi baice komai ba, kasancewarsa bamai yawan maganaba
Feenah ce tace" kaka yayan saudat nefa, "

Sannan kaka a kace" au to, yanzu naji batu,yasu sauden yaro? "

Oh ya Allah feenah tafada da karfi tare da dafe kanta 🤦🏻‍♀️

" to menene zaki fara iyayin naki, menene laifi dannace saude yaro,".

ahmad yayi murmushi yace" Babu komai kaka,"
" Yauwa kokaifa, yaya sunanka ne?"
" Sunana Ahmad Muhd marzuq kaka, "

" Oh Allah sarki amadu, (kawai sai kaka tafara kuka) amadu anacan karkashin qasa
Yaro ai sunan majina kaci, shima haka yake akwai shi da fara'ah
Allah yaji kanka amadu tafada tana goge hawaye, "
ahmad yace" amin kaka Allah yaji kansa, "

Dago kai tayi ta kalli feenah tace" nafi ko shine wanda kika cemin kwanaki yanada kyau?"🤣 🤣

" Wayyo kaka bashi bane "
Tabe baki kaka tayi," ke kika sani "

Tashi yayi zai fita Yabar wa kaka kudi masu yawa, feenah tabi bayansa suka tafi
Ajikin mota sukai ta firarsu daga karshe yace yagaji dole sai ciki suka koma, Gaba daya yagama kashe Mata jiki da sanyaiyar muryarsa

" Nafeesa tah"

yakira sunan ta, kafin ta amsa yaci Gaba da cewa "nafeesa ina kaunar ki, inaso Allah ya mallakamin ke ki dinga haifa min yara masu matukar kama dake,"

"Nafeesa," yasake Kiran sunana, kafin in amsa yaci Gaba da fadin" a koda yaushe idan na daga kai na kalli sama sai inganta cike take da taurari masu matukar haske, Amma haske mafi mafi haskaka kyawun fuska da yaye duhun zuciyata yana tare dake Nafeesa, ina sonki, ki kulamin da kanki pls"

ya qarasa a hankali tare da riqo hannu na, wani yarrr mukaji lokaci daya, dagani har shi, saboda Abu ne wanda bamu taba tsintar kanmu aciki ba sai Yau, Amma abinda yabani mamaki shine yanda nakasa yimasa musu, haka shima yakasa cikani,
Saida yagama jaddada min kaunar dayake min sannan yasakeni, ajiyar zuciya nasauke, yajuyo ya kalleni," na takura miki ko?" Nace masa" Dame kenan? "
Yace" gashinan narike miki hannun ki", kawai murmushi nayi, yacemin zai tafi, tare da miqomin leda nace a a yabarshi,

Yace "ashe kuwa bazaki fice daga motor ba, karbi mana baby bayan dazu aka Gama fasamin qwan, ashe nima ina da kyau" 🤣

Yafada yana murmushi

"Allah yaya zan ma kuka,"

to naji karbi ki shiga ciki, Dan dole na karba, nace ya gaida su momy da mami

Bina yayi da kallo saida na shiga gida sannan yatafi

Ina shiga gida kaka ta nunamin kudin daya bata dubu a shirin, haka tayi ta shimai albarka, muka duba kayan daya kawo min, nabaje mana mukasha
Saide kuma dazaran natuna yanayin da muka kasance tare dashi dazu, Gaba daya sai jikina yayi sanyi, inji dama kada lokacin ya wuce 🙈

** *** **

"Sofy Yau nayi babban kamu, gaskiya bazan iya hakura dashiba saina dandani zumarsa, yaron akwai kudi da gayu, bakiga yanda yake wasa da nera ba ingaya miki,"

"Kai qawata bani nasha" , anan tabata labarin ahmad," ke yanzu haka nasa amin bincike akansa da komai da komai nasa, sati daya yayi yawa na dandaneshi na wullar,"
dariya Sofy ta saki" Allah qawata,"

" wallahi nake fada miki, "

" Gaskiya ne qawata dole ajinjina miki,"

Tace" waya fada miki LAILA CHILLING WASA CE"

Tofa

Mrs usman ce🖊️[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

15

"To kayi hakuri Abban husna, ai abin bana zafi bane, duk ka daga hankalin ka"

" to ai kedin ce naga alama nema kike ki sande,"
"to alhaji Allah yabamu nagari,"

"yauwa kokefa."

** *** **

After 2 months, a wannan lkcin soyaiyar ahmad tayimin mugun kamu, har banajin zan iya auren wani bayan shi, banga abinda zai nema in hanashi ba inde ban sabawa addini naba, koda yaushe muna liqe awaya, haka a chting dinma ba banza ba, sosai ya koyamin yanda zan soshi, ta yanda bazan iya mai musu ba, haka shima idan muna waya tamkar bawana yake zama.

** *** **

Wayarta ce tayi ringing, tana kallan wayar, wannan ne kira na hudu, dakyar de ta amsa, tana wani yauqi, iklima Kenan 'ya awajan mai bawa gwamnan katsina shawara🤣, kai tsaye tace "doctor ya akayi,"

"Haba iklima sau nawa ina kiranki, baki amsaba, meyasa ke bakya bani time dinane, kamar kin manta da soyaiyar da mukayi, iklima kema kinsan irin soyaiyar danake miki, a school fa har sha'awarmu ake"

" dakata doctor tahir, yanzu menene laifi na saboda ban amsa wayarka ba,? So kake infatse abubuwan dasuke gabana inqare akanka?
Sannan Bama wannan ba, iklimar da daban ta yanzu daban, a yanda nake jina kam, na wuce ajin doctor, saide matar governor, rayuwar school dakake magana, kawai nasoka ne saboda ka taimakamin kuma kagama, Dan haka banda case dakai, dif takashe wayar ta"

Daskarewa doctor tahir yayi awajan, baisan lokacin da wayar ta fadi qasa ba, nan take ta tarwatse.

** *** **

"My feenah yaushe zaki bani dama inzo inga wannan kyakykyawar fuskar taki ne?"

"Karka damu my ahmad nabaka dama koda yaushe zaka iya Zuwa"

"serious?"

"My ahmad kenan da gske nake"

"Toshikkenan zaki ganni very soon,"
sukai sallama

Number tahir yake kira Amma akashe, to me yake damun wannan gayen shida baya rufe waya, cigaba yayi da nemansa ganin yakasa samun sa saiya yanke shawarar Zuwa office din nasa, domin yafada masa yazama ready zai kai shi su gaisa da gimbiyarsa feenah.

Asbitin tahir din yanufa, dayake yanada hospital nasa nakansa, halinda yatarar da abokin nasa aciki yayi bala'in daga masa hankali, tahir yagani kwance shame shame Babu alamar numfashi atare dashi
Acan cikin asbitin kuwa marasa lafiya suna ta jiransa wanda shi zai dubasu da kansa
duk suna tunanin yana wani uzirinne, shiyasa bai futo ba, ahmad Gaba daya ya rude Yama rasa

ya zaiyi, fita yayi daga office din, saura kadan suyi Karo shida wata nurse, anan yayi Mata bayani ta kira wani likitan aka kai shi wani Dakin, aka fara bashi temakon gaggawa

Bayan wani lokaci ya farfado, ruwan da aka qara masa ya kallah, yajuya ya kalli ahmad dake zaune agefensa, ya share qwallar idonsa, "ahmad shikkenan iklima ta gujeni bansan Mena mataba ta gujeni, iklima tacemin bazata iya aure naba, shikkenan yanzu burin hajiya bazai cikaba, bazata ga jikokinta ba,
Haba, haba iklima Mena miki meyasa zaki gujeni alokacin da ni nafi buqatar ki a kusa Dani, Mena miki iklima,"
yana magana yana hawaye abin tausayi

Ganin abin nasa zai zama kamar sambatu ahmad yatashi yakira wani doctor yazo yayi masa allurar bacci, yana fita daga Dakin, office din tahir ya nufa, Yau saide ayi abinda za'a yi, Amma saiyaci mutuncin iklima, saita gane kuranta, saide yana Zuwa office din yaga wayar a tarwatse, haka ya hakura Dan kansa yace Allah yasaka Maka abokina, insha Allah, Ubangiji zaiyima zabi da mafi alkhairi wadda tafi iklima

Dakin yakoma ya zauna yana jiran farfadowar tahir
Yakusa awa daya yana zaman jiransa, sannan yafarka, saide ba magana yana kallan silin Dakin, yayi shiru, ahmad ne ya dinga kwantar masa da hankali da dadadan kalamai,
"man bazaka ganeba, ni tun farko nayi tunanin wannan Zata kasance, dole nasan iklima akwai abinda ta taka shiyasa take wulakanta ni, Amma Babu komai Dan kanta, rayuwa ce, ba governor ba, ta auri shugaban qasa ma,🤣 ahmad baisan sanda ya kwashe da dariya ba yace" baba buhari fa kenan"

"yes" inji tahir

"Ahmad kaga idan bazaka bani hakuri ba Dan Allah ka tashi katafi kabarni da abinda nakeji araina," ganin serious yake maganar hakan yasa ahmad ya daina dariyar yace," yanzu menene mafita?"

Tahir yace" damuwa ta dayace ahmad ummi ta matsa insami mace inyi aure, Sanin kanka ne ni kadai suka mallaka, yanzu haka jiyan suka zaunar Dani Akan inyiwa yarinyar danace musu inaso magana, zasu tura ayi maganar auren mu, yanzu ya zanyi? Yaya take so nayi Dan Allah, meyasa tun farko bazata fadamin Ba? "

"Ahmad yaja dogon numfashi yace" karka damu abokina nasan yanda za'a yi, matso kaji, "
Tahir ya matsa, ahmad yayi masa rada akunne, dagowa yayi,
" Kana ganin hakan zai iyu?"

" Mai zai hana, ta so muje wajan ummin ni zanyi Mata bayanin komai. "

Mrs Usman ce 🖊️

🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

16

"Oh ni rabi'atu, yar nan tun dazu kike ta kwalliya kamar zakije wajan zabar  sarauniya,"

"hmm kaka kenan, ai wannan ba kwalliya nakeba, kawai gyaran fuska nake,"

kaka tace "ahakan?" "Emana kaka,"

"To yanzu nafi ina zakije,"
"Kaka baqi fa zanyi,"

"au to to to, to jikanane ne zaizo?"
"Kai kaka yan makarantar mu nefa zasuzo,"
"Bawani nan munafuka, ai zanji zan gani, kinga mayafina ma nadauka zani unguwa, Amma nafasa sai naga qwaqwaf," 🤣

"Ke kaka ashe kin koma sa'ido bansaniba?"

"Tun yaushe, tun yaushe nafi, ainajima a wannan halin
Tunda ki kazo gidan nan baki taba irin wannan caba adoba, tayaya Yau zakiyi, sannan kicemin wai qawanki ne zasuzo nayarda, kema kinsan ba wannan mgnr nafi"

Fari nayi da idona, nace" to kaka zauna wallahi, inkin gaji da kanki zaki tafi, zakice nabaki labari"

"Aiba inda zanima nafi"

** *** **

Ahmad na hango ya rike tahir suna tafiya dakyar, tahir ya dora kansa Akan kafadar ahmad suna tafe dakyar, me gadi yana ganinsu, ya matso "sannu alhaji, sannu, ba shida lafiya ne?"

"Eh"
kawai ahmad yace suka qaraso cikin qayataccen falon gidan, wanda yaji kujeru na alfarma, ummi na hango a zaune ta zubawa TV ido tana kallah hankalinta kwance

Bayan sunje wajan ummi ahmad ne yayi Mata bayani, da yanda yasa meshi a office dinsa, da kuma dokar likita na adena takura masa Akan tunani, (duk wannan shirin ahmad ne) haka ta dinga sababi, wai wata shegiya zatayi Mata sanadin ran danta, daga karshe de tace zatayi masa addu'ah Allah yabashi mace ta gari, ta San da iklima dinma ya aura bazata haifi da mai idoba, shi tahir kawai yana jinta ne Amma baya tunanin zai qara San wata yarinya kamar yanda yaso iklima

Daga karshe tace "to Allah yasawaqe kamashi, ahmad kuje daki,"
tahir kuwa sake langabewa yayi, saida tataso da kanta ta rike hannu a kaje da kinsa aka kwantar dashi
Dakin yayi kyau komai neat, black and white komai, sosai Dakin ya yi kyau
Saida ahmad yaqara Jan kunnansa Akan yarage tunani sannan yatafi

Tafiya yake yana so yaje gida ya shirya, yana so yaje yaga babynsa tunda shide tahir Zuwa bazai iyu dashi ba
Wani super market yashiga yana so ya siya Mata koda ice-cream da chocolate ne
Shigarsa keda wuya kawai daga siyan chocolate saiya wuce wajan perfumes

Wani turare yagani mai kyau na Mata aqallah kudin sa zaiyi 50k yakai hannu zai dauka itama ta dora nata hannun, dasauri ya janye hannun sa, ya kalleta, mace ce aqallah zatayi 28 year's, murmushi tayi masa tace "sorry fa,"

"no problem" yace
Yabar Mata turaren aikuwa tasa hannu tadau ka, memakon taga yadauki yadauki wani irinsa kawai sai taga yadauki Dan 95k yasa akwando yayi Gaba ko a jikinsa

Murmushi tasaki tabbas nasamu wanda ya dace da rayuwa ta, yana gama abinda yake yaje yabada ATM dinsa suka cire kudin su yayi gaba
Motorsa yashiga ya dau hanyar gida

Har gate man ya Bude masa, tana kallansa harya shige sannan tasake sakin wani murmushin tayi rebus Takoma gida

Wanka yadauka yayi shigar manyan kaya, yadi yasaka fari mai ratsin ash color, sosai yayi kyau bema shiga ta wajan su momy ba kawai wucewa yayi

Yana tafiya amota suna waya, shida ita, saida yazo har kofar gidan sannan yace ta futo, mayafi ta yafa ta fice, kaka ta bita da kallo, tun kafin taqaraso ya zuba Mata shanyaiyun idanunsa, yana cikin mota,
Saida ta qaraso sannan yabude ya futo wani qamshi ya bugeta, ta lumshe idonta, shikuwa yasamu abin kallo yayi shiru yana kallanta, firgigit ta dago kanta aikuwa suka hada ido
Tayi murmushi ta sunkuyar da idonta
"my feenah yakike ya missing dina?"

"Bayan tun dazu inata jiran ka shine ka shanyani,"
"sorry feenah abokinane baida lafiya, aina fada miki da tare dashi zamuzo tahir, Amma kuma hakan bai samu ba,"
nace" ayya to Allah ya bashi lafiya "
Yace" amin
Danma likita ne yasan yanda zai kula da kansa," nace" au doctor ne?"

Yace" babba ma kuwa,"

" Allah yabashi lpy, "

" amin my feenah"

"Muje kimin iso na gaida kakarmu ko"

"ok"

kawai nace
Gaba nashiga, yana Bina abaya, Gaba daya ya shagala da kallan yanda nake tafiya, duk natafi da imaninsa
Kawar da wannan tunanin yayi sbd agaskiya baida burin daya wuce suyi aure ba tare da komai ya gifta ta tsakanin suba, yaqi jinin zina haka yana Allah wadai da masu aikatata

Kaka Ana zaune akujera yar tsugunno sai ganinsu tayi, kallan mamaki take masa, saida ya tsugunna har qasa ya gaisheta sannan tace" Dan nan ban wayekaba,"

yayi murmushi baice komai ba, kasancewarsa bamai yawan maganaba
Feenah ce tace" kaka yayan saudat nefa, "

Sannan kaka a kace" au to, yanzu naji batu,yasu sauden yaro? "

Oh ya Allah feenah tafada da karfi tare da dafe kanta 🤦🏻‍♀️

" to menene zaki fara iyayin naki, menene laifi dannace saude yaro,".

ahmad yayi murmushi yace" Babu komai kaka,"
" Yauwa kokaifa, yaya sunanka ne?"
" Sunana Ahmad Muhd marzuq kaka, "

" Oh Allah sarki amadu, (kawai sai kaka tafara kuka) amadu anacan karkashin qasa
Yaro ai sunan majina kaci, shima haka yake akwai shi da fara'ah
Allah yaji kanka amadu tafada tana goge hawaye, "
ahmad yace" amin kaka Allah yaji kansa, "

Dago kai tayi ta kalli feenah tace" nafi ko shine wanda kika cemin kwanaki yanada kyau?"🤣 🤣

" Wayyo kaka bashi bane "
Tabe baki kaka tayi," ke kika sani "

Tashi yayi zai fita Yabar wa kaka kudi masu yawa, feenah tabi bayansa suka tafi
Ajikin mota sukai ta firarsu daga karshe yace yagaji dole sai ciki suka koma, Gaba daya yagama kashe Mata jiki da sanyaiyar muryarsa

" Nafeesa tah"

yakira sunan ta, kafin ta amsa yaci Gaba da cewa "nafeesa ina kaunar ki, inaso Allah ya mallakamin ke ki dinga haifa min yara masu matukar kama dake,"

"Nafeesa," yasake Kiran sunana, kafin in amsa yaci Gaba da fadin" a koda yaushe idan na daga kai na kalli sama sai inganta cike take da taurari masu matukar haske, Amma haske mafi mafi haskaka kyawun fuska da yaye duhun zuciyata yana tare dake Nafeesa, ina sonki, ki kulamin da kanki pls"
ya qarasa a hankali tare da riqo hannu na, wani yarrr mukaji lokaci daya, dagani har shi, saboda Abu ne wanda bamu taba tsintar kanmu aciki ba sai Yau, Amma abinda yabani mamaki shine yanda nakasa yimasa musu, haka shima yakasa cikani,
Saida yagama jaddada min kaunar dayake min sannan yasakeni, ajiyar zuciya nasauke, yajuyo ya kalleni," na takura miki ko?" Nace masa" Dame kenan? "
Yace" gashinan narike miki hannun ki", kawai murmushi nayi, yacemin zai tafi, tare da miqomin

Ieda nace a a yabarshi,

Yace "ashe kuwa bazaki fice daga motor ba, karbi mana baby bayan dazu aka Gama fasamin qwan, ashe nima ina da kyau" 🤣

Yafada yana murmushi

"Allah yaya zan ma kuka,"

to naji karbi ki shiga ciki, Dan dole na karba, nace ya gaida su momy da mami

Bina yayi da kallo saida na shiga gida sannan yatafi

Ina shiga gida kaka ta nunamin kudin daya bata dubu a shirin, haka tayi ta shimai albarka, muka duba kayan daya kawo min, nabaje mana mukasha
Saide kuma dazaran natuna yanayin da muka kasance tare dashi dazu, Gaba daya sai jikina yayi sanyi, inji dama kada lokacin ya wuce 🙈

** *** **

"Sofy Yau nayi babban kamu, gaskiya bazan iya hakura dashiba saina dandani zumarsa, yaron akwai kudi da gayu, bakiga yanda yake wasa da nera ba ingaya miki,"

"Kai qawata bani nasha" , anan tabata labarin ahmad," ke yanzu haka nasa amin bincike akansa da komai da komai nasa, sati daya yayi yawa na dandaneshi na wullar,"
dariya Sofy ta saki" Allah qawata,"

" wallahi nake fada miki, "

" Gaskiya ne qawata dole ajinjina miki,"

Tace" waya fada miki LAILA CHILLING WASA CE"

Tofa

Mrs usman ce🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

17

Laila bukar kenan, 'yace guda daya tilo awajan iyayenta, mahaifinta mutumin kirki ne haka yanada kudi sosai, wannan ne dalilin yasa Laila take wadaqa da kudi San ranta, mahaifiyar ta hajiya salaha mace ce mai izza Sam taqi jinin talaka,
Ita take daurewa yarta gindi tayi abinda ranta yake so
Acewarta me amfanin kudin ta inde Laila bazataji dadi ba, tana aikata komai Dan Jin dadin yarta, yayinda alhaji bukar baisan wainar da'ake toyawaba,
Saide in sunce suna buqatar kudi kawai zaice su dauka ne
Laila tana kyau dai dai ita, babbar mace ce, meji da aji, da kuma gayu, qawarta daya sofy
Basa komai sai shashanci Yau sune gun wannan alhaji, gobe sune gun wancan
Duk wannan kudi na mahaifinta hakan bai hana Laila zurma zuciyarta Akan masu kudi ba
Itade kawai abata
Idan Laila ta qyalla ido akanka tofa saita samu abinda take so take barinka
Babbar yar iskace ta bugawa a jarida

** *** **

After one week
Zaune muke aqasan bishiya, saudat ta kalli agogon hannunta, tace "wannan bawan Allah fa ya shanyamu dayawa,"

hararar wasa nayi Mata "nifa banasan raini, bazaki yiwa majina ba wallahi,"

zaro ido tayi, "lalle feenah yaushe yaya yakoya miki rashin kunya ina zaune a gefe?"
Nace" bawani rashin kunya ai inda mutunci nima anty yakamata kina cemin "
Baki ta riqe," lalle soyaiya mai raba sis da sis, ni banda yace kar direba yazo dauka na da tuni nayi tafiya ta, inyaso ku qone ma bayan soyewa," budar bakina kuwa nace "wallahi kuwa "

Tace "kaji masoya,
Wannan idan kunyi auren ma Babu mai Zuwa gidanku,"
nace" toda waye zaije yaga abinda yafi karfin idonsa, "

Zata sake magana, waya ta tayi ringing
My ahmad yafuto baro baro Akan 'shaasha' (screen) cike da shagwaba na daga, Itade saudat tazama yar kallo
Nace" gaskiya my man, nayi fishi, tun dazu muna ta jiran ka bayan da tuni ina gida, Amma shine ka shanyamu ko? "

Yace "a kowanne lokaci, kowanne sa'ah kowanne minti kaunar ki sake qaruwa take acikin raina my feenah, soyaiyar ki kamar assignment ne Allah yabani, kinga kuwa bazan denaba, Tuba nake sarauniyar kyawawa,"

nace "anyi Maka, irin wannan kalaman ba dole mutum yayi hakuri ba"

Bansan me yace mataba tace "ok gamu nan Zuwa,"
Najuyo da nufin in cewa saudat tazo mu tafi sai naga tayi sakare tana kallo na, tace "um duniya Gaba dayanku naga alama kunyi nisa,"
nace Mata "yes kuma bazamuji Kiran kiba"

Muna fita daga gate muka ga motarsa a gefe yayi parking, tun daga nesa yazuba Mata shanyaiyun idonsa, tana sanye da atamfa ja mai ratsin baki, da hijabinta har qasa,
Ni kaina kasa dauke idona nayi akansa, ahmad karshene wajan tsafta da gayu da kuma kyau, yana sanye da wando jeans da Riga yellow da kuma jacket kalar jeans din, yana jingine Ajikin motarsa Mercedes brabus, gaisawa mukai dashi duk ya zubamin ido, nide nakasa hada ido dashi, saudat tayi zuruf tashige baya, gamida rufowa, yaqi dauke idonsa akaina, Gaba daya sai naji na takura, ashe saudat idonta yana kanmu ta cikin motar dayake glass din tinte ne ita tana ganinmu, mune de Bama ganinta, "sannu sarkin kunya duk kin wani boyemin beautiful face dinki, tun daga nesa nake ganin wani haske agate din, ashe kece sinadarin dake haskaka wannan hasken"
, dago daradaran idanuna nayi nace "ni din?"

"Ke kuwa, aike kamar hasken wata kike mai hasken dake haskaka zuciyata, haka kuma kalaman ki tamkar suger suke, ma'abocin zaqi, tabbas kinyi kama da...... Dakatar dashi nayi nace" my ahmad saudat fa tana jiranmu "

nafada cike da shagwaba,
Shafa kansa yayi "to ai kece my feenah" shima ya kwaikwayi muryata yafada
Amma kinsan me, maimaita abinda kika fada saina barmu mu shiga mu tafi, wannan sunan da kika fada nakeso ki maimaita,"
nace" nide Dan Allah mu tafi, "yace" saifa kin fadamin, "
da naga da gske yake yanaso yabata mana lokaci saina kalli idonsa nace" my ahmad, shikkenan? "Kafin yabani amsa nasa hannu zan bude gaban motor in shiga, dai dai lokacin shima yasa hannun sa, haduwar hannayenmu waje daya shine ya haifar mana da wani yanayi, tuni narigashi janye hannu na, cikin sauri yabudemin na shiga, kafin ya zagayo yashiga mutafi, saudat tace" wallahi saina Rama kun wani shanyani sai soyaiya kuke, ai ina kallanku, "najuyo na kalleta ina murmushi kafin nabata amsa, yashigo motor, muka dau hanyar hotoro
Babu wanda yake magana acikin mu, kawai wa'azi muke saurara, har mukazo gidan, saudat tayi sauri tabude tashige ciki, nima zan Bude in fita naji kofar a rufe, da niyya yarufe kenan, najuyo na kalleshi, yace "yanzu Babu sallama kawai saiki tafi?" Nide nayi shiru ina wasa da yatsun hannu na,
"FEENAH"

yakirani acan kasan maqoshin sa
Kasa amsawa nayi saboda Gaba daya kwarjininsa ya cikani, "nafeesa bazan gaji da fada miki ina sanki ba, pls nafeesa ki daure kici Gaba da kaunata pls," yana magana kamar wani qaramin yaro,
"Bansan adadin kaunar danake miki ba, Dan Allah kema ki soni ni kadai kinji,
Nafeesa wani lkcin idanuna sukanyi kishi da zuciyata, saboda a koda yaushe kece mafi kusanci da zuciyar tawa, su kuma idanuna kin kasance maiyin nesa dasu,
Feenaaaah, yakirani gamida Jan sunan nawa, har saida hakan yayi tasiri ga jikina, ya haifar min da kasala, banyi auneba naji ya ruko min hannayena duka biyun
Jin haduwar hannayenmu shiya haddasa mana Jin wani yanayi, shi kansa yaji abin har ransa, yanaso koda yaushe yaji hannun ta anashi, saboda yanayin dayake tsintar kansa aciki yana masa dadi
Babu yanda ya iya dole yasaki hannun nata gudun afkuwar "mishkila" (matsala)

** *** **

"Saude kina jinako, ki dinga yiwa nafi fada, sannan ban isa inyi magana ba, yarinya saita fara zinburamin baki, na matsu ku Gama karatun nan, kotayi aure muhuta," saudat tayi dariya, "to kaka ki daina damun kanki zanyi Mata magana,"
"Yauwa Saude nikuwa da gske yayanki yake Santa?"

"Emana kaka sosai yana Santa, ai shine ma zai aure ta insha Allah"

"To ai shikkenan, zanyi magana da babanta, ni gara ayi auren ma nahuta,"

Saudat ganin karfin halin kaka take, kebada 'yaba kece mecewa zaki aurarta ki huta 😃

** *** **

"Yaya zan shiga gida kasan halin kaka, yanzu saita fara sababi danma saudat tana ciki, banaso ta futo saboda kaima yanzu Zata hada dakai,"

"a a my feenah ni fa angon tane bazatamin ba"
Dariya nayi nace" Toshiknn wataran zamu jiku ai inde ka kace "
" To yanzu ki fadamin kalma daya dazan tafi ina tunanin ta "

Nace" I love you my ahmad, "
Shima Bude idonsa yayi dasuka kankace," I luv u too "yace can kasan maqoshin sa
Badan munyi kusanci ba, Babu abinda zaisa nima nakasa jinsa
" gawannan ki shiga dashi "

" na menene?" Na tambayeshi

" Idan kin shiga kya gani," nace" Allah yaya um um kabarshi, "
Hade rai yayi yadawo ahmad yayan saudat

" Bansan musu karbi "

Nakarba nace" toshkn nagode, "
ina turo bakina," feenah"

yakirani, najuyo "pls yimin murmushi Dan Allah"
Dole murmushin namasa sannan ya budemin nafita ina masa bye bye

Mrs usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

18

Gida na shiga na tadda kaka da saudat sai fira ake suna raha, kaka tace" irin wannan dadewa haka nafi, Allah yasa de ayi damu, "🤣

Uffan bance ba danna lura neman magana take

" Bari ma'azu yazo muji ta bakinsa, "🤣

" Wai kaka miye haka, nida ko dedetawa bamuyi ba, "
Kaka tace" eh gaskiya kam, inaga sai kun kwana Kuna fira shine zaku dedeta, inba hakaba awarku nawa? "
Tajuya ta kalli saudat tace
" ke saude awarsu nawa?"

Saudat tanata dariya tace" kaka minti talatin nefa, "

" Au to minti talatin me marabarsu da awar,
Mugani meya baki aledar",🤣

ko kula ta banyi ba, ta zari ledar ta bude, "
Aikin kenan yaran zamani bakuda aiki sai shan zaqi, idan watanku yazo ciwon mara yakusa yimuku illa, wallahi Allah yakaimu idan watanki yazo kikazo kina cemin kina ciwon mara, ba asbiti ba ko chemist bazan rakaki ba
Saide shi daya daure miki gindi yazo ya kwashe ki yakaiki "

Saudat tana dariya tace" kaka nide bari intafi wannan drama taku bamai qarewa bace, "

" Um saude tunda kin hada ai dole ki zame, saikuma ki fada masa zamu hadu ne, zamu gauraya "

Nide nace" saudat ki gaida twins sai munyi waya," tace" aiwa "

Kaka tace" yara kuyi ku Gama duk tsiya de iyayenku hausa suke, ahh mu ayi mana karyar larabci,"🤣

itade saudat tana dariya ta fice suka tafi

Mujima da yawa hammad da sauda

** *** **

" Hassan tunda kun dedeta tsakanin ku, ai ina ganin Babu wata matsala, kawai kafada Mata zamuje kano din domin muyi magana da iyayenta, akwai gidanmu na gado nasa anfara gyara makashi, saikuje can ku zauna, maganar kayan lefe kuma zamuje nida yayarka maman nafeesa zamu siya nadauki nauyin wannan, inyaso kai kuma saika basu sadakin "

Ammu Yama rasa bakin magana kawai saiya rungume yayan nasa," yaya nagode Allah yasaka da alkhairi, "

" haba haba hassan
Idan banyi maba wanake dashi dazanyiwa, karka mantafa mu kadai iyayenmu suka bari, hassan kadena yimin godiya
Ka cancanci ayi Maka komai,"

Haka Ammu yatashi yana fara'ah, bakin nan kamar gonar auduga 🤣

After 5 day's

Su Abba sunje gidansu anty maimuna dake kano rijiyar lemo, kuma alhmdlh anyi musu karba ta mutunci an tsaida ranar aure nanda 4 month's

** *** **

Kwanci tashi rayuwa na tafiya har muna semester qarshe, yayinda soyaiyar mu nida ahmad tayi nisa, har idan bamu haduba Bama Jin dadi.

** *** ***

"Musa ya maganar aikin dana baka,"

jikinsa na rawa yace. "hajiya anfara de saboda aikin yanada yawa, Amma yanzu nafara nasamo number sa da kuma gidansu"

"OK to ka turomin Number ko,"

"To hajiya laila,"

"Dan waye shi?"

"Dan gidan sanata ne meci ayanxu,"

murmushi ta saki
"OK jeka saikaji alert"

Tundaga wannan lokacin laila kullum saita kira ahmad, shikuma baya amsa new number, daga nan ta koma text, ganin yanda ta da meshi da kira ne yasa, ya amsa, anan ta zayyana masa yanda take sansa kawai sai yayi rejecting Kiran

Ran laila ya baci, kuma tunda yayi Mata haka ta qudurta bazata barshi ba, saita samu abinda take so awajansa.

** *** **

"Khadijaty yakamata fa, gobe mu shirya da wuri, tunda kinga doctor din da aka gayyato mana, ance baida mutunci, ba shida wasa Akan aikin sa,"

"wallahi husnaty haka naji Ana fada, baida fara'ah, kullum fuska atsuke, to kinga kuwa ai gara mu kiyaye, da ayi mana rashin mutunci"

"Ato shiyasa nake miki tuni khadijaty Dan nasanki da nawa, in kika fara kwalliya zaki dau lokaci,"

"to husnaty ni kece da bazan tsaya inyi kwalliya ba, haka kawai Dan kinga da kyanki ni saiki hanani,"

"to khadijaty naji pls nide kiyi sauri,"

"karki damu qawata, insha Allah zamu rabu lafiya dashi,"

"Allah yasa qawata
Wallahi bakijiba gabana har faduwa yake"

"lalle husnaty, nikuma yanda kike da ilmi har addu'ah nake dama nice ke
Kawai ki kwantar da hankalin ki, Babu abinda zai mana, munga doctor marafa ma, kuma mun rabu dashi lafiya,"

"Toshiknn khadijaty sai anjima, sai mun hadu goben"

Mrs Usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

19

Ta shirya tsaf cikin atamfarta pink da sirkin green, dinkin Riga da sket, sosai dinkin ya karbi jikinta, ta dauko lapcourt dinta ta saka, taje gashin kanta tayi, tayi faking dinsa, powder kawai ta shafa, ta dansa pink lipstick, taja mayafinta pink tayi rolling, Jakarta ta dauka tafuto,
"Mama na tafi,"

"Zonan husna, yanzu duk jiya cikin dare kika hanamu bacci, saboda bakyajin dadi, Amma bazaki hakura da Zuwa asbitin nan ba?"

Agogon hannun ta ta kallah, goma da rabi, kuma adaidai wannan lokacin doctor dinsu zaizo
"Mama ai nasha magani naji relief,"

"to shikkenan idan bazaki iya bade ki nemi izni ki dawo gida"

"To mama insha Allah"

"Saikin dawo,"

"to"

Wayarta ce tafara ringing, "hello khadijaty,"

"husna kina inane, doctor fa yazo, wallahi ba fuska awajansa meya zaunar dake ne?"

"Khadijaty Babu Ikcin bayani, kawai sai nazo gani nan, ta katse wayar"

11:6 dai dai tayi Mata agaban Dan qaramin ajin dasuka shiga domin qarin bayani Akan lemonia dawasu daga cikin cutukan da yara suke fama dashi

Yana sanye da suit baqa tayi masa kyau sosai, kansa sai sheqi yake, bayani yake cikin qwarewa da salonsa na qwararran doctor
Yanmatan kan Gaba daya yadau hankalinsu yana bayani Amma duka tunanin su yana kansa, gaskiya basu taba haduwa da likita maiji da kai da iya bayani kamar doctor TAHIR ba

Takai kusan minti ashirin a tsaye, ita bata nemi iznin shiga ba, shima kuma sarai yaganta bai bata damar shiga ba, kawai bayaninsa yake
Sam baya San yara masu sakaci Akan aikinsu, ahakan suke tunanin aiki bayan abinda zai amfanesu ma, basu maida hankali sunzo Akan time ba

Su yan ajin dayake bayanin dansu dayawa hankalinsu baya kan bayanin nasa, ita kuma baiwar Allah dataga ba shida niyyar bata iznin shiga, kawai saita nutsu ta maida hankalin ta Akan bayanin nasa,
Tun tana tsaye harta nemi waje Ajikin window ta jinkina tana jinsa
Har 12:30 tayi
Su kansu yan ajin sun gaji bare ita datake tsaye 🤣🤣

Shiya fara futowa daga ajin yana takun qasaita yazo daf da ita ya kalleta ya wuce

Khadija ce tafuto, tajanyota jikinta, "husnaty meyasa haka?"

"Wallahi sister ciwon kai cikin dare, dakyar mukai bacci nida su mama"

"Ayya sorry kinji,"

"Ok ngd" cewar husna

"Muje muci abinci muyi sallah Ana jimawa zai dawo"
Munci abinci a capteria, mun idar da sallah muna jiran lokaci ya qarasa mu tafi, khadijaty tace "wallahi doctor din nan baida mutunci
duk yanda akai baida Mata, Dan da yanada iyali bazai bar mace awaje ba, tunda baiji dalilin lattin ba,"

nace
"Toya za'ai sai hakuri"
Jakarta ta janyo, tafara kwalliya saida ta kammala sannan tajuyo ta kalleni
"Gashinan gyara fuskar ki mu tafi,"

"Share kawai khadijaty,"

"A a husnaty gaskiya ko powder ne ki shafa,"

Haka Babu yanda na iya nakarba nasake gyara fuska ta
Kai tsaye ajin muka tafi, duk Ana zaman jiransa, 1:45 yashigo muka dora daga inda muka tsaya
Saida yagama bayanin sa kaf, kafin yayi tambaya
Nanfa yan aji kowa yayi shiru, yasake maimaita tambayar nan de dakyar wani acikin maza, yayi bayani shima doctor tahir yace bai gamsu ba,ko akwai me qarin bayani?

Aji akai shiru, khadija sai zungurin husna take da kafarta

Husna tana jinta ta share ta,
Muryarsa suka tsinta yana cewa

"dama ku dakikai ne?🙈😳 In bata lokaci ina koya muku Abu karshe cikin ku arba'in da daya, mutum dayane zai iyamin bayani?
Ina hankalin ku yake?
Zanyi magana da director dinku, ni kwata kwata ma bai dace ku fita this year ba, 🙆🏻
Ahakan zakuje asbiti?"

Haka yake ta banbamin fadansa saida yagama, sannan acikin Mata wata ta daga hannu, tana ta kwarkwasa itama de bayanin kamar na namijin ta kwashe ta sake fada 🤣

Yasake tambayarsu Babu mai qarin bayani?

Khadija tayi kasa da murya tace" husna ki fada nasan kin sani sarai
Pls ki fitarmu kunya, ni wallahi ko na tashi, inna fara bayani murya ta rawa Zata fara karshe ya

tsinka min mari yace in zauna 😱🤣🤣

Dariya taso kama husna, aikuwa kai tsaye ta daga hannu

Shi kansa mamaki ne yakamashi, ganin bata shigo ajiba, Amma ta daga hannu
Aransa yace zanyi maganin ki 🤒
Yace Mata "futo kiyi bayani,"
aikuwa yan aji aka bita da ido yuuuu👀
Tafita gaban ajin tafara bayani cikin nutsuwa, kawai ruwan bayani take zubawa
Shi kansa tun kansa yana sunkuye saida yadago kai ya kalleta, saboda shi a tunanin sa yarinyar bazatayi wani abin kirki ba
Aikuwa ya zuba Mata ido, kamar yasamu TV, kawai Dan karamin bakinta yake kallah yanda take bayani filla filla harma da abin da ba'a tambayeta ba, take qarin bayani akansa, maganar gaskiya itace shi kansa baiso tagama bayanin ba,🙈🤣 Takoma wajan zaman ta ta zauna,

Sake qarin bayani yayi sannan yayi musu sallama yafita, Amma zuciyarsa tana ingizashi Akan yaqara kallanta ko sau daya ne, haka ya share, saboda gudun renin dalibai

Office din abokinsa yanufa kai tsaye, doctor Bashir yana daddana system din gabansa, yace "kaga manyan likitoci, yaya daliban namu?"

Murmushi yayi, yace" daliban ku, sai alkhairi, nagama dasu Amma bazan sake dawowa ba koda kun turamin requesting "

" Haba doctor tahir, me yayi zafi haka,? "

Anan yabashi labarin abinda yafaru, yace" saida qyar wata yarinya tayimin bayani filla filla, Amma abinda zai baka mamaki shine wallahi ta window taji lecture, hanata shiga ajin nayi, saboda tazo late, wallahi yarinyar ta birgeni sosai "

D. Bashir yace" Amma wacece wannan kuwa, kode husna mu'az ce? "

Tahir yace" doctor taya zan sani nida Yau nafara ganinsu, "🤣🤣

Bashir yace" gaskiya tunda naji kace bayani filla filla nasan cewa ita kadai ce me wannan qwarin gwiwar, "

** *** **

" Khadijaty yi sauri mu tafi, wallahi banasan ciwon kaina yadawo, mama bazata min ta dadi ba, saboda dama saida tace karnazo"

Riko hannun ta khadija tayi suka fara tafiya abinsu gwanin birgewa, adaidai lokacin su kuma sunata qyaqyata dariya, sun futo daga office dinsu, ai suna ganin doctor Bashir har hada baki suke wajan fadin" Malam ina wuni? "

" Lafiya khadija, husna sannun ku ko, "
sukace yauwa suka wuce abinsu

" Khadija kiga mutumin nan Dan renin wayo, yanda yake dariya mukuwa yawani daure mana fuska kamar tsohon kumurci, "🤣

" hmm husna kenan abinda zan fada kenan kika rigani "

** *** **

" Yes doctor Bashir me pink din kayan ita nake fadama labarin ta dazu,"

" OK aidama nafadama husna ce
Sosai tanada kokari yarinyar
Gata saliha Babu ruwanta "

" OK" kawai yace

anan sukai sallama yashiga motarsa yadau hanyar kano

Fata nagari doctor tahir

** *** **

After one month
Karatu nake tuquru saboda zamu fara jarabawa ta karshe, nida saudat saide waya, kaka tayi mitar indena zaman daki ina futowa tana ganina Amma nayi mirsisi da ita, 🤣wuni nake ina karatu na, ahmad kuwa yayi nacin mu hadu naqi yarda saboda karatu

** *** **

Wayarta ce tayi ringing, cikin hanzari ta daga, "musa ya ake ciki?"

"Hajiya laila, hajiya laila ikon Allah, ai angama komai hajiya, nayi shige da fice na, nayi magana da yar aikin gidan,
Dafarko ta nuna gardama Amma dataga ruwan kudi, tuni ta amince, yanzu haka angama komai, nabata saqon kuma nayi Mata bayanin yanda zatayi amfani dashi, yanzu haka da ita nagama waya, tacemin taji mahaifiyar sa tana shirin aikensa gidan qawarta hajiya bilki, to zatayi kokari tasa maganin, kuma zatasa ido da kunne tasan lokacin dazai futo daga gidan saita fadamin, dazaran yafuto kuma zaije inda aka aike shin, saiki tareshi acan kawai kisan yanda zakiyi tunda de abun ansaba, kawai sai kuma me afkuwa ta afku, ya fada yana dariyar keta "

Laila cikin farin ciki tace" aikinka na kyau musa, zakaji kyakykyawan alert"

Musa cikin murmushi yace "nagoge sosai hajiya laila"

Tsalle tayi ta dira Akan gadonta, shikkenan burin ta yakusa cika, takusa dena mafarkin ahmad, yanayin datake so tagansu aciki shida ita zai tabbata kenan

Mrs usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

Tunani take adakin ta, ita kadai, anya kuwa Zatayi amfani da maganin nan?
Shin idan aka ganota yaya karshenta zai kasance?
To Amma kuma ai sunyi yarjejeniya da mutumin nan, sannan yace Mata idan komai ya kammala zai qara Mata wani abun
Idan tasamu kudi kafin ma agano ta saita bar musu gidansu

"Walaya!  Walaya!!"

Taji Ana kiranta da gudu ta futo, "hajiya gani,"

"yauwa ga yan biyu nan da maryam zasuyi lattin school tun dazu suna jira baki shiryasu ba"

"To hajiya, ayi hakuri,"

Hannun maryam taja," taho qawata, tana Mata dariya gamida Jan kumatun ta.

** *** **

" My feenah yakamata inganki fa, gaskiya na gaji, haba wannan wanne irin karatu ne, "

" Tokayi hakuri my ahmad yanzu yaushe zakazo?"

"Yaushe zaku fara exam"

"nanda 3 days"

"ok kafin lokacin inasan naganki pls ki amince"

"toshkn yaya, bye bye"

"OK bye," shima ya ajiye waya

** *** **

"Eh inajin ka Abi,"

"ya walad yaya maganar da mukai dakai Akan daukan ma'aikatan company din nan danakesan budewa ahmad?"

"Eh Abi yanzu haka angama karbar information dinsu, komai yagama kammala kawai lokaci muke jira, da kuma kai"

"Toshiknn katuromin shi ahmad din, akwai wani company babba anan, dayake fitar da wasu sababbin motoci sabuwar qira, inaso muje dashi domin yaga komai, bazai dau lokaci ba insha Allah
Idan yadawo kuka sai ayi bikin Bude company nasa"

"To Abi, Allah yaqara budi, ka gaida ummi bara'ah"

"to zataji sosai"

** *** **

"Waladeey"

"na'am momy"
, "ga wannan lesunan idan kasamu dama ka fita kayi kokari kakaiwa hajiya bilki qawata, Bama sai Yau ba kawai duk lkcin daka samu kanka,"

"OK momy zanyi kokari nakai Mata insha Allah"
Tace "yauwa"

Kayan yafuto dashi ahannunsa, walaya nagani tana moping afalo, tagaban ta ya wuce zaije bangarensa, gabanta yayi mugun faduwa, gashi zai fita kuma bata aiwatar da aikin da aka ba taba, kawai abinda zatai yanzu shine Zata saka maganin tafada musu ta saka, koma yaushe ne yayi amfani dashi su suka sani, itade tariga datasa

Daddy ne yashigo da alama daga waje yake

Ahmad naganinsa ya qarasa ya gaidashi, yace" yauwa my son, inasan magana dakai kabiyoni part dina,"

" OK daddy "

Yabishi abaya suka tafi.

Duk abinda yake faruwa a ido da kunnan walaya
Tana ganin shigarsa, ta wullar da mofar hannun ta, tayi Dakin ta, kayanta tashiga zazzagawa ta dauko qullin maganin, ta cusa agefen zaninta
Baqar leda ta dauko tayi part din ahmad cikin sauri

Megadi ne yaga giftawar mutum, yajuya yace to waye wannan kamar ba yallabai ba, yatashi domin ya duba yaga ko menene.

** *** **

My son munyi magana da abi "qabla qalil" (dazu)
Yayimin magana Akan companynka,"

ahmad ya daga kansa" company kuma daddy,?"

" Eh ai aikin wannan sabon company din da akeyi abi ya fadamin mallakinka ne
Yanzu haka yace ya nasan ganinka Akan wasu motoci dayake so kagani ko zaku buqacesu a kamfanin, "
Ahmad aransa yace shikkenan ma, kafin ya dawo yasan su feenansa sun Gama, exam,
Daya fara aikinsa kuma sai suyi maganar auren su
Daqo kansa yayi yace," daddy nine da company, gaskya nagode wallahi,"
Daddy ya dora hannunsa Akan lebensa yace" Shshshh
Bani zakaiwa godiya ba, abi zakayiwa, abi zai iya yima komai saboda kaunar dayake ma "

" Toshiknn daddy zan kirashi,"

" yauwa my son daga nan kuma sai asamo mana matar aure ko "

Ai ahmad najin haka ya suri ledar da momyn sa ta bashi yayi waje

Daya futo falo har yayi hanyar part dinsa, sai kuma yafasa yace gaskiya gara yafara fadawa mahaifiyar sa wannan daddan labarin, kai tsaye yakoma Dakin momy

** *** **

Yana tafiya har yaje kofar Dakin, ta window yaleqa anan yaga walaya, ta Bude fridge, yace "ah ah, 'yata ashe kece"

Arazane ta juyo shi kansa saida yayi mamaki
Tsaye ta tashi tace" sannu baba, wallahi nazo gyara masa bangaren ne,"

baba maigadi yayi mamaki, yasan shide tunda yake ahmad yanada qyanqyami masu aiki basa yimasa gyaran daki, inba saudat ko mabaruka ba, Amma kawai saiya basar
Be kawo komai ba yace" to Allah yatemaka sannu"

, be jira amsar ta ba yayi waje

Wata nannauyar ajiyar zuciya tasauke, tayi sauri tafutar da lemukan cikin fridge din duka, ta dauko na ledar datazo dashi, wanda already tasan lemon dayake sha, tunda ita take aiki agidan, ta Bude ledar datazo da ita, ta futo danata lemukan already tariga da tazuba maganin aciki, kowanne kwali daya na lemon tasa drug guda uku acikin sa
Aqa'idar maganin guda dayama ya isa, Amma walaya Babu ilmin boko balle ta karanta haka ta babbanka maganin acikin lemukan, ta dauke nasa lemon tayi waje

Dakin ta ta nufa, taboye lemukan, sannan ta kwanta a gado tana maida numfashi, aranta tana fadan Allah yasota Babu wanda yaganta

** *** **

Yana zaune a office dinsa yayi tagumi da hannu bibbiyu, yakai sati uku kenan yana fama da tunanin yarinyar nan,🤣 yanzu shi ai abin kunya ne ma yakira doctor Bashir yace yahadashi da ita, yanda yaga Bashir din yana masa maganar yarinyar shi kuma yana wani babbasar wa,aida

kunya,
Wayarsa ce tayi ringing  best friend naga ansa, yana dagawa yace "man ya akayi,"

Ahmad dayake kwance Akan gadonsa yayi wulli da ledar da momy ta aikeshi, ya kyalkyale da dariya, tahir yasake kallan wayar danya tabbatar anya ahmad ne kuwa, kafin yagama mamakin sa yaji ahmad yace "matumina katayani murna
"jaddiy"na(kakana) ya budemin company"

Cikin zaro ido tahir yace "wow
Wai da gske?"

"Yes da gske nake"

"Kai Amma gaskya yakamata mu hadu
Dan asake taya Juna murna,"

ahmad yace "toshkn bari inzo gidan in same ka, kaga daga nanma saika rakani gidan qawar momy zan kai Mata saqo daga nan kuma saimu wuce wajan feenah, muyi sallama da ita Dan so nake, next week in wuce Cairo"

Tahir ne yadafe kansa, yace "wallahi abokina ina office"

Ahmad ya kalli time, yace" office kuma tahir, kokuna da tiyata ne? Yanzu fa bakwai saura, "

Tahir yayi ajiyar zuciya yace" wallahi ina cikin matsala ahmad "

" Subhanallah "

fadin ahmad
" Meyake faruwa haka tahir? "

Anan tahir yafada masa komai
Ahmad yayi ajiyar zuciya yace" wallahi ni jinake wani Abu nema"

, tahir yace "wani Abu ne mana ahmad yanda naje musu ina Jan ido, ina zare musu ido, harda ce musu dakikai, tayaya kake tunanin zan tunkari yarinyar?"

Ahmad yace "haba man, karka bani kunya mana, kamar ba doctor ba, kuda yan Mata ke rububinku"

Doctor tahir yace "wato kafara ko?
Serious ahmad ban taba zatan zan so wata yarinya sama da iklima ba, wallahi ahmad idan ban

samu yarinyar nanba, yanda nakeji zaku iya rasani"

"Subhanallah haba tahir kadena fadar haka
Yanzu kasan me zamuyi?"
Doctor tahir yace "a a saika fada"

Anan ahmad yafada masa hanyar dazaibi yasamu kan yarinyar
Doctor tahir yayi masa godia

Ahmad yace "yanzu ka tashi nazo na daukeka mu tafi,"

tahir yace "man, kayi hakuri kaje tunda kace sallama zakuyi, bazan bika ina ganinku kuma soyaiya ba, bayan ni banma saita kan tawaba,"

"Toshiknn next time idan na dawo sai muje, Amma Dan Allah kafin na dawo daga Cairo kaima kayi kokari kashawo kan yarinyar nan Dan musamu yan dagwai dagwai da wuri,"

Dariya tahir yasa, yace" wallahi Allah ya shiryeka,"

sukai sallama

Jin Kiran sallah yasa ahmad yashiga wanka, yayi alwala, shirin masjid yayi, yaje yayi sallah, bayan yafuto daga sallar yakira feenah bata dagaba, saiya share, yaje ya shirya cikin qananan kaya baqin jeans da milk din Riga, sai qamshi yake,ya dauko ledar dazai kaiwa hajiya bilki, tsautsayi yasa yabude fridge bai kawo komai aransa ba, ya daga kan lemo ya kwankwada,🙆🏻🙆🏻 ya rufe yabarshi anan kan fridge din yafuta da sauri

Kosu momy baiyiwa sallamaba yaja motarsa yafice
Walaya najin tashin motarsa ta kira musa ta shaida masa ahmad yafuta yanzu, Amma bata saniba abinda tasa yasha ko bai shaba, Amma de su bibiyeshi sugani koya sha
Musa yamata godia ya kashe wayar

** *** **

"Mom nafita saina dawo,"
inji laila, anci kwalliya ansha kyau dinkin nan yakamata tam, kirjin nan duk rabinsa awaje, "OK my daughter saiki dawo,"

kawai hannu takadawa uwar tayi waje

Waya take da musa tana driving, shine ya ke kwatanta Mata hanyar gidan hajiya bilki, har tazo layin gidan tasamu waje tayi parking tana jiran isowar ahmad ayita ta kare

** *** **

Yayi nisa a tafiya wayarsa tadau qara, yana dubawa yaga ansa my feenah
Bayan ya daga tace masa tana wanka yakirata, yace dama zaizo yaganta ne, Dan yasan idan tafara exam bazai samu ganinta ba,sannan yanaso zasuyi wata magana, to
Itama kuma ganin ta Dade bata ganshi ba yasa tace to sai yazo, ajiye wayar yayi,
Har ya hau titin dazai kai shi gidan hajiya bilki yafasa, yajuya kan motar Zuwa gidansu feenah

Mararsa ce yaji ta murda masa, yana magana afili yace "Meyake faruwa ne,"

dayaji ciwon yana lafawa kawai saiya share yaci Gaba da tuqi har yaje kofar gidan
Kiran ta yayi awaya, tana zaune ta idar da sallar ishsha'i, hijabin ta cire tafeshe jikinta da turare, doguwar Riga ce a jikinta, ruwan siminti, rigar hannun vest ce da ita, kaka tasamu afalo tace" kaka ina Zuwa, zan gaisa da ahmad awaje indawo,"

" to nafi saikin dawo, "

Feenah na fita yaganta, yayi Mata order, ta isa jikin motar ta Bude ta shiga
A wannan lkcin maganin da ahmad yasha yafara yimasa aiki, Gaba daya wani irin yanayi yakeji ajikinsa

Tana shiga yashaqi kamshi turaren ta me dadi, "my feenah, koda yaushe ke mai kyau ce,"

murmushi nayi na sunkuyar da kaina

Yace "unguwa zanje, momy tabani saqo in kaiwa qawarta,"

nace "ok, to saika dawo,"

ina kokarin fita da ga motar, hannu na yariko, " haba my feenah pls ki rakani mana,"

yafada da rinan nun idonsa,
Ahmad yanayin dayake ji baisa yakawo komai aransa ba, tunda yanajin yanayin Aduk lokacin daya kebe shida ita,

Nace" my ahmad meyasami idonka naga yayi ja? "

Cikin kasa kasa da muryarsa yace

" nima bansaniba haka nakeji wani iri, kamar inasan bacci "

" Toka koma gida mana,"

" a a my feenah aida nisa, kawai bari inyi kokari muje mudawo, zanyi sauri kinji, a yankaba take matar,"

banyi musu ba, yaja motar muka tafi,

Munyi nisa sosai mun wuce government house idon ahmad yafara lumshe wa, Gaba daya wata irin muguwar sha'awa yakeji, yawo yafara dasu Akan titin, hannun motar yanaso ya kwace masa

Feenah cikin firgici tace," yaya! Yaya!! Meyake damunka ne?
My ahmad!!!"

Tafada da karfi, kokari yayi yadawo gefen titi yayi parking, ya jinginar da kansa Akan kujera, feenah tazubawa sarautar Allah ido,
Gani tayi yana wani irin numfashi

Cikin rashin damuwa, takai hannunta kan fuskar sa, tana shafa kumatunsa tace

" yaya, Meyake faruwa ne?
Bakada lafiya ne? "

Ahmad dajin tattausan hannunta Akan fuskar sa, hakan yaqara haifar masa da matsala

Hannunta yariko yace Mata "bari mana feenah"

Itade tanata kallansa, tace

"yaya kawai mukoma gida, nikam duk atsorace nake hankali na bazai kwantaba ina ganinka a wannan halin pls mu tafi"

Bakinta yakebi da kallo kawai tana maganar nan, baisan lokacin daya fisgota jikinsa ba,
Ido feenah tazare tace

" ya....

Kafin taqarasa ya hade bakinsu waje daya

Ayayinda Hannunsa yake yawo ajikinta, Gaba daya taji wani iri, tana kokarin kwace wa yana qara rike ta, Dan a yanda yakeji ayanxu bazai iya hakura da ita ba

Bakinta ta kwace da kyar, tace" ahmad menene haka? Mekake shirin aikatawa ne? Dama wannan ce maganar dazaka min din,?"

Tafada cikin rawar murya

" Please my feenah, ki temakeni, bansan Meyake damunaba nima "

A wannan lokacin kam feenah tafara hawaye, tace" ahmad kasan mekake fada kuwa? "

Hannunta yakama yana kokarin sakashi a inda batai zato ba 🙈🙆🏻

Ahmad na hawaye feenah na tayashi Babu mai rarrashin dan'uwansa

Bude kofar motar dayaga zatayi hakan yasashi qara fisgota, batai auneba sai ganinshi tayi dab da ita hijabin jikinta yake kokarin cirewa ita kuma tana qara rikewa dole saida ya cireshi, saboda ba karfinsu dayaba
Hannu tasa tana kare kirjinta tace cikin kuka,

" Dan Allah karka cutar Dani, kayi hakuri idan nama laifi kayafemin, Dan Allah karka ketamin haddi na"

Yayinda feenah take wannan mgn ahmad jiyake kamar qara tunzurashi take, Gaba daya baya cikin hayyacinsa,
Hannunsa yasa yacire Mata hannayenta dasuke kan kirjin ta, yasa hannu ya yaga rigar jikinta, baiyanar na shanunta shiya kara fitar dashi daga hayyacinsa
Tuni yakai musu wata irin cafka,
Feenah tana dukansa da hannayenta biyu Amma shiru kakeji
Kara tasa gamida ihun atemaketa Amma Babu wanda yaji kasancewar duka glass din motar arufe suke, hannu yasa ya kwantar da kujerar, yaci gaba da wasa da dukkanin jikinta

"Ahamd kayi hakuri karka cutar Dani,"

shine kawai abinda feenah take fadi, sake hade bakinsu yayi waje daya

Yayinda feenah ta kwace Bakinta tasaki wata gigitacciyar qara gamida sumewa, shikkenan ahmad yacika aiki.

Mrs Usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

21

Tsawon lokaci ta dauka, tana duba agogon dake tsintsiyar hannun ta
Ajima tasaki tsaki, Ajima tasake sake sakin wani tsakin
Daga karshe ta yanke shawarar Kiran Malam musa

Wayarta ta janyo qirar samsung, bugu hudu ya daga
"Hajiya da fatan komai ya kammala, dama tayaya zaija dake, nasan kinfi gaban nan wallahi,"

Cikin tsawa tace "dakata Malam musa, ba wannan ne yasa nakira kaba, dama kasan yaron nan bai futo ba, Amma kasa na bata lokaci na, nabar alhaji gali yana jirana, nataho nan"

Musa yace," kiyi hakuri hajiya Amma tabbas yafuto, kuma nasan cewa ba za'a samu matsala tunda ya futo, kede kawai kiyi ta jira" 🤣

"Inyi ta jirafa kace musa, Toshiknn zanyi ta jira kaima yashafeka,🤣
wallahi a kudin ka,"

musa yace "a a hajiya baza'ayi haka ba, bari nasake tuntubar hanyar gidan matar, tunda yar

aikin tayimin bayanin komai,"
ba tare datace masa komai ba, ta katse wayar

** *** **

Ahmad bai tashi dawowa daga duniyar daya Lula ba ta dadin kowa, sai bayan kusan 46 minutes
Awannan lokacin feenah batasan inda kanta yake ba, Babu alamun numfashi atare da ita
Jikinsa yazare daga nata, daga baya kuma ya rungume ta gam ajikinsa, kukan ma Gaba daya yaqi Zuwa, kawai kallan ta yake
Yau shi ahmad shine da yiwa wata yarinya fyade,😭 raping dinma yarinyar dayake mutuwar so,😭 Gaba daya sai tausayin ta ya kamashi

" feenah, feenah, feenah!!!"

Yafada da karfi, saide Babu alamun Zata iya tashi,
Sai Awannan lokacin kuka mai karfi da cin rai yazo masa, tana rike ajikinsa yana buga kansa
Ajikin glass din motar, har hakan ya haifar da tsagewarsa

"Nafeesa Dan girman Allah ki yafemin, nafeesa na yaudareki, tabbas nacika mayaudari, kiyimin ko wanne irin hukunci nafeesa

DANA SANI daban daukoki ba, saida zaki fita nahanaki nafeesa, kiyi hakuri,"

yafada yana kuka tamkar, mace, tunda yake arayuwarsa bai taba kuka irin haka ba, yaci amanar wadda ta yarda dashi fiye da kowa da komai

Jijjigata yayi, yaga de tabbas idan baiyi da gske ba zai iya rasata, hakan yasa yatashi yagyara wandonsa
Futowa yayi da ita a hannun sa, kamar matacciya, yabude bayan motar yasaka ta aciki yarufe
Hawaye shabe shabe Akan fuskarsa yazago yajasu aguje, sai wani private hospital dayake kusa

Yana parking ko kofar motar bai rufe ba yabude yadauko ta, Babu alamun rai atare da ita, mantawa yayi da hijab dinta yakoma yadauko yarufa Mata, yayi cikin hospital din aguje

"Malam baka rufe motar ba,"

wani mutum dayake gefe yayi masa magana,
Ahmad yace" Dan Allah bawan Allah rufemin"

bai jira amsarsa ba, yayi ciki

"Nurse!"
Yake fada cikin daga murya
Wasu Mata biyu suka karbeta ahannun sa, wani daki sukayi da ita Akan gadon tura marasa lafiya,
Dafe kansa yayi kawai yana hawaye, har yanzu ganin abun yake kamar amafarki, Ajikin bango yadora kansa yana kuka 😭

** *** **

"Oni rabi'atu wannan wacce irin fira ce haka, yarinya tun dazu tafita Babu alamun ta, to kode wani wajan sukayi, bari nakirata"

Wayarta me torch light ta dauko ta kira har sau uku, ba'a dagaba Awannan lokacin wayar nacikin aljihun ahmad, yakasa dagawa, tome zaice Mata, irin wannan cin Amana
Kaka taja hijabi tayi kofar gida, taga Babu kowa, sai gida ta dawo tace
"bari Ajima nasake kira, Allah yasa de lafiya

** *** **

8:56 pm, ahmad yana Dakin da feenah take, ansa Mata ruwa, fuskar ta tayi wani iri, kawai kallanta yake yana hawaye, Awannan halin nurse tashigo tace" masa doctor yana kiransa a office "

Jiki asabule yatashi yabita, yana tafiya yana waiwayen feenah

Yazauna akujera a gaban doctor, doctor yagama rubuce rubuce yadago kansa yace,

" haba abokina, irin wannan barna haka kamar ba amaryarka ba, ai yakamata kabita a hankali,"

Hawaye ne ya zirarowa ahmad yace "doctor kayi hakuri, tsautsayi aka samu, insha Allah hakan bazata qara faruwa ba,"

Doctor yayi ajiyar zuciya yace "ok, yanzu de Dan Allah kabarta ta huta Tsawon sati daya, sannan munyi Mata dinki, munyi Mata allurar dazata kashe Mata zafin ciwon, da abinda yakamata
ga wannan, yabashi takarda kaje kasiyo Mata magungunan nan, dole Zata buqacesu"

Karbar takardar ahmad yayi, yafuto
Maigadin ne yanuna masa inda zai samu magungunan

9:8pm wayar dake gefen gadon ta dauki qara, itace ta taimaka Mata wajan farkawarta
Bude idonta tayi wanda yayi ja, saboda kuka, ta kalli Dakin, sannan takai hankalinta kan wayar, gani nayi ansa kaka, Akan screen din wayar, kashe wayar tayi gaba daya, ta yunqura ta tashi, ruwan dake hannun ta ta cire, tasauko, zafi taji agabanta nan tasaki qara, tana yarfe hannu, Kamar me tafiyar ta ta ta, haka ta futo daga Dakin, Babu wanda yakula da ita, haka ta zare jiki tafuto harabar hospital din,
Dakyar taje gate din asbitin, baba mai gadi harda ce Mata sannu yarinya ganin yanda take tafiya yasan Babu lafiya
Kawai daga masa kai tayi, ta wuce
Gaban titi ta tsaya ta tsaida mai adaidaita, tayi masa kwatancen inda take so yakaita, dari biyu yace Mata, Babu musu tace masa Amma sai sunje Zata shiga gida ta dauko masa, yace.
"ba damuwa"

Tashige suka tafi

** *** **

Laila nagani tana waya, tace "Malam musa bazai zoba kawai zan hakura Yau din inci Gaba da bibiyarsa, kokuma mu sake wa dabarar,"

"Toshiknn hajiya ngd"

** *** **

Kaka nagani ta rafka uban tagumi a kofar gida, tun dazu take Kira wayar nafi akashe, acan kuwa feenah kukan zuci kawai take, tana kuma share hawayen ta, kasa danne zuciyar ta tayi, tasaki kuka mai sauti, mai "raksha" (adedeta) yace

" hajiya kiyi hakuri, cuta ba mutuwa bace, Allah yabaki lafiya, saboda naga daga asbiti na dauko ki," 🤣

qyaleshi tayi taci Gaba da share hawayen ta, har sukazo kofar gidansu, kaka tagani atsaye itada wani saurayi da alama cikiyarta ta take bayarwa
🤣

** *** **

" Abban husna, nifa Gaba daya banajin dadin jikina,"

Abba yayi murmushi yace "to maman nafeesa me yake damunki,"

tace "haka kasala kasala nakeji, bakina banajin dadin sa,"

Abba yace "to kiyi hakuri Zuwa gobe sai muje asbiti,"

mama tace "haba alhaji wanne irin asbiti kuma,"

Abba yace "a a banasan musu,"
hannu yasa yashafa wuyanta, aikuwa zafi kamar gidan biredi, yace

" subhanallah maman nafeesa me yake damunki haka?"

Mama tace "alhaji ni kalau nake,"

Abba yace "a a Babu wannan maganr kawai de kice bakyasan fadamin abinda yake damunki Dan kada hankali na yatashi, narasa yaushe zaki dena wannan halaiyar taki,"

"to alhaji kayi hakuri,"

"Kinga tashi, tashi maza muje ki kwanta ki huta gobe insha Allah sai muje asbiti kiga likita,"

mama tace "to Allah yakaimu"

** *** **

Futowa nayi daga adedeta dakyar nake dingisa kafata ina hawaye, badan kaka tana cikin tashin hankali ba, Babu abinda zai hana ta fahinci halin danake ciki,
Dasauri ta qara so gareni, "sannu nafi, sannu daga ina kike naga kina tafiya a hankali kamar marar lafiya bayan nasan kalau kika fita,"

kafin na bata amsa me adedeta yace "mama, ai asbiti na dauko ta, batajin dadi,"

salati kaka tasa, ta janyoni jikinta,
Gaba daya tausayin kaka yakamani yanda ta damu Dani, take kaffa kaffa Dani, ga abinda naje na aikata, mema ya kaini bin saurayi unguwa, nayi DANA SANIN Sanin ka arayuwa ta ahmad, Cikin kuka nace" kaka ki bashi dari biyu kudin sa, "

Kaka tace" yaro yi hakuri bari nadauko ma kudin,"

me adedeta yace" a a mama ki barshi, ai jinya ce tana kan kowa, "

kaka tace" to Mungo de Allah yasaka da alkhairi, kafin tajuyo kaina tana fadin nafi meyasameki? Ina shi amadun?
Ya akai kuka rabu? "

Nikam nama rasa amsar dazan bata, kawai sai wani tunanin yazo min, nace" kaka hatsari mukayi, "

Salati kaka rafka" hatsari nafi
Innalillahi wa inna ilaihir raju'un
Garin yaya? "

Nide da nake ji ajikina nace" kaka muje, "

kamani tayi mukayi ciki,

Anan nafada Mata me mota ne yabuga mana motarsa shine motar mu tayi gefen titi, anan aka taimakemu, shi yana asbiti ma yakarye, nice de nasamu targade aqafafuna
Hawaye kaka ta share tace" sannu nafi, bari nahada miki ruwa kiyi wanka, "

bayan tatafi awajan na kwanta kan tabarma ina tunanin rayuwa ta
Zancen kakane yadawo Dani daga tunanin dana fada, tace" nafi na dora miki ruwan dumi, saiki gasa kafar, bari inje in kira me gyara,"

nace" a a kaka ai an gyara min a asbiti shiyasa nataho, "

kaka tayi tagumi tace," to waidaku ina zaku je ma?"

Nace" kaka wajan qawar mamansa zamuje zaikai Mata kaya,"

kaka tace" dama da kunyi shawara Dani bazakuje yanzu ba, saida safe,"

nide Bama najin me take fada
ruwan tajuyemin tace inje in sirka yanda zaimin saina watsa kozanji karfi ajikina, haka natashi nayi "hammam" (toilet)

** *** **

Gudu gudu sauri sauri ya qarasa office din doctor din, yabashi magungunan, doctor ya duba yace "eh sune sunyi, yanzu muje Dakin idan ruwan yaqare sai abata maganin, kokuma idan kunje gida sai kabata,"

Doctor na Gaba ahmad na binsa abaya, Gaba daya kunyar hada ido yake ita, 🤣

suna Bude kofar Dakin sukaga wayam Babu feenah Babu alamar ta, gaban ahmad yayanke yafadi, duhu yafara ziyartar idanunsa, nan take ganinsa ya dauke

((to Malam amadi daukacin makaranta wannan novel suna Maka fatan farfadowa lafiya))

Mrs usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my brother Abdulmumin Muhammad El Yaqoub Happy birthday 🎂

22

Da taimakon doctor aka daukeshi aka maida shi gadon da feenah ta tashi, doctor yafara duba shi

** *** **

Ruwan da kaka takaimin a bucket na raba biyu, daya najuye acikin bahon wanka, nadan sirka, kasan cewar ina karance karancen littafi shiyasa nabi duk hanyoyin dana karanta wajan gyara kaina, ina shiga cikin ruwan namike nasaki qara
Kaka datake zaune tadaga murya tace "sannu nafi yi a hankali"

Maganar kaka ce tasa na rufe bakina da hannu na, nadaure na shiga ruwan, saida zafin yaragu sannan nasake Zuba wani ruwan zafin, na shiga, shikuma sauran nayi wanka dashi, ba laifi naji dadin jikina
A hankali nazo na wuce kaka, tana zaune atsakar gida, badan wankan danayi ba, Babu abinda

zai hana taga hawayan fuskata
Daki naje na zauna nasauya kayan jikina, ina zaune da humra a hannu na, nakasa shafawa, kaka ta shigo tace "sannu nafi,"

nace" yauwa kaka, "

tace" me yake miki ciwo yanzu bayan kafar,"

nace" kaina,"

tace" to ina Zuwa "

Bayan jimawa kadan tashigo da pure water da maganin ta bani nasha na kwanta, tace " to ki huta yaude karkiyi wannan jarababban karatun naki, ki huta,"

saida tayi maganar karatu natuna da exam din datake gabana, wutar Dakin ta kashe min ta rage fanka kadan sannan tafita
Tana fita nakafa sabon kuka, yanzu shikkenan ahmad ya cuceni, duk mutumin dana aura bazai ga mutunci naba, nayi DANA SANIN haduwa ta dakai Ahmad, wallahi bazan yafe maba, dama ashe yaudara ta kake akwai abinda kake so ajikina, saudat DANA SANI tun farko daban karbi qawancen dakika zomin dashi ba, wanda shine silar haduwa ta da wannan azzalumin saida nace yayi hakuri, idan wani laifi nayi masa yayafemin Amma shine ya nunamin ba shida imani, afili na furta "insha Allah saika yi DANA SANI ahmad"

** *** **

11:00 yana zaune gaban ummi suna kallo afalo dagashi sai jallabiya yana shan iska, tunani yake shin yakira doctor Bashir Akan maganar yarinyar nan kokuwa? Kawai wata zuciyar tace yakirashi Dan shine kawai mafita
Ummi tun dazu tana kallansa taga Gaba daya hankalinsa bayama kan abinda suke kallo daga gani cikin tunani yake, Amma zataga gudun ruwasa ai
Gani tayi yadauki waya yana dannawa hakan yasa ta kawar da kanta daga kallansa
Bugu daya doctor Bashir yadauka, "abokina ya fama da jama'ah,"

tahir yace "wallahi gasunan alhmdlh kullum muna fama,"

tahir yace "yauwa Bashir nikuwa Yama sunan yarinyar nan daka nunamin rannan,"

aikuwa karaf akunnan ummi tayi murmushi aranta tace ai nasan arina wai ansaci zanin mahaukaciya
Doctor Bashir yace.  "yarinya kuma wacce iri,?" Tahir yace "yarinyar nan daka nunamin har sukazo suka gaida kai muna tsaye menene ma naji kace sunanta?"

Bashir sarai yaganeshi Amma da niyya yake Jan maganar, yace "kai ban gane taba gaskya ko tayi ma wani laifi ne?"

Tahir dayaji kansa yawani sara yace
"a a kaida baka gane taba tayaya kasan ko tayimin laifi, wai nazo office dinka ina fadama abinda yarinyar tayi, har na hanata shiga aji," 🤣

doctor Bashir yace "oh abokina sorry sai yanzu nagane ta husna kake nufi" 🤣

, tahir yace husna aransa suna me dadi, afili kuma yace "no bande saniba,"

Bashir yace "to me kake so,"
tahir yatashi daga falon yayi daki yana waya yace" number ta nakeso ka nemomin kokuma kabata tawa number kace ta nememi yanzu,😳"

ummi
murmushi tayi akaro na biyu ta daga hannuwanta sama tace" alhmdlh addu'ah ta ta karbu Allah yasa wannan yarinya a dace kar a kuma irin ta baya, "
Bashir aransa yace lalle tahir wato shide bazai futo fili yace inasan yarinyar nanba, gara ya dinga wannan kwana kwanar 🤣
Yanzu banda abinsu wacce budurwa ce mai hankali kawai za'a bata number ace ta kira, kuma ma Abu kamar umarni ta kira yanzu yanzu 🤣
Bashir yace "a a bari inturo ma kawai ka kirata, Dan nikam bazan iya wannan karfin halin ba,"

"OK" kawai tahir yace, ya kashe wayar

Yana zama agadonsa yaji shigowar text yana dubawa kuwa yaga Num yarinyar, yawwa yafada a fili,🤣 yaude za'a yi ta takare, wannan labari dole yafadawa ahmad, a wannan lokacin kuma ahmad yana kwance baima farfadoba, doctor din daya duba shi, yana shirin fita daga falon yaji wayar ahmad din tana qara hannu yasa ya dauko wayar best friend yagani, doctor kai tsaye ya daga yayi masa bayanin halin da ahmad din yake ciki, tahir baisan lokacin daya tashi ba yace
"wanne asbitin?"
Nan doctor yayi masa kwatance
Falo ya futo cikin sauri ummi tana tambayarsa ina zaije yace Mata ahmad ne baida lafiya zaije wajansa, cikin alhini tace to Allah yabawa wannan yaro de lafiya, hankalinsa yayi Gaba baima ji abinda take fadaba, mota yashiga aguje maigadi yabude masa yadau hanya

** *** **

Yana Zuwa yafaka motarsa yashiga ciki cikin sauri,ahmad yagani a kwance ga doctor a gefe, anan doctor din yace kawai tashin hankali ne yayi masa yawa, ganin yazo Dakin matarsa bata nan kuma muma bamusan inda tayi ba, sannan mai gadi yace yaga fitar ta, da nasa aka tambayeshi
Tahir yace "matarsa kuma?"
Doctor yace "eh aishi da ita sukazo shiya kawo tama,"
tahir ya nemi waje ya zauna, yace "doctor in bazaka damuba kabani shi mutafi zan kula dashi dan'uwana ne," ID card dinsa ya nuna masa nan take yace Babu damuwa yafita, tahir hannun ahmad yakama yarike, yace ahmad cikin mamaki, tome yakawo ku asbiti bayan nasan sallama zakuyi

Yakai kusan minti talatin a zaune sannan ahmad yafarka, bai Bude idonsa ba, yafara magana

" feenah karki barni wallahi ba laifi na bane, please feenah ki yafemin,"

tahir ne yace "ahmad, ahmad, ahmad tashi, ba feenah bace nine"

Bude idonsa yayi, yana ganin tahir ya rungume shi yana kuka,

" tahir feenah bazata yafemin ba, wallahi nayi mata laifi"

Kamashi tahir yayi suka fita daha hospital din

Amota ahmad banda kuka babu abinda yake, tahir bai hana shi ba, yasan akwai abinda yake faruwa babba, suna Zuwa gate din gidansu ahmad tahir yabawa driver gidan key din ahmad din yayi masa kwatance yace yaje yadauko masa motarsa

Suka shiga ciki, maryam tafuto da gudu tana musu oyoyo, ahmad bai kula taba, sai tahir ne yace "auta me kike bakiyi bacci ba?"

"Tace banga yaya ba shine naqi yin bacci,"

tahir yace "to yaya bayajin dadi jeki kwanta ki huta kema"

Tatafi da gudun ta,
Bangaren ahmad din suka nufa, ahmad ya zauna a qasa yajingina da bangon Dakin, hawaye

suka ziraro masa, tahir yace "ahmad me yake faruwa ne?"

"Tahir na ha'inci feenah, yarinyar tana sona dayawa, Amma na yaudareta,"

kansa yafara bugawa da bango, tahir yatashi da sauri ya rikeshi, "haba ahmad, meyake damunka haka wai meke faruwa ne,"

ahmad ya rike tahir yace" tahir meyasa baka bini ba?
Meyasa tahir?
Kasan me hakan yajamin? Tahir nayi abinda ban taba tunanin ko amafarki zanyi ba, wallahi inasan feenah nasan duk abinda zan fada Mata ayanxu bazata yarda daniba, "

Tahir ne yarike shi, suka zauna abakin gado, tahir yace" ahmad fadamin meyake faruwa? "
Nan ahmad yafada masa komai
Salati kawai tahir yakeyi, yace" ahmad Amma ina tunanin ka yatafi? Tun muna yara bamuda wannan dabi'ar ahmad"

yafada yana goge qwallar idonsa

Ahmad yace "tahir nayi asara, wallahi na cuci wadda ta yarda Dani sosai"

Tahir yace "to Amma menene sanadi? Meyakawo hakan?"

Ahmad yace "Allah ne masani tahir, nayi DANA SANIN daukarki feenah har zaki fita nahanaki, wallahi nayi DANA SANI Akan abinda na aikata miki feenah"

Tahir kawai kallansa yake, shi kanshi ahmad din yabashi tausayi,
Tahir yace "ahmad toko akwai abinda ita yarinyar tayima har hakan ya kaika ga aikata hakan, Dan nasan kaide wannan ba halinka bane,"

ahmad yace "tahir wallahi batayimin komai ba
Kawai de nasan kalau nafita daga gida, nayi nisa ne ahanya naji cikina yana murdawa, haka marata tanamin ciwo kadan kadan, to saida mukai nisa da ita ahanya shine al'amarin yafaru wanda nide a wannan halin ji nayi bazan iya hakura ba, inde bansamu abinda nake soba, "

Tahir yadago cike da mamaki yace" to kaci abinci ne kafin kabar gidan? "

Ahmad yadago kansa yace" banciba, banci komai ba tahir.... Tunanin sa ne ya tsinke dayaga lemon dayasha kafin yabarshi Akan fridge kafin ya fita
Tsaye ya Mike yana nuna just din da hannunsa, tahir ya Mike yace "me kake nufi?"

Ahmad yace "nasha... Tabbas nasha wannan, shine last abin danasha nafita,"

tahir cup yaje yadauko, ya tsiyaya lemon aciki, nan su kaga kalar lemon ta sauya kadan
Tahir yace "kagani ba?Ahmad tabbas ansama wani Abu acikin lemon nan, kabani kwalin lemon zanje gida gobe zan bincika duk abinda nagani zan fadama"

Ahmad kawai yazama mutum mutumi

"Aikuwa akwai rashin mutunci agidan nan, 🤣inde nagane dasa hannun wani aciki, wallahi duk wanda yayi silar bacin ran feenah to tabbas shima saiya tabbata cikin bacin rai,"

juyowa tahir yayi yana kallansa Jin irin furucin dayake futowa daga bakinsa

Mrs Usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

24

Baba naganinsa yatashi tsaye cikin ladabi yace" sannu maigida, yakarfin jikin Naka? "

"lafiya baba yauwa nace kwanaki kuwa lokacin danake rashin lafiya bakaga yaran nan sun shiga part dinaba?"

Baba maigadi yace "yara kuma ranka ya Dade, ai yanbiyu da auta basa shiga su batama kofa"
Ahmad yace "eh baba basu ba haka de Babu wanda kagani yashiga?
Yara ko manya"
Baba maigadi yace "gaskiya banganiba ahmad"
"OK" ahmad yace zai juya yatafi
Sai yaji baba maigadi yace "saide ko in kafin rashin lafiyarka de nake tunani"

Ahmad asukwane ya juyo yace "wacece? Wakaga ta shiga?"
Baba maigadi baiboye komai ba ya kwashe komai yafadawa ahmad
Yaci gaba da cewa tabbas naganta da idona tana gyaran firinji (fridge) ta futo da lemuka tana maidawa
Huci ahmad yake kamar wani tsohon zaki
Har baba maigadi yace" lafiya kuwa? "
Ahmad baice komai ba yajuya ciki, walaya tasaki labulan data rike ahannunta jikinta yana rawa ta tsaya Ajikin window
Kawai shawara ta yanke tahada kayanta tabar gidan, saide kafin ta juya taji taku abayanta, yanayin dayaganta shiya tabbatar masa dacewa itace ta aikata masa wannan aikin kai tsaye yace Mata "zo"
Moper hannun ta tayar Garin sauri kafarta tana hardewa ta tuntsirar da ruwan da take moping din, tabishi abaya har part dinsa
Bakin gado ya zauna itama ta zauna aqasa kanta asunkuye
Ahmad yace "menamiki kika cutar Dani walaya?"
Walaya shiru ba amsa
Yasake tambayarta cikin tsawa "nace uban Mena miki kika cutar Dani?
Kudi ko?
Nawa aka baki kika zabi ki lalatamin rayuwa?"
Walaya cikin kuka tace" Dan Allah kayi hakuri, wallahi bazan sake ba "

Dauuu kakeji ahmad ya wanke ta mari, kafin ta dago yaqara Mata wani,
Idanunsa sunyi jajir yace" uban waye yasaki, "
cikin kuka tace" wallahi wani ne nima bansan Shiba, kawai cewa yayi na temaki shi, "ahmad yace" owk shine kuma kika temakeshi kuka hadu kuka cutar Dani
Nayi DANA SANIN zaman ki agidan nan walaya,
Bazaki fadamin waye ba,? "
Cikin kuka tace" wallahi bansan Shiba, "

belt dinsa yacire yafara dukanta dashi
Ganin yana neman illatata ne yasa tace" ga wayar danake magana dashi, "

karbar wayar yayi ya dokata da qasa
Nan take ta tarwatse
Ihun ceto walaya take nema, Amma ahmad ko ajikinsa, su momy ne da mamy sukaji kamar ihu ake agidan, aikuwa dukansu suka futo afalo suka hadu momy tace" me yake faruwa ne," bukhari ne yace" a bangaren yaya ne," aikuwa suka tafi Gaba dayansu
Zuwansu yayi daidai da Suman walaya, salati momy tafara tana tafa hannaye" anya kuwa ahmad kanka daya?" Jin sunan data kira shi shiya tabbatar masa da cewa ranta yabaci, kuka yafashe dashi yace" momy wallahi Yau ko ni ko wannan yarinyar," momy kawai saita fara hawaye, wannan wacce irin masifa ce ace danka kuma ma babba mai hankali yakama mace yana duka, hawayan idan ta ta goge tace" shikkenan gatanan kakashe ta ahmad "
tajuya tayi waje, suma yan biyu ganin tana kuka abinda basu taba ganiba sai suma suka fara,

sukabi bayanta, mamy hakima tace" my son me yayi zafi hakane?"
Ahmad cikin kuka yace" mamy wannan yarinyar ta cutar Dani, Allah ya'isa tsakanina dake walaya," mamy bata kula shi ba, taje ta debo ruwa a fridge ta shafawa walaya, nan take tafarka, ai tana ganin ahmad ta tashi Zata gudu, yace" basai kin gudu ba, "

janyo ta yayi kamar kayan wanki, yayi waje da ita, mamy tana" ina zaka kaita? Ahmad dakai nake fa,"
Amma ko juyowa baiyi ba, haka yajata har compound din gidan yayi wulli da ita, kowa kallansa yake yana ganin ikon Allah, shigowarsa gidan kenan saura kadan yabi ta kanta da mota, da sauri yafuto yana gyara malun malun din dake jikinsa,😃 a daidai lokacin ahmad yana nunata da hannu "karna qara ganin kafarki agidan nan, ko ahanya karki nuna kinsanni, fice ki barmana gida mayaudariya, azzaluma,"

"saboda gidan Kane? To Babu inda zataje" inji daddy daya tsaya yana ganin wannan karfin Hali Danme zaka kama yar mutane kayi da duka kowa yanajin kukan ta agari, irin tarbiyar danama kenan? "
Ahmad cikin share hawaye kawai yajuya Yakoma part dinsa, daddy yajuyo da nufin ya yiwa walaya magana Takoma ciki, saiyaga wayam ba ita ba alamar ta, maigadi ne kawai yaga fitar ta, shikuma yasan maigida yanada gaskya shiyasa yabarta tafi ce, inba neman magana ba ina ita ina shiga bangarensa?
Daddy ne yayi ciki, suma su saudat dasu mamy suka bishi abaya

Momy suka gani afalo tana zaune yan biyu suna gefenta, daddy ya zauna yana cewa "meyasa mu wannan yaron?"
Momy tace "aida ka barshi ya kasheta, shima sai akashe shi,"

"haba hajiya wai meyasa kike hakane?"
Inji mamy

daddy ne yace" ke mabaruka kiramin shi "

Part din taje, yana zaune agefen gado yarike kansa da hannu biyu "
Tace yaya Dan Allah kayi hkr, kabarwa Allah komai," dagowa yayi yaga mabaruka ce, cikin tsawa yace" ke tashi ki fita, "

Tace" to daddy yace kazo,"

wuf tayi waje tun kafin itama yahada da ita

Tashi yayi yaje, duk suna falon, ya zauna aqasa idonsa jajir, daddy yace." ina jinka metayima? "

Ahmad shiru, aransa yace Tome zance musu magani tasamin nasha naje nayi wa yar mutane

fyade?
Kansa ya girgiza yace" ba komai daddy, "
Daddy yace" au haka kace toshkn, tashi kaje kahada yanaka yanaka katafi Cairo, da tafiyar ka jibi ne Tona fasa, kaje kahada kayanka katafi yanzu, banasan tashin hankali "

Auta ce tafashe da kuka tafara birgima" Allah daddy a a, nide bazai tafi ba"mamy hakima tace" maryam kin rufe min baki kosaina bigeki anan?" Momy tace" kyaleta mana hakima, haba yarinya cefa "

Saudat ce ta dauki maryam tana rarrashinta sukayi sama, suma sauran yaran mabaruka da twins suka bisu,
Mamy hakima cikin sigar rarrashi tace" my son kayi hkr kayi mana bayani menene tayima? "
Ahmad kansa aqasa yace" mamy Babu komai "
Momy kuwa dama bata tambaye Shiba, yaje can yaqara ta

" Tashi katafi, Allah yakiyaye, zanyi waya yanzu anemama ticket na kowanne jirgi ne inde zaije masar, ka gaida abi, Allah yatsare," inji daddy

Ahmad baice komai ba, yatashi yayi part dinsa, kayansa yadauka kala uku, sai su singlet, yadau trolly dinsa Babu wanda ya yiwa sallama agidan yatafi "mad'aar" (Airport)
To dama zaman me zaiyi aqasar ma, feenah taqi tsaya wa yayi Mata bayani, iyayensa sunajin haushinsa, gara ma Yabar qasar ya huta

** *** **

Yadade yana faman kiranta Amma wayar akashe, Amma Yau cikin sa'ah sai gashi ta shiga, yana zaune afalo baidade da dawowa daga hospital ba, yana tsiyaya ruwa a glass cup yaji ta daga

"Amincin Allah yatabbata agareki, ma'abociyar nutsuwa da kamala"

Sake duba wayar tayi, anya kuwa da ita yake? Itade tasan batada biye biyen samari balle tace

Husna tace "pls wake magana?"

"Kina tare da doctor tahir"

Tace "doctor tahir kuma?"

"Yes wanda yayi muku lecture kwanaki harna hanaki shiga" 🤣

Husna ta zaro ido tace" Dan Allah kayi hkr, wallahi bansan kai bane "
Murmushi yasaki yace" no karki damu, dama zan gaisheki ne kuma nabaki hakuri Akan abinda nayi miki "🤣

Husna tace" Babu komai na gode "

Yace" cewa zakiyi nayafema, "

husna da mamaki yagama cikata tace" to komai ya wuce "

Yace"good girl, dama inasan tambayrki,"

husna tace "ina jinka" yace "kina sona?"

Husna cikin kaduwa da kalamansa tace "so kuma?"

Yace, "nasan bakya sona husna, Amma ina neman alfarma awajanki Dan Allah ki aure ni, wallahi nakasa samun nutsuwa tun lokacin dana fara dora idanuna akanki, zan baki lokaci kamar kwana biyu kiyi tunani zan sake kiranki inji me kika yanke game Dani"
diff ya kashe wayar Yabar husna da waya akunne kamar photo

** *** **

Text ne yashigo wayarsa, yana dubawa yaga company dayayi apply sun daukeshi aiki, cikin murna yafuto yazo zai fadawa yayansa wannan labarin
Yana Zuwa falon yaga yana shiri yace" yaya lafiya naga kana shiri cikin sauri haka? "
Abba yace" hassan yayarka ce batajin dadi inaso nakaita asbiti ne,koda yaushe jikin nata ba dadi, "

" husna! Husna!! "

" Na'am Abba gani nan,"

Ammu ne yace" to yaya kawo key din saina kaiku Gaba daya, "
Babu musu Abba yabashi key din motar suka tafi asbiti dukansu
Gwajin farko doctor ya shaida musu mama tanada jaririn ciki na wata daya

Da murna suka dawo gida bakin kowa yaqi rufuwa, anan kuma Ammu yasake fada musu labarin samun aikinsa awani company mota sabo da aka Bude a kano, ance ma wani balarabe ne ya budewa jikansa, haka sukai ta farin ciki ranar

** *** **

After 2 weeks, hannayensu sarke cikin na Juna, saudat na kuka feenah na kuka, saudat tace "yanzu feenah mun rabu kenan," feenah tace" haba saudat meyasa kike wannan mgnr, "saudat tace" Toshiknn yaushe zaki tafi zaria?"

Feenah tace" eto sai nanda 3days, "

saudat tace"ki qara sati daya kafin nan yaya yadawo daga masar, kakanmu yarikeshi yace sai yayi sati uku kafin nan yahuta zai dawo," feenah saita nunawa saudat tasan komai tace" ai zaizo zaria," saudat tace" nasani duk da haka
Gashi zabe yana matsowa, "

feenah tace" to menene? "
Saudat ta kalleta da mamaki tace" wai kina nufin bakisan babanmu Dan siyasa bane?" Girgiza kai feenah tayi gabanta yana ci Gaba da faduwa, saudat tace" kiyi hakuri laifi nane daban sanar dakeba babanmu sanata ne, nasan kema da a kano kike dole zakisan yan siyasar Garin, yanzu kuma suna neman takarar deputy governor, "
hawaye feenah ta share tace" to Allah ya tabbatar da alkhairi sister", saudat rungume ta tana kukan rabuwarsu, yayinda feenah take kukan bakin cikin abinda ahmad yayi Mata, haka suka rabu

Tana cikin adaidaita tana goge hawaye, inda tasan ahmad Dan gidan Dan siyasa ne da bata saurareshiba, domin kuwa tasan yafi karfin ta, yagama cutar ta yatafi wata qasa wai yana hutawa hawayen idonta ta goge aranta tace nayi DANA SANI ni nafisa

Mrs Usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

23

Tahir yace "haba ahmad, meyasa kake neman sauya halinka ne? Bahaka nasan ka ba ahmad, pls kadauki kaddara mai kyau ko marar kyau wannan shine abinda manzonmu yace"

shiru kawai ahmad yayi
Saida tahir ya tabbatar yabashi kulawar data dace sannan yadauki lemon yatafi gida
Tashin motar sa ne ya farkar da mamy hakima daga bacci, Amma sai tayi zatan ko ahmad ne yadawo, tayi juyi taci Gaba da bacci

** *** **

Awannan daren ahmad bai runtsa ba, kawai hango kanshi yake yana Dakar wanda yayi masa wannan aikin, sai gab da a suba sannan bacci ya daukeshi gamida zazzabi mai zafi, hakance ta faru awajan tahir ma, dakyar yasamu baccin ya daukeshi

** *** **

Karfe 6:48 natashi, kafafuna na ziro kasa, ba laifi jikin nawa da sauqi, banajin komai saide abinda baza'a rasaba, falo na futo anan naga kaka tana lazimi, tace" sannu nafi, da naga bakya

Jin dadi shiyasa ban tashekiba, "

nace" aikuwa kaka yanzu ma baccin bai isheni ba,"

tace" sannu, aide da sauqi ko? "

Nace" kaka da sauqi sosai ai jiyan an yimin allura nasan shiyasa naji dama dama, "

tace" to sannu, Allah yasawaqe "

nace" amin, "

nayi "hammam" (toilet)
Bayan na idar da sallah awajan bacci yaqara fizgata dakyar de natashi nakoma gado, naci Gaba da bacci, saide har yanzu bandaina Jin wani Abu a maqogaro naba, hakan kuma baya rasa nasaba da bala'in dana shiga jiya

** *** **

Da break suna zaune kowa yanacin abincin sa, shiru shiru suna neman tashi basuga ahmad ba, mamy hakima tace "nifa banga Dan gidanaba, kode har yanzu murnar company din ce, jiya ma ina bacci naji shigowar motarsa,"

auta maryam datasa indomie dinta agaba tanaci tadago tace

"laaa ai yaya tahir ne yatafi, ba yaya ne ba,"

kowa yajuyo yazuba Mata ido cikin mamaki,
Tace" nima jiya inata jiran yaya yazo naga baizo ba shine naqi bacci, saida naganshi shida yaya tahir, wai yayama ba shida lafiya "

Momy ce tace" auta"
cikin mamaki
Mabaruka da basa ga maciji tace "kuma Dan iskanci kiyiwa mutane magana shine zaki zauna kina ma cin abinci ko Ajikin ki?"
Cikin shagwaba maryam tace" to ina ruwanki, Momy kin ganta ko," tafada tana kallan momyn ahmad,

Momy tace" yi shiru auta, kyaleta keda yaya ai mutu ka raba"

mabaruka harara ta zabga Mata ta tashi tayi part din ahmad,
Akan gado ta ganshi ya takure kansa yana bacci, qarasawa tayi ta yayeshi, wani zafi ya bugota, tace " subhanallah, yaya, yaya,"
dakyar ya Bude idonsa tace" ashe bakada lafiya, sannu,"
gyada kansa yayi kawai
Ruwa ta hada masa na wanka mai sauqin zafi, tatashe shi yaje yayi wanka, yana shiga wankan ta gyara Dakin sannan tafita

Komawa tayi ta sanar dasu halin da ake ciki, aikuwa dukansu suka diba yuuuu suka tafi ganinsa, ita kuma taci Gaba da cin abincin ta

Yana zaune Akan gado harya futo, suka zo suka zagayeshi, idan kagansu anan ne zaka tabbatar gidan akwai kwanciyar hankali da hadin kai
Saudat, Muslim, bukhari, Momy, mamy hakima, yayinda auta ta dane jikinsa, bata damu da zafin da jikin nasa yake yiba
Momy ce tace "waladeey ya jikin Naka? Meyasa bazaka kira waya kasanar mana ba?"

"Momy ai ban kwanta da zazzabin ba, kuma yanzu ma da sauqi,"
mamy hakima tace" sannu my son, "

Yace" yauwa mamy,"

" bani wayarka, "

dauka yayi yabata, ta Nemo number tahir
Yana dagawa yace" ahmad ya jikin Naka?"

Mamy hakima tace" pls tahir, zoka duba shi yanadan Jin zazzabi kadan, "

doctor tahir yace" to mamy gani nan insha Allah,"

takashe wayar

Mabaruka ce tadawo Dakin cikin shirin school tace to saiku tashi mu tafi ai, bukhari da Muslim ne suka tashi, auta ko motsi batayiba, Muslim yace" toki tashi mana,"
tace" nide bazaniba tunda yaya ba shida lafiya, "

saudat ce tace" a a auta, karma ki fara wannan rikicin danba me bullewa bane, oya tashi, "

aikuwa yarinya tafashe da kuka, ahmad ne yace " auta naji sauqi fa, idan kika dawo zamuyi wasa da jirgi da mota, "tace" to yaya Amma saide in Zata goyeni," saudat tace" wa zai goyeki

yarinya, garama ki warke," maryam tace" Allah saikin goyani," ba yanda saudat ta iya haka ta goyeta saida ta kaita har mota sannan tajuyo

** *** **

" Salamu Alaikum,"

" wa'alaikumus Salam, "

" a a adamu kaine agidan namu Yau, "

" eh wlh nine mama, yagida, "

" lafiya kalau adamu, ya su aisha mutanan Uganda,"

"wallahi aisha tana can karatu yafara nisa,"

"to Allah ya temaka,"

"amin mama,"
Daga murya tayi tace" nafi, nafi, "

" Na'am kaka, gani nan,"

" zoki karbo wa adamu ruwa yi sauri, "

futo wa nayi da hijabi a hannu na, nace" baba ina wuni "
yace" lafiya kalau nafeesa ya karatu,"

" alhmdlh baba jibi ma zamu fara jarabawar karshe, "

" to Allah ya temaka,"
" amin baba "

Kaka tace" yi sauri mana nafi, "

" Ka ganta nan batajin dadi ne kwana biyu, "
baba adamu yace" kaiya, haba mama aida kin kyaleta, dawo ki zauna nafeesa Allah yasawaqe"

" amin baba,"

nakoma daki
Baba adamu yace "mama dama munyi magana da baban husna ne, Akan zamanki agidan nan, da yace kikoma can zaria kokuma ki dawo gida na da zama, muna so zamuyi wa gidan naki gyara,"

Kaka tace "gyara kuma adamu me yasamu gidan nawa,"
baba adamu yace "mama ai muna so ne a maida miki shi na zamani"
Kaka ta fashe da kuka tace "adamu Allah yasaka muku da alkhairi, na gode na gode adamu, shima mu'azun zanyi masa godiya,"

baba adamu yace "haba mama ai mun daukeki tamkar mahaifiyar mu, Babu komai," tace "to ngd kawai zan dawo gidan Naka, basai naje zaria ba," yace "to nima hakan Naso dama, to Dan inji ra'ayinki shiyasa nabaki zabi," haka
kaka ta dinga godiya ga surukan nata, mutanan kwarai

** *** **

Gumi ne yagama wanke masa fuska ganin irin illar da maganin yake dashi, sosai ansa maganin dayawa acikin just din, kuma ko waye yayi hakan da mugunta, domin kuwa Babu marar imanin dazai aika ta haka, dama yasan wannan al'amarin akwai sa hannun wani aciki, sannan bayan haka qwayar tanada hatsari sosai, Amma bazai tabbatar da shin ahmad din yasamu abinda yake tunanin ba, saide idan yayi aure ne zai tabbatar, zubar da lemon yayi, Yabar asbitin yayi gidansu ahmad din

** *** **

Duk suna zaune inda suke da, saide saudat da hand out ahannunta tana dubawa, tahir yayi sallama yashigo, shi kanshi sun bashi tausayi, gaskya suna kaunar ahmad dayawa, wai nan zazzabi ma kenan an zauna anyi jugum inaga sun San gaskiyar abinda yafaru kuma.

Abinci yagama ci dama, Dan haka yabashi magunguna da qarin ruwa,sannan su Momy suka fita suka barshi ya huta,
Ahmad ya kalli tahir yace" kai Malam nifa na warke kawai idan na tuna abinda yafaru ne banajin duniyar tanamin dadi "

Tahir yace" dole kacire abin nan aranka, kar hawan jini ya kamaka,"

ahmad yace" hakane insha Allah zan kiyaye dahiru, "

harararsa tahir yayi
Ahmad yace" toba dahirun bane, dahirun ummi "
Tahir kallansa yayi, yana murmushi yace" nawan har naji dadi wallahi daka warware "
Ahmad yace" toya zanyi tahir Allah yadoramin abinda dole saide inyi hakuri in karbi kaddarata, Amma kuma fa yarinyar tayi, tayi, ba karya akwai zaqi, 🙈wallahi tana kukan nan banma San me take fadaba, "

tahir ne yakai masa duka, yace" Allah mutumina,"

ahmad yana murmushi gamida hawaye yace" serious tahir, gaskya yanayin akwai dadi "

Tahir yace" muma de zamu dage mu yi auren muji yaya akeji, "

ahmad yace" gaskya kam, nima zan nemi yafiyar nafeesa ne kawai inta amince ayi mana auren mu, "

tahir yace" why not"

Ahmad yace "yauwa ya mgnr abin nan,"
anan tahir yafada masa komai ahmad yace" acikin gidan nan ina zaune ake wannan qulla qullar lalle kuwa zan bincika, akwai rikici "

Tahir yace" kaide kabi komai a sannu insha Allah komai zai warware, "

" Hakane, "
inji ahmad

" Yawwaa Tahir ya maganar babyn ka din nan, dakake tunani, "

Tahir yace" ina tunani ahmad kana jinya, so nake ka warke saina kirata infada Mata "

Ahmad yace" no kakira ta Yau inka koma gida, ka tsarata sosai yanda bazata qi amincewa ba,"

" Toshiknn" inji Tahir

Ahmad wayarsa ya janyo gabansa na faduwa, yayi dialing number feenah, gara yakirata inma zaginsa zatayi kawai tayi inzata huce
Saide kuma wayar akashe, dole saide idan ruwan yakare yaje ya nemeta agida, Allah sarki rayuwa su kuma haka tasu kaddarar take
Wayar ya cillar gefe, Tahir yayi masa allurar bacci yace yakamata ya huta, shikuma yakoma bakin aikinsa

Saudat ce tanata shiri Zata je wajan feenah, tunda batazo Dan ziyara ba aitazo Dan jinyar yaya, Momy ce tashigo Dakin tace "kekuma ina zaki,"

saudat tace "Momy nayi ta Kiran wayar sister feenah ne, inasan magana da ita Amma wayar akashe shine nakeso inje inga ko lafiya,"

Momy tace "saudat rigima, banda abinki ai jibi zaku shiga exam
Dole zaku hadu, kiyi hakuri nasan insha Allah tana lafiya, kiyi karatu dakyau, idan Baku haduba Zuwa jibin daga school dinma saiki wuce, Amma yanzu de kije ki kula da brother dinki,"

"Toshiknn Momy"

** *** **

Bayan kwana biyu ahmad ya warke sosai, saide Gaba day ba shida walwala, Gaba dayansa ya canja, shiru shiru Babu magana, yayinda feenah sun Dade da fara exam, inda tabawa saudat uzurin cewa batada lafiya ne, shiyasa kuma ga exam agabansu ta karshe shiyasa ta kashe Wayarta, haka saudat ta hakura badan ranta ya soba, a bangaren feenah kuwa ita kanta saudat din haushinta takeji 🙊🤣

Ahmad yashiga Hali na wahala kullum cikin tunani ga tafiyarsa Cairo na matsowa ga shi yana so ya gyara tsakanin sa da feenah, Amma taqi bashi damar hakan
Kullum saiyaje kofar gidansu, haka kullum sai ance masa bata nan, kaka tayi tambayar duniya Akan su waye suke kiranta tace kawai samarin unguwa ne, wanda ita feenah tasan ahmad ne, Akwai lokacin da kaka tace Mata taje ta duba ko yayan saudat ne, Amma qememe feenah tace ai suna waya dashi bashi bane haka kaka ta hakura

** *** **

Gidan yashigo ransa abace yayi part din Momy tadaga kai ta kalleshi tace "waladeey lafiya kuwa?"
Yace "Momy lokacin danayi rashin lafiyar nan waye yashiga part dinane?" Tace "gaskya Babu, kasan saudat tana karatun exam so bata shiga mabaruka kuma kasan dama akwai kasala saudat tafi ta gyaran, bana tunanin tashiga,"

"OK" kawai yace yatashi yafuta fuuuu
Momy tabishi da kallan mamaki, tome aka masa?

Main falo yadawo yana kwalawa walaya kira," walaya!  Walaya!! Walaya!!!"
Yasan cewa tana aiki afalo sosai may be zatasan wayashiga

Kai tsaye yace "Mata wakika ga yashiga part dina kwanaki acikin yaran gidan nan?"
Lokaci daya ta firgita da Jin furucin sa, har ahmad yaso yayi tunanin wani Abu, cikin duburcewa tace "wal..... Walla... Wallahi bansaniba ba," baice komai ba yajuya yayi wajan baba maigadi, ai walaya tana ganin yatafi wajan baba maigadi damm gabanta yayi wani irin faduwa, nan take ta dora hannun ta aka 🙆🏻

Mrs Usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

25

Tana shiga gida Dakin ta ta wuce ta dinga kuka, Bama wannan ne abin damuwar ba, yanda takasa cireshi acikin ranta, gaskiya so masifa ne, ta tabbata yanzu shi yana cikin kwanciyar hankali, kaka ce take Jin sauti kamar na kuka, ta futo, tana daga labulan Dakin tace "ah nafi ashe kin dawo, menene kuma abin kuka?
Dama rabuwa da abokai ai tazama dole, nima haka zaki tafi ki barni nafi nasaba dake agidan nan" kaka takarashe maganar tana kuka
Haka suka rungume Juna suna kuka itada kaka Babu mai rarrashin wani

Kwanana uku a kano, nayi shirin tafiya zaria, banajin kuma zan qara waiwaitar wannan Garin, danma na taya kaka hada kayanta dazata koma gidansu aysha

** *** **

"Husna najima ina bin kanki Akan ki bani dama na shiga cikin zuciyarki, Amma hakan yaqi samuwa ko?"
Husna tace "bahaka bane doctor kawai nayi tunani ne" yace "to me tunanin naki yabaki?"

Tace "nabaka"
Tahir yace "mefa?"
Tace "zuciyata" dif taka she wayar
Wayarsa yarike ahannunsa yana murmushi shi kadai

** *** **

"Wlh khadijaty haka mukai dashi,"

khadija tace "gaskya mutumin nan ya yanke mu, ashe dama yana ciki shine yake ta wani cin magani," husna tace" aini abin yabani mamaki da farko, Amma bakiji yanda yake min magiya ba

Akan na aure shi," khadijaty tace" wlh ki amince, "
nace" ai nafada masa na amince, "daria suka saki Gaba dayansu suka tafa

** *** **

Aguje nafada kan mama ina mamaaaa! Da karfi, kai ta dafe tace" auta bansan yaushe zakiyi hankali ba, "

baki naturo nace" kai nayi missing dinku fa," tace" to dagani banajin dadi, "

tashi nayi nahau cire kayana agabanta
Tace" wai nikam haka kikewa maman ma acan kano din? "
Nace" kai mama ai kaka Babu ruwanta Dani, abinda nakeso nake yi wlh, bana aiki sosai, "
tace" to shige daki ki shirya "

Nace" wai sister bata dawo ba har yanzu," mama tace" ai sai wajan yamma,"

jakata naja nayi daki, bayan nagama shiryawa nayi wanka na futo falo na kwanta Akan kujera nadora kaina Akan cinyar mama

Tace" to ya karatun"

" nace wlh mama karatu mun barshi sai jiran results dinmu kuma,"
tace "to Allah yasa a dace" nace "amin"

Mungama cin abinci kenan husna ta dawo aikuwa da ihun murna muka dane Juna, mama kawai kallanmu take tace" Allah ya shiryeku," aifa nan aka baje sabuwar hira, ina bata labari tana bani anan take fadamin labarin ta da doctor tahir, nace" wlh ki amince" tace "ai na yarda muna gaisawa de kadan kadan, ta waya," nace "to sister nunamin pic dinsa" tace "bai turomin ba saboda Bama chting Amma zanyi mai magana ya turomin saina tura miki," nace "to"

** *** **

"Guy kaje ka zauna, please ka dawo mana,"

ahmad yace "wlh wannan tsohon ne yarikeni tahir, Amma jibi zan dawo,"
Doctor tahir yace "yauwa kokaifa, munyi missing Naka," ahmad yace "wlh nima haka, ga kuma feenah datake raina inaso inzo in bata hakuri Akan abinda yafaru"
Tahir yace "eh gaskya ne nima maje Gaba dayanmu in tayaka bata hakuri," ahmad yace. "Amma naji dadi sosai nawan," tahir yace "karka damu,"

"Friend ya maganar babynka ne?"
Murmushi tahir yayi yace" husna, tana nan acikin zuciyata, dazu muka Gama waya," ahmad yace" harka gyaro ta kenan, "suka sa daria Gaba dayansu, ahmad ne ya kwaikwayi maganar tahir yace"
Ahmad iklima, iklima tabarni ahmad wlh ina sonki iklima, "🤣 katse wayar tahir yayi

** *** **

" Mamana, "

" na'am daddy, "

" nasan ke mai biyayya ce, kuma nasan duk abinda zan fada miki bazaki qi yimin biyayya ba,"

tace" hakane daddy,"

" to munyi magana da Dan abokina, muna so mu hadaku aure nanda 3 months,"

gaban saudat ne yafadi cikin rawar murya tace" to daddy,". yace " yauwa, Allah ya miki albarka Zaizo ku daidai ta sunansa farouq, "

" to daddy nagode,"

yace" tashi ki tafi "

Daki Takoma ta dinga kuka, Wayarta ta janyo ta kira feenah saide wayar akashe, tun lokacin da abin nan yafaru kwata kwata ma wayar tafita daga ranta
Momy ce ta shigo tace " sauda, haba kiyi hakuri mana, idan yazo inbai miki ba kawai kiyi rejecting dinsa ni sai nayiwa daddynku bayani, a hankali, shi dama abinda yake so shine ayi bikin kafin su fara zabe,"

"to Momy nagode,"
tafada jikinta tana kuka

** *** ***

One month later
"Feenah, feenah, tashi kiyi sallah mana,"

"kai anty husna ke akwai damu,"

nayi juyi naci Gaba da bacci na, kyaleni tayi taje tayi alwala tayi sallah, da taga de banda niyyar tashi, ta dakamin duka, na tashi ina goge idona, tace "ke miye haka, tun dazu ina tashin ki sallah sai wani magagin bacci kike min,"

baki naturo Gaba, na tashi nayi toilet

Bayan sati daya, su husna sun Gama school, haka soyaiyar su da doctor sai abinda yaqaru koda yaushe suna cikin waya, suna kaunar junansu sosai harma da alkawarin aure atsakani

** *** **

Farouq yazo yaga saudat, baida matsala, haka kuma yanada hakuri, hakanne ma yasa ta amince, yana zaune a Abuja, Dan haka aka ci Gaba da shirin biki, ya rage saura 2 month's

** *** **

Yayi zurfi cikin tunanin mafita, Gaba daya bayajin dadin wannan aikin dama Garin baki daya, yaje yaje yaje harba adadi, karshe ma ance masa kaka tabar gidan, wayar feenah akashe tun lokacin da wannan matsalar tafaru, Gaba daya yadawo wani shiru shiru

Saudat ce tafado masa arai,
Daga murya yayi yana kiranta, ta futo "
Yaya gani,"

wayarsa ya miqa Mata, tace "yaya bangane ba,"
Yace "sakamin Num feenah, kokuma number da kikasan zan same ta idan naje zaria"

Saudat tace "wallahi yaya bansaniba,"

mamaki shinfide kan fuskar sa yace "bangane ba, kamarya baki sani ba?"
Tace "wlh yaya nima kaina nema nake,"
yace "toko zamuje zaria din mu dubata,"

saudat tace "yaya to zaria ina?
Ina zamu nufa? Sannan ko jiya nadau mota naje gidan kaka an tabbatar min tariga da tatashi agidan, ni maganar bikinama nakeso nasanar Mata,"

alama yamata da hannu Akan tatafi, karta qara masa wata damuwar 😃

** *** **

"Mama ga maganin naki fa da doctor yabayar nasan baki shaba,"

"wlh husna banasan maganin qarin jinin nan banajin dadinsa,"
"to mama kiyi hakuri kisha,"

"to bani nasha, tashi kiramin autata tazo ta dora abinci,"

"yanzu mama saura 7 months ki haihu,Amma kina ce Mata auta,"

mama tace "husna gidanku, kunji yarinya ke har wani lissafi ma kike, tashi kiramin ita"

Daki tashiga zaton ta, karatun novel nake, Amma sai taga sabanin haka, bacci na nake shararawa haiqam, kallo na tayi da mamaki, aranta tace Tome yake damun yarinyar nan, tashi na tashiga yi, dakyar na tashi, ina tashi na shaqi qamshin turaren ta, aikuwa da gudu nayi toilet na dinga shara amai, husna tabini da kallo gabanta yana faduwa
Ina futowa tabini da kallo, nace "sister wannan turaren naki bana sansa, Dan Allah fita daga Dakin nan,"

husna tace "yar renin wayo dagani har ke dashi muke amfani kafin kitafi school......

Kafin tagama magana nasake yin toilet da gudu nayi wani aman, aikuwa ina futowa tajani, ta duba idona, takama hannu na, ta duba, cikin loka ta dauko pt strip, tace" jeki iyo min fitsari anan"

tabata wata roba, aikuwa ba musu feenah taje tayi, jikinta duk yayi sanyi, ta futo tabawa husna Jikin husna ne yadauki rawa ganin layi guda biyu Ajikin pt din, wato kenan abinda take tunani ne yake San tabbata, lokaci daya hawaye yasilalo daga idanunta tana hawaye tace "feenah"

Nakalleta da mamakin meyasa ta kuka, tasake cewa "feenah wayayi miki ciki?"

Kuka nafasa da karfi, nadora hannu na akaina, hakan yasanya mama dataji shiru daga kiramin auta itama tayo Dakin cikin sauri
Abinda kunnuwanta suka jiye Mata ne yahanata qarasawa Dakin

Mrs Usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

29

Ganin yaqi bata wayar yasa tasa hannu ta karba, "hello yata yagida?"
Husna cikin ladabi tace "mama ina wuni?"
Ummi cikin Jin dadi ta nemi wajan zama tace "alhmdlh ummin tahir ce"
Husna zare ido tayi tace "ummi ina yini ai ban ganekiba"

Ummi Ana murmushi a kace "a a ai ba komai yarinya, yaya sunan kine?"
Tace "husna"
Ummi tace "masha Allah, yaushe zakizo naganki?"

Husna tace "ai da nisa, saide wani lkcin idan munzo kano sai nazo"
Ummi tace "a a ba'a nan Garin kikeba?"
Husna tace "eh wlh muna zaria"
Ummi tace "Toshiknn yata Babu komai kinji, ki gaida ummanku,"

"to Ummi na gode sai anjima,"
ta kashe wayar
Ummi tajuyo ta miqawa tahir wayarsa wanda yazuba Mata idanu yana kallanta kamar tv

Tace "ita kuma wannan fa?"
Tahir yayi qasa da kansa yace "Ummi dalibata ce"
Ummi tace "um aikam nagani, yanzu ma ai naga karatu kuke, idan kun Gama karatun ne zaku samu yan biyun" 🤣

Tahir yace cikin shagwaba "kai Ummi nifa bance haka ba"
Ummi cikin Jin dadi tace "to koma de menene ka shirya kuje ku gana, idan da Hali ma ayi komai agama cikin wata daya," zaro ido yayi yana kallanta, tace" to menene?
Bakasan yanda na matsu kayi aure bane tahir shiyasa, kai kadai gareni
Banda kowa, mahaifinka ya rasu, koso kake nima in mutu banga auren kaba? "
Cikin sauri tahir ya girgiza kansa yace" a a Ummi insha Allah zanje cikin satin nan "
Ummi ta shafa kansa tace" yauwa Dan autana "

** *** **

After 3days
12:6 suna manne da Juna awaya, ba abinda yake Mata sai aikin shagwaba, husna tace" wai nikam doctor bakada qanne ne? "
Tahir yayi murmushi yace" banda qanne banda yaiyu, ni kadai Ummi ta haifa, kafin daga baya Allah yadauki ran mahaifina, itace ta tsaya wajan kula da komai nasa har na mallaki hankalin kaina, har Zuwa yanzu "

Husna tace " Allah sarki shiyasa "🤣

Tahir yace"shiyasa me?"
Tace "shiyasa kake shagwaba,"

daria tabawa tahir, yace "yanzu ahakan inada shagwaba?"
Tace "sosai ma,"
yace "lalle Dan bakiga dan'uwana bane,"
tace "waye hakan?"
Yace "aminina ahmad, shi agidansu shine babba, Amma idan ya kwaba miki wani abin, saiki dauka shine auta"
Husna tayi daria tace " lalle, nima kuwa Dan bakasan autar mama bane, Babu abinda tabari, Amma ganin batada qani ne shiyasa,
Kai karshe ma rikicin ta ne yasa Ammu yace akaita boarding, kwata kwata bataji"
Tahir yace "um kaji manya wato ke babba ko?"
Husna tace "bakasan rikicin yarinyar nan bane, idan na share ta saita rainani"
Tahir yace "um kaji manya," husna cikin shagwaba tace "Allah my one zan kashe," cikin sauri yace "no yi hakuri nadai na, shikkenan?
Yanzu fadamin yaushe zanzo?"
Tace "duk lkcin daka samu dama," yace "toshkn zaki ganni jibi insha Allah" tace "to Allah yakaimu"
Yace" to yanzu fadamin abinda zanji dadi indinga tunashi har inyi bacci "
Husna tace" to rufe idonka"

** *** **

Yayi neman number ta harya gaji
Gaba daya yarasa me yake masa dadi
Daga karshe ya saduda yamiqa lamuransa ga Allah, yasan Babu wani bawa da zai kaucewa qaddararsa, abinda yasa aransa dayane shine kawai shida qara kula wata mace da sunan soyaiya har abada
Itama azal ce ta fada masa harya furta Mata kauna, Dan tunda yake shide ba ma'abocin kula Mata bane, saide ma su soshi, zai sawa ransa dangana, yayi addu'ah Allah yakawo masa karshan wannan matsala

Gaba daya yazama shiru shiru, dama yaya aka qare
Kamar kullum yauma yana kwance adakinsa yazuba wa P. O. P din Dakin ido
Tayi sallama ta shigo, tashi yayi zaune yace" momy kece? "

Tace" waladeey, menene yake damunka? "
Ahmad yace" Babu komai momy kawai aiyukane sukai yawa"
Tace "Ahmad bakada wata mahaifiya bayan ni, bansan meyasa kake San boyemin damuwarka ba, ko kanaga kanada wadda tafini?"
Cikin sauri ya girgiza kansa, nanda nan idanunsa suka ciko

Momy janyo shi tayi jikinta ta dora kansa Akan cinyarta
Tace "yi hakuri to, menene abin kuka kuma, yi shiru kaji waladeey na"
Haka tayi ta rarrashinsa daga karshe tace yadaure yafada Mata abinda yake damunsa, tiryan tiryan yafada Mata budurwarsa ce tunda tagama karatu har Yau ya nemi number ta yarasa, kuma baisan gidansu ba,
Momy jikinta yayi sanyi tasan tunda ahmad yashiga damuwa Akan Abu to tabbas ya nasan abun sosai

Momy ta nisa tace" ahmad kayi hakuri mana, kamiqa lamuranka ga Allah insha Allah zakaga abinda zai biyo baya ka dinga addu'ah Allah yabaiyana mana ita "
Kasa magana yayi saide kawai ya daga kai alamun to

Kansa taci Gaba da shafawa har taji jikinsa yasaki alamun yayi bacci sannan ta gyara masa kwanciya ta fita

** *** **

Gaye kayi sauri fa, nasan halinka, ahmad cikin kasala yace" dallah Malam ni majima da shiryawa zakaje gidan surukai kamar zakaje wata qasa "

Tahir yace" eh naji, futo nazo kofar gidan zan daukeka "
Futowa yayi cikin baqin yadi da baqar hula yasa agogo shima baqi, da takalmi shima de baqin, kalar fatarsa saita qara futowa fara tas acikin kayan duk da yanada Dan duhu kadan, Amma mai karatu kaso kaga ahmad a wannan kayan

Su momy suna falo, yazo ya tsugunna har qasa ya gaida su, mamy hakima tace "dana duk wannan kwalliyar ta office dince?"
Shide kawai murmushi yayi ya miqe yace musu saina dawo

Momy kawai da ido ta bishi Dan tasan abinda yake damun Dan nata

Yana fita ya ganshi acikin motarsa fara, shiga yayi yace" muje, "tahir yace" abokina irin wannan kwalliya haka kamar kaine saurayin? "🤣
Wannan ai saikasa husnan ta dawo wajanka"

Ahmad yace "kaga Malam Dan Allah muje haba, sunyi nisa sosai wayar ahmad tadau qara, yana dubawa yaga hassan ne, ya daga can daya bangaren Ammu yace" masa" yallabai baqin turawannan sunzo, wanda kace idan sun zo ayima magana zaka gana dasu, ahmad yace" ya Salam wallahi na manta gani nan Zuwa," bayani ya yiwa tahir, badan yasoba haka yasaukeshi, ahmad ya leqo ta glass din motar yace saika dawo abokina dama ni wannan tafiyar wallahi

gabana faduwa yake," tahir kawai harara ya miqa masa yaja yatafi, daga baya ahmad yayi waya company su azo a daukeshi

** *** **

" Abban husna yaufa muna da baqi, "
Abba yace" waye zaizo ko mutanan kano? "
Mama tace" a a bakaga mutuniyarka ba tun safe takasa zama, ayi wannan lemo ayi wancan
Girki, Abba yace "me yake faruwa?"
Mama tafada masa komai yayi murmushi yace" to Allah yakawo su lafiya "

** *** **

Kasan cewar unguwar ba boyaiyiwa bace yasa tahir ya gane da wuri
Motsi kadan husna zatai saiya dubeta, duk ta takura da irin kallan dayake zuba Mata

Husna ta kai shi har cikin gida yagaida mama, inda Yabar kudi Akan kujerar kusa d mama yace "gashi asiyawa auta alawa"

Dasuka futo husna daria, tahir yace "menene?" Tace "autan fa kanmu daya da ita,"
d mamaki yace" haba?" Anan ta dinga bashi labarin feenah har yaji yanasan ganinta, suna tsaye Abba yadawo daga unguwa

Tambayoyi ya yiwa tahir Babu bata lokaci ya amsa, Abba ya yaba da hankalin sa, gudin kada azo ayi DANA SANI irin na nafeesa 🤣shiyasa Abba yace yabashi dama ya turo magabatansa ayi maganar bikinsu, duk wani bincike daya kamata ayi, zaiyi insha Allah

Bai barta haka ba saida yacika ta ta alawa da kuma less, sai takalmi da jaka su kayan kwalliya sannan yatafi yana mai farin ciki

** *** **

Kaka gaskiya nikam kwadon nan kiyi shi da yaji, "
" a a nafi banasan yaji,"

" gaskya kaka nito da yaji nakesan nawa, inyaso ke sai kiyi taci Salam, "

kaka ta kalleta da mamaki" , kyaci gidanku keda yajin, kina fama da kanki Amma kina wani neman yaji, "turo bakina nayi Gaba, na kyaleta, gashinan idan zakici kici, idan bazakici ba meqomin zogale na, kwadayaiya kawai," harararta nayi na shige daki, tace" kyaji dashi, da kanki zakizo ki dauka "

** *** **

Abba yayi duk wani bincike Akan tahir, sosai yaji dadin sakamakon daya samu akansa
Dan haka iyayensa suna Zuwa aka tsaida ranar aure nanda wata hudu

Feenah Babu wanda yakaita murna, Akan auren nan, har kaka tagaji dajinta tace" kai ni rabi'atu kamar akanku za'a fara aure, wannan kekam idan naki auren yatashi ba musan irin rashin kunyar da zakiyi ba, "
Nace" kaka kenan kinci naki zamanin nima saiki barni naci nawa, ke wayasan abinda kukayi a naku bikin keda Amadu "

Kaka aka murmusa a kace" Allah sarki Amadu, a nacan sai Hali sai sallah, Allah yaji qanka," nace" amin kaka, "

Can kuma tace" nikuwa nafi ina yaron nan Dan albarka? "
Nace" kaka wakike nufi?"
Tace" ah Amadu mana yayan saude, wazan tambayeki inba Shiba? "

Dif kakeji nafi ta dauke wuta

Mrs Usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

Ihu nasa da qarfi ina fadin "na shiga uku na, Abba Dan Allah kayafemin wallahi ba laifi na bane,"

mama ce tatashi tace. "gaskya alhaji Babu inda Zata, yaya baka tsaya kaji abinda yafaru ba zaka yanke hukunci cikin fishi,"

husna ganin iyayenta zasu fara samun sabani abinda basu taba ganiba tunda suke, nan itama takama kuka, tana rokon mahaifinsu Akan Dan Allah yayi hakuri
Abinda yabasu mamaki shine yanda shi kansa Abban su kaga yana hawaye

Mama ce tasauko tafara bashi hakuri, yace "to shikkenan tunda bazata barmin gidan ba ni bari in bar muku gidan"

Mama ce tayi sauri ta riko kafarsa, tace "Abban husna Dan girman Allah kayi hakuri,"

tana kuka tana bashi hakuri, tace "yanzu yaran nan su biyu garemu, meyasa kake so su fuskanci matsala arayuwarsu?
Karfa ka manta Amana ce Allah yabamu tasu"

Abba yace "haba me zaku fadamin, ina zaune agidan kunsan abinda yake faruwa Amma kukasa sanar Dani, to so kuke saita haihu sannan zaku sanar Dani?"

Mama tace "kayi hakuri alhaji munsan munyi laifi, Amma kayi hakuri ka fuskanci abinda zan sanar dakai

Mama bata boye masaba ta bashi labarin komai, idanunsa yayi jajir

Yadago yace" uwa ta kin tabbatar haka abin yake? "
Ina kuka nace" Allah Abba hakane, wallahi fyade yayimin, Allah bahalina bane hakan "
Yace" to shikkenan kuskure de anriga da anyi
Hakika kuma nayi DANA SANI Akan zuwanki kano ma baki daya
DANA SANI lokacin da yaron nan auwalu yanuna yana sanki dana baki shi kunje can kun qarata, nayi DANA SANI nafeesa, "

dago kai nayi ina kallansa Jin sunan daya kirani sunan mahaifiyarsa Amma tashin hankali yahanashi boyewa

Yace " uwa ta ki fadamin inkin San inda yake ko Dan uban waye inje in qwato miki hakkin ki,"

nace" Abba wallahi bansan inda yake ba,"
Wanda saida nafadi hakanne mamakin kaina yakama ni, meyasa ba zance Dan gidan sanata ne ba?

Yace " kinyi kuskure uwa ta, shikuma duk daren dadewa zaizo ya sameni, insha Allah sai yayi

DANA SANI"

** *** **

sun nutsu kowa yana cin abinci Amma Gaba daya hankalin sa bayama kan abincin

Mamy hakima tace "a a son, me yake damunkane, Gaba daya kamar bakai ba, kana juya spoon cikin abinci Amma kakasa ci,"

auta maryam ce tace " yauwa yaya dama kace zaka yi mana ankon anty sauda, kaga Yau ba school sai muje ma har wajan shan ice cream ko yaya"

Mabaruka ce ta kalleta tace " kekam bansan yaushe zakiyi hankali da tunani ba wallahi"

"To ina ruwan ki Dani, ko yayanki ne?" 🤣 Inji auta,

Banza tayi da ita, Dan tsaf Zata bige bakinta yanzu
Baice musu qala ba, yamike gamida ture abincin yayi daki
Gaba daya suka bashi da kallo

Mamy hakima ta cewa momy," hajiya nifa yaron nan akwai abinda yake damunsa nalura tun barin walaya gidan nan yake cikin tunani,"
momy tace "to ai sai yayi tayi," mamy hakima tace " a a,
Bazamuyi tayi ba"

ta tashi itama tabi bayansa

Dakin tashiga, sai ganinsa tayi acan karshan gado, yana sheshshekar kuka, da sauri ta qarasa tace "Ahmad
Meyake damunka?
Please sanar Dani mana kaji"

Hawaye yagoge yace " Babu komai mamy"

ita mamy abin yabata mamaki, Gaba daya yasauya yaron kamar bashi ba, hakuri ta bashi taqara kwantar masa da hankali, waya tayi wa saudat tace takawo masa ko indomie ce yaci, bayan takawo tafice, tasan matsalar bazata wuce ta feenah Ba, Dan tasan basa waya tunda Wayarta akashe, to inbanda abin yaya Dan karasa budurwa awaya menene abin kuka? 🤣

Lalle sister tayi sa'ar saurayi mai sonta

** *** **

After 3 month's

Abubuwa da dama sun faru ciki harda bikin saudat inda ta Lula Abuja itada mijin ta farouq

Takarda yabata, ta karba tace "to Abban husna takardar menene kuma wannan?"
Yace "Bude ki gani yana murmushi"
Tabude tace " kamar qarin girma nake gani alhaji"

Abba yace "hakane maman nafeesa, nasamu qarin girma, nasamu lecturing awata NCE"
Mama tace" kai alhmdlh, gaskya Allah abin godiya
Ina kuke?
Mama tafada da karfi"

da sauri muka futo Gaba daya muka taya Abba murna, Abba ya kalleni Baice komai ba ganin cikin dake jikina yana qara futowa, yace " to a tashi aje ayi wasa yaran Abba"
Gaba dayanmu mukasa dariya, mama tace "haba alhaji yaran sun girma sai aure kana zancan wasa?"
Abba yace "aini yanda nake ganinsu wallahi maman nafeesa banqi ace na siyo musu yar baby ba suyi wasansu," mama tace "eh lalle Abban husna, aikuwa dole ku rabu Kodan aure ma,"
Abba yace "hakane," mude haka mukai daki muna daria

** *** **

Yana kwance awata "hadiqa" (wajan shan iska)
Ya lumshe idonsa, Zuwa tayi kwanta ajikinsa, yana Jin qamshin turaren ta, ya tabbatar itace ta qara so, hannu yasa yana shafa gadon bayanta

Idanunsa a lumshe Yace "haba my feenah meyasa zaki gujeni?"

Dora kaina nayi akirjinsa, ina shafa sumar kansa nace "my ahmad ina tare dakai a koda

yaushe, kaima kasan bazan iya qinka ba, ahmad ina sanka,"
Bude idonsa yayi yayi tozali da kyakykyawar fuskarta, Dan lips dinta yasha pink din Jan baki, yayi kyau, tana magana ya Zuba Mata idanu, iska ta hura masa a fuska tace" haba hammad wannan kallanfa? "

Baice komai ba yahade bakinsu waje daya
Kokarin kwace wa take, dakyar de ta kwace tafara gudu yana binta sunata gudu suna dariya, tajuyo tayi masa gwalo" yeeee yakasa kamani"

Juya war da zatayi kawai ta afka cikin rami, da gudu yakaraso yace " my feeeeenahhhh!!!"

Azabure ya tashi daga baccin dayake, Gaba daya yahada wani uban gumi, Dakin ya kalla da esi da komai rigarsa ya cire Yabar best din ciki

Sumar kansa yashafa, ya kalli agogon dake ajiye a drowar gefen gadon karfe hudu na yamma, da sauri yatashi domin yagabatar da sallar la'asar

** *** **

"Yauwa maman nafeesa dama inaso zamuyi wata magana dake,"

"to Abban husna ina jinka"

"Munyi magana da Adamu akan maganar gidan mama, Toni shawarar dana bayar shine kawai asaida gidan ta nada mu siya Mata wani anan kusa da gidan adamun, toshi adamun yace minma akwai gidaje dayawa alayin zaije ya duba kawai sai asiya Takoma cikin satin nan, saboda can hotoron karya zama can din tana zaune ita kadai koda wata matsalar Zata tashi kinga kalatin tasu taje ta ganota"

Mama tace "eh hakanma yayi wallahi, Allah yasa hakanne yafi alkhairi, Allah kuma yaqara budawa," Abba yace "amin"

Yace "sai kuma magana ta biyu, Akan maganar uwata, nace saboda mutane masu shigowa meze hana Takoma can kano da zama gidan mama, kafin Allah yasauketa lafiya sai asan ya za'a yi, tunda kinga bazai iyu mu qara daukar wani zunubin ba wajan zubar da cikin kokuwa ya kikace "

Mama tace" gaskiya alhaji Babu abinda zamu ce dakai sai godia hakan ma yayi idan ta zauna anan muna tare ni na haihu itama ta haihu Babu dadi, "Abba yace" nima shine abinda nagani

Yanzu saiki fada Mata tahada kayanta Zuwa jibi saita tafi, nikuma zan kira maman nayi Mata bayanin komai, mama" tace "Toshiknn Abban husna Mungo de," yace
" da cikin wata nawane?" Mama tace " watansa biyar"
Abba yace "to Allah yaraba lafiya"
Mama tace " amin"

"Nafeesa!"

"Na'am mama"
"zo nan zamuyi magana dake"

Mrs Usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

26

Wani dumm takeji akanta, Gaba daya ganinta yake neman daukewa hakan ya haddasa Mata zama aqasa dabas
Cikin daki kuwa kuka na dinga yi hannu na yanakan kaina, ina na. "shiga uku na, Ahmad ka ha'inceni,"

husna ce ta zabga min mari, tace "zakimana shiru kosai na qara miki?"

Amma ina kojinta ba nayi kuka na nake haiqam, tace "nacemiki uban wa ya miki ciki, tun muna yara nasan wannan ba halinki bane, meyasa zuwanki makaranta kika sauya daga yanda muka sanki nafeesa,"

Jin Kiran sunana datayi kanta tsaye, shiya tabbatar min da lalle ran husna ya baci

Ban boye Mata komai ba, ina kuka nafada Mata, tana kuka itanma ta rungume ni kamar masu zaman makoki muna kuka, tace" ki shirya kawai gobe muje gidansu"

Nace Mata "bansan gidan ba"

Sake wani kukan tayi, mu kadai adaki muna koke koke, husna ce ta tuna da Aiken da mama tayi Mata, ta miqe da sauri tayo falo, kanta ne yayi wani mugun sarawa ganin mama datayi a zaune a kofar dakinsu, tana kallan waje daya kamar mutum mutumi, saurin goge idonta tayi tace "mama bari indora girkin autar bacci take,"

tayi hanyar waje, kallanta mama take, wato so suke su biyu Susan maganar ba tare da I yayansu sun saniba, basasan asirin daya daga cikin su ya tonu, tashi mama tayi ko magana bata yi Mata ba, tashige Dakin
Ina zaune abakin gado ina goge hawaye tare da tsinewa ahmad🤣 mama tashigo ta sameni

Tace "auta"

dagowa nayi cike da tsoro qarara Akan fuska ta, tace "ki fadamin tsakanin ki da Allah abinda naji haka yake"

kuka nafashe dashi nace " mama Dan girman Allah ki yafe min, wallahi mama ba laifi na bane Dan Allah mama ki rufamin asiri, wallahi mama badan duk wanda ya kashe kansa yamutu Dan wuta ba, wallahi mama dana kashe kaina da wannan abin kunyar, nayi DANA SANIN zuwana kano ma Gaba daya mama, "

Mama kasa hakuri tayi, ta rungume ni tana kuka, husna ma datake tsaye abakin kofa tashigo mama duka ta rungume mu muna kuka, tace" auta kiyi hkr, haka Allah mukuma ya jarrabemu da wannan masifa, "

tafada tana kuka kamar ba mama ba

Mike wa tayi tace" husna ku dauko mayafinku mu fita, "

Babu musu muka tashi, itama taje daki ta futo cikin hijab dinta

Waje muka fita, muka tari taxi, bamu zarce ko ina ba, sai wani private hospital, bamu dadeba muka nemi ganin likita, aka nuna mana office dinsa, zamu shige Gaba dayanmu wani yace mana" bayin Allah mutum dai dai ake shiga,"

mama tajuyo tace" dukanmu lalurar dayace,"🤣

mukasa kai ciki
Kujerar mama ce ta zauna, doctor ya kalleta da mamaki yace" mama yanaga ku uku,"

tace" kayi hkr dana "

Anan mama tayi masa bayanin tana so acire cikin dayake jikina, ko nawane yafada Mata sai su bashi kudin, likitan ya kalleta da mamaki
Yace" mama ni musulmi ne kema kuma nasan hakance, meyasa kun aikata laifi abaya kukesan qara wani laifin? "

Mama tace" yaro ka taimaka mana, bansan halin dazamu fuskanta ba daga wajan mahaifinsu dagani harsu,"

likita yace" mama kiyi hakuri gaskya bana wannan aikin

Kema ina baki shawara kiyi hakuri, kuje kuyi masa bayani idan bai yarda ba, ki sanar Dani nayi miki alkawari zan auri yarinyar ki ahaka, koda kuwa ata biyu ne,🤣"

mama tace" to yaro Mungo de "

Muka futo dukanmu jiki asanyaye,
Gida muka koma direct anan muka ga Abba yadawo yana zaune afalo, gabana ne yayi mugun faduwa, ganina shima zai gane halin danake ciki, yace" maman nafeesa ina ku kaje ne?
Tun dazu na dawo Gaba dayanku bakwa nan gida Babu kowa gashi ko abinci ma Babu,"

mama tace" ayi hakuri Abban husna yanzu za'a dora,"
tafada tana cire hijabin jikinta, nida husna muka zauna ahannun kujera kamar wasu baqi
Abba yakalllemu yace

" kukuma miye haka kamar wasu yara, Yau Babu hatsaniyar da kuka saba kenan? "🤣

Mama tayi karaf tace" to alhaji munje gidan gaisuwa ai dole jikinsu yayi sanyi, can bayane wata baquwa datazo ziyara, ta haihu danta ya mutu shine take kuka abin tausayi shine suma nan kagansu haka🤣😳"

Idanu muka hada nida husna, lalle iyaye Mata sunyi a rayuwa, Abba ne yace" kajiku da shirme

to mutuwa ai tana kan kowa
Ke auta zonan ki hadamin wannan takardun,"

jikina yana rawa nace" to Abba,"
nakarba ina shiryasu

** *** **

After one month

Biki biki biki
Awannan nan lokacin anata hidimar bikin Ammu, kowa yana busy, musanman mama, saide duk ta rame, wannan Abu na nafeesa yana nukurkusarta, Gaba daya batada nutsuwa, ta kasa sanar da mahaifinsu, bangaren feenah kuwa, sai abinda yakaru Dan ciki yana Nan yana qara girma abinsa, watansa biyu yanzu yayinda na mama yake wata uku

Anata hidimar biki agidanmu duk dangi da yan uwa sunzo, munyi bala'in kyau cikin anko nida husna, dinkin Riga da sket
Yan'uwa kowa sai tankani yake, kai nafeesa kinyi fari, wannan yace kai kinyi qiba, haka de aketa min magana, basusan abinda yake raina gara ace ina zaune a yanda nake da ne ba Boobs dina yawani ciko, haka hips dina sun qara baiyana, dinkin yamin dam dam ajikina

Hayaniyar mutane ta haddasa min ciwon kai, haka de na daure naketa kai kawo, muna tsakar gida, muna hada kayan miya, husna tana waya da doctor
Abba ya shigo da leda a hannun sa ta Maggi
Yace "uwata zoki karbi wadannan zan fita"
da sauri
Natashi nakarba kenan jiri ya debeni sai yarafff aqasa,
Abba yafara fadan" subhanallah husna batada lafiya ne? "

Husna tayi wulli da wayar hannun ta, tazo ta taimakamin mukayi ciki, tana fadawa Abba banajin dadi dama

Dakinsa na kwanta saboda ko ina akwai baqi
Yace wa husna" kiramin maman ku "
Bayan mama tazo yace" Mata meyasa mu yarinyar nan ne ba kuje asbiti ba har jiri nadibanta?"

Mama tace" zazz...zazzabi.. Ne yake damun ta, "

Abba yace" haba maman nafeesa kuma sai abarta haka? Ko husna aita rakata asbiti
Dauko hijabi muje mu kaita,"🙆🏻 gaban mama yayi wani mugun faduwa
Tace" Abban husna muna da baqi, tayaya zamu fita yanzu? "
Yace" ai yanzu zamu dawo ga husna nan ta zauna agidan "
Mama tace" a a kawai a bata magani tasha zataji sauqi "
Abba yace" to mahaifiyata, ina fada kina fada,😃 "
yayi Gaba
Mama tasan fishi yayi shiyasa yafadi haka
Dan haka taja hijab dinta ta rike feenah sukai asbiti tare da Abba

** *** **

Acan kano kuwa iyayan amarya maimuna sunata hidimar biki suma, daidai misali komai yana tafiya yanda yakamata
Zuwa dare kuma amarya Zata tafi zaria gidan mijin ta

** *** **

"Am likita kayimin bayani yanda zan gane, wannan yarinyar na kawo ma ba maman ta ba, 🤣maman ta itace mai Juna biyu,"

doctor Bala ya cire glass din idonsa, yace "alhaji haka bincikemu ya nuna, batada wani zazzabi ko malaria, munyi Mata text abinda sakamako ya nuna kenan"
Abba Gaba daya ya nemi nutsuwarsa yarasa duk jikinsa rawa yake, yajuyo yace "mamana," kawai yaga ina share hawaye

Yajuyo ya kalli mama yaga takasa hada ido dashi, kenan abinda likita yafada gaskiya ne, Awannan rana dayake farin ciki zai aurar da qaninsa mafi soyuwa aransa Amma wannan yarinyar ta dauko masa wannan abin kunyar

Tashi yayi yana kade binjimar jikinsa yana fifita da ita ya cewa doctor "toshkn likita na gode sosai,"

yayi waje cikin sauri
Su mama ma sum sum suka bishi abaya

Amota Babu abinda kakeji sai sautin kukana, nasan tunda Abba yayi shiru tabbas akwai abinda yake shiryawa

Mama kanta tama kasa kallansa bare ni

Har muka zo gida Babu wanda ya cewa uffan acikin mu, muna Zuwa nafice daga motar da gudu nayi cikin gida, Abba yafuto ya kalli mama yace Mata "kin kyauta"

shima yayi hanyar masallaci

** *** **

Bayan sati daya, amarya ta tare agidan ta, suna zaune lafiya, Amma ta bangare na, Babu wannan lafiyar, Gaba daya Abba fishi yake damu

Ko gaishe shi nayi baya amsawa haka zan qaraci zamana Natashi, ta bangaren mama kuwa har gara nima
Ita kwata kwata bata ganin fuskar gaisuwar ma
Na rame nakara lalacewa

Cikin jikinane kawai yakesa aga kumari na

Washe gari Abba yana zaune afalo, yakira mama bayan tazo yace taje takiramu Gaba daya

Gabana yana faduwa naziro hijabi na na futo kaina aqasa
Husna ma tana Bina abaya muka zauna aqasa kanmu a sunkuye

Abba yace "Nafeesa"

Gabana yayi mugun faduwa yace "kafin nace dake komai nafeesa tashi ki dauko min jakar ki"

Mama ta kalle shi da mamaki me zaiyi da jakarta?
Daki nakoma ina kuka ina hada kayana, kusan kala biyar nadauko na futo, na tsugunna

agabansu ina goge hawaye

Hannu yasa a aljihu ya dauko kudi dubu biyu yabani, nakarba

Yace "yauwa kama hanya kifice ki barmin gidana,"

mama batasan lokacin data tashi ba, tace "alhaji kamar yaya?
Ina kake so taje mace cefa," Abba yace "taje koma inane, nide bazata haifamin shege agidanaba, wallahi nayi tirr da halinki nafeesa nayi DANA SANI Akan karatun dana turaki kano, maza fice ki barmin gidana.

Mrs Usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

28

"Gani mama,"

"to autar mama, kinji de abinda Abban ku yace, kuma ni aganina hakan ai yafi ko auta?"
Nace "hakane mama, yanzu yaushe zamu tafi?"

"A a kibar husna anan taringa tayani wasu abubuwan kokuwa?

Idan kuka tafi Gaba dayanku kuma ai Babu me taimaka min,"

"hakane mama Toshiknn bari inje in shirya kayan"

** *** **

"Mama wallahi kinji de abinda yafaru,"

kaka cikin kuka tace "Amma ma'azu Baku kyauta minba, yanzu yarinyar mu zauna tare da ita Tsawon lokaci, wannan Abu yafaru bazaku sanar daniba, haba ma'azu,"
Abba yace "mama kiyi hakuri, wallahi abin ne ba shida dadin fadi, nasan kuma hankalin ki zai tashi Akan hakan,
Shiyasa nace kada su bari ma kisani, Amma yanzu de ga halin da ake ciki,"

"to yaushe Zata taho nafin"

"Gobe Zata taho insha Allah"

"To Allah yakawo ta lafiya"

"Amin mama"

Bangaren qanwar mama ta nufa, tana kuka ta sanar da ita komai, haka kalatynmu itama tahau kuka abin, gwanin ban tausayi

** *** **

"Salamu Alaikum,"

"wa'alaikumussalam," Abba yace "ah hassan anyi aure kuma shiru ake jinka" 🤣

Ammu yace "yaya kayi hkr wallahi awajan aikinmu ne suka doramin abubuwa dayawa, kuma dama gashi sai weekend ake samun damar Zuwa gidan,"
Abba yace "to Babu de wata matsala ko?"
Ammu yace "a a Babu komai, yaya dama ita maimunan ce tasamu Juna biyu, yana Gama fadar

haka ya kashe wayar" 🤣

Abba yace "kai yaran zamani al'amarin su, saisu hassan ko kunya, to Allah de yaraba lafiya"

Haka yayi ta farinciki aranar

** *** **

"Sis kisa wannan ma may be zaki buqata,"

"kai barshi anty husna, wannan kayan ma sun isa,"

"tokisa books dinki, karki zauna kina tunani gara kina dubawa ko?"

"Ok" nace nakarba nasaka acikin jaka, tsaf nagama hada komai

Abba zai wuce school yabani dubu goma yace in rike, koda abinda zan buqata, mama ma tabani kayan miya da komai tace na kaiwa kala, husna kuma tace idan naje na mintsini kaka 🤣

Su dukansu ne suka kawoni inda zan hau mota, hijabin dana zirma ajikina shine ya boye abinda yake tare Dani

Saida motar mu ta tashi, sannan su Abba suka dawo gida, shikuma ya wuce mkrnta daga nan

Anty maimuna anata fama da laulayi, danma husna tana Zuwa wani lokacin tana taimaka Mata, ga kuma mama da itama kusan kullum batajin dadin jikinta

** *** **

Ina hanya araina nace, Allah sarki su mama koyaya suka koma gida, abinda na tuna ne yasa natura hannu na cikin jakata da sauri
Wayata na dauko wadda ni kaina namanta lokacin dana kashe ta, so nake kawai inji muryar su mama da husna

Ina kunnata tafara hooking, text ne suke ta shigowa ba ma adadi, wasu na qawayen mu ne wasu na Zeey Akan tayi missing dina, saina Atu tana fadamin takirani bata sameni ba, Amma tanamin albishir Akan ta haihu tasamu mace, murmushi kawai nakeyi, text mafi yawan kuwa daga ahmad sai saudat

Kuka nafara lokacin dana karanta na saudat

"sis mene duniyar kuma? Kin wani tafi zaria kin share ni "

" sister feenah wallahi nayi kewar ki, wai kinsan ma meya faru, wallahi daddy yayimin miji "

" sis feenah yasu mama Allah yasa de lafiya Bama samunki, dan'uwana yana cikin tashin hankali feenah, har kuka yi yake a dalilin ki "

" sister andaura aurena Yau, shikkenan kinji dadi tunda kinsan banda hanyar dazan sameki balle in fada miki "

" sister sunan mijina faruoq, yana sona sosai, mun tafi Abuja, kema ina muku fatan kasan cewa tare keda yayana "

Ire irin wannan text din saudat taita turomin, nagama karantasu ina hawaye

My ahmad, shine sunan da na ambata araina, text dinsa rututu, harma narasa wanne zan Buda

" my feenah, ina kika shiga ne, Dan girman Allah ki yafemin"

"nafeesa nime laifi ne awajanki, kuma gani na durqusa kafafuna aqasa ki yafemin "

" my feenah, bansan wacce kalma zanyi amfani da itaba wajan neman yafiyarki, ki yanke min kowanne hukuncin da kikaga ya dace Dani "

Ina karanta wannan afili na furta zakaga abinda ya dace dakai kuwa, na goge hawayena

" Haba yarinya tun dazu sai kuka kike, haba ni wallahi kinsa duk jikina yayi sanyi, ni natsani kuka wallahi, ai sai kisa muyi zatan mutuwa zamuyi ahanya, a a, muka sani koke alama kika gani" 🤣

Wata tsohuwa ce a kusa da feenah take wannan mgnr,
Ban kula taba kawai nagoge hawayena,
Su mama nakira, saida naji muryarsu hankali na ya kwanta, ina sauke wayar a kunne na, kiransa yana shigowa

My ahmad yafuto baro baro a fuskar wayar, yana zaune a office kamar wasa ya gwada number,

aikuwa yanaji ta shiga ya miqe tsaye
My feenah daga mana, yi sauri ki daga Dan Allah, shi kadai yana magana kamar zautacce

Har wayar tayi ringing ta kare ban dagaba, wani Kiran yasake shigowa, nayi rejected, dana uku ya shigo a fusace na daga, nace

"waye?"

Acan bangaren baiyi mamaki ba, yace "feenah,"
nayi shiru
Yace "Dan Allah kiyi hakuri"

Nace "hakuri? Ahmad ashe kasan hakuri?"

Cikin kuka naci gaba dacemasa "ahmad wanne irin hakuri ne ban baka ba Akan ka kyaleni? Menayima ahmad? Kasan halin daka sani kuwa? Wallahi nayi DANA SANI Akan kula ka ma danayi tun farko,"

kuka yaci karfina, cikin sheshshekar kuka nace" Dan Allah ka fita daga rayuwata, bana sanka na tsaneka ahmad karka sake nemana, "

nasauke wayar daga kunne na

" Kayya yarinya kiyi hakuri, haka mazan suke, rayuwar aure da kika ganta sai hakuri,"🤣

kawai tafara goge hawaye, kallanta nayi da mamaki ni shaf ma namanta tana kusa Dani

Cikin sauri nayi copy din number's dina suka dawo kan waya, nakarya layin, na wullar dashi ta tagar motar

** *** **

" Wash Allah kirjina,"

yafada yana dora hannunsa Akan kirjinsa, kansa ne yasara yagaza zama, har saida yadora kannasa Akan tebir din dake gabansa

** *** **

Adedeta na saukeni, naja jakar kayana nayi cikin gidan, kai tsaye bangaren kaka nayi, tana ganina tataho da sauri tazo ta rungumeni, sai kuka, ni kuka ita kuka
Zama mukai afalo tace" sannu nafi, ashe wannan ne abinda yafaru, Amma kika kasa fadamin," nace" kaka to ai nima bansan Shiba, "

Tace" keee nafi
Ki fadamin gaskya, nasan yaron dayake Zuwa wajanki kawai yayan saude ne, kifadamin idan shine wallahi anbinciko min shi, kokuma inbada cigiyarsa agidan radio"

Bansan meyasa ba kawai de na tsinci kaina da fadar " ba shi bane kaka," tace "to koma wanene Allah yasaka miki," nace "amin kaka"

** *** **

Cikin sauri yake tafiya har yazo gaban office din nasa, hannun sa dauke da takardu, sakatariyar ya yiwa magana cewa" yallabai kuwa yana Nan? "
Tace" eh yana ciki tun dazu "
OK kawai yace, yasamu waje ya zauna yace" kiramin shi, kice masa maganar takardun sababbin motocin nan ne"

Takira 2 time's Amma bai dagaba, Dan haka tace kawai yashiga may be, wayar bata kusa dashi ne

Ahankli ya tura kofar office din yashiga, gaskya office din ya tsaru, ga photon sa nan yasa manyan kaya farare yana murmushi amanne Ajikin bango,
Nishin dayaji ne yadawo dashi daga tunanin daya tafi
. "Subhanallah yallabai, Garin yayi haka?"
Kamashi yayi, ya kwantar dashi Akan doguwar kujera wayar office din yadanna, nan da man likita yazo,
Yayi Dan dube dubensa yadago yace "gaskya oga saide muje asbiti" "Ok" kawai Ammu yace

Ya cicciboshi, sai mota, shawara kawai yasake yajuya kan motar sai asbitin doctor tahir

Dayake ahmad sananne ne, nan da nan aka karbeshi aka kai shi wani daki

Office din tahir yanufa, yamiqa masa hannu suka gaisa, tahir yayaba da kamala irin ta Ammu, haka shima Ammu nan take yaji tahir ya kwanta masa arai, bayanin abinda yakawo su yayi wa tahir, ai cikin second da basu wuce biyar ba yanayin tahir yasauya, cikin hanzari yayi Dakin da ahmad din yake

** *** **

Naci abinci dakyar, inajin wani daci amaqogarona, dakyar de nadan caccakali abincin, nayi wanka na kwanta, kala ce ta shigo, tace "idan na huta saina tashi nakoma bangaren ta"
Ai kaka najin haka tace" a a Babu inda nafi Zata ina nan tare da ita,"🤣

ba yanda kala ta iya haka tahakura,
Ina kwance ina tunanin duniya na shafa cikina araina nace kome zan haifa? Ko idan ya tambayeni mahaifinsa yaya zance?
Wai nice da ciki, cikin ma na shege
Hawaye naji ya ziraro min nasa hannu na goge wallahi banasan cikin nan, tunda de shima jinin ahmad dinne
"wallahi bana sanka"

nafada afili hannu na nadauke daga kan cikin, nasake cewa "nikam bana sanka," 🤣

wani motsi naji cikin yayi, nace "shikkenan qarasa ni ma kamar yanda shima yanemi kashe ni, ranar nan"

** *** **

Tahir yace "haba ahmad, meyasa kake San saka kanka cikin matsala ne?"

Ba tare daya kalleshi ba, yace "tahir najima acikin matsala ai, har Zuwa Yau dana same ta"
Tahir yace "bangane ba," ahmad tiryan tiryan yabawa tahir labarin komai
Tahir yace "gaskya tadau zafi dayawa, yanzu yaya za'ai?"
Ahmad yace "wannan mgnr da fadamin itace takemin yawo akaina tahir ta tsaneni, nafeesa ta tsaneni," sai hawaye
Tahir jikinsa yayi sanyi yace "ahmad kasan Mata, zafi ta dauka dayawa, nanda wani lokacin

Zata huce komai ya wuce ka kwantar da hankalin ka, muci Gaba da addu'ah kaji, kaga yanzu jinin ka yahau, kuma sosai ma hawan jinin dole saika rage tunani, kayi hakuri abokina haka tamu qaddarar take, "

ahmad baice komai ba, ya lumshe idonsa

Turo kofar Ammu yayi, yace" doctor yajikin yallaban? "
Tahir yace" alhmdlh jikin da sauqi, dan Allah abokina ka dinga kula dashi nabaka amanar amini na,"🤣

Ammu yace" Babu komai insha Allah "

Bude idonsa yayi a hankali ya cewa Ammu," kaje kaci Gaba da kula da komai, zan wuce gida ta nan,"
Ammu yace" to Amma yallabai dakazo namaida ka gidan aiko? "
Ahmad ya girgiza kansa yace" karka damu tahir zai maidani"

" Toshiknn yallabai Allah yasawaqe,"
gyada kansa kawai yayi

Bayan ya fita tahir yace" Amma wannan mutumin yanada kirki, "

ahmad yace" eh wlh nima tun ganina dashi na farko naji y kwanta min, shiyasa bana shakkar bashi kowanne aiki daya shafi company" tahir yace "gaskya ne"

** *** **

Bayan sati uku, companyn su ahmad sun bawa ma'aikatansu wajan zama wadanda suke Zuwa daga nesa, cikinsu kuwa harda Ammu

Yakira waya gida yafada musu, anty maimuna murna kamar me Zata koma kusa da yan'uwan ta
Dakuma mijinta

** *** **

Baba adamu yayi duk wani zirga zirga Akan maganar gidan kaka, an sai Mata wani gida sabo gwanin sha'awa anan bompai saide fa sun kashe Mata kudi, shida Abba, ita kanta tana godia tana kuka, haka muka koma sabon gidan kaka nida ita, nikaina nafijin dadin zama agidan nafi sake wa, Dan haka dakaina nafita waje naje nasiyo sabon sim card, kuma alhmdlh naji dadin tafiyar danayi, tunda Babu inda nake Zuwa kullum muna gida amanne, nakira kowa na nuna masa sabon layina, banda mutum biyu, saudat da ahmad, a wannan lokacin cikina watansa shida, yayinda na mama yake wata bakwai

** *** **

"Ahmad! Ahmad!!
Ahmad!!!"
Tafada da karfi, cikin sauri yaduro daga kujerar daya kwanta akai,
" na.. Na... Na'am momy"

"Waladeey na me kake tunani hakane, tun dazu inata kiranka?"

"Momy kawai ina tunanin office ne,"
badan ta yarda ba, tace "kuma office kamar Yau kafara Zuwa Waladeey?" Shiru yayi

Saide ita aranta tasan karya yayi Mata, wani abun ma da sakacinta, bata fiya kula dashi ba, yakamata ta janyo shi jikinta harya sanar da ita damuwar sa,
Tace "munyi waya ne da hajia bilki tana min maganar kaya, tace tazubamin ido tayi zuru tayi zuru bataga kayaba, nace nikuma aina manta ma dana baka wannan kayan kuma nasan ka kai Mata,"

Ahmad yace " Momy wanne kaya kuma?"
Tace "lesuna dana baka kwanaki,"
ahmad yace "tab ni wallahi Momy nama manta dasu, suna can adakina, mabaruka taje tadauka takai Mata" , yana fadar haka yayi hanyar waje, tabishi da ido, tabbas akwai abinda yake damun yaron nan, shikuma yayi hakane Dan karma tace yaje yakai kayan, saboda bayasan ganin kayan kokadan, DAYA SANI ma tun farko bai karba bare wannan sabanin yashiga tsakaninsa da feenarsa

** *** **

"Gaskiya baby nide nagaji yakamata ki barni nazo na ganki hakanan, haba husna Allah nide ki barni kokuma inyi miki kuka," husna tace "haba doctor kuka kuma kamar ba namiji ba," yace "inde Akan kine zan iyayin komai ma husna, zaki haifamin twins idan mukai aure?"

Husna cikin mamaki tace "yan biyu de, a a bazan iyaba," tahir yasake gyara kwanciya Akan doguwar kujerar dake shinfide afalon nasu yace" aikuwa ke, danni inasan yan biyu, "tace" toka dena, danni kam banaso akwai wahala fa doctor, tafadi haka cike da shagwaba,"
nan danan mutumin ku ya rikice yace" to to naji baby ni karki min kuka shikkenan? "
Kafin husna tayi magana can cikin wayar taji Ana cewa" Dan ummi da yar tawa kake waya ne? "🤣

Dagowar da tahir zaiyi yaga ummi a tsaye akansa, haba qasa Bude tahir yashige, yaji kunya ta Kamashi, Allah yasa de bataji zancan duka ba
Husna taji shiru har Zata kashe saita qarajin ance bani ita mu gaisa
Tahir ya daskare da waya akunnan sa

Mrs Usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicatedg to my family

30

"Kinyi shiru nafi,"

nace "kaka ai baya nan, yatafi misra,"

" au to shiyasa naji shi shiru, nasan da yasan inda nake aida tuni ya zo"

Nace "um" 😠

Natashi nayi daki

** *** **

Akwana atashi Babu wuya awajan Allah, har cikina yacika wata tara, duk kafafuna sun kumbura, nayi wani fari, kaka bata barina inyi aikin komai, ina kwance kokuma in tashi inta zagaya gidan

** *** **

Baba adamu shine yayi shige da ficensa ya karbo min takarduna, yahada dana wajena yatafi dasu gidansa bansan me zaiyi dasu ba

** *** **

"Maman nafeesa anya kuwa ba zamuje asbiti ba aduba lafiyarki?
Tunda kika samu cikin nan bakida lafiya Yau fari gobe tsumma, gashi naga watan naki ma ya haura, ga kuma bikin husna dayake ta matsowa saura wata daya da sati daya"

Mama tace "Babu komai Abban husna, aidama Ana samun hakan, yanzu Babu abinda nakeji," Abba yace "Toshiknn"

** *** **

Su ahmad tunda bikin nan ya matso ake ta zirga zirga kai kace bikinsa ne za'a yi,🤣 baya zama Yau shine can gobe shine can

Kullum suna shirya yanda bikin zai kasance,
Haka a bangaren su mama ma, basu zaune basu tsaye, Ammu yayi kokari sosai wajan ganin ya qawatawa yar tasa gidanta, sosai yayi Mata siyaiya ta gani ta fada Babu abinda su mama zasuce sai godiya

** *** **

"Kaka ni banajin dadin jikina, tun jiya wani irin ruwa nake zubarwa,"

kaka tace "a a nafi to haihuwar ce ta matso inaga zaqi ne, shiyasa banasan wannan ciye ciyan naki,"

tunda kaka ta ambaci haihuwa gabana yafadi, gaskya ina tsoro, qila ma Garin haihuwar na mutu, sai hawaye, kaka ta kalleni tace "to nafi ki adana kukan ki ba yanzu🤣🤣 ba akwai lokacin da zakiyi mai dalili,"

maya finta taja, tace "bari inje in karbo miki rubutu kyasha," bata jira amsa taba tayi waje, na zauna ni kadai na rafka uban tagumi, tashi nayi naje nayi alwala domin gabatar da sallar la'asar

** *** **

"Wash Allah Abban husna mu tafi asbiti, ina tunanin haihuwa zanyi,"

Abba Gaba daya yarikice, Yama rasa yaya zaiyi
Husna yakira ta futo da sauri, suka hada duk wani abin buqata sai wani asibitin kudi
Suna Zuwa kuwa likitoci suka karbeta sai labour room, husna sai kuka take, Abu tun la'asar sai gashi mama takai kusan isha'i bata haihu ba, duk nurse din data futo amsar daya ce bata haihu ba tukunna

** *** **

Ina zaune kan sallaya na idar da sallah kenan da carbi ahannu na, naji wayar kaka na kuka, kira na qwala Mata, nace " kaka Abba yana kiranki,"

ta futo daga daki ta amsa wayar, sai ji nayi kaka tana salati,
"ma'azu to anya kuwa Babu wata matsalar ka boye min?"

"Mama Babu komai wallahi kawai de dama Dan in fada miki ne kisan halin da ake ciki,"

kaka cikin sanyi jiki tace" to Allah yarabasu lafiya"

" amin" Abba yace

Ta zauna akujera nace " kaka lafiya kuwa,?"

Cikin jimami tafadamin abinda yake faruwa gabana naji yabada dam, araina nace nima fa inakan hanya, bayana naji ya riqe da sauri nasa hannu na awajan, nace " wash Allah, kaka bayana,"

ina yi ina yarfe hannu, kaka tace "subhanallah nafi karde kema haihuwar ce?"

"Wayyo kaka marata ciwo, zan mutu kaka,"
kaka tace " tsaya nafi bazaki mutu ba insha Allah,"
Wayarta ta dauko tafadawa baba adamu abinda yake faruwa, yace gashinan Zuwa

Kala taso ta biyo shi yace ta zauna tunda kaka tana nan, sai ihun kuka nake Mata ina yarfe hannu, yana Zuwa muka shiga bayan motar nida kaka, sai ihun kuka nake musu
Kaka tanaban hakuri, asibitin gwamnati muka fara Zuwa, saide sun shaida mana sun tafi yajin aiki, haka baba adamu yajuya kan motar sai wani asibitin kudi shi kansa ya rikice, yana tausayi na, ga halin danake ciki gani yarinya

Inata kaina banma kula da sunan asibitin ba nide nasan muna Zuwa wasu Mata suka karbeni aka dorani Akan gado, suka turani Zuwa labor room

** *** **

10:30 na dare, wata doctor tazo tace "alhaji saide fa kasa hannu anan, dole aiki za'a yi mata, Dan gaskya karfin ta yaqare, bazata iya haihuwa ba, sannan gashi ta manyanta,"

Abba cikin rawar jiki yasa hannu, anzo tura gadon za'a maida ta Dakin operation Allah cikin ikonsa ta sauka, ta samu danta namiji

Nurse dince ta futo, Abba da husna har rige rigen Zuwa gareta suke, tace musu " ta sauka,"

hamdala Abba yayi, yace" meta haifa,? "
Tace" tasamu danta namiji, Amma saide kayi hakuri yaron yarigamu gidan gaskya, sakamakon wahalar da babyn yasha, "

Abba yace" yanzu a wanne Hali take?"

Nurse din tace" alhmdlh munkai ta Dakin hutu, Amma kafin nan kaje wancan office din likita ya nasan ganinka, "

Abba ya wuce, yasamu doctor, anan doctor din yake masa bayani Akan abarta ta huta haka, yakamata ace a shekarun ta, tadaina haihuwa ma, yanzu ma Allah ne yatsare da saide ayi biyu, Amma sunyi iya kokarin su ganin kare lafiyarsu Gaba daya, shide yaron Allah yayi hukuncin sa, Abba yace " Babu komai likita, insha Allah za'a kiyaye"

Daga nan suka wuce Dakin da mama take ciki shida husna

** *** **

11:56 ahmad yace "to man ni zan wuce gida, kaga dare yayi, wannan de shine tsarin yanda dinner din zai kasance
, kaga har lokaci yaja ban tafi gida ba duk ka wani hanani sakat saboda wannan auren,"

Kafin tahir yayi magana, wata nurse ta shigo afirgice, tace "doctor ankawo wata Mata tana naquda, munyi iya yin mu Amma takasa haihuwa, batada jini tana buqatar jini, ko zakazo asan yanda za'a yi?"

Tahir yace "nawane group din jinin nata?"

Nurse din tace "wallahi bamu dashi doctor group O negative gareta"

Tahir yace " to ina yan'uwanta?"

gaskya suma mun gwada baiyi daidai ba

Tahir ya miqe da sauri, zai fita, ahmad ya tareshi yace  " kaga muje kawai na bata nawa, ainima shine Dani,"
tahir yace "a a ahmad kaima fa bakajin dadi sosai," ahmad yace

 "kaga da Allah muje," lab sukaje aka gwada jininsa, yayi daidai, haka kuma ba shida matsalar komai
Dan haka gado Aka bashi ya kwanta aka dibi jinin

Doctor tahir da kansa yasa mata jinin, kaka tana waje banda kuka Babu abinda take yi

Saida yasa Mata jinin sannan yaje, wajan ahmad,

 "man mungode fa," ahmad yace "Babu komai, bari in wuce," tahir yace  " no kabari na kaika, jini aka diba ajikinka kada kayi wani abin wahala yanzu,"

haka ahmad y hakura, suka fita shida tahir yasaukeshi agida, shikuma tahir din yadawo

12:30 daidai na haihu, nahaifi 'yata mace, muna Dakin hutu nida ita, tana kwance a gabana ansa Mata kaya farare masu shegen kyau, gata bul bul da ita yarinyar, masha Allah wannan yarinya badai kyau ba, na zuba Mata ido ina kallanta, Babu abinda ta dauko na uban ta, komai nawa tayi,
Daga farin har hancin hatta yan yatsun ma irin nawa ne, idonta kar Akan glof din wutar Dakin
Na shagala ina kallanta kaka ta shigo Dakin, maganar tace tadawo Dani da duniyar tunanin dana afka
"Um yaran zaman, su nafi ko kunya Babu anzubawa ya ido" 🤣

, kallanta nayi, ni banma San tana kainaba, tunawa nayi da yarinyar nanfa bata hanyar aure nasameta ba, sai wani baqin ciki ya to kare ni, nan take na juya Mata baya

Kaka tace " zancen yaushe kuma nafi, 🤣"

Wata nurse ta shigo tabani magani nasha da tea mai kauri, baba adamu ma yazo yaga yar sosai yarinyar ta shiga ransa, yarinya kamar wata yar baby 🤣

** *** **

Karfe goma nasafe nayi wanka, naci abinci na shirya tsaf Dani, ga jaririyar dana haifa nan a gefe na, kaka sai magana takemin Akan na bata nono tasha naqi bata,
Wayar tace tadau qara, ta daga kawai ji nayi tace

"to Allah yaji kanshi ita kuma tunda de Allah Yabar mana ita to Allah yabata lafiya"
Can naji tayi shiru, bansan me take jiba, sai tace "eh hakan ma yayi ma'azu, insha Allah gobe zan taho, sai nabar nafin awajan kalatynsu to, to sai nazo,"
ta juyo tafadamin komai, nace "kash dama yaro maman ta haifa, to Allah yabata lafiya,"

kaka tace " amin,"

Amma batamin zancan tafiyar ta taba goben

Rarrashi na tashiga yi, Akan nabawa yarinya nono, dakyar de na dauketa nasa Mata aikuwa cikin sauri takama tanasha
I nayi ina rintse ido

Kofar Dakin dr Tahir ya turo yashigo,kaka tashiga toilet, saini kadai, sai muka birgeshi a yanda ya ganmu, ina shayar da yarinyar, sannu d jiki yayimin, ya tambayeni ko akwai abinda yake damuna nace a a, yarinyar yadauka yaji dama abashi ita yarinya saikace yar turawa, wasa yayi Mata gamida yimin sannu yafice daga Dakin

Mundawo gida da yamma yin duniya kaka tamin yar nan tana kuka in bata tasha, nayi mirsisi nahana, araina nace kyayi kya Gama kaka Amma bazasu zubar min nono ba itada ubanta
Haka kaka ta kyaleni taje tasiyo madara tabata tasha daqyar sai kuka take, duk da inajin kukan a raina haka na qyaleta

Washe gari da safe muna zaune afalo nida kaka ta tashi tahau shiri, zani naga ta dauka ta goya yarinyar, tacemin " to ni na tafi saina dawo"

Cikin sauri nace "kaka ina zaki kaita?" 🤣 🙈

Mrs Usman ce 🖊️[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

Kaka tacemin "siyar ta zanyi,"

turo Dan qaramin bakina nayi Gaba, nace "to ki kawo ta in bata tasha," tace "riqe abinki nafi," tajuya ta fice

Bata zame ko ina ba sai gidan baba Adamu tayi masa bayanin komai da gashi har qanwar mama kala, sun amince da wannan batu sosai sunji dadi, daga nan kuma ta wuce sai tashar mota, cikin sa'ah suna Zuwa saura mutum daya lodin zaria yacika, saboda haka tana shiga suka dau hanya

** *** **

Suna zaune adakin da aka kwantar da mama, danma jikin nata da sauqi suna Dan taba fira kadan kadan, husna tana shan tea, yayinda mama take shan farfesun kayan ciki wanda husna takawo daga gida, shikuma Abba yana zaune akujera a gefe, yana waya da Ammu

Da kuma abinda ya yanke, Ammu yace "yaya hakanma yafi, mu kanmu shine rufin asirin mu, da kuma ita kanta nafeesan"

Abba yace "to shikkenan dama shine, ka gaida ita maimunan"
Ammu yace "to zasuji"

Wayar Abba ce tasake ringing ya daga tare da fita

Bayan wani lokaci sai gasu sun shigo tare shida kaka

Mama ta tashi zaune, husna tace "ga kaka ga kaka"
ta cacimeta
Kaka tace " kai bari karki karyani, duk sai kunga bayana daga ke har nafi"

Husna tasa daria
Kaka ta kunto babyn bayanta, Abba ya meqa hannu zai karbeta husna tace "a a Abba bari in fara daukanta"

Tayi zuruf ta karbeta, Abba yace "eh lalle husna yanzu de kin nunamin yarinya taku ce" 🤣

Su mama suka sa daria

"Masha Allah kaiii mama wallahi kin ganta kamar baturiya, Dan Allah nide kiban ita wallahi ina Santa" 🤣

Abba yace "husna banasan shirme kinji ko, bani ita,"
dakyar de husna ta bashi ita, yace "masha Allah, Allah yaraya," kaka tace " amin,"

"gatanan batada aiki sai kallon wutar lantarki, kamar agidansu Babu"

Mukasa daria, husna tace "kaka aike ta biyo"

Abba ya miqawa mama yarinyar, ta karbeta tace " to Allah yatayamu riko," kaka tace "amin"
Husna tace "mama yanaga tana kama dake ne"

Kaka tace "kamar uwar ta ta iyo, bakya ganin yatsanta sak irin na uwar ta, abinda yasa zakiga haka itama nafin kamar mahaifiyarku tayi shiyasa"

Abba yace "eh hakane kam

Kinyi Mata bayani ne mama?"
Kaka tace "bance Mata komai ba, ai ita nasan dadi ma zataji anrabata da qaya, wallahi ma'azu Yau yar nan ba tasha nono ba, madara kawai nake bata har mukazo nan, uwar taqi bata, nayi nayi da ita taqi, shiyasa nima na dauko ta ko bayani banyi mataba" 🤣

Abba yace "to bari ayi Mata huduba,"
ya karbeta, idan ta cikin na Abba, 🤣

Abba yace "husna yar nan taku batada kara, kallo haka ido cikin ido," 🤣
kallanta yayi yace "
To bazan aure kiba de,"

duk mukasa daria

Husna aranta tace lalle feenah tayi kokari, nikam idan yata ce wallahi bazan yarda ba, gara abar min abata 🤣

Ina kwance afalo ina kallo, naji wayata na ringing ina dubawa naga Abba bayan mun gaisa yace "
Uwata dama akwai maganar danake so muyi dake, Akan maganar yarinyar nan na yanke shawara maman ku Zata rike ta, kema hakan zaifi miki rufin asiri,"
cikin sanyin jiki nace" to Abba na gode, "Abba yace" a a Babu godia atsakanin mu

Sai magana da biyu wanne suna kikaga ya dace asamata? "
Nafada masa, yace" Toshiknn ki kwantar da hankalin ki kinji, idan kin Gama hutawa kema sai ki dawo gida a fara shirin bikin yar'uwar taki, "nace

" to Abba a gaida su mama "

Bayan nakashe wayar bansan meyasa ba kawai naji kuka yazomin, shikkenan kuma nida baby, sunan danaji zuciyata tasa Mata kenan, ina kaunar yarinyar saide tabon mahaifinta bazai goge ba a idona

Abba yayi murmushi aransa yace wannan suna nafeesa ai saiku yan zamani, ya daga baby yayi Mata huduba, husna tace" Abba ya sunan ta? "

Abba yace " IZDIHAR," husna tace "wallahi yayi dadi," mama tace "aikam wannan suna kamar na larabawa," Abba yace "eh sunan larabawa ne"
Kaka aka Tabe baki a kace
"Lalle nafi Babu kara, yanzu Akan ta dubi irin wahalar danasha tun daga kano Zuwa zaria ai yaci ace Rabi'atu tasawa wannan yarinyar 🤣🤣"

Husna tace "tab lalle kaka, ai sunanki yanzu saide inna haihu na tausaya miki nasa sunan ki, Amma wannan fine girl din a a bazamu samata ba"
Kaka tace "kyaji dashi"

** *** **

Babu yanda na iya haka na tattara nakoma gidansu kala, saboda kaka taqi dawowa tace sai anyi suna, kala tayi kokari akaina haka ta dinga bani magunguna na matsi ina amfani dashi, da kuma wanda zai taimaka min wajan zubar nono na, cikin yan kwanaki kuwa, yadena zuba, na dawo normal kalau nake jina kamar ma ban fidda wata halitta daga jikina ba

** *** **

Sati na zagayowa akayi suna yarinya taci suna IZDIHAR kamar yanda nafadawa Abba, kaka saida taqara kwana biyu bayan suna sannan tadawo gida

Haka na baje inacin kayan suna kamar ba gobe musanman nama🤣😃

🤣

Takawo pictures din da akayi na suna, duk sunyi kyau Babu wanda zai ce ba mama ce ta haifetaba, haka kuma husna ta tutturomin wasu ta whtsp, kawai nace Allah yaraya

** *** **

Bayan sati daya na wuce zaria, lokacin bikin husna saura wata daya daidai

Tunda nakoma gida kwata kwata bana kula yarinyar, saide in tana wasa inta kallanta, mama Zata barta Akan kujera a kwance idan ta gaji da baccin tafara kuka inaji zanyi mirsisi na kyaleta

Saide husna ta goyeta, har tayi shiru
Hatta wankin fitsarinta bansaniba, bana tsinana Mata komai

Akwai lokacin datake kuka tana kan doguwar kujera Garin daga kafa datake yi irin na jarirai qiris yarage ta fado qasa , Allah yakawo mama tayi sauri ta rike ta, ina zaune Akan kujera, mama ta kalleni, tagade abin nawa harda rashin hankali aciki, 🤣anan tamin tatas daga karshe tacemin shashasha dabatasan ciwon kanta ba balle tasan na wani

Haushin yarinyar yakamani, duk itace sila dabatazo duniya ba da mama batamin wannan fadan ba

Kalatynmu takira husna tace taje kano, ta huta kafin bikin, ganin haka yasa nima nace zan bita, Babu wanda yahanani, mama tace min ala raka taki gona 🤔

Dasafe muka shirya zamu tafi, nasa doguwar Riga nayi rolling da Jan mayafi, har zamu tafi naga baby afalo, nasa hannu na dauketa, nabawa husna wayata nace tayi mana pictures
Aikuwa cikin sauri ta karba tayi ta mana, tana bani style, har saida nace ya isa sannan tabari, na ajiye ta, mu kayiwa mama sallama muka tafi

** *** **

Kala takanas takira mai gyaran jiki take gyara husna, nima kuwa nace ayimin, cikin sati uku muka wanke fes damu, kamar hardani za'a yi bikin
🤣

** *** **

Saura sati daya biki, lokacin muna gidan kaka baba Adamu yazo da wata magana, yayi mana bayani Akan yasama min Scholarship kamar yanda aysha tasamu tatafi Uganda, tonima ya nemamin Dan haka na shirya kayana, cikin satin nan zamu tafi, kaka tace " to Adamu wacce qasa zataje?"

Yace "Sudan,"

kaka tace "eh hakanma yafi idan Allah yakawo mijin sai ayi Mata auren,"

baba Adamu yace "eh wlh, Allah yakawo nagari"

dukanmu mukace "amin,"

cikin kwana biyu akayimin passport, kawai jiran visa nake, su mama ma kansu sunji dadin wannan batu

** *** **

Muna kwance a gado nida husna ni ina chting, ita kuma tana waya da tahir, tace masa "yaude ga auta ku gaisa,"
nakarbi wayar yace "autar mu, kin buya,"

nace "doctor ai kaine ka buya bamu taba haduwa ba,"

yace "tunda biki yazo kinsan abubuwan zasuyi yawa, Amma insha insha zamu hadu ai, keda mukeso ma ki taro gidanmu," 🤣

nace "a a mama bazata Baku ba,"
haka muka sha raha dashi daga qarshe nabata wayar

** *** **

Bikin husna saura kwana uku visar mu ta futo, gwamnati ta nememu, Dan haka muka shirya washe gari muka tafi, ina kuka mama ta nayi, muka rabu haushi na daya bazanga bikin sis ba, Abba ne me dauriya, kaka ma kuka haka kowa de jiki yayi sanyi suka rakani airport anan nahadu da abokan tafiyar mu, kafin lokacin tashinmu yayi, inaji ina gani su mama suka tafi, na sunkuyar da kaina Akan cinyata ina kuka,

Tunda tazo wajan hankalinsa yake kanta Gaba daya tatafi da imaninsa, yarinyar tahadu ba qarya 🤣

Karfe 9:30 jirginmu yatashi sai Sudan

Mrs Usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

32

Umarni aka bayar musa belt, nima nasa nawa na rufe idona, ina tunanin rayuwa ta

** *** **

Suna zaune afalo, daddy yana karanta jarida, ahmad da waya ahannunsa, Amma Gaba daya hankalin sa baya kan wayar, daddy yace" my son ina fatan de komai yana tafiya yanda ya dace Babu kowacce matsala ko? "

Kamar da gunki yake magana
Daddy yace" my son "

Amma shiru, cikin tsawa yace  "ahmad!!"

Azabure yajuyo har wayarsa tana faduwa, "na.. Na'a... Na'am daddy"

Daddy ya kalleshi da kyau yace "me yake damunka ne ka zauna kana tunani kai kadai?"

Ahmad ya shafa sumar kansa yace "Babu komai daddy"
Daddy yace "tashi kaje ka kwanta"

"To daddy gud night"

Yana fita daddy yakwala wa momy kira
"Hajiya! Hajiya!!"
Sai gata tazo, ta nemi waje ta zauna, "me yake damun yaron nan ne?"

Momy tace "alhaji halin ahmad fa ba'a iya masa, nan nasamu waje nazauna nayi masa nasiha, Amma kamar qara zigashi nake"
Daddy yace "cewa nayi me yake damunsa? Yazaku barmin yaro ya lalace haka, duk yafita a haiyacinsa, yaro me kuzari duk ya susuce,😃"

momy tace "alhaji kayi hakuri insha Allah zamu kiyaye
Amma ba komai ne yake damunsa ba, kaji kaji," nan momy tabashi labarin komai, daddy yace "kai halin ahmad ma saishi, to ai dasai yasamu wata kafin Allah ya baiyana masa wadda yake so din,"
momy tace "to nide namasa fada," daddy yace" shikkenan tashi kije zan sa meshi muyi magana," momy Takoma Dakin ta

** *** **

Ina jikin window ina kallan gajimare munyi nisa a tafiya, narasa yaya zanyi in manta dashi, koda yaushe yana cikin raina, ko menene dalilin sa na yaudarata?
Kome namasa dazai sakamin da hakan,?

"Ahmad kenan"

nafada abaiyane, watace a kusa Dani ta juyo ta kalleni, tace "sannu fa"
Nace "yauwa"
Daga haka banma qara kallanta ba

Daniyya yake tashi, yaqara gyara zaman sa, duk Dan yahangota kasancewar tana kujerar Gaba shikuma suna can baya, "kai Allah ya mallakamin wannan babyn," yafada aransa😃

Awa uku muka diba muna tafiya takai mu ga Sudan, muna sauka, mukayi yan cike ciken takardu muka futo daga airport din, wakilinmu ne yakawo mana motoci muka shiga, bamu zame ko ina ba sai gidansa, maza kuma yakaisu wani gidan daban
Munci abinci munyi wanka, daga nan kowa ya nemi wajan hutu
Inajin yan uwana Mata sunata firarraki Amma nide bana cewa komai, kawai tunanin su mama nake

Da daddare, yazo yace mu shirya muje asiya mana sim card, haka muka fita, doguwar Riga ce ajikina kawai Dan mayafin rolling din nayafa akaina muka tafi, ina kallan wannan yarinyar da muka zauna tare tanata kallo na, Amma na share ta
Wata mota muka shiga takai mu wajan, na daga kaina na kalli wajan naga ansa AFRA da turanci da larabci, muka shiga, muna shiga wani sanyin esi ya bugoni na lumshe ido nace "um duniya" 🤣

Bamu bar wajan da wuri ba kasancewar saida aka gamawa kowa, sannan muka tafi gida, daga nan kowa yasai kati, yayi mana bayanin yanda zamuyi amfani dashi, ina kwanciya nasa nawa, nakira su mama, husna ihun murna kamar Zata fasamin kunne
Da zamuyi sallama nasawa mama kuka, itama de daurewa tayi ta kwantar min da hankali, bayan nagama wayar nakashe ta na kwanta bacci kasancewar lokacin ba daya ne dana Nigeria ba

** *** **

Hannu ya miqa masa gamida sallama yace" Malam Dan Allah ko masu gidan nan kuwa sun dawo? "

Me shagon ya kalleshi yasake kallansa yace" Amma bawan Allah ko yan'uwanka ne wadannan mutanan yaci ace ka rabu dasu, kazo kazo, ance basa nan Amma kaqi hakura, haba"🤣

"To sun saida gidan, sun siyar shi, yanzu haka wani alhaji ne zai rushe wannan din yasake sabo"

Ahmad yace "to Malam na gode,"
mutumin yace "to Allah yatsare,"
yana tafiya ahanya aransa yace shikkenan tafaru taqare tabbas nasan narasa ta, narasa feenah

** *** **

"Gaskya musa wannan zaifi,"

"kai ahmad fararan nan zasufi kyau, Allah,"

"nikuma sai naga blue din zasufi yi mana kyau tahir"

Tahir yace "a a ranace ta farin ciki, Dan haka gaskya musa farare,"

"ok" kawai Ahmad yace, yadi ne fari ahmad ya dinka musu, yaji aiki mai tsada, fararan agogo, farar hula, da babbar Riga wadda taji aiki mai kyau, shikuma tahir ya dinka musu blue mai kyau, daddy ne yakira su yace to shi zai wuce, su idan sun Gama batawa kansu lokaci saisu futo

Aida sauri suka futo, masha Allah kowa yagansu saiya sake waigawa sunyi kyau sosai kamar asace su a gudu, sunzo harabar gidan, tahir ya daga wayarsa yace "my man kalla,"
ahmad yana juyowa tahir yayi musu selfie, sunyi mugun kyau, daddy dayake zaune a bayan mota shida driver aransa yace wadannan yara saisu, kuda ake jiran ku kune masu photo😃
kallansu yasake yi, kamar su biyu ne angwayan, shima ahmad inda ace tasan tana nan aida an hada anyi musu auren shida abokin nasa

Suna shiga mota driver yaja, sannan tawagar mutane sukabi bayansu

Amasallacin juma'ah aka daura auren tahir da husna bisa sadaki naira dubu hamsin lakadan ba ajalan ba, ango yaja ahmad suka sulale suka futo waje, ahmad yace " shikkenan de alkawari yacika," tahir yace "wallahi kuwa gwauro"
Ahmad yace "iyee yaushe akama auren dazaka fara min tsiya zaka sameni ne inde nine,"
abokansa ne su doctor Bashir duk sukazo suna masa tsiya wai y dauke musu dalibarsu, to daga yanzu sun dena nemansa,🤣 Dan kar yaga wata ya yiwa dalibarsu kishiya, haka sukai ta masa tsiya da fatan alkhairi suka juya gida
Tahir yakira husna yace yanaso yaganta kafin yatafi, Babu yanda ta iya haka ta cewa mama zataje su gaisa dasu tahir
Mama tace to ai nan akwai cikowar mutane kuje can gidan ammunku saiku gaisa anan
Anty maimuna ce mai cewa karde ki bari komai yafaru🤣🤣 husna tace to my anty

Duk inda tayi Ana ga amarya
Haka ta futo taje gidan Ammu, tayiwa su tahir din kwatance sukaje
Ruwa takawo musu da lemo suka zauna afalo, sannan ta futo domin su gaisa, dama a kace jini daya yafi karfin wasa, ahmad yana ganinta yaji gabansa yafadi
Duk Dade ba wata kama suke d feenah ba saide kama ta yan'uwan taka, bayan sun gaisa ne tahir yace " husna ga babban abokina aminina kuma dan'uwana ahmad," husna tace "au dama shine?"
Ahmad daya Zuba Mata ido yana kallan yanayin ta da muryarta kusan ta feenah yace "eh nine yakike?"

Husna tace "lafiya,"
yace "to alla yabada zaman lafiya," 🤣

daga haka yatashi yayi waje
Husna ta dubi tahir tace" my heart dama haka yake? Daga gaisawa sai tafiya?" Tahir yace" haka yake, dama budurwarsa ce tadan sauya mana shi, kuma yanzu basa tare shine yakoma halin sa nada, "

husna tace" Allah sarki, to Allah ya bashi ta gari"

tahir yace "amin,"

daddy ne yakira wayar tahir yana jiran su suzo su tafi, Dan haka tahir yamike ya yiwa husna sallama, harya fara tafiya dayaga de batada niyyar tashi yazo yatsugunna agabanta yakama hannun ta yayi kissing, yasake yi Mata akumatu sannan yafice da sauri, kunya tasa husna rufe idonta da hannun ta 🙈

Yana fita ahmad yace" gaye ka shanyani da yawa fa, kaje ka wani liqe Mata,"
tahir yace" to kasan masu aure, ai Baza ayi sallama Babu dan hugging ba bare kiss,"🤣

ahmad yace" nawan nema kake ka fitsare tun ba'a je ko ina ba, gara ma d Allah yasa agaban ummi zaku zauna," tahir yace" eh wlh banasan zaman nan Dan gaskya nafiso ina jina ajikin iyalina," ahmad yace" tahir kafi karfina muje daddy najira "
Awajan su daddy can masallacin da aka daura aure anan sukaga Abba, tahir ne yaja ahmad yace " ga Abba nan muje mu gaisa "

Sosai suka birge Abba yaji aransa dama ace duka su biyun surukansa ne, saide haka Allah yatsara, haka sukai sallama da mutane ko gidansu husna basu jeba suka tafi kano
Wasu daga ciki kuma suka dakata saboda daukan amarya

** *** **

Cikin kwana biyu aka nema mana gida awata unguwa mujahideen kusa da makarantar danake, an tambayeni me nakeso in ci Gaba da karanta kai tsaye nace inaso inci Gaba da Arabic dina, nan da nan kuwa aka kaini wata mkrnta Khartoum international instute of Arabic language, kuma inajin dadin karatuna kasancewar inajin larabci shiyasa wasu abubuwan basamin wahala Dana dawo daga mkrnta zan shige dakina nini kadai, inyi wanka inyi bacci idan Natashi kuma inyi karatu
Gida daya nake da wannan yarinyar damuka zauna da ita a jirgi, saide kowa dakinsa, kullum ta ganni zatamin murmushi tamin magana, nikuwa daga wajena bahaka bane

** *** **

Ankawo amarya lafiya ummi ta karbesu hannu bibbiyu, kowa ya yaba da part din husna, haka suka tafi suka barta, angwaye sun rako tahir inda ahmad yaja masa kunne Akan wallahi yabi musu yarinya a hankali, Dan shikam bai manta karan su da mutuniyar tasa ba🤣
Haka suka tafi suka barshi

Tahir ya umarci husna ta tashi suyi nafila saisu kwanta, gabanta yana dukan tara tara ta tashi

Mrs Usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

33

Toilet tashiga ta dauro alwala, suka gabatar da sallah, bayan yayi Mata tambayoyin daya yakamata, yatashi yakawo musu kaza gasashshiya ya tura Mata gabanta, ya tallabe kumatunsa da hannayansa guda biyu, yazuba Mata ido yana Mata wani mayan kallo, husna tace " ya haka?"
Tahir yace "um so nake kawai inta kallanki," murmushi tayi batace komai ba, Dan haka ya janyo da kansa ya yago kadan yace to Bude bakin inbaki, bakinta ta Bude ahankli yana kallanta yana bata saida ya tabbatar ta qoshi sannan yakyaleta shima yaci kadan, yadauke sauran yakai kitchen, yadawo Dakin tana nan zaune inda yabarta saide yanzu ta cire mayafin sabanin da data lullube jikinta dashi, idonsa yasauka Akan kirjinta yakasa dauke idanunsa yace Mata "ki shirya ki kwanta zanje wajan ummi, "
husna ta daga masa kai tana kallan idonsa inda yake gani daban kuma yana Mata magana 🤣

Tana gani yafita, tashiga cire kayanta, doguwar Riga marar nauyi ta dauka tasaka, takashe wutar Dakin tashige cikin bargo ta kwanta

Acan kuwa yana Zuwa ummi ta kalleshi da mamaki tace "a a ya ango da yawo cikin daren nan,"

tahir yace "ummi sha biyu saura fa shine daren?"
Daquwa tayi masa tace" toda da yanzu ba daya bane kaje ka kula da amanar da aka baka"
Tahir yace "to ummi dama saida safe zanyi miki," tace "to Allah yakaimu"

Yafice, yana Zuwa dakinsa yatafi ya shirya cikin kayan bacci, sannan ya koma Dakin husna, yana tura Dakin yaga harta kwanta, Dan haka shima ya kwanta agefenta, ya janye bargon data rufa dashi cikin rada yace Mata "amarya," tana jinsa tayi kamar bacci take, ganin ta kyaleshi yasa ya janyo ta jikinsa, husna tace " doctor bacci fa nake," yace "nasani nan dinma baccin zakiyi,"

yafara bubbuga bayanta, qamshin turaren datake ne yaqara fizgarshi har yahade bakinsu waje daya, daga nan labari ya canja

** *** **

Ina zaune afalo, da yamma, ina duba hand out, gajeran wando ne ajikina iyakarsa gwiwata sai vest, na daura dankwali kalar wandon jikina, da madara a gabana ta ruwa kamfanin kapo, wannan yarinyar cede tazo wajena tace "sannun ki"
Nadaga kai nace Mata " yauwa," tace "Dan Allah in bazaki damuba inasan Sanin sunanki,"

nace Mata "sunana nafeesa mu'az Amma feenah ake cemin"

Tace "nikuma Zarah Ali Bashir, ni yar kano ce, unguwar rijiyar zaki,"
nace "ok nikuma zaria"

Haka Zarah taitamin tambaya ina amsa Mata, har tace "a wanne school kike,"

nace Mata "ina jami'atul daulil Arabia,"

tace "no da English,"

nace "Khartoum international instute of Arabic language"
Tace "laaa ai kusa da makarantar mu ne,"

nace "ke kina ina?"

Tace "ina international University of Africa,"

nace "jami'ah ifriqiyya kenan?" Tace "yes"
Taci Gaba da cewa "nafara karatu a yusif maitama sule, dake kano to kuma dana samu scholarship saina barshi na dawo nan, kinsan kasar tamu lokaci kadan sai ace yajin aiki,"

nace
" hakane to Allah yabamu sa'ah"

tacemin "amin"
Tasake cewa "kina level nawa ne yanzu?"

Nace " level 2"
Cikin mamaki tace
" kamarya?"
Nace "eh ai nayi amfani da kwali na na diploma ne saboda haka sai suka bani direct level 2"
Tace "ok kinyi diploma agida"

nace "emana"
Tace "eh dama sunayin haka,"
"to Allah de yabamu sa'ah ni, ina level 1 yanzu"
nace "Allah ya temaka," tace "amin"

Cikin lokaci kankani Zarah ta shigemin dayake tanada surutu Dan danan tadinga jana da fira tun bana sake wa har yazamo nasaki jiki muna ta daria
Hakan yasa naji dadi Dan dama ina cike da kewar yan gida

** *** **

"Yi hakuri mana daure ki taka,"
tana yarfe hannu tana hawaye tace "doctor bazan iyaba,"

Dan haka yadauketa ya kaita toilet yahada Mata ruwan wanka sannan yafuto, shima Zuwa yayi yasake wanka, sannan yadawo Dakin yana zuba qamshi, lokacin tana zaune agefen gado tana shafa mai, kayanta yadauko Mata yazo yace " to taho insa miki," batayi musu ba ta tsaya, yana saka Mata Riga hannun sa yatafi yawo wani wajan hakan yasa tace "nide Allah nahakura kabani rigata,"
ganin idonta yaciko da qwallah yasa yace cikin murmushi "to naji saka, shikkenan?" ta gyada masa kai
kansa yasa atsakanin kirjinta yayi kissing sannan yace "natafi wajan ummi" 🤣

Yafice da sauri
Yana Zuwa part din nata yaganta tana hada break yace "ummi morning," tajuyo ta ce "Dan ummi har antashi?" Agogo ya kallah yaga 11:30yace" ummi yanzu ne har? "
Tayi murmushi tace" ashe kasan ka Dade kaima, kunata baccin gajiya najira Baku tashiba nace

to nide bari inci abinci na, ku kuma ga naku nan nagama hada muku yanzu, "tahir yace" to ummi thank you "
Dining yanufa yaci abincinsa ummi tana kallansa saida yagama taga yatashi tace" a a yanaga ka cika cikinka ita kuma husnan ko nemanta bakayi ba?"
Tahir yace" zanje in kira tane, "

girgiza kai kawai ummi tayi, yana Zuwa yaga tana fesa turare yaje ya janyo ta jikinsa, yace" muje kiyi break "tace" to"

suna tafiya a hankali kamar me koyon tafiya husna tace " Allah nide nagaji," tahir yace "yanzu yaza'ai,"
husna tace "kuma ni wallahi kunyar ta nake naje ahaka," tahir sabarta yayi ahannu suka tafi, husna tana "kasaukeni" yace "haba yarinya," saida sukaje har falon ummi tana ganinsu ta kawar dakai kamar bata gansu ba, aranta tace oh ni yasu wannan yara ko kunya, saida ya kaita har gaban ummi sannan ya ajiye ta, husna idonta aqasa tace "ummi ina kwana?"
Ummi ta shafa kanta tace "sannu husna ya gajiyar biki"
husna tace "alhmdlh," ummi tace "tahir kuje kazuba Mata abincin mana,"
cikin sauri tahir yace "a a ummi batajin dadi ne bari inkawo Mata nan," ummi aranta tace waini za'a yiwa wayo, oh tahir ko yaushe ma yagirma
Abincin yahada Mata taci Dan kadan, ummi tace "a a husna ci mana," tace "wallahi ummi na qoshi," tahir yayi qasa da murya ita kanta husnan taqyar takeji, yace "meyasa bazakici ba?"
Tace "bakina ba dadi doctorcc
Aikuwa ya daga murya yace" ummi wai bakinta ne ba dadi," husna kamar kasa ta zaqe ta shige Dan kunya, ummi tace" a a to ai sai Asa ayi Mata wani abin "
Me aiki ta kwalawa kira tazo cikin sauri, tace" dafawa husna ferfesun kaza medan yaji, batajin dadin bakinta,"🤣 me aikin ta juya cikin sauri

** *** ***

Alhmdlh anyi zabe lafiya angama kuma muhd marzuk mahaifin ahmad yayi nasarar samun kujerar daya nema, gida kowa yana farin ciki, shi kansa marzuk saida yazo daga masar shida matar sa baraa'ah tsoho mai ran karfe, gida yacika da yan'uwa da abokan arziki, su saudat da farouq duk sun zo
Ana ta zance kowa da kowa saide baraa'ah da bata iya hausa sosai ba itama tana kwabawa Ana daria
Amma ahmad yana danne danne awayarsa, marzuk ya kalleshi yace "me yake damunka ne abokina?" Ahmad yace" tsoho Babu komai "
Haka sukaci Gaba da firarsu, saida daddare bayan daddy da mahaifinsa sun kebe, anan daddy yake fadawa mahaifinsa abinda yake damun ahmad din, anan alhaji marzuk yace" to ni inaga abinda za'ai shine, zan yanke hukunci Akan hakan kafin natafi "daddy yace" to abeey "

** *** **

Muna zaune afalo dukanmu mu hudu Ana ta fira dayake weekend ne Babu makaranta, ina karanta novel awaya ta, Zarah tana gefan kaina zaune suma sauran biyun suna zaune , Zarah tace" gaskiya feenah kanki yaci tsifa," nace

" wallahi wannan makarantar ce tasa banda lokaci," kaina ta dora Akan cinyarta tace

" zona tsefe miki gobe sai muje wajan wankin kai," nace" ok," tanamin tsifa da hannu daya, kasancewar gashina yanada laushi dayan hannun tana chting
Kawai mukaji tasa qaran murna, dukanmu muka kalleta kowa yana tambayarta menene? tace wallahi yaci, inasan mutumin nan wallahi, MUHD MARZUQ sunci zabe
Aikuwa kowa yadau murna, gabana yafadi araina nace muhd marzuk, mahaifin su saudat kenan, bangama tunanin ba, naji daya daga cikin mutum biyun nan tace "ni wallahi dansa ne yake birgeni," 🤣
gabana yabada dam
Taci Gaba da cewa "har a Facebook ina dashi saide matsalar ba kullum yake hawaba, wallahi gayan yatafi Dani, ina sansa dama ya aureni, ya iya dressing, ga shiga mota kala kala,"

zarah ma tace "to ba dole yashiga motaba, shida a kace yanada kamfanin mota,"

sauran suka hada baki wajan cewa "kamfanin mota!!!" 😳

Zarah tace "eh wlh, ai kwanaki gwamnatin kano tayi bincike Akan kamfanin tana tunanin da kudin gwamnati babansa yabude masa kamfanin, saida akayi bincike sannan aka gano kakansa ne dayake Egypt yabude masa kamfanin"

Wadda tace tana sansa, tace "um kamfanin mota wallahi harna qaraji na tsunduma asansa" 🤣

Itama dayar tace "niko dazan ganshi ma kawai so nake muyi pic, Dan Allah sister da wanne suna yake amfani a Facebook?"
Ta tambayi yar'uwarta, dayar tace "da AM MARZUQ yake amfani, kuma nasan Dan kar agane shine yasa yake amfani da hakan
maimakon yabarshi a Ahmad muhd marzuk dinsa,"
Zara tace "tab aikuwa kema kinsan irin wannan ba ganinsu ake sosai ba," ta kalleni tace "feenah kinyi shiru," 🤣

cikin takaici nace "Tome zance nida ba jihar muba,"
cikin raina kuwa jinake kamar na shaqesu su duka, wai sunasan my Ahmad

Zarah tace "au gaskya kam bazaki sansu ba, suna da kirki sosai mahaifinsa kowa yana sansa,"

nace "uhm,nide karasamin tsifata" 🤣

** *** **

Tsoho marzuk ya kalli ahmad yace, "nayanke shawarar zamu wuce dakai Zuwa Cairo nanda kwana biyu, Dan haka kayi shirin komai kabar komai na kamfanin ka a hannun mutum mai Amana," ahmad daya rasa dalilin tafiyar yace "to Allah yakaimu," yatashi yatafi, marzuk ya kalli daddy yace "inaga hakan zaisa ya manta da yarinyar harya warware kamar da," daddy yace "abeey hakan yayi sosai shukran (na gode)" marzuk yace "afwan (you're welcome)"

** *** **

Tahir yace" inaga hakan yafi saboda mutumin yanada kamala, zai iya komai yanda ya dace", ahmad yace "toshkn," sakatariyar sa yakira yace takira masa hassan, Ammu yana shigowa suka miqe suka gaida shi, Ammu yace "haba menene kuma abin tashi?"

Tahir yace "to ai kai yanzu gaisuwa har qasa,"
Ahmad yace "tunda muna auren yarsa ba" 🤣

Dukansu suka sa daria
Anan ahmad yayi masa bayanin yanaso yabashi ragamar manaja na wannan kamfanin, saboda akwai tafiyar data kamashi Zuwa Egypt, Ammu ya dinga godia da kuma alkawarin kula da komai insha Allah, tahir yasosa kansa yace "aimune da godia Ammu," 😉

Ammu yace wa ahmad, "yallabai wannan sirikin nawa kaja masa kunne," 🤣 Yafice yana daria

Ahmad ya kalli tahir yace "to kai kaji,"
tahir yace "ah to ai gaskya ne, mune da godia bakasan abinda nake ji bane shiyasa" 🤣

ahmad yakai masa duka yace "wallahi bakada kunya"

** *** **

Next day, su ahmad shida kakansa suka Lula kasar Egypt

Mrs Usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

35

Tahir yajanyeta daga jikinsa yatashi ya zauna dakyau da wayar ahannunsa, husna ta dafashi tace "doctor lafiya?" Tahir yace "ai nasan wannan yarinyar," husna tace "Zata iya yiyuwa tunda anan tayi karatunta
Amma A'ina ka ganta?" Bai bata amsaba fuskarsa cike da mamaki yace "Amma tanada aure ne?"

Husna cikin mamaki tace "gaskiya bata dashi, wai a ina ka ganta?"
Doctor yace "Amma in hakane kamar ta baci, husna anya kuwa ba yan biyu bane su?"
Husna ta dafe kanta da hannun ta, tace "doctor please a ina kaganta?"

Yace "wallahi kwanaki aka kawo mana wata yarinya kamar de ita wannan din asbitinmu Zata haihu Amma kuma batada jini, cikin mamaki yaci gaba da cewa to ni dakaina naje nasa Mata jinin, Ahmad abokina shine ma yabata jinin," 🤔

gaban husna yayi mummunar faduwa,😳🙆🏻 karde feenah hospital din doctor sukaje lokacin haihuwar baby, Amma koma menene Zata tambayeta taji, tahir yace
" ya kikai shiru,"

husna aranta tace dole ne inrufawa auta sirrinta, tace cikin in-ina "gaskya ba... ba.. Ba'ita bace, kawai karatu tayi anan kuma taqi dawowa gida tayi zaman ta gidan kaka"

tahir cikin ko in kula yace
" ok shikkenan Amma gaskya kuwa dama nasan waccen yarinyar inkawo miki ita ki ganta"

Husna cikin faduwar Gaba ta kwanta akirjinsa ta rufe idonta alamun bacci duk Dan Yabar firar
😔

** *** ***

Waya nadauka nakira kb, cikin zaquwa ya dauka yace "my sweet feenah," nace "please kb inbaka wani Abu muhadu a ahadiqar siniya (wajan shan iska)"
Cikin hanzari yace "karki damu feenah karfe nawa?"

Nace "karfe biyar da rabi,"
yace "toki huta lafiya masoyiyata,"
nide kawai na kyaleshi nakashe wayar

Karfe hudu nagama komai, wandon jeans nasa nadora abaya akai, nayi rolling, inde ba wanda ya sanni ba, Babu wanda zai ce ni bahaushiya ce, Gaba daya na sauya

Biyar nafita, saida nayi tafiya mai nisa, har naje dede sharka-addal (kamfanin Mota na dal) sannan nasamu adedeta
Nahau muka tafi, naje na shiga na nemi waje nazauna, jakata na dauko nafitar da computer ta yar qarama mai kyau, na shiga ina duba lectures aciki, wani balarabe ne yazo yace " zai iya zama?"
Nace masa "maizai hana,"
Yama hanani karatun sai tambaya ta yake ina bashi amsa, yacemin "shima yana jiran habibiyarsa ne,"
nace " yayi kyau,"

Yace " kinyi kyau,"

nace masa "shukran,"

can saiga kb yazo, nace "masa "kadib" (wanda zan aura) yazo zan tafi," yana min daria yadagamin hannu, alamun bye bye

Waje muka samu muka zauna na fuskanceshi dakyau nace" kabir kasan me? "

** *** **

" Gaye ka koma kasar larabawa kayi zaman ka,"

ahmad yace" tahir bazaka ganeba wallahi nima Garin ya isheni,"

tahir yace" to ai kamar Yau ne zaka dawo, kayi hakuri na feenah "
Ahmad yace" kamar kasan kuwa lokacin ta ne yanzu kakirani, kasan fa kawai wannan lokacin

na ware Mata kawai na tunanin tane, yanzu haka photonta nake zanawa, Dan haka Malam sai anjima, ka kirani latter anawa lokacin,"

tahir yace"wallahi Baku isaba daga kai har ita, Allah inka kashemin waya ko hmm"
Ahmad yace "to naji me yake tafe dakai yanzu?" Tahir yace "kawai jinka zanyi," ahmad yace "to na gode ya madam? Ana nan anata fama ko?"

Tahir yace "wallahi," ahmad yace "to gaskiya inta haihu sunana ne na farko, ban yarda da wani suna na daban ba," daria tahir yayi, yace "kasan me? Kuma wallahi twins Zata haifa, jiya jiyan nan mukaje nayi Mata scanning, Amma ban fada Mata ba, Dan batasan yan biyu, kajifa rigima kamar ita ba yar biyun bace"
, ahmad yace " twins tahir, wow dama ace nawa ne, gaskya to Ana haifarsu zan qwace su,"
tahir yace "saboda mudin zubama ido zamuyi ba aure ko?"
Ahmad yace " kaga mubar zancan Dan Allah"
Tahir yace "serious nifa harna ma Mata ma, wallahi sister husna ce yarinyar ta hadu ba qarya, Dan gaskya yarinyar nan ko kaffara bazan yi ba, tafi feenanka duk da banganta ba,"

Ahmad yace " please tahir, gara ka kusheni daka kushe rayuwa ta, 😏😠saboda haka sai anjima"
dif ya kashe wayarsa, tahir yazubawa waya ido, yace "wannan yarinyar ba kalau ta barka ba ahmad, dole in tayaka da addu'ah" 🤣

** *** **

Hawaye ya share yace "wannan dalilin ne yasa bakya sona?
Menene aibu na danna kasance Dan gidan Dan siyasa?"
Feenah tace "kawai
Hakanan bana so"
Hannu ya miqo zai rike hannu na, na daga masa hannu cikin fishi nace " kb ya'isa haka, nafadama dalili na Dan haka toka kyaleni,"
nayi Gaba yabini da kallo kawai, afili ya furta "zaandau mataki, bazan iya hakura dake ba feenah"

** *** **

After 4 months, shaquwa ta da mukhtar sai wanda yagani, naje Dakin Zahra muna kallan film a computer, mukhtar yakirani, nadaga mukasha fira, ta zubamin ido tana kallo na, saida nagama tace "feenah Amma soyaiya kike keda wannan gayen ko?"

Nace "a a me kika ga,"

"gani nayi bini bini bashida aiki sai kiranki,"

nace "Zahra bahaka bane, kawai mutunci muke," tace to "koma de menene banga abinda wannan ustaz din zai gayawa kabir ba" 🤣

, nace "Zahra nabaki kb din ke," 🤣

Zahra tace "banasan kb, shima baya sona, Dan haka ki rike abinki," nunfasawa nayi nace "a bar maganar to," nan mukaci Gaba da kallo

** *** **

Mama na wanke wanke taji sallama, ta dago da mamaki tace "husna, kune atafe?" Husna tace "wallahi mama mune, kawo wanke wanken," mama tace "a a keda bake kadai ba husna jeki zauna,"
husna tashige daki kenan, tahir ma yashigo mama tace " au tare kuke dama?" Tahir ya Sosa kansa yace "wallahi tare muke mama,"
Mama tace "Amma wannan yarinya da shirme take, kuma shine taqi fadamin,"
tahir ya tsugunna ya gaisheta, tace "tashi ka shiga ciki mana,"
shima yayi ciki, mama ta qarasa falon suka sake gaisawa, tace "kuma Zuwa Babu sanar wa husna," husna tace " mama kawai fa dama ganinku zanyi,"
mama tace "to ai kinganmu saiki tashi kukoma," husna tace "kai Dan Allah mama,"

mama tace "yanzu tahir shine kaima ka biye Mata kuke yawo a wannan kamar tata?"
Tahir yace "mama dama mun shirya zuwan, kawai fada ce bamuyi ba,"
tace "to sannun ku Mungo de,"

tashi yayi yafita
Husna tace " mama ina baby?"
Mama tace "na siyar ta, ke yar karar da iyaye suke yima bakya yi, 😀to tayi bacci karkuma ki tadar min yarinya a bacci,"
husna tace "to bari in ganta kawai,"
aikuwa tana shiga Dakin taga izdihar anbaje Ana bacci ga window abude, husna taje taja kafarta a hankali, aikuwa baby aka Bude ido, tayi fici fici da ido tana kallan husna, husna akasa daria ta meqa Mata hannu tace

" baby na zonan,"
izdihar taqi meqa hannu, husna ta dauketa, suna Zuwa falo kuwa tana ganin mama ta rarrafa da sauri tayi wajan ta, mama tace "yanzu husna saida kika tashi yarnan, nasamu tana baccinta,

kin ganta nan batada aiki sai bari, Gaba daya halin nafeesa ta dauko, haba tun yanzu inta fara wasa ta zubar da ruwa akofi, ta wargaza tsintsiya, rannan ma cajar abbanku tasa abakinta tana sha, gashi cajar na jikin socket, haka Yai tamin fada ranar, nikuma shaf banma kulaba wallahi,"

husna tace" lalle baby to mama kawai ki bani ita,"
harararta mama tayi, suna wannan firar almajirai suka shigo da kaya niqi niqi, su katan din lemo dasu kayan shayi, sai uwar alawa wai duk na baby ne, tahir ne ya shigo mama tace
" kaikam baka gajia da kashe kudi ko tahir," murmushi yayi, yace
" mama ai ba yawa kayan baby ne"
Muqullin motarsa ya karkada wa izdihar yace" fine girl, zonan, "

husna tace" hmm nima kaga daga wajena ta gudu," hannu ya miqo zai dauketa aikuwa ta qanqame mama tasa kuka, mama tace" nikam ku tashi ku tafi gidanku, subarmu mu biyu ko izdihar, mama taci Gaba da cewa maimuna fa ta haihu jiya, kinji haihuwar?"
Husna tace" gaskya bansaniba, kuma shima Ammu bai fadamin Ba," mama tace" a a ai ita yakamata tafada miki ba Shiba, "husna tace" zansa meta ne, idan mun koma yanzu saimu shiga ta wajan ta," mama tace" yakamata de kam, ta haifi namiji, yace ma sunan babanku zaisa," husna tace cikin daria" to Allah yaraya Abba," tahir yace" amin," mama tace
" kuma Abban naku ma baya nan, yaje kaduna, da yasan zakuzo shima nasan ba inda zashi,"
husna tace" inna dawo wani satin ma gaisa," tahir ya dago da sauri ya kalleta, mama tace" uwar sakarci sai kinzo "🤣

Sun Dade agidan mama sannan wajan yamma suka tafi

** *** **

Mun futo daga makaranta kamar kullum nida mukhtar muna shan fira, yace" nahau adedeta akaini gida, "
nace masa" a a kawai muje aqasa," muna tafiya muna firar makaranta da abinda ya shafi karatu, har mukazo inda zamu rabu, nace masa" to ngd da rakiya, zan wuce gida,"

saide da alama hankalin mukhtar baya tare Dani, kawai ya zubamin ido yana kallan Dan karamin bakina, saida na sake cewa" mukhtar "
da Dan karfi, gamida hura masa iska a fuska, sannan yacemin

" t...to..to..nafeesa, sai munyi waya, "

nace" Amma me yake damunka haka?" Yace

" karki damu Babu komai,"
kafada na daga, nace" to shikkenan, sai munyi waya, "

yana tsaye yana kallo na najuya nabi ta wata hanya , takusa da wani faculty of madecine (kulliyati dib)

Hannun sa yatafa, yana kallansu ta tsallaken kwalta, yace anzo wajan,

kb kenan

** *** **

" Wash doctor zan mutu,"

tashi tahir, cikin bacci yaji kukan ta, asukwane yaduro daga kan gadon, yace "subhanallah husna, sannu,"
bari in kira ummi,
Dagashi sai gajeran wando yafuto, duk ya rikice, da sauri ya qarasa part din ummi, ummi cikin bacci taji bugu bana hankali ba, da sauri tatashi ta Bude kofar, tace "tahir haihuwa ce tazo ko?" Tahir yace "eh ummi," tace "to muje," suna Zuwa yasa hannu ya tashi husna, yakamata har sunje kofa ummi tace "ahaka zaka tafi ne?" 🤣

Sai asannan yatuna da shigar datake jikinsa, komawa yayi da sauri yasa jallabia suka tafi hospital, suna Zuwa masu aikin dare suka karbeta, nurses din hanashi shiga sukayi Dan sunga gaba daya arikice yake, Babu daukan lokaci sosai husna ta haifi yarta mace, mai kama da tahir sosai, sauran nurses sunyi tunanin tagama saide nan su kaga tafara wata sabuwar naqudar,sunyi sunyi ta haihu takasa, saboda karfin ta yaqare, dole suka futo sukayiwa tahir bayani, nan yasa hannu, aka shiga da ita operation, ciki kuwa harda shi, sunyi nasarar ciro Mata wata babyn, itama Babu abinda ta dauko na husna, komai na tahir ne, saida aka musu wanka aka gyara su cikin kayansu, anan ne zaka tabbatar identical twins ne
Husna Dakin hutu aka kaita, yaran ma aka kaisu wani Dakin, ummi kuwa baki yaqi rufuwa Yau itace da jikoki har biyu,🤣 Allah abin godiya,

Kafin gari ya waye tahir yabaza labari ko ina, husna ta haihu, yadauki pictures din yaran yayi ta turawa, ahmad murna kamar shi akayiwa haihuwar, feenah kuwa kuka tasa, da mama ta kirata tafada Mata, wannan takaici dayawa yake,🤣 aure bata nan, haihuwar ma bata nan,🤣 gida suka dawo inda tahir yaci gaba da kula da matarsa, Jikin nata kuma yana warware wa a hankali, dangi kowa yazo ganin husna da yara, sati na zagayowa yara sukaci sunan ummi da mama, Amma Ana kiransu  mama da mima, mai sunan ummi itace mima

** *** **

After 1 year, ahmad yagama masters dinsa, kawai yana jiran result ne, yaqara kyau naban mamaki, yayi wani fresh, Jin dadi ya zauna, daka kalleshi zakasan yana cikin hutu, bashida wata damuwa saita feenah 🤒

Yaran husna suna tsaiwa yanzu, baby kuwa an girma magana take gwaranci, tana yawonta ko ina, yarinyar akwai kyau kamar ita tayi kanta, dole inde kaganta kaji tashiga ranka, mama bata Zuwa da ita gidan biki ko suna, saboda kowa yaganta saiya tanka, shiyasa saita dinga barinta amakota inzata fita wajan taro

Kamar kullum yauma muna makaranta akazo aka sanar yan ajinmu zamuje occation, akwai University din dazasu je Dan haka za'a hadamu muje tare, duk wanda yake so zai bada kudi, ciki kuwa harda makarantar su Zahra, haka ta dinga magiya Akan muje, to qasa biyu za'a je, wasu zasuje Uganda wasu kuma misra
Dan haka nacewa Zahra nide zanbi yan Uganda, dannaga sister na aysha datake can, danma itama munyi waya tace saura 1month Takoma Nigeria Gaba daya, Zahra ce tadinga yimin magiya Akan Dan Allah na hakura mu tafi Egypt din, itama tayi shige da ficenta tashiga cikin wanda zasu tafi

Babu yanda na iya, saboda Zahra nace na amince, saimuje Egypt din

Saimun hadu a egypt fans💃

Mrs Usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

34

Tsawon wata daya ahmad yadauka amasar, Babu abinda yake banda yawo sai kwanciya, sai

chting, dayaga de zaman Babu inda zai kaishi saiyayiwa kakansa magana Akan kawai yanaso yakoma gida, yarasa wannan tafiya ta mecece 🤣
Marzuk ya dubeshi yace" yaro man kaza, ai mahaifinka yafadamin abinda yake damunka, to nide daga cikin dangina Babu Rago, Dan haka banaso kasa tunanin mace aranka har haka yataba lafiyarka "
Ahmad aransa yace taba lafiya na nawa kuma?

Marzuk yaci gaba da cewa" Dan haka ma nayi magana da mahaifinka jiya zaka koma makaranta kayi master's degree dinka, "ahmad yadago kansa yace" kaka masters kuma? " Marzuk yagyada kai

** *** **

"Innalillahi, nikam wannan hand out din bana ganeta wallahi,"

ni kadai ina faman karatu a masallaci, wata yar Sudan ta dubeni tace " me kike fada?"

Na kalleta nace "wannan hand out din bana ganeta"

Saitace "mazai hana ki samu wani ko wata suyi miki bayani?"
Sainace "eh hakane," Natashi nafita
Ina fita naga wani Dan Nigeria nayi masa magana nace "da Allah ko zai iya yimin bayanin wannan hand out din?"
Yakarba yace "eto gaskya saide nahadaki da wani yayi miki" 🤣

Kai tsaye nabi shi, mukaje wani aji, yana zaune yana daddanna wayarsa
Kansa yasha gyara, yasa qananan kaya, wannan mutumin ne yayi masa magana, yana juyowa muka hada ido nagama ashe nasanshi Dan ajinmu ne
Bayani yayi masa Akan Dan Allah yayi min bayanin wani waje daban ganeba, baiyi musu ba yakarba, shikuma yamana sallama yatafi
Waje nasamu nazauna na fuskanceshi, nasake gaida shi, ya amsa
Hand out din na bashi, yace "a a rike, kawai ki dinga karantowa saina dinga yi miki bayani" 😳

Kallansa nayi da mamaki araina nace lalle me Abu da abunsa 😃
Karanta masa nake kamar yanda yafada, ya dinga yimin bayani filla filla, har saida yagama, nayi masa tambaya inda bangane ba, yaqara yimin bayani sosai, daga karshe nayi masa godia kuma na rokeshi Akan idan Babu abinda yake yi a irin wannan lokacin Dan Allah ya daure ya dinga yimin karatun, Babu bata lokaci ya amince Natashi na tafi

Cikin lokaci kankani nasaba da mukhtar, har cikin weekend da safe muna Zuwa makarantar yana min karatu, kuma sosai inajin dadi saboda dama ance ko kanada kyau to ka qara da wanka

** *** **

"Sis wallahi Yau, sha'awar bread nake da gyada,"

nace " lalle Zahra, yanzu ina zamu samu wata gyada?"
Tace "muje gaban jami'ah, Allah nagani," nace "to gaskiya kibari rana tayi sanyi sai muje"

Yamma nayi, ni har namanta ma, naganta ta futo ta sameni adakina ina kwance, tace " yanaga haka?"

Saida naganta na tuna, da sauri na shige toilet nawatsa ruwa, sannan na futo, abaya nasa, nayi rolling da mayafin abayar, muka futo, muna fita muka tsallaka titi, nace "to mu fara Zuwa musai bread din kawai
Me "raksha" (adedeta) muka tare, yakaimu Wani waje Tasamoh mukasai bread, daganan mukasai kayan miya da kaji
Muka wuce gaban jami'ah tasai gyadar sannan muka dawo gida, muna Zuwa muka zube afalo nace "wallahi kin gajiyar Dani"
Tace "to yanzu ba shikkenan mun huta ba"
Nace "hakane," sauran yan gidan mune su biyu suka mana sannu dakyar na amsa nide,🤣 Dan har yanzu ban manta ba da cewar sunasan my ahmad, "feenah lafiya kuwa kika amsa da kyar?"
Nace "wallahi gajia ce kawai," basu kawo komai aransu ba suka yarda

Sau dubu zan kirasu mama awaya mu gaisa haka sau dubu zan manta da baby
Duk da yarinyar tana raina Amma kuma wani lokacin sai naji raina yana baci Akan ta itada mahaifinta
Yauma da daddare nakira su mama muna Gama waya nace to saida safe, mama datake kusa tace "Amma auta ke mahaukaciya ce ko?" 🤣 🤣
Nace "na shiga uku mama me nayi kuma?" Tace "Amma ko dabba kika bari agida aikya na tambayarsa ko ya yake ko?"
Qasa nayi da kaina kamar tana ganina nace
" mama kiyi hakuri"
Tace "a a bani zaki bawa hakuri ba nafeesa, gyarawa nakeso kiyi
Yarinyar nan ba itace tayi miki laifi ba Dan haka banasan shirman banza" , nace "to mama kiyi hakuri, ki gaishe ta." 🤣

Haushi yasa mama kashe wayar ta wai ki gaishe ta, Babu irin tafara zama,? tana daria?Babu

komai, Allah ya shirya😃

Husna nakira mukasha fira, har tanamin tsiya wai tunda na tafi bantaba turo Mata pictures dinaba, nace tayi hakuri zan turo Mata idan nasamu lokaci nayi

** *** **

Kamar kullum yauma na shirya ina tafiya zanje school dayake ba nisa akafa nake tafiya saide idan na gaji ne zan dawo a adedeta
Kawai sai ganin mutum nayi a gabana, cikin sauri naja baya, nace" subhanallah Malam lafiya? " Yana sakin murmushi yace" wallahi tun ranar da kikazo Garin nan nake nemanki bansameki ba sai Yau, kamar wasa naga giftawar ki," nasake kallansa da mamaki nace" kamarya tun ranar danazo? Kasanni ne?"
Yace" sosai ma, ai tun acikin jirgi naganki kuma daga nan naji ina bala'in kaunar ki "
Nakalleshi dakyau nace" to na gode, Amma inada wanda nakeso kayi hakuri, "ban jira amsar sa ba nayi Gaba
Ina Zuwa gate din makarantar mu nayi shige wata, makarantar ya kalla yayi murmushi yajuya

Kabir yusif Bala kenan, da ne awajan tsohon gwamnan katsina, yana karatu a bangaren kimiyya, bayaji kwata kwata, akwai shi da harkar hutu, yana sakarwa yanmata kudi inde zai huta dake, baya shaye shaye saide neman Mata kawai, yana zaune awata unguwa mai suna balabil, gida aka kama masa shi kadai, kullum cikin kawo yanmata yake, Yau shine da waccan gobe shine da waccen, kwatsam yazo gida hutu ahanyarsa ta dawowa yaga feenah, tunda ya dora ido akanta yaji duniya Babu wadda yake so sai ita, shifa inde Akan feenah ne to zai iya rabuwa da kowa

** *** **

Acan misra kuwa ahmad yamiqa takardunsa jami'atul azahari, cikin sa'ah da nasara yafara karatun master's dinsa dayake ba kullum suke da lecture ba, saide yadawo gida yayi ta karatunsa, saide har Zuwa wannan lokacin tunanin ta yana ransa, har lokaci ya ware musanman na tunanin tane, idan lokacin yayi har fara'ah yake, haka zai kwanta shi kadai yana magana kamar tana gabansa, hakan dayake shine kwanciyar hankalinsa

** *** **

"Haba yata ki dinga aiki ke kadai, bakya gajia," husna tace "ummi Babu komai ai aikin baida yawa"
Ummi tace "to na aiki yarinyar nan me aiki, bari ni indora girkin kafin ta dawo,"

husna na wanke wanke, ummi ta dauko albashi tafara yankawa zatayi jalop, kamshin albasa na tashi husna ta to she hancinta, kafin ummi tayi magana sai amai
Aida gudu ta qarasa toilet din dayake falon taita amai sai kakarin amai take, ummi tazuba Mata ido tana kallan ikon Allah, ba shakka yarinyar nan ciki gareta, ummi tai murmushi tabita toilet din,
Husna ta dafe kanta, ta juyo kenan taga ummi ta qaraso, tace " sannu husna, me yake damunki ne? "
Husna cikin jigata tace" nima bansaniba ummi "

Ummi ta kamota suka dawo falo, tace" kwanta akujera ki huta, ko nakaiki daki? "
Suna wannan jayaiyar tahir yashigo
Yace" ummi me yake damunta "
Ummi tace" a a tahir ai kaine likita, kai zan tambaya, "🤣 🤣

tahir yace Mata" sannu "

Tace" yauwa,"

" me yake damunki? "

Tace" zuciyata ce take tashi banasan Jin kamshin albasa saikuma kaina kadan"
Yace "to sannu tashi muje nabaki magani kisha," 🤣

ummi tace "a a wanne magani? Kaga muje asibiti,"

tahir shide Gaba daya kunya ma yakeji Dan yasan abinda zai biyo baya
Dan haka yace "ummi Dakin barta inta Dan huta saimu tafi," 🙈

ummi tace "a a mutafi"
Ba yanda ya iya haka yakaisu asibitinsa gwajin farko kuwa sakamako ya nuna tana dauke da Juna biyu
Nurse din tazo har office dinsa tasamesu tace

" doctor congratulations madam na dauke da Juna biyu,"
husna ta dago cikin mamaki suka hada ido da tahir ya kashe Mata ido daya, ummi kuwa baki yaqi rufuwa, nan take ta cire zobenta na gold tabawa nurse din, tace "to tasheta ka maida mu gida" 🤣

Tahir yaqi hada ido da ummi ya cewa husna" to tashi mana "
Ummi tace" kamata mana sai wani sunkuyar dakai kake kamar munafuki "🤣

** *** **

Cikin wata biyar danayi a Sudan nashaqu da mukhtar sosai
Dan takai yanzu kullum sai munyi waya dashi kokuma chting
Haka kb duk inda yasan ina nan to sai yazo wajan
Kamar Yau ma munshirya zamuje taron graduate na wata makaranta ahfat, munyi kyau Sosa nida Zahra, atamfa mukasa sai Dan qaramin mayafi da muka dora a kafada, inajinshi yana "feenah
Feenah pls ki tsaya mana" ,najuyo nace
" kabir, Dan Allah ka kyaleni na huta, haba nacema karabu Dani, kaqi ji ya kake so nama?"
Yace "so, shinakeso kibani"
Bai qarasa magana ba nayi Gaba abina, gabana yadawo ya tsugunna a gabana ya hade hannayansa yace " pls feenah"
Aifa nan kallo yadawo kanmu Gaba daya mutane aka zubamin ido
Harda masu dauka awaya, ganin saurayi maitashe, wanda aka sanshi, ya tsugunna agabana, raina nabata nace " miye haka kabir?

Kabari zamuyi magana daga baya," yace "kinyi alkawari?" Nace "nayi"
Aikuwa duk inda mukayi anata kallo na, Dan haka nacema Zahra gaskiya mutafi, nikam atakure nake
Tace "eh kawai mutafi, kinga akwai Dan nisa daga umdurman Zuwa Khartoum,"

muna tafiya ahanya Zahra tace "nikam feenah, meyasa bakya San kula kb?
Yana sanki sosai, kuma na tabbatar idan kin saurareshi watan wataran zaki soshi, inma yanzu bakya sanshi"

nace "Zahra bazaki ganeba," tace "to ganar Dani," nace " bawai sansa ne ba nayi ba, shidin Dan gidan Dan siyasa ne"
Tace " to menene danya kasance hakan? Kina so kicemin bakya San yayan yan siyasa?"
Nace "Zahra mayaudara ne, basuda adalci, dana saurareshi zaici mutunci na yatafi,"
tace "haba feenah kiyi tunani mana, menene aibun yan siyasa?"
Nace "still bazaki ganeba Zahra, kawai mubar maganar"
tacemin "Toshknn" dahaka muka qarasa gida

Da daddare ina kwance adakina ina tunani, araina nace bazan iyaba, bazan iya sake afkawa cikin wani tashin hankalin ba, ahmad ya yaudareni, daga karshe ma wata qasa yatafi kamar ya yiwa kiyashi laifi, wannan ma idan na saurareshi hakan ce Zata kasance, zan fada masa gaskya bazan iya hulda dashi ba, baby ce tafado min, afili nace

"nasan yanzu kina rarrafe baby, ko ya kike yanzu,? Inasan ganinki, inasan Jin duminki ajikina"

da naga tunanin bazai kaini ba, kawai saina hau chting, aikuwa naga anty husna online, pictures din da mukai dazu awajan taro nida Zahra natura Mata, nace me ciki, ga pictures din nan yaude sai ki barni nahuta, pictures dinane masu masifar kyau natura Mata, adaidai wannan lokacin kuma wayar na hannun tahir husna tana kwance ajikinsa text din yashigo wayar, yace

" Mata maman twins ga text nan auta ta turo miki,"

husna tace "nide banasan sunan nan,"

ya bubbuga bayanta yace
" to sorry baby nadena,"

tace "Bude mugani,"

aikuwa tahir yabude, yana budewa yaga pictures din, husna tace
" wayyo auta wallahi tasake fari kalli kagani doctor,"
tahir yana kalla yasake Bude idonsa yace

"wai shin wannan itace auta?"

Mrs Usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

36

"Anty husna albishirinki," husna tace "goro auta,"

"wallahi ingaya miki zamuje misra," husna cikin mamaki tace

" misra?"
Feenah tace "eh wlh," anan de tabata labarin komai, husna tace "ok nagane to Allah yakaiku lafiya auta
Yaushe zaku tafi?"
Nace "cikin satin nan insha Allah," tace

"to Allah yakaremin ke auta," nace "amin sister"
Husna tace "yauwa feenah, nikuwa lokacin haihuwar baby wanne asbiti kuka jene?"

Feenah tace "gaskya bazan iya tuna sunan asbitin ba, Amma menene yafaru?"

Husna tace "wallahi pictures din da kika turomin rannan doctor yagani yacemin wai yasanki, wai kin taba Zuwa asbitin su, kin haihu
wai bakida jini ma lokacin haihuwar, abokinsa ne yabaki, to Amma nide nace masa gaskiya bake bace, saboda abinda yafara tambayata shine kinada aure nace masa bakida, tunda keda bakida aure tayaya har zaki haihu, anan de yake cemin Amma kamar tayi yawa idan bake bace, shine nakeso na tambayeki ko kinga wani likita aranar? "

Feenah ta numfasa tayi wani murmushi mai ciwo, tace " eh washe gari, lokacin kaka tashiga toilet tabbas akwai likitan daya shigo Dakin, lokacin ina shayar da baby, Amma gaskya yanzu de namanta shi,
Ko zaki turomin pic din mijin naki, in gani ko shine mutumin dana gani?"

Husna tace "zan turo miki insha Allah,"

"OK" inji feenah, dahaka sukai sallama
, wayar ta wullar agado, tace "ahmad ka cuceni, ka lalatamin rayuwa, har tunanin mutumin dazan aura nake, tayaya zai fuskanci bayanin dazan masa?

** *** **

Kice " mama,"

" ma.. ma..",

" yauwa yata to kice Abba, "

tace" ab-ba,"

" yauwa izdihar
To kice Ammu"

tace "am.. Mu,"

"yauwa yata"

Abba dayake kallansu yace maman nafeesa karfa kuso kanku, su kuma iyayen natafa ba za'a koya Mata sunan suba? 🤣

Mama tace " rabu da wannan iyayen nata, ai suma basa 'ya da ita,"

Abba yace " a a yazakice haka, bayan husna tayi tayi dake kibata ita tahadasu dasu mima, Amma kinqi,"
Mama tace "wallahi alhaji, husna ce me nemanta kawai, kaga auta, koda munyi waya bata neman yarinyar nan kwata kwata, nima shiyasa ko sunanta ban koya Mata ba, Amma ai tasan husna,
Izdihar kice anty husna"
Yarinya kuwa tafada🤣mama tace "yauwa, suma wanda basa sonmu suje can suyi zaman su ko?"
Baby ta daga kai, duk da batama San abinda ake nufi ba

** *** **

Agajiye yashigo gidan,yana sanye da suit baqa, rigar cikin fara, yana, Zuwa yafada jikin matar kakansa, ummi bara'ah tace" wallahi zaka karyani,"
Ahmad yace" shikkenan sai kaka ya auro wata," ranqwashi takai masa, da sauri yadagata, yace" gaskya dole kaka yasake sabuwa, "yafada yana gyara kwanciya Akan cinyarta, kansa ta shafa tace," zan kuwa koraka kasarku," ahmad yace

" wallahi Dakin temakeni, na gaji da zaman nan," data gane so yake yatafin sai tace" aikuwa zama daram, anan zamuyi ma Mata,"
ahmad yace" aiku kishi ne daku larabawa, dasai in yarda kuyimin auren," bara'ah tace" gaskya mukam bazamu yarda kahada yarmu da wata ba," ahmad yace" to ai kinji nikuwa inasan na auri Mata hudu,"

bara'ah takai masa ranqwashi tace" kai tafi can Rago, jinake mace daya ce tasa duk ka sauya," ahmad ya sauya fuska yace" to shikkenan naji abar maganar" yafada yana lumshe idonsa, tace "eh de saina fada din," kansa taci Gaba da shafawa, jimawa kadan tana dubansa taga yayi bacci

** *** **

Juyowa tayi ta kalleni tace, "sister wallahi murna nake, zan fita wata qasar, ban taba tunanin Sudan dinma zanzo ba, Amma gashi zan sake fita wata qasar," kallanta nayi, lokacin danake daura belt dina, nace "Zahra kenan, ki godewa Allah, nasan duk tsiya mahaifinki yafi nawa komai da komai, nice yakamata nafadi wannan maganar," Zahra tace "to Allah yasaukemu lafiya, Amma feenah ko sau dayane, inaso kiban labarin ki, koda yaushe idan namiki magana Akan Abu, to sai naji kin kawo min wani abun daban, wanda yake sani cikin mamaki," kallanta nasake, lokacin jirginmu yafara tafiya aqasa, ina daukar video, nace" Zahra kenan, insha Allah wataran zan baki inde labari ne, "
tace" toshkn,"
video nakashe, najuyo nace" Zahra,"

Tace" na'am, "
nace" gaskya ayi video," aikuwa ta matso mukai ta video muna shirmanmu iri iri, ahaka har kowa yagaji

Karfe uku na yamma muka sauka agarin, kasan cewar ba dadewa zamuyi ba, kwata kwata sati daya zamuyi, Dan haka aka kaimu wani hotel mai kyau da tsada, awata unguwa Alqaddamiyya , kowa dakinsa, Amma nida Zahra mukace abarmu adaki dayama ya isa, sukace bazai iyu ba, haka qa'idar take, dole muka rabu, Amma Zahra kulle nata Dakin take tadawo nawa muyi zaman mu

Duk wani Abu da ake buqata anyi mana, washe gari aka fara fita damu waje waje, har gidan tarihi ankaimu
, ahaka har muka kwashe kwana hudu
Akwana na biyar dinne a kace za'a kaimu wajan tarihi na irin gidajansu nada, daga nan kuma zamu wuce yawo, wajaje daban daban,
Tun bayan sallar asuba bamu koma bacci ba, muna ta shiri nida Zahra, doguwar Riga nasa gown light blue, ta kama jikina tamin daidai, daga kasan kirjin akwai dutsuna ajikinta, daga kasa kuma rafa ce, sai daga bayanta kuma net ne akai ado dashi, ina tafiya net din yana Bina abayana, sai mayafin rigar shikuma nayi rolling dashi, sosai nayi kyau, hips dina yafuto sosai akayan, Zahra tace "wow feenah kin hadu kin hadu kin gaji da haduwa, 🤣
keba mekyau bace feenah, kece shugabar kyawawan kawai,"

nace" Zahra kin isheni, Allah zan yi Gaba  nabarki,"
Zahra tace" to naji jarababbiya,"

itama tashiga shiryawa

** *** **

Cikin sauri yafuto, daga daki, ya yiwa kakansa kiss tare matar kakansa ummi bara'ah, yace

" sabahul khair ya jaddy wa jaddaty, "

suka amsa masa cikin fara'ah, yahade cikin suit mai launin ash colour
, shima zama yayi,yafara break, bayan yagama ne marzuk yace "yakamata yaje wajan mutumin nan, Dan yaga motocin, yanaso idan zai koma Nigeria yatafi dasu, tunda manaja yace Ana neman su sosai," kada kai ahmad yayi, yana Gama cin abinci, yashiga motar sa qirar Benz s550 yafita da sauri

Adede wannan lokacin muma mun futo muna cikin bus, muna tafiya, Zuwa inda zamuje
Munzo daidai wata danja motar mu ta tsaya, muna jira abamu hannu

Haka shima Adede lokacin danjar ta tsaida shi

Zahra na kalla nace "kai Zahra zafi,"
ina kusa da window Dan haka kawai na Bude window, adaidai lokacin ahmad ya kalli agogon hannun sa ya furzar da iska, yace "wannan zasu batamin lokacin"

Kamar ance musu sujuya su kalli Juna, tana juyowa damanta tayi tozali dashi, shima yana juyowa hagunsa yaganta, gaban feenah yayi mugun faduwa, hakance ta kasance awajansa, da sauri ya nuna ta da yatsa yace "feenah"

Bazai iya manta wannan fuskar ba, shide burinsa da fatan sa kawai shine ta yafe masa, inde ta yafe masa, to shi yaji ya yarda saiya hakura da nemanta

Kasa dauke idona nayi akansa, yagirma, yaqara zama cikakken mutum, Zahra tanamin magana taga de hankali na baya kanta, ta juyo taga inda nake kallah, aikuwa tana ganin ahmad
Cikin daga murya tace "laaa ga AHMAD MUHD MARZUQ"
Aikuwa duk yan Nigeria dasuka sanshi, aka juyo yuuuuu Ana kallansa, Mata kuwa nan suka fara daga masa hannu, wasu suna "ahmad, ahmad, ahmad," wasu kuma suna "A'M marzuk," kowa da abinda yake fada, wata tace "pls zamuyi pictures,"
"ahmad hi," wasu suna "hello ahmad,"

Shikuwa idanunsa suna kanta, sauri yayi yafuto daga motar, yazo jikin motarsu yace "feenah,"

hade hannayansa yayi, yana fadin "feenah, feenah ki amsa mana"

Nikuwa zuwa yanzu ina kuka yaci karfina, cikin kuka nadago kaina, nadake duk da gabana yana faduwa nace "Ahmad"

Ahmad yace "feenah kece?"
"feenah,"

nace "nice ahmad, bakaso kaganni araye bako?"

Zahra tazama photo tana kallona, dama nasan shi 🤔

Sauran yanmata kuwa ganinsa a kusa da bus dinmu nan suka fara selfie, dashi

Hannu aka bada, nan bus dinmu tafara tafiya, ahmad yana bin motar da sauri, har yadawo yana bin motar da gudu yana Kiran
" feenah! Feenah!! Feenah!!! Ki tsaya kiji feenah"

Har motar tafara masa nisa, nikuwa kaina na sun kunyar ina kuka, Zahra kuwa saboda mamaki ma takasa min magana

Ahmad kuwa yana Kiran
" feenah fee... Feen... Feenah," nan numfashinsa yafara sama, nan da nan yafara tari, yariqe gefen da zuciyarsa take yafadi awajan

Mrs Usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

37

Kuka nake Sosai tamkar raina zai fita, Zahra ta janyoni jikinta tana Dan bubbugamin bayana alamar inyi shiru, ta sunkuyo daidai kunne na, tace "feenah kiyi hakuri kidena kuka, kar hankalin mutane yadawo kanki kuma yanzu"
, cikin kuka nace "Zahra wallahi ina sanshi

Inason ahmad Zahra, yaya zanyi da son danake masa acikin zuciyata?
Ban taba Jin inasan wani mutum ba kamar yanda nake sanshi Zahra"

Zahra tace "to naji kiyi shiru haka, zamuyi magana daga baya"
Awannan ranar haka na wuni sukuku
Babu abinda nake sai aikin tunani

** *** **

Dasauri wani driver yazo yatemaka masa, yakai shi wajan motarsa, Gaba daya baya cikin hayyacinsa
Mutumin yace "kwatanta min gidanku muje"
Amma ina ahmad yakasa magana kawai de yarike kirjinsa da hannun sa

Mutumin yarasa ya zaiyi, Dan haka cikin sauri yakaishi asbiti, kafin suje ahmad baya motsi
Suna Zuwa likitoci suka karbeshi, suka shiga bashi temakon gaggawa

Wani tunani mutumin yayi, Dan haka ya duba wayar ahmad dake hannunsa
Number yagani ansa daddy
Bai lura da number misra ce kota wata qasa ba kawai yakira

Daddy nadagawa yace
" hello my son"
Mutumin cikin harshen larabci ya yiwa daddy bayanin komai, Allah ya rufa asiri daddyn yanajin yaran 🤣

Godia yayi masa, yakira babansa, marzuk naganin kira yace "Muhd  bakada kara, 🤣to inde ahmad ne cikin month din nan zai dawo "

Daddy yace "abbey bahaka bane,"
nan yamai bayanin komai ciki harda sunan asbitin
Gaba daya marzuk Yama rasa ina tunanin sa yake, bara'ah tana tambayarsa lafiya kawai shide yace" Mata futo mutafi"
Driver ne yajasu sai asbiti

** *** **

Har muka koma hotel din da aka saukemu Zahra bata cemin komai ba, kawai ta barni ne in samu kwanciyar hankali, hakika ta tabbatar ko menene yashiga tsakanina da wannan mutumin

babban al'amari ne
Tunda nide nace banasan yan siyasa

Haka dazamu ci abinci ma, hakuri tayi tabani Akan naci, dakyar de nadaure naci kadan, koma menene akwai lokacin dazata tambayeni

** *** **

Gumi ne yake sake futowa bayan wanda yake gogewa duk kuwa da sanyin esin dake tashi a office din doctor din, bayan yagama Jin bayanin da likita yamasa, marzuk yayi masa godia yafita
Dakin da ahmad yake ciki nan ya koma ya tarar dashi, yana bacci, ga qarin ruwa anyi masa, bara'ah tana zaune agefensa, kujera yasamu ya zauna, yariqe hannun ahmad tare da rafka uban tagumi

Bayan wani lokaci ahmad yafarfado, a hankali yabude idonsa
Yakallesu, marzuk yayi masa sannu, bara'ah tafita ta kira doctor
Yazo yadubashi yace zasu iya tafiya, Amma Dan Allah a dinga kula dashi sosai

Bayan sun dawo gida, dakinsa suka kaishi, aka hada masa shayi, yasha tare da magani, bara'ah ta rufa masa bargo tafita
Shima marzuk din futowa yayi bayan yaga ahmad din yafara bacci

Falo yadawo ya zauna, bara'ah ta dubeshi tace "me yake damun ahmad ne? "
Anan marzuk yayi Mata bayanin komai, tace
" subhanallah, yanzu yaya za'a yi?"
Marzuk yace" ni kaina bansaniba "

Kiran daddy ne yashigo wayar sa, yadauka bayan sun gaisa ne yake tambayar jikin ahmad din, marzuk yace" jiki da sauqi, idan yatashi zan kiraka "
Daddy yace" to abbey "
Momy ta dubeshi tace
" me yake damun waladeey na," tafadi haka cikin damuwa
Daddy yace" nima bai fada min ba, Amma yace idan ahmad din yatashi zai kirani "
Momy tace" to Allah yasa de lafiya, "daddy yace
" amin "

** *** **

Bayan kwana biyu, su feenah sun Gama komai, sunyi pictures dayawa awajaje daban daban
Haka suka koma Sudan cike da kewar Garin masar domin kuwa yayi musu dadi sosai

** *** **

Bayan sungama cin abinci, ahmad yasha maganin sa, marzuk yakira daddy, bayan sungama gaisawa ne, yahadasu dasu Momy ma kowa ya yiwa ahmad sannu
, tashi ahmad yayi zai koma daki, marzuk yadakatar dashi, yadawo ya zauna, marzuk ya cewa daddy, "muhd har yanzu ban fadama abinda yake damun ahmad ba ko, to kayi hakuri nabari ne yadan warware tukun na,"
Daddy yace "Babu komai abbey"

Marzuk yasa wayar a hands free, yanda ahmad da bara'ah duk zasu ji, nan ya yiwa daddy bayanin komai
Daddy yace "subhanallah
Bani ahmad din," marzuk ya kalli ahmad daya sunkuyar da kansa qasa, kamar munafuki yace "ai yanajin ka muhd"
Daddy yace" ahmad," ahmad yace" na'am daddy "
" Yanzu ahmad dama har yanzu kana wannan tunane tunanen Naka na banza da wofi?
Mu muna nan, muna tunanin kadena, ka warware, ashe bahaka bane?
Yanzu my son bakasan kwanciyar hankalin ka da namu?
Shikkenan kai bazaka dauki qaddara ba?
Yanzu badan anyi gaggawar kaika asbitin ba, kasan mezai faru? "
Ahmad yayi shiru
Daddy yace" ba tambayarka nake ba? "
Ahmad yace" a a daddy "

Daddy yace" toda tuni ciwon zuciya yakamaka," ahmad Dasauri yakalli wayar, yace" zuciya kuma daddy "
Daddy yace" qwarai kuwa, likita yace idan baka dena wannan tunanin nakaba, tabbas kana gab da kamuwa da ciwon zuciya
My son idan kakamu da ciwon zuciya bazan taba yafewa wannan yarinyar ba, domin kuwa dalilin wannan rashin sukunin Naka mutane dayawa, sun shiga damuwa

Abinda nakeso dakai shine, ahmad ba rarrashinka nake ba, kaci Gaba da tunani kaji,🤣 zamu fidda hannun mu daga dukkanin al'amarinka
Sai magana ta biyu, badai Akan mace ne kake wannan haukan shirman ba? Har kanaso ka kamu da ciwon zuciya, to bari kaji abinda zan fadama, kahada yanaka yanaka, ka dawo gida cikin satin nan, kuma duk yarinyar da naga tayimin zan aura ma ita, kaje can ka qarata, "ahmad yace
" daddy kayi hakuri, insha Allah bazan sake ba, " daddy yace" nagama magana ahmad, "

Marzuk ya karbi wayar yace" muhd hakan yayi, zai taho insha Allah," nan sukai sallama

Momy ta dubi daddy tace
" anya kuwa alhaji wannan hukuncin baiyi tsauri ba? "
Daddy yace" dole sai mun rage soyaiyar damuke nuna masa sannan ne zamu dawo dashi kan hanya hajiya
Duk mace macece, abinda wannan zatama, wannan ma zatama, illa iyaka wata tafi wata, hanyoyin da waccan tayi amfani dasu harya sota, itama wannan Zata iya,
Hajiya idan ya rabu da wadda yake so bawai shine bazai iya San wataba, Dan haka nagama magana inde nasamu yarinya aure zan masa, yin hakan shine zai taimaka masa wajan manta waccan "
Momy ta numfasa tace

" hakane alhaji, Allah yasa hakanne yafi alkhairi "
Daddy yace" amin "

** *** **

After one day, ina kwance adakina ni kadai, Zahra tashigo, na kalleta da murmushi nace" Zahra sannu da Zuwa,"

Tace "yauwa," tana tsaye ta jingina da bangon Dakin, ta kalleni kallo na tsanaki tace

" feenah inaso kiban labarin ki"

Na kalleta banga alamar wasa atattare da itaba, nace "zan fada miki Zahra, Amma idan kinyi alkawari zaki rikemin sirrina," Zahra tadawo gefena ta zauna, tace "inde wannan ne karki damu nafeesa, ki daukeni tamkar husna"

Zamana na gyara, na fuskanceta dakyau, nace "Zahra, mahaifina mai qaramin karfine ba kamar yanda wasu daga cikin mutane sukemin kallan yar me kudi ba,
Arayuwa tunda nake, ban taba kula kowanne saurayi da sunan soyaiya ba, sai mutum daya auwal, shima kuma halin danake nuna masa na ko in kula yasa ya rabu Dani, tunda ya gane bana sansa

Hawaye nafara, bandamu dana goge suba, naci Gaba da cewa zuwana kano yin karatu shine mafarin komai, nahadu da saudat.......

Anan nagama bata labarin komai, ina kuka tana kuka, rungmeni tayi ajikinta, tace "please

feenah yi hakuri, kiyi shiru"
Dakyar nayi shiru, na dubeta nace" Zahra, tayaya kike tunanin zan sake saurarar ahmad?
Mutumin dana yarda dashi, na bashi dukkanin Amana ta, nadauki son duniya nadora masa,
Zahra kuka nake ina tambayarsa yayi hakuri, idan wani laifin nayi masa yayafemin
Amma kamar qara zigashi nake"

Zahra ta share hawayen ta, tace "feenah abin kamar almara, yanzu feenah ke kin haihu, harma kinada 'ya mace"
Kallanta nayi nace
" Zahra, baby dakikaji ina cewa qanwata, ba qanwata bace 'yatace, nida ahmad Zahra,"
nakarashe maganar ina kuka, Zahra tace "feenah, Dan Allah ina neman alfarma daya awajanki, kiyimin wannan alfarmar koda kuwa itace karshan alfarmar dazaki min azamana dake feenah"

Nadubeta nace "inajin ki Zahra, wacce irin alfarma kikeso?"
Tace "feenah Dan Allah ki yafewa Ahmad"
Dasauri na kalleta, ta gyadamin kai, tace
" kiyafemasa feenah na rokeki "

Nace" meyasa? Meyasa zan yafe masa Zahra?"

Tace" alabarin dakika bani kince lokacin da abin yafaru, dakansa yadaukeki yakaiki asbiti, feenah kiyi tunani idan yayi miki haka da niyya bazai kaiki asbiti ba

Sannan kin barshi a asbiti baki bashi dama yayi miki magana koda guda dayaba

Sannan yana zarya agidan kakarki, kinqi bashi dama ku hadu, feenah kiyi tunani idan baya sanki bazai dinga bibiyarki ba
Idan yaudararki yake yi, tunda yasamu abinda yake so bazai qara kulaki ba

Sannan yakiraki awaya, lokacin dazaki dawo kano, nanma baki bari kunyi maganaba,sannan kun hadu rannan still kin sake fada masa wata baqar magana

kinada numbers dinsu shida sister sa, baki nemesu ba, tayaya kike tunanin zai miki bayani feenah?

Tabbas abinda ya miki bai kyautaba, kowacce mace kamila wadda ta killace kanta, Tsawon shekaru, Amma rana daya wani ya keta Mata haddinta, tabbas abin da ciwo feenah, na tausaya miki,
Muna aikatawa Allah laifi, dayawa kuma yayafe mana feenah

Kikasan ce mai yafiya, Allah yana tare dake feenah, "

Kallanta kawai nake, hakika duk wanda yasamu qawa tagari, ya godewa Allah,

Numfashi nasauke nace
" hakane Zahra, nikam da bacin rai yahana ni gane komai, nayafe masa, nayafe masa Zahra "

Rungmeni tayi, muna kuka, daganan kuma tadinga yimin godia, nace "Babu komai Zahra wallahi har cikin raina nayafe masa"

Zahra tace "feenah kinsan me?"

Nace "a a, tace wallahi kunyi bala'in dacewa da ahmad, kawai ki bashi dama, yadawo, kuyi aurenku , ku rike yarku shikkenan, kinga kema kin huta da darurar, wani mijin dazaki aura, wajan yimasa bayani,"
nace "hakane Zahra

Amma kina ganin ahmad zai soni ne yanzu?"

Hararata tayi tace "shidin me, ba dolen saba," nace "a a Zahra ba dole,"
tace "serious feenah zai soki fiye da da insha Allah,"
Nace " to shikkenan zan kira shi tawaya insha Allah"

Zahra tace "kinada number sa ta Egypt ne?" Nace "gaskya banda,"

tace "ga shawara,"

nace " mecece shawarar ki?"
Tace "kawai ki nemeshi ta Facebook dinsa,"
nace "ko?"
Tace "emana"
Nace "to shikkenan insha Allah zan nemeshi, duk yanda mukai dashi zakiji"

Rungumeni tayi tace da karfi "na gode sister feenah"

Mrs Usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

39

Kan gadonsa yafada gamida rufe idonsa, takardar hannunsa ya wullar, Yama rasa wanne irin tunani zaiyi
Wayarsa ya janyo yakira tahir, bugu daya ya amsa
Cikin sanyin muryarsa yace "tahir please zo"
Tahir yace "ahmad Allah yasa de lafiya"
Ahmad yace" ina kuwa lafiya please yi sauri "
Yakashe wayarsa
Tahir ya dubi husna yace

" ina Zuwa zanje wajan ahmad, "
mama da mima sukace daddy zamu, yace" a a kuje wajan ummi,"

mama cikin muryar kuka tace" to ai ummin ta koromu, "🤣

mima tace" toba kece kika zubar Mata kayanta ba,"
mama tace" bawani nan ai kece"
Tahir ya kallesu ya girgiza kai yafita
Yasan renin wayon dasuka saba yi ne sukayi wa ummi shiyasa ta korosu, 😃sai daya tayi laifi saboda tasan ba'a ganesu saitace dayar ce, itama dayar tace ba ita bace dayar ce, Dan dolenka ka hakura

Yana Zuwa part din ahmad ya nufa, yaganshi a kwance kamar mai bacci, waje yasamu ya zauna yace "gaye ya akayi ne?"
Ahmad yatashi idanunsa sun kada yace "tahir auren dole za'a min," 🤣

yanda yayi maganar ne yabawa tahir daria, cikin daria yace "auren dole kuma, kamar ya? Kana namiji? Dama Ana haka?"
Ahmad ya numfasa nan yabawa tahir labarin abinda yafaru tsakaninsa da daddy
Tahir yace" to menene abin damuwa ahmad
Maganar de itace bakasan ta, tofa itama bata sanka, 🤣 a hankali zaku saba ahmad"

Ahmad yace " tahir bazaka ganeba, feenah"

Tahir ya dafe kansa da hannunsa yace "feenah, feenah, feenah, koda yaushe maganarka feenah, na tabbatar yanda kake Santa ita bata yima wannan soyaiyar"

Ahmad yace" a a tahir   nasan tana sona kawai laifin dana matane yasa ta tsaneni kuma nima nayi DANA SANI"

daddy ma inajinsa yana cewa wai bazai yafewa wannan yarinyar ba, baisan daya ji abinda namata shine ma, zai nemi yafiyar taba, tunda shi sanannan mutum ne, abinda yafaru tsakanina da feenah yana iya taba mulkinsa "
Tahir yace "hakane, na feenah bada kanka asare" 🤣

Harara ahmad ya aika masa
, tahir yace "yanzu menene abin yi,?" Ahmad yace "ni kaina bansaniba shiyasa na kiraka," tahir yace" a ina yarinyar take?" Ahmad yace" kaga paper da daddy ya rubutamin address dinta can na wullar ta, "kallan p.o.p din Dakin ahmad yayi, afili yace" Naso ace feenah nafara aura, bantaba yiwa iyayena gardamaba dole yanzu ma inyi musu biyayya tahir koda aikata hakan yana nufin fitar numfashi na ne karshe"

Tahir ya dafashi yace
" kayi hakuri ahmad, idan feenah matarkace, duk daren dadewa zaku kasance ma'aurata," ahmad yace" hakane, shiyasa nake sanka "🤣

Harararsa tahir yayi, yace
" saboda nayi maganar feenah ba, oh duniya feenah! feenah!! feenah!!! , nikuwa zanso haduwata da feenah "
Ahmad yace" me kakeci nabaka na zuba, kamar yaune ai"
Tahir yace "yanzu me kake ganin za'a shirya?"

Ahmad yace "shiri kuma tahir, ai Babu wannan maganar, Babu wanda zan sanarwa zanyi aure, biyayya de zanyi inyi auren, Amma maganar sanarwa Babu ita"

Tahir yace "ahmad wanne irin aure ne wannan?"
Ahmad yace " tahir mubar maganar nan Dan Allah"

Tahir yace "ok, to yanzu yaushe zamuje wajan yarinyar sai muji wanne tsare tsare ne yakamata ayi," ahmad yace" Babu inda zani tahir, aide so suke su ganni da auren ko, to ayi auren, Amma maganar gaskya banajin zan iya San wata bayan feenah "
Tahir yace" a a kadena fadar haka "

** *** **

"Mom nafada miki Babu abinda zanyi, haka kawai dad baiyi shawara daniba zai tashi yabadani saikace wata mage"
Mom ta dafa kafadar ta tace "
LAILA
meyasa wani lokaci bakya tunani ne, yanzu ashekarunki baici ace kinada yara ba?

Nide abinda nakeso dake shine kiyiwa mahaifinki biyayya, inba haka ba,tun baya fishi dake to zai fara yanzu"
Laila tace "mom nikam banasan wannan auren, nafisan rayuwa ta haka, mom bansan fa wanda zan aura ba, saboda me dad zaimin haka?"
Dafa kafadarta hajiya salaha tayi, tace "laila zaki auri yaro, yaron ma me tashe, me facaka da nera, kuma yaro danye domin kuwa kin girmeshi" , laila tace "mom kamarya? Me kike nufi?"
"Dan gidan alhaji muhd marzuk zaki aura laila, ko banza zaki zauna cikin daula kiyi yanda kikeso da kudi laila, ki hau motar da kikeso"

** *** **

"Momy gaskya ankon nan yayi kyau, ina farin cikin auren nan na yaya, Amma zan so ace da qawata feenah akayi," Momy tace "saudat muma munso hakan Kodan farin cikin my son Amma toya za'ai, haka Allah ya qaddara,"
saudat tace "hakane, Allah yabasu zaman lafiya," mamy hakima datake shigowa Dakin tace "amin" , tace "saudat abinci yazama ready, yakamata kije ki zubawa farouq din ko, kada ace munyi baqo mun barshi da yunwa"
Saudat tace "ai mamy Dakin barshi ma nayi masa da kaina, Dan bayasan abincin masu aiki," mamy hakima ta kalli Momy, suka hada ido, mamy hakima tace
" um lalle zamani sannu saudat"
Shiri suke sosai yan wannan gidan, kowa yana walwala saide uban gayyar baya maraba da wannan aure

** *** **

Kan gadonta tafada, tasaki ihun murna tace, "cikin sauri haka?
Abinda na Dade ina nema ne Yau yazo har gida yasameni, ta shege da wata uwar daria
Tace ahmad zanyi yanda nakeso dakai, tunda kazama mallaki na, dana Gama da mangoro zan yarda qwallansa in huta da quda

** *** **

Rana bata qarya

Ayau ne dubban mutane suka shaida daurin auren ahmad muhd marzuk, da laila bukar
Wanda akai Akan sadaki naira dubu dari, lakadan ba ajalan ba
Ana daura auren ahmad ya sulale Yabar wajan, tahir ne mai kula da komai
Haka kuma har wannan lokacin shide bai nemi laila ba, bayama ta kanta, dakinsa yashiga ya

kulle yaita kuka shi dakai (toya zakai Malam amadi)

** *** **

"Mom ni narasa gane wannan wanne irin aure ne, angonfa har yanzu bai zoba, sannan akwai dinner da qawayena suka shirya shima kuma naga alamar bazai zoba, tunda nima bansamu matsayin dayazo yaganni ba,"

Hajia salaha tace "laila 'yata yi hakuri bari nakira step momynsa"
Mamy hakima ta kira tayimata bayanin komai, nan mamy hakima tace
" karta damu aci Gaba da hada komai insha Allah zaizo"

Nanfa su laila aka fara shiri baji bagani
Tun magrib aka fara ta ruwa awajan dinner, ango de bayan Mamy hakima tayi masa fada, saida tahir yadage sannan yayarda suka tafi

Amarya ta Dade awajan itada qawayanta, tun daga nesa data hangoshi ta shagala akallansa, yana Nan yanda yake, sai kyau da haske da kuma hutu dasuka sake baiyana atare dashi, daga kallo daya bai sake yi Mata na biyu ba, yana qarasowa tazo ta rike hannun sa sai kwarkwasa take, aikuwa nan masu pictures suka ce in bakayi ban waje🤣

Tahir ma yafara yi musu pictures, laila sai wani kanannadewa take ajikinsa, shide tahir yanata musu pic, azahiri shide yarinyar bata wani kwanta masaba, Amma Babu yanda zasuyi da hukuncin Allah
Ahmad yajuyo yace Mata "kewai miye haka eye?"
Daidai lokacin daya juyo kuwa tahir yayi musu pictures sai ka dauka wasu zunzurutun masoya ne 🤣

Kusa da ahmad yaje daidai kunnansa yace, "abokina bani aron wayarka mana"

Ahmad ba tare da tunanin komai ba yabashi, yace "haba ahmad kadan saki ranka mana," yajuya yakoma wajan zamansa

Yana karbar wayar ahmad whatsApp dinsa yahau yayi posting pictures din ahmad da laila, a status, aikuwa nan da nan mutane suke masa fatan alkhairi, yanmata kuma suke DANA SANI da cizon hakori, daga baya kuma ya koma Facebook nanma yayi posting cewa nayi aure ina buqatar addu'ar ku fans
Sannan yadora pictures din guda biyu, aransa yace nasan ahmad zaiyi fishi Dani Amma zai dawo yahuce, yaya za'ai ace mutum yayi aure Amma kace Babu wanda zai sani

Dahaka aka Gama dinner din

Washe gari ne ranar kaiwa amarya, alhaji bukar ya yiwa laila fada sosai Akan tabi mijin ta, saide ita aranta bahaka bane,
Hajia salaha kuwa, ta gargadeta Akan kada ta kuskura tayi aikin wahala, laila tace "haba mom kamar baki sanni ba, nifa mom banajin auren nan zai wuce 3 months, gaskya dana samu abinda nakeso,kuma nagama samun kudi, to zan kashe auren ne indawo gida, daga baya dad saiya yafemin"
Hajia salaha tace "lalle sai Yau na tabbatar bakida wayo laila
Daki Debi kudi kidawo gida, bagara ki zauna kisamu ciki ba, daga bisani kibar masa gidan,saimusa agama dashi , kinga yayinda aka raba gado kinada tarin dukiya mai yawa"
Laila tace "wow mom banyi wannan tunanin ba"
Hajia salaha tace "toki kula de yata"
Dahaka aka dauki laila aka kaita gidansu ahmad cikin part dinsa dayasha gyara

** *** **

After one week, tunda akai auren ahmad bai taba takawa wajan ta ba, dasafiya tayi yake fita, bazai dawoba sai can dare yayi sosai,🤔 laila abin duniya duk ya da meta, daga baya ne ta kira mom dinta, nan tabata shawara

** *** **

Yau da safe nagama karatu na, ina kwance ina chting, kamar wasa nace bari de Yau in duba inga ko ahmad yahau Facebook dinsa

Hawana keda wuya, naje nayi searching sunansa, kai tsaye wajan photos na shiga, abinda nagani ne yayi mugun dagamin hankali

Afili na furta, "ahmad! Ahmad!!
Aure ahmad, sai kuka," nan danan gabana yafara faduwa, nace "na shiga uku
, ahmad yayi aure, ahmad da gaske dama aure zakayi ka kyaleni?"
Ihun kuka nasa nayi wulli da wayar, wannan ihun ne yajanyo hankalin Zahra da dakinta yake kusa da nawa
da gudu ta shigo Dakin tace "feenah lafiya?"
Ban iya bata amsa ba, sai kuka nake
Ta cacimeni tace "menene wai feenah kiyimin bayani mana"
Wayata na nuna Mata cikin sheshshekar kuka, nama kasa magana nace Mata "Ah.. Ahm... Ahmad ne"

Zahra da sauri taduba wayar, nan take tafara salati

Cikin kuka nace "Zahra kingani ko? , yanzu kin yarda yaudarata yake ko Zahra"
Zahra ita kanta hawaye take, nace "Zahra...."
Kafin nayi magana naji qirjina ya rike, durqusawa nayi na dafe qirjina da hannu na
Dif numfashi na ya dauke

Mrs Usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

38

Haka na wuni ranar cikin sa'adah

After 2 days
Waya nake ina cikin farin ciki, nida husna, ni kaina har mamakin kaina nake yanda nake cikin farin ciki, kuma nasan hakan baya rasa nasaba da shawarar da Zahra tabani, "anty husna wai kin manta ne?"
Husna tace "me kenan?"
Nace "pictures din baban twins" , husna ta dafe goshinta da hannun ta, tace "yi hakuri, nifa banama San tada maganar feenah"
Cikin kwanciyar hankali nace "karki damu, ki turomin yanzu, idan nagani zan kiraki"

Whtsp tahau, tajirata, aikuwa ta turo Mata pictures din dayawa, dana twins dana baby, saide na baby yafi yawa sosai
Wani wajan tana wasa, wani wajan tana daria
Wani wajan kuma kuka, ni kadai nake ta murmushi ina ganin pictures din

Saina mijin ta, ina gani bansan lokacin dana zaunaba, na dafe qirjina, afili nace "shine, shine wallahi shine"
Sauka nayi ko datar ban kasheba, nakirata,
Gabana yanaci Gaba da faduwa nace, "anty husna wallahi shine"
Cikin mamaki tace " wai da gaske shi din kika gani?"

Nace "shine sister"

Husna tayi shiru takasa magana
Nace "sister, ke yar'uwata ce, nasan bazaki cutar daniba, kuma zaki riqemin sirrina
Mijin ki shima sirrinki ne, kawai kiyi masa bayani, Babu komai"

Husna tace "nasan da haka feenah, Amma kina ganin hakan babu matsala?"
Nace "matsala sister?
Ai shima yanzu yazama kamar dangi ne awajan mu, kuma shima kamar yaya yake awajena, nasan zai tsayamin Aduk inda nasamu matsala
Karki damu sister kifada masa gaskya, tunda nasan cewa duk daran dadewa dole zai sani"

Husna ta numfashi tace

" Toshiknn zan sanar dashi Amma ba yanzu ba"
Nide nayi murmushi nace "duk yanda kikayi, tsakaninku,"
tace "Toshiknn"
Nace "toki gaida su mama, kice maman su tana gaida su, naga pictures dinsu sunyi kyau sosai sun qara girma"

Husna tace "feenah, wai sai yaushe zaki manta da abin daya faru ne?
Su mama kawai kika gani bakiga baby ba?"
Daria nayi nace anty "husna kenan, naganta tagirma, shikkenan?"
Husna tace "ke kika sani kinaso kina kaiwa kasuwa"
Nace" bahaka bane sister, wani Ikcin inajin Santa sosai araina
Saide idan natuna ta hanyar dana same ta sai inji ni kaina natsani kaina ma bare ita ko mahaifinta,"

husna tace" hakane feenah ki dinga manta komai insha Allah komai zai zama kamar ma ba'a yiba, tunda ba ganinta kikeyi agabanki ba", nace "hakane insha Allah zanyi kokarin hakan"
Nan mukai sallama

Mama nakira, danmu gaisa, nakirata bata dagaba, nasake kira kawai naji muryar yarinya ance "hello"
Araina nace "yar halak" 🤣

Nace "hello Baby"
Tace "ke waye?"

Araina nace uwar data haifeki ce🤣

Baby taji shiru tace "hello"

Nace "izdihar"

Tace "na'am"
Nace "bawa mama waya"
Tace "tokedin waye?"
Tsaki naja a hankali, nace "baki sanni ba?"

Tace "anty husna"
Nace " a a dayan antyn ce"
Baby tace "um um nikam bansanki ba,"

Cikin Jin haushi nace Mata, "nace kibawa mama waya ko,"
yarinyar tana nema
Tabatamin rai duk da naji dadin wayar da ita,😃 Amma wai ace yarinyar nan batasanni ba
Kawai ma saina kashe wayar 😠

Baby tayi daki da gudu ta kaiwa mama waya, mama tace "izdihar nahanaki daukar min waya bakyaji ko?"
Tace "um um mama ban daukaba,"
tafada tana rufe bakinta da hannun ta
Mama tace "waye yakira?"
Tace " nima bansaniba
Tace daya antyn ce"

Mama cikin mamaki tace "daya antyn kuma?"
Wayar ta duba, nan taga feenah ce
Tasaki murmushi tace lalle fa daya antyn 🤣

** *** **

"Alhaji bukar! alhaji bukar!!"
Cikin hanzari ya juyo, ya kalli hagu da damansa yace ashe har angama taron

Daddy ya dubeshi dakyau yace "haba alhaji bukar, wannan wanne irin tunani ne? Bansan me mutane suka dauki tunani ba"

Alhaji bukar yace "wallahi alhaji banyi tunanin nafada tunani mai tsawo har haka ba"
Daddy yace" to Allah yarufa asiri", alhaji bukar yace" amin,"
Yatashi yafara tafiya a hankali kamar wanda qwai yafashewa aciki

Daddy ya qarasa ya janyoshi, yace" alhaji bukar kamar kana tare da damuwa"

Alhaji bukar yace "hakane alhaji muhd, akwai abinda yake damuna, narasa yaya zanyi dashi"

Daddy yace "menene kuwa, inji ko zan iya temaka"

Alhaji bukar yace "wato alhaji, Allah yabani wata 'ya, wadda kwata kwata batajin magana, ga shekarun ta sunkai ace tayi aure Amma hakan bai iyuba, itace kula wannan Yau gobe itace wannan, ta fitineni narasa yanda zanyi da ita"

Daddy yayi murmushi yace "wato alhaji idan na lura da bayanin ka maganar de Akan mace ne"

Alhaji bukar yace "hakane alhaji"

Daddy yace "nima Dan wajena, yafada matsala a dalilin soyaiya, mazai hana mu hadasu aure, nasan insha Allah zasu so junan su sosai," alhaji bukar yace" Amma alhaji kana ganin hakan babu matsala? Yarinyar nan tawafa bataji "
Daddy yace" insha Allah Babu matsala alhaji, muyi musu fatan alkhairi, inka samu lokaci kayimin magana Asa lokacin auren su kawai "

Nan sukai musabaha, suna daria, daga bisani kowa yatafi, yashiga motar sa, dama sun hadu ne awajan taron da akai tsakanin yan siyasa da yan kasuwa, domin sasanto Akan saida kayan masarufi

Alhaji bukar sanannan mutum ne awajan Daddy, haka yanada kamala da dattako

** *** **

Yau gidan ahargitse yake, kasancewar wanda akeji dashi zai dawo Yau,
Girki anyishi kala kala kamar ba gobe

Auta ta hana kanta sakat Yau yaya zai dawo
Yan company sun hana yan gidansu suje su dauko shi, sunce zasuje, haka kuwa akayi, su suka tafi, cikin su harda tahir, jirginsu na sauka aka taroshi kamar wani gwamna
Ma'aikatansa kowa kallansa yake, yayi kyau yayi wani fari, hutu ya zauna, sosai yayi kyau cikin suit dinsa me launin blue
Tahir yace "mutumina kode ansauya mana kai ne, Gaba daya kamar injin hutu Yama wanka," ahmad yace "tahir bazaka sauya ba, kabari akwai labari sai mun hadu kawai"
Saida suka kaishi har gida sannan suka dawo, agidanma kowa murna yake auta tana jikinsa yana cin abinci, dahaka harya Gama yaje daki ya huta, shi kansa yana cikin farin ciki, saide daya tuno mgnr Daddy akansa sayaji gabansa yafadi, afili ya furta "me yakai feenah Egypt, me taje yi? Gaskya akwai abubuwan dasuke faruwa,"
da wannan tunanin yatashi yayi wanka, ya kwanta domin yahuta

** *** **

Tsawon sati biyu kenan, kullum saina duba account dinsa na Facebook ko yahau Amma Baya hawa, abun tun baya damuna har yafara damuna, ban tura masa da friends request ba, kawai haka nake dubawa idan yahau saina masa magana, Amma naga kwata kwata ma rabonsa da hawa yakusa wata daya🤦🏻‍♀️

Zahra nafadawa halin da ake ciki, tace insha Allah indinga dubawa, zansa meshi wani lokacin, inyi masa uzuri may be yana busy ne dahaka take kwantar min da hankali

** *** **

"Kana nufin abinda kafadamin da gaske ne?"

Ahmad yace "tahir wallahi naganta, harma munyi magana kamar yanda nabaka labari, sanadin haduwa ta da ita shine dalilin tashin rashin lafiya ta, wannan dalilin ne yasa daddy yayanke min wannan hukuncin, tahir nagama yarda feenah tamin nisa, ayanxu abinda nake nema awajanta shine yafiya,"

tahir ya numfasa yace" gaskiya ne, insha insha zan tayaka da addu'ah nima abokina, ka kwantar da hankalin ka, yanzu yaya maganar company babu wata matsala deko? "
Ahmad yace"a a Babu komai, komai yana tafiya yanda ya dace hassan yayi kokari saboda haka nema nayanke shawarar zanyi musu qarin albashi," tahir yace "ok Toshiknn"

** *** **

"My son,"

"na'am daddy"
Daddy yace "ahmad dama nakiraka ne Akan mgnar auren ka"
Ahmad yadago da sauri yace daddy "aure kuma?"

"Qwarai kuwa aure ahmad, Sanin kanka ne mungaji da ganinka haka, Dan haka nayi magana da abokina, yabaka auren yarsa, mun tsaida magana za'a daura muku aure nanda sati biyu, Dan haka kaje kayi duk wani shirye shirye, ga wannan
Daddy yabashi wata takarda ahmad yakarba jikinsa asanyaye, daddy yace address din gidansa

ne, zaka iya Zuwa kuga Juna, umarni nabaka ba shawara ba, "
Ahmad cikin sauri yace
" Amma daddy..... "

" Dakata ahmad banasan Jin komai tashi kabani waje"
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

40

Gaban Zahra ya yanke yafadi, tashiga uku, karde yar mutane ta mutu ahannun ta, 😳jijjagata tashiga yi tana fadin "feenah! Feenah!! Na shiga uku na feenah Dan Allah ki tashi"

Dataga kukan bazai kaimata ba, da gudu tayi Dakin abokan zaman su, suma suna zaune suna fira
Su kaga Zahra tashigo bagatatan
Cikin kuka tace musu
" feenah, wallahi Babu feenah ta mutu," 🙆

"Ta mutu? !!!" 🙆
Suka hada baki wajan fadar hakan
Janyosu tayi sukayo dakina, basuyi wata wataba, daya daga cikin su ta fita ta kira musu adedeta, su kuma suka dauko ta, sauqinsu daya batada wani nauyi 🤣

Wani asbiti naga sun nufa  maisuna mustashfa sheik
Suna Zuwa kafin ma ayi wani cike ciken kati suka karbeta, ganin yan'uwanta suna kuka
Saida aka karbeta ne su Zahra suka fara siyan kati da abinda yakamata, feenah kuwa suna Zuwa aka saka Mata abin nan mai temakon janyo numfashi Wato oxygen

** *** **

Riga ce a jikinta, marar hannu rabin kirjin nan duk awaje, ta feshe jikinta da turare, Tsawon rigar Gaba daya iya rabin cinyarta ta tsaya
Yau de za'a yi ta taqare
Wayarta ta janyo, ta kira sofy
Safiyya tace "a a kaga amarya, ashe Ana jinku, saida kika Gama amarcin zaki nemi mutane"
Laila tace "hmm kede qawata bari, abin duniya duk ya dameni, sofy ahmad baya zama, duk zulamata kikaga de nakai wannan lokacin Babu abinda yafaru ai kinsan nayi qoqari ko"
Sofy tace "haba laila, karki bani kunya mana, kamar ba lailan dana saniba, ni wallahi harkinsa

naji kunya, inda nice aida tuni anwuce wajan wallahi

Haba laila mai amfanin kissar mu ta Mata, inba haka ba, me amfanin qwaya, kawai ki dura masa yasha, kuyi komai cikin nishadi, balle ma ke dakika Dade kina mararin abun "
Laila ta numfasa tace
" kede bari sofy, baya dawowa da wuri, idan kinga yadawo to yafaki idona yaga nayi bacci,🤣 shiyasa nima Yau nace komin dare ina nan ina jiran sa, idan yasan wata baisan wataba "

** *** **

Tsawon lokaci nadauka sannan numfashi na yadawo normal, ina kwance abin duniya yadameni, saide idona yana rufe, araina nace

" my ahmad, ashe bazaka zama mallakina ba, 😭nikam nayi DANA SANI Akan yin soyaiya ma baki dayanta"
Salma ce daya daga cikin wanda suka kawoni, tace
"
Zahra to ki kula da ita zamuje gida ko abinci ne akawo"
Zahra tace "a a ai likita yace sha biyu ma zai iya sallamarmu, ba'a kwana a asbitin"
Salma tace "to bari muje de"
Taja hannun yar'uwarta suka tafi

Basu Dade da fita ba, likitan yazo yace zamu iya tafiya ma kowanne lokaci,
Zahra ta amsa masa
Bude idona nayi wanda yayi jajir saboda kuka, nace "Zahra Tome muke jira kawai mutafi, Babu abinda yakemin ciwo yanzu"
Zahra tace "a a mujira su Salma su dawo saimu tafi baki daya"
Komawa nayi na kwanta, Zahra tace "feenah kiyi hakuri, haka Allah ya qaddara mana
Banyi tunanin ni kaina zai iyayin haka ba
Amma ki dauki komai a matsayin kaddara, kicire ahmad aranki,"
Cikin sauri na tari numfashin ta, nace
" bazan iyaba, bazan iyaba Zahra" 🤣

Zahra tayi murmushi tadawo kusa Dani ta zauna tace "feenah dole kicire ahmad aranki, Kodan lafiyarki"
Duba nan
Ta miqomin katin asbiti na, kallan katin nayi ba tare dana karba ba, nace
Mata "menene?"
Tace "hawan jini feenah
Likita yace kinada hawan jini,

Kinga kuwa yakamata kicireshi aranki Kodan lafiyar ki feenah, nafi kowa sanki da ahmad feenah, Amma tunda kika ji nafadi haka, banasan ciwon so yasa kikamu da wani ciwon da hakan zai taba lafiyar ki, tun kina yarinya "

Tashi nayi zaune, nakamo hannun ta, na rike, nace"Zahra, nasan bazaki bani shawara marar kyau ba, insha Allah zanyi amfani da shawararki, Amma maganar incire shi araina Gaba daya, bazai iyuba, zande kamanta
Zahra nayi tunanin likita zai fadi wani babban ciwo akaina, Amma hawan jini, najima da Sanin ina dashi,duk a dalilin ahmad duk da likita bai fadamin ba, "

Zahra ta rungume ta, tana bubbuga bayanta alamar rarrashi

Nace" Zahra, nagama lura mukhtar yana sona, kawai zan bashi dama, muyi soyayyar mu, idan ma auren ne, kawai zan aureshi Zahra "
Zahra tace" hakane feenah, bazan hanaki ba, Allah ya tabbatar muku da alkhairi "

Su Salma ne suka shigo da leda ahannun su, sin siyomin kayan marmari, Allah sarki
Anan Zahra tafada musu abinda likita yace, nan suka fara hada yanasu yanasu

** *** **

Tanajin dirin motar sa ta tashi aka gyara gashin attached din data dora akanta

Bakin qofar Takoma ta tsaya
, agajiye yadawo gida Yau, yana sanye da farar Riga, baqin wando, sai yar saman itama baqa, Amma ahannun sa yariqeta
Sai wayoyinsa dasuke hannun sa
Yana shigowa hankalin sa kwance
Kawai yaji yayi Karo da mutum, da sauri ya kalleta ya kawar da kai, yace "ke miye haka?"
Bata bashi amsaba kawai ta rungume shi, Ahmad yace "a a ke cikani mana, wanne irin shirme ne kikeyi haka?"
Laila fara shafashi , cikin qissa tace" haba ahmad, meyasa kakemin hakane?
Please kagane mana "😉
Ahmad tureta yayi ya wuce
Dagudu taje ta rungume shi tabaya, tana shafa kirjinsa da hannun ta, daga baya kuma abubuwan nan guda biyu suna mintsininsa
Jiki da jini, nan da nan yanayinsa yafara sauyawa, laila dataga tarkon ta, yafara aiki, nan da nan, tafara kissing dinsa, Gaba daya ahmad yafara fita hayyacinsa, cikin rada tace "masa my ahmad muje daki please

"my ahmad "

Ya maimaita sunan aransa, inaaaa bazai iyuba, mace dayace ta dace da Kiran wannan sunan, wato feenah

"Keeee kirabu Dani nace" 😠

Yafadawa laila hakan cikin tsawa, yashige dakinsa gamida rufowa
Dafe mararsa yayi da hannayensa, innalillahi me yake shirin faruwa dashi ne

** *** **

Waya tace tadau qara, ina dubawa naga mukhtar ne, nadauka muka gaisa, Zahra tana gefena a zaune, tana kallo na, saida muka muka Gama gaisawa
Zahra tace "masoya," kallanta nayi nace "aikuwa munkusa zama hakan
Danma ban fara bashi kulawar data daceba"
Zahra tayi tagumi tana kallo na cikin murmushi batace komai ba

** *** **

After 3 month, tuni mun shiga level 4
Na warware ina mu'amula ta, kamar da, saide ahmad yana Nan daram araina, Amma ina kokarin kawar da hakan araina

Soyaiya tayi nisa tsakanina da mukhtar, harya kasance baya awa biyu kyakykyawa ba tare daya kiraniba, yanzu haka saura wata hudu ingama karatu na, haka kuma munyi alqawarin aure a tsakanin mu
Bai taba boye min komai nasaba, saide nice baisan nawa sirrin ba
Dan haka nace nima inasan magana dashi mu hadu a school gobe kuma ya amsa min, zai jirani a school din Zuwa goben

Rufe idona nayi, araina nace gara infada masa gaskya tun yanzu, idan yanaga zai iya aure na shikkenan

** *** **

"Nagaji! Nagaji!! Nagaji!! Sofy, kawai zansa masa magani yasha ba tare daya saniba komai yafaru cikin salama, yafi ace ina zubar da ajina Akan wannan yaron"

Sofy tace "ato aina fadamiki, Kodan magungunan dakike dirkawa kanki ma yaci ace ai kin nemi wani alhajin kun huta"

Laila tace "bari kiga naki wasane sofy"

Fridge din Dakin ahmad ta nufa Gaba daya ruwa da lemon dayake ciki, saida tasaka qwaya aciki, ta shege da daria, tace "zancenka yaqare ahmad"

Mrs Usman ce ✍️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

41

Tana dawowa falo ta cewa sofy, "aikin Gama yagama sofy, saura yasha kawai"
Daria suka sa gamida tafawa, nan sofy tayi Mata sallama tatafi
Dakin ta tashiga tasake wanka tasa wani kayan bacci mai suna dashi da Babu
11:45 yadawo gida
Laila tana labe tana kallansa harya shiga dakinsa yarufo kofar
Sake fesa turare tayi, tafita ahaka, bata zarce ko'inaba sai dakinsa, tana shiga taga baya nan, motsin danaji a toilet shiya tabbatar Mata da wanka yake
Zama tayi agefen gadon, tana qara Baza gashin kanta
Zuciyarsa daya yafuto daga toilet din, dagashi sai towel iya qugunsa
Ganinta haka yasashi cikin wani yanayi, Amma yayi fuska ya share ta, gaban madubi ya nufa yafara fesawa jikinsa turare masu shegen qamshi, sannan ya dauko wani mai zai shafa
Laila da taga yamaidata gunki awajan Dan haka ta tashi tana wata karairaya, sai qara turo kirji take ta qarasa gabansa
Ta bayanshi ta rungume shi, ta karbi man dayake shafawa cikin qissa tace

" bari in tayaka shafawa ahmad,"

mansa ya qwace yace "no barshi kawai"
Cikin yanga tafara shafa jikinsa tace "ahmad ina sanka,"
hannunta yana yawo ajikinsa, tana masa magana a kunne, shiru ahmad yayi yana sauraren

abinda bai tabaji wata mace tayi masaba, hakan yabawa laila damar daukar man, taci Gaba da shafa masa,
Ahmad yayi shiru yana daukar karatun, Jin hannunta cikin towel dinsa yasashi juyowa da ita yace
"keee, fyade zaki min ne? Miye haka? Haka yadace mace budurwa tayiwa mijin ta?"
Laila da idanunta suka sauya kala saboda tsabar jaraba, tace "eh, shi zanma, tunda kaqi bani haqqina,"

ahmad yace "to inke mayya ce saide kici kanki da kanki, bana sanki, bana kaunar ki dole ne? Ke wacce irin..."

Dif laila ta hade bakinsu waje daya, ta nayi masa wani irin salo
kirjinta take gogawa anasa, haduwar fatar jikinsu ba tare da kaya ba, shiya haifarwa da ahmad shiga wani irin Hali, laila ta riqeshi gam, shide ahmad baisan lokacin da hakan yakaisu ga gado ba, laila tafara aiwatar da komai akansa
, ganin tana nema tafi karfinsa ne yasa, aransa yace wannan idan banyi Mata abinda take soba, Babu zaman lafiya
Hakan yasa yabata hakkinta, saide yanda yayi tunanin ta, hakan ce ta kasance, dama yasan yanda take nuna zulamarta afili yasan, tabbas mazinaciya ce

Bayan komai ya lafa, nan Yabar laila tana kwasar bacci, tashi yayi tsaye, ya kalleta, aransa yace jarababbiya
Toilet yashiga yayi wanka, yadauro alwala yafuto, falo yakoma ya tada kabbarar sallah
Cikin sallah yana kuka yana adduah, ya Allah haqiqa nasan na aikata laifin zina, shiyasa nima ka jarrabeni da auren mace mazinaciya, ya Allah kasani cewa wannan al'amari daya faru tsakanina da nafeesa ba laifi na bane, qaddara tace tazomin da haka, kuma nakarbi kaddara ta, ya Allah kasani banasan wannan auren, iyayena nayiwa biyayya, ya Allah kasa naga sakamakon biyayya, ya Allah kabimin haqqina, haka yaita addu'ah daga karshe bacci ya daukeshi anan falon

da safe Dakin yakoma, yashiga toilet yayi wanka cikin sauri ya shirya cikin farar Riga mai ratsin baqi, sai farin wando, sumar nan tasha gyara sai qamshi yake, wani akwati ya bude, agogo ne aciki kala kala, ajere, yadauki daya yana daurawa cikin sauri,fridge yabude yadau ruwa zaisha, saiya fasa yace kada cikinsa yayi ciwo baici komai ba yafara da ruwan sanyi, maida ruwan yayi, kallan gadon yayi laila tanata bacci, ba sallah bare salati, ahmad yace inkin gaji kya tashi, cikin sauri Yabar part din
Wata farar mota yahau Range Rover Yabar gidan, kosu momyn ma yana sauri bai shiga wajansu ba

Sai wajan 11 tayi juyi ta tashi, agogo ta kallah da sauri ta tashi, tayi miqa, tasaki murmushi, tace ahakama baisha magani ba, naji dadin abin, inaga yasha magani kuma yanda zai dinga komai yana cikin shauqi

Wanka tashiga tayi, ta shirya cikin atamfa, ko Dakin bata gyara masa ba, bare toilet din, ma'aikata takira tabasu umarni su kwashe duk kayan fridge din Dakin ahmad su zubar, su saka wasu, nan da nan suka cika umarninta,

part din su momy
Tanufa tana shiga tagansu a zaune, momy da mamy, tana sallama suka zuba Mata ido, domin kuwa suna gida daya, tafi sati ba tazo inda suke ba,🙆🏻😳 shiyasa mamy hakima tahana maryam da Muslim da bukhari Zuwa inda take, tunda itama batazo ta gaida suba, dasuke iyayen mijin ta

Har qasa ta zauna ta gaishe su, suka amsa ba yabo ba fallasa, tace
" momy dama... am dama magana nazo muyi," momy tace Mata

" Babu komai laila inajin ki, nida hajia ai duk daya," laila ba kunya tace" dama so nake kiyiwa ahmad magana bayasan saukemin haqqina na aure, nikuma nagaji, shine naga ya dace infada miki ko zaki masa magana," mamy hakima da momy suka hada ido lokaci daya

** *** **

"A a Aysha kifara fadamin naki albishir din," aysha tace "a a feenah kifadamin naki first," feenah tace ," saura 4 months na dawo gida, Amma hutu zanzo inyi na wata daya, zan dawo inyi masters, akwai wani gari anan madani, anayin masters cikin 1 year, shine nakeso inzo inga su mama, saina dawo"

Aysha tasaki ihun murna awaya, tace "feenah, shekara uku bakya Nigeria, yanzu kin kusa dawowa wayyo, Allah yakaimu feenah, wallahi tun safe muna airport"
Daria feenah tayi tace "to naji, yanzu fadamin naki," aysha tace "ansa bikina nanda wata shida, Naso ace kina nan feenah, Amma gashi kince hutun wata daya zakiyi," feenah tace "kash, inama wata hudu akasa ko wata biyar, Amma ai muna tare babu damuwa," aysha tace "kyace haka mana, danki kare kanki," feenah tace "ai na dena damuwa Akan irin wannan abubuwan aysha, tunda akai bikin husna bana nan, kinga ayi na kowama," 🤣

aysha tace "kut"
Tuni feenah ta kashe wayar tana daria

Idan kin Gama dariyar nide ina jiranki, taji maganar mukhtar abayanta, cikin sauri ta juya, dama tana jiran sa ne a school, Akan maganar dasuka ce zasuyi
Feenah tace "har kazo?" Mukhtar yace "emana,"
Waje suka samu suka zauna, na fuskanceshi nace "mukhtar da gaske kake zaka aure ni?"
Mukhtar cikin mamaki yace "meyasa kikamin wannan tambayar feenah,"

tace "saboda inaso inji inda gaske kake zaka aureni, akwai maganar danake so muyi," mukhtar

yace "feenah, Amma nafada miki, zan aure ki ko? Please feenah kidena tunanin Akan soyaiyar danake miki, nayi miki alkawarin zan aure ki feenah,"

Feenah tace "wato mukhtar abinda yake faruwa shine...."

** *** **

Momy tace "to laila, insha Allah za'a yi masa magana kinji, ki kwantar da hankalin ki," laila ba kunya tace "to momy na gode sai anjiman ku," tana fita mamy hakima cikin tsananin mamaki tace "hajiya?"
Momy tace "toya zamuyi hajiya tunda alhaji ya janyo mana wannan jarabar,🤣 yanzu ina hankali awajan wannan? Saide kiyi masa magana, nikam wannan maganar tamin girma"
Mamy hakima tace "um duniya tazo qarshe, insha Allah idan yadawo zamuyi magana," momy tace "a a kirashi, kirashi yanzu yazo kuyi maganar," mamy hakima tace "to hajiya," gamida daukar wayar ta

** *** **

"Feenah kidena kuka haka mana, ya isa, hakika na tausaya miki, kuma insha Allah zan tabbatar miki da maza ba duka muka taru muka zama daya ba, insha insha zan baki kulawar da ahmad yakasa baki, karki damu feenah koda 'ya' ya goma kika haifa zan kasance tare dake, kinji? Yauwa togoge hawayen ki"
yafada yana miqa Mata handkerchief

** *** **

"Oh tahir, to yanzu kafadawa husna ne?"
Tahir yace "wallahi har darura nake infada Mata, saboda nasan rikicin ta" , ahmad yace "yakamata kayi Mata bayani, aiba wani dadewa zaka yiba, 1 year ne, kamar yaune ai," tahir yace "hakane,"

"yaya madam laila?" Ahmad yace "wayasan inda takene wannan"
Tahir yace "angon laila," ahmad cikin sauri yace "da feenah, kamata yayi kace angon laila da feenah, Amma zuciyata guda dayade na mallaka wa feenah ita," tahir zaiyi magana, kira yashigo wayar ahmad yadauka yace "ok mamy gani nan Zuwa"
Ahmad yace "to mamy na kirana, mayi magana daga baya," tare suka futo shida tahir din kowa yayi gida

** *** **

"Kiyi hakuri mana, to menene abin kuka? Baga wayaba,"
ummi data rafka uban tagumi tace "kayya tahir barta, barta tayi kukanta, nima kaina inakan hanya," 🤣
tahir yace "haba ummi yanzu Dan Allah yazaku hadu dukanku Kuna kuka, tafiya ba mutuwa bace ummi, zakusa nima jikina yayi sanyi," ummi tace
" Toshiknn, yi hakuri kinji husna," ummi takamata tana rarrashinta, ummi tace "yanzu yaushe zaku tafi Spain din?"
Tahir yace "next week zamu wuce mu uku ne zamuje, insha insha bazamu wuce 1 year ba"

** *** **

Suna zaune shida ita adakin ahmad nada, komai tsaf kamar yana ciki har yanzu, "Kaji de abinda tazo mana dashi dazu,"
ahmad yace "Amma nayi mamaki mamy,"

ya furzar da iska mai zafi, yace "Amma Babu komai mamy insha Allah zan gyara,"
mamy hakima tasha fa kansa, tace "kayi hakuri ahmad nasan abinda kakeji akwai ciwo, Amma kadaure kaci jarabawar da Allah yadorama,"
dora kansa yayi Akan kafadarta, ya lumshe idonsa ba tare dayayi magana ba

** *** **

After 2 months, a wannan lokacin karatu yayi mana nisa, ina shirin kammala degree Zahra kuma tana shirin shiga level 4
Da ita muka shirya zamuje hutu mudawo, karatu muke sosai, Amma mukhtar ba zaije hutu ba, tare dashi zamuyi masters din, Dan haka shi zai zauna ya nema mana admission din

Agidan su ahmad kuwa rayuwa tana tafiya yanda yakamata, haqqi ne yana sauke Mata tunda tahadashi da mahaifansa, saide abinda yake Mata ciwo shine yanda yake Kiran sunan feenah, feenah, idan sun kasance tare yayin raya sunnar manzo, abinda yadami laila kenan, Amma Zata yi maganin hakan

** *** **

Lokaci na tafiya komai na sauyawa, harsu feenah sun kammala school, sunyi bikin graduation,

Amma bata karbi result dinta ba, mukhtar zai karba musu yanema musu admission kafin tadawo

"Kinga wannan kayan zaiyiwa twins din sister husna kyau sosai ko?"

Zahra tace "sosai ma, kuma gasu iri daya babu banbanci,Amma feenah sai tsaraba muke siya banga kin siyawa izdihar komai ba,"
feenah tace "ke share ta," duk da acikin ranta, tanasan hakan,
Zahra tace "wallahi bazai iyuba,"
haka taita daukarwa baby kaya masu shegen kyau, dole saida feenah tasiya mata suka bar wajan, Gaba daya Cikin kwanakin basu da zama sune nan sune nan, suna shirye shiryen tafiya gida,
Agajiye suka dawo gida, suna Zuwa suka zube aqasa suna maida munfashi, feenah tace

" bari inkira kaka"
Tana kira kuwa kaka ta daga, cikin qara feenah tace "kakaaa"

Kaka tace "oh ni rabi'atu nafi zaki kashe min kunne"

Feenah tasa daria tace "to albishirinki"

Kaka tace "goro fari qal nafi"

Feenah tace "next week zan dawo"

Mrs Usman ce
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

42

Kaka tace "keni nafi wannan yaran naku saiku, nikam bazan gane Shiba,"
feenah tace "to rana itayau zan dawo," kaka tace "ayyiriri, alhmdlh har karatun, yaqare ko?"
Feenah tace" eh, Amma hutu zanzo inyi na wata daya saina dawo inyi shekara daya "
Kaka tace" to Allah yakawo ki lafiya nafi,
Amma idan ki kazo ai anan zaki sauka, saikinmin kwana biyu sannan zaki wuce ko? "

Feenah tace" kaka me kika ce? Inaaaa banyi miki alkawari ba kaka, bazan zauna ba, zaria zan wuce kai tsaye"
, kaka tace "to ai shikkenan nafi, dama wani abin dadi ne zan hada miki," 🤣

feenah tace "a a wallahi kaka rike abin ki, nikam wajan mama zani,"

kaka tace "to ai shikkenan," nace "eh din, sai anjima tsohuwa," nakashe wayata

Zahra tace "kai feenah bakida dama, Akan ki kwana biyu agarin namu, kika sanima kokiyi kwalli da gwanin ki," 🤣

nace "Zahra Dan Allah dena yimin zancan mutumin nan," kama bakinta tayi da hannun ta, tace "shikkenan zance ya wuce
Yaushe zaki rakani unguwa zanje inyi sallama da qawayena," "wanne unguwa?" Na tambayeta
Tace "ma'amura,"

nace "saide wajan yamma, sai muje"
Tace "ok"

** *** **

Afalo ta sameshi yana aikin danna computer yana daga kwance, Dagashi sai singlet da gajeran wando, ga ruwa nan agefensa, tazo cikin shiri tace

"majnunun laila, ni zan fita,"

ahmad ya kalleta da kyau, shi sai maganar tata ma tabashi daria, wai majnunun laila,🤣duk yanda yaso boye dariyar sa saida ya murmusa, cikin murmushi yace Mata "aiba saikin tambayeni ba, kawai kije duk inda zaki,"

laila tacika tayi fam,😠 aranta tace wato saboda baya sona, baya kishina, shiyasa zai fadi haka, har murmushi yake yana murna, saboda Zata fita tabar gida, kallansa tayi tace "ok thank you,"

tayi gaba, da kallo yabita, yana murmushi, wai majnunun laila, ina laifin ma tace majnunun feenah, cigaba yayi da aikinsa

** *** **

"Mom nagaji, gaskiya nagaji da wannan zaman na kulle, haka kawai kullum mutum yana zaune agida, Babu fita yawon nan nabude ido,"

hajiya salaha tace" to menene laila, ai kema hakan kamar hutu ne agareki "
Laila tace" sannan mom duk lokacin danake tare dashi, bashida aiki saikiran sunan wata wai feenah, bazai iyuba mom, nida biyan buqata wata da samun waje azuciyar sa, wallahi dazan ga wannan yarinyar dayake kiramin ita cikin dare acikin kunne na, wallahi saina Mata illa "
(niko Amnah nace to ina zaki ganta, shima nemanta yake) 🤣🤣

" sannan har yanzu shiru, Babu alamar ciki awajena, mom ko batan wata bantaba yiba
Maganar data kawoni kenan, gaskya idan naqara wata uku, Zuwa hudu bansamu ciki da kudin da nakeso ba, to zaki ganni da kayana nakashe auren na dawo gida," hajia salaha tace

" Toshiknn yanda kikeso yata haka za'a yi, danni dama wannan auren kawai de Dan yaron yana da kudi ne shiyasa na yarda, Amma ace yaro kullum fuskarsa cikin qunci "🤣

Cikin ransa yace kina kashe auren ki kuwa daga ke har uwarki saide kufuce kubarmin gidana, nagaji da halinku, maganar alhaji bukhar kenan daya Gama Jin duk zancan dasuke

** *** **

" Momy kin ganta ko, Allah saikin bani alawa ta,"
inji mima kenan dasuka zo gida tare da maman su husna, Ana shirye shiryen zuwan feenah gobe 😃
Husna tace " baby, bakyaji ko, wannan fa yarinya ce, qanwarki ce kibata alawarta saina baki sabo,"

izdihar tace" to ai anty itace tafara daukemin nawa,"

mima tace" Allah bani bace mama ce, "

mama datayi shiru tana jinsu tace" kaiii Allah mom bani bace mima ce,"

husna tace" ke baby waye ya dauke miki alawa? "
Izdihar ta kallesu Gaba daya takasa banbance wacece ma mima balle mama,🤣 sai tace" dukansu, dukansu ne anty, shiyasa nima nadau wannan kuma bazan Baku ba "
Mima tasa kuka, tace
" mom kingani ko "

Husna tace" a a bazaku samun hawan jini ba, ina Zuwa, "daki tashiga ta dauko musu wasu tabasu
Mama datake gefe tace

" yafi miki de, ai wannan yaran su kadai ma aka barka dasu sun isheka,"🤣

husna tace" Allah mama baby bataji," daria mama tayi, tace" ai duk halayan nafeesa babu wanda wannan yarinyar tabari, Kuna yara itama hakan take "

** *** **

" Yallabai dama ina neman afwa ne, yarinya ta tagama karatu zatazo daga makaranta zanje in dauko ta, in kaita can gida, " cewar Ammu

ahmad yace" haba hassan, aibabu damuwa kwana nawa zakayi?" Ammu yace" jibi zan dawo insha Allah,"

ahmad yace" babu damuwa, Allah yakiyaye,"

godia Ammu yayi masa tare da ficewa

** *** **

Dagashi sai Abba ne amotar dayazo daga zaria yadauki Ammu anan kano suka wuce airport, dayake ta kano zasu sauka, saida suka biya gidan da company su ahmad suka bawa Ammu, suka dauki maimuna sannan suka tafi Gaba daya

Jira kadan sukayi, jirgin su feenah yasauka, bayan tagama komai ta futo, kawai ganinsu tayi daga nesa aikuwa da gudu taje ta rungume anty maimuna, Abba sai daria yake, yace "a a nafeesa angama karatu kuma,"

feenah cikin murna tace
" eh wlh Abba,"

Zahra ce tazo suka gaisa itama tayi wajan yan gidansu Abba yace "a a hassan mu qarasa mu gaisa dasu mana," har feenah duk sukaje suka sake gaisawa da iyayen Zahra, sannan sukai sallama suka tafi, feenah tace Mata "sai munyi waya,"
hannu kawai Zahra ta daga Mata

Direct zaria suka wuce, suna Zuwa husna ta futo da gudu ta rungume feenah, Gaba daya gida de kowa yana ta farin ciki
Mama baki yakasa rufuwa, gata ga feenah, ta kwantar da kanta Akan cinyar mama, Abba yace

" mamana Hali de yana Nan," aka sa daria, takama su mima sai kallansu take, tace "anty husna basa kama dake yaran nan,"

husna tace "eh da babansu suke kama,"

Taga kowa Amma bata ga baby ba, to ina take,🤔 kuma taga babu wanda yayi maganarta, Batasan lokacin da maganar ta futo ba, kawai de ji tayi tace

" mama ina baby?" 🤣

Mama tace "aiji nake bazaki tambaye taba, tana nursery, yanzu zaki ga tadawo"
Anty maimuna tace "baby ta qwace Mata fada awajan mama kuma yanzu bata ganta ba ai dole ta tambaya," wannan maganar da anty maimuna tayi, shiya tabbatar min da batasan baby yata bace, kenan Ammu bai fada Mata ba, lalle wadannan mutane suna kaunata

Aikuwa  kamar jira take su Gama magana, sai gata da gudu ta shigo, tana cikin uniform dinta da school bag dinta a bayanta, kayan yayi Mata kyau sosai, tana Zuwa falon taga baqi dayawa, batabi takan kowa ba tayi wajan mama da gudu, ta rungume ta, wata sallamar suka sakeji abayansu, wani yaro ne yashigo yace
" mama kice baby tabani kallo kallo na,"
saida yafada sannan mama takalli hannun baby, aikuwa yana hannun ta, mama tace
" bashi abinsa kafin na dakeki," baby tace "to wayace shima ya tsokaneni,"

yaron yace "karyane niban tsokanetaba," mama ta karbi abinsa tabashi, tace " baby nahanaki rigima, bakyaji ko," turo Dan qaramin bakinta tayi gaba, tace "to mama nadena"
Ammu ne yace "baby ba gaisuwa?"

Wajansa taje suka gaisa, tana juyawa taga husna Takoma wajanta da gudu, feenah tana kallanta, husna tace " baby ga anty Baku gaisaba,"

kallanta ta maida ga feenah, suka zubawa Juna ido, baby sai kallanta take, tasauri Takoma wajanta, tace" ya sunanki? "

Feenah tace" baki sanni ba?"
 Baby tace" daga ina kike? "
Feenah tace" makaranta," baby tace" Amma zaki zauna damu bazaki gudu ba irin na anty husna"
Feenah tace "eh zan zauna," baby tace

" to Amma... "

Mama tace "baby barta ta huta tagaji banasan tambaya kinji,"

Abinci mukaci  nayi wanka na tafi daki nakwanta, baby ce tashigo Dakin ta tsaya abakin kofa, tace
" sabuwar anty in shigo?"
Feenah tace " shigo," tana Zuwa tahau jikinta, takama kallanta, feenah tace "baby lafiya? Wannan kallan fa,"

baby tace "ina sanki,
Nan dinki nake kalla irin nawa," takai hannun ta kan dimple din feenah,
Feenah tace "um nagani, yanzu bacci zanyi, nagaji, tashi kije wasa,"

baby tace "tonima zanyi baccin," 🤣

feenah tace "to kwanta kiyi" , kwanciya baby tayi, feenah tana rufe ido bacci ya dauketa, baby tatashi a hankali taci Gaba d kallanta, tanata daria ita kadai
Matsawa tayi jikinta tashiga jikinta sosai nan itama tayi bacci

Mama ta kalli husna tace, "kiramin baby nasan tanada home work, yanzu haka wasa take," husna na fita ta duba ko ina babu baby, Dakin feenah tashiga, kawai tagansu sunata bacci, husna tace "mama zokiga" 🤣

, mama nazuwa tagansu aranta tace Allah sarki, uwa da d'a kenan soyaiyar nan de dole saita wanzu atsakanin su
Juyawa tayi, tace "ashe bacci suke," tabar husna anan
Itakuwa husna kallansu take cikin birgewa

Gab da magrib nafarka, ina juyi naji mutum ajikina, kallanta nayi da mamaki, yanzu yarinyar nan saida ta kwanta ajikina, kallanta nake da mamaki nashafa kanta, Natashi zan shiga wanka, ina motsawa itama tatashi, cikin muryar bacci, tacemin "nima natashi," 🤣

nace "to jeki wajan mama," tace "wanka zakiyi?" Nace  " eh,"

tace "nima to kiyimin wankan"
Nace cikin raina Yau nagamu da jaraba,🤔 nace "jeki mama tayi miki," tace "um um ni kece zakimin" , girgiza kai nayi nashiga wanka, na shirya nabarta,dataga zan fita nabarta adakin kawai yarinya tasa kuka,🤣

 tace "Allah saikinmin," kallanta nayi kawai, Babu yanda na iya dole saida nayi Mata wankan

da daddare nabawa kowa tsarabarsa yan biyu sai murna suke, kayan su iri daya su ribom su takalma, saina husna itama kaya, sai na Abba da mama kuma,
Baby cikin sanyin kuka tace" Toni ina nawa?" Feenah tace " ai banda ke"
 tajuya wajan mama tace

" wai mama banda ni,"

mama tace "yi shiru mana baby kefa sai ragwanta ko?"
Feenah tayi daria tace
" toga naki," cikin murna izdihar tace "yeeee"

Haka ta ishi kowa da surutun kayanta ranar, washe gari su Ammu suka koma suma da tasu tsarabar, tare suka koma da husna, gidan ya rage daga su sai su, da yamma su aysha sukazomin sannu da Zuwa da ita da kala da kaka sai baba Adamu, sun jima sannan daga baya suka koma gida

Sati na daya agida, ina kwance afalo, ina kallo, dayake da weekend ne Babu school saiga baby ta futo daga daki tace
" sabuwar anty"
Nace "menene,? Kinfa dameni baby,"

hannun ta ta dora Akan maqogaronta tace "anty kinji zuciyata tauri ne da ita" 🤣

Na kalleta naga inda hannun ta yake, batama San inane zuciyar ba,🤣

nadaura hannu na Akan maqogaron nace "um aikuwa zuciyar taki tauri ne da ita kamar ta ubanki" 🙆🏻😳

Mama da futowarta kenan daga daki taji wannan firar tasu, cikin mamaki tace " nafeesa kinada hankali kuwa?"

Mrs Usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

43

Baby ma tazaro ido takama bakinta,🙊cikin mamaki tace "da Abba kike?"
Mama ce taqaraso wajan da sauri, ta dakawa feenah harara, taja hannun baby sukabar wajan

Dafe kaina nayi da hannu na, oh ya Allah, meyasa na aikata haka? Yakamata indinga daidai ta kaina Akan yarinyar nan

Tashi nayi natafi daki

Mama ta kalli izdihar tace "baby, idan anty tana hutawa kidena Zuwa wajan ta kinji?"
Baby tace "to mama, Amma ina Santa,"

mama tace "naji, naji baby nasan kina Santa, Amma kidena damunta kinji, oya dauki littafin ki, kiyi karatu"

** *** **

"Gaskya my heart yakamata kazo mana hutu, yanzu fa watanka biyar," tahir yace "maman mima, tunda nayi wata biyar ai kamar yaune zan dawo, ki qara hakuri, yakika ga autar mama?Da fatan tazo lafiya,"

husna tace "lafiya kalau, takusa Zuwa minma," tahir yace "eh gaskiya kam yakamata, Allah yakawo ta lafiya,"
husna tace "amin"

** *** **

"Mama zanje maqota mu gaisa na dawo,"

"to saikin dawo, ki gaishe su,"
baby tayi sauri tatashi, tana kade hannunta, zatabi bayan feenah,🤣

mama tace "zo nan izdihar, karkije aturaki titi da niyya mota ta kashe ki, 😃"
buta tadauka Zata shiga toilet, feenah ta girgiza kai kawai ta fita, izdihar naganin mama tashiga toilet, tayi wuf tafice da gudu, 🤣
Nayi nisa atafiya, naji anjamin hijabi na, cikin murna tace
" yeee nataro ki, "
kallanta nayi da mamaki nace" ke meya futo dake daga gida? Ba mama tahanaki ba?" Kallo na tayi, tana murmushi tace

" to ai inaso inbiki, Dan Allah zaki tafi Dani wajanki idan zaki koma inda kika zo?"
Feenah tace" nima inasan tafiya dake, Amma bazai iyu ba, kiyi hakuri kina Zuwa school kuma

gasu mama da Abba, da qawayen ki na school,"
cikin murna tace

" eh tona fasa binki, Amma de ina sonki"

Nima nace "ina sanki baby," tafiya mukaci Gaba dayi, nace "baby baki gaji bane? Oya zona goyaki,"
tsugunna wa nayi tahau bayana, muka tafi, tace " sabuwar anty, kina goyani kullum, mama bata goyani,"

nace "baby bakisan sunana bane?"
Tace "emana, ya sunanki?"
Nace "sunana baby nima, irin naki,"
tace "laaa ashema sunanmu daya,"

nace "keni bansan shirme sunana nafeesa," tace "nide baby zance," 🤣

nace "kina fada ina bige wannan bakin naki," daria tasa, ahaka mukaje unguwar kafin mudawo tayi bacci, mama na falo taga mundawo, tace
" ashe ta biki," nace "eh mama, ai tayi bacci ma," mama tace  " itama de batada zuciya,"

murmushi nayi kawai na kyale mama
Naje na kwantar da ita

Da daddare ina karanta novel awayata, nayi wanka nayi shirin bacci, saiga baby tazo da littafi tace, "sabuwar anty inzo ki koyamin karatu?" Nace

" eh, zo ki zauna,"
ta zauna nafara yi mata, kuma sosai nafahinci yarinyar tanada kokari, nace "to yimin bayani,"

filla filla tafara yimin bayanin, nashagala ina kallanta, har muka Gama, nace "to ki tashi kije ki kwanta,"

matsowa tayi jikina tace
" um um, sai anjima tukun," 🤣

nace "to karfa kimin bacci mama tazo tanata nemanki," tace "nifa anan zan dinga bacci, nabar Dakin mama," 🤣

nace "a a baby yahaka,"

tace "Toni wajanki nakeso," tafadi haka kamar zatayi kuka, nace
" toyi shiru, kwanta,"

Maimakon ta kwanta Akan gadon, saita matso jikina ta kwanta, tace
" sabuwar anty,"

nace "baby kidena fadamin sunan nan,"
tace "to, taci Gaba da cewa kema kina sona ko?"

Kallanta nayi nace," sosai ma baby, ina sonki, kamar cikin duniyar nan baki daya,"

murmushi tasaki bata sake magana ba, bacci yadauketa

After 1 week
Nagama shirya kayana tsaf, nace " to mama zan tafi, Abba saina dawo,"

Abba yace" to mama na idan kinje ki gaida su husna," nace" to zasuji Abba, "
Jakata na dauka, aikuwa baby tasa kuka tariqe jakar
," Allah Abba zan bita, nide bazata tafi tabarni ba,"

Abba yace" ke izdihar, banasan shirme kinji ko, idan kin bita makarantar fa? "
Nima idona yayi ja, Inason tafiya da ita, acikin raina, to naga su mama basu ce intafi da ita ba,
Na dago kai nace" to Abba kabarta mutafi," Abba yace" mamana school dinta fa?" Nace
" zan shiga makarantar inyi musu bayani", mama tana kallanmu tace "nide nafeesa karki dauki yar nan kinga babu idonmu ki cutar da ita," 🤣

nace "mama wallahi Babu abinda zai faru," tace "Toshiknn"
Aikuwa aka hada mana kayanmu awata jakar, dole Abba ne yace shi zaije school din ya nema Mata alfarma
Amota haka taita bani labarin school dinsu, gidan husna direct muka sauka, ummi sai nan nan take damu, Gaba daya bangarenta muka dawo, sai dare muke komawa part din husna, washe gari agidan kaka muka wuni, nida baby dasu mima
Har mijinta tahadani dashi mun gaisa, yace shima yaso yana gida nazo, Zahra ma takawo min ziyara, haka muka wuni muna bawa anty husna firar Sudan
Munje gidan kala ma, mun wuni, aysha anata shirin biki, mai gyaran jiki tanata fama, wani watan za'a sha biki

Duk wani wajan yawo da wasan yara babu inda bankai baby ba, muyi ta pictures nida ita, muna wanka zan zare ta mu shiga gari, mune gidan zoo, mune Park, sosai munsha yawo,
Nima na kaiwa Zahra ziyara nida baby, haka tabawa baby sweet sosai, har su pictures sunyi dasu video sunata shirmansu
Satin mu daya a kano muka dawo gida

Cikin sati biyun danayi agida, sosai muka shaqu da baby, bana iya bacci ba tare dana jita ajikina ba, pictures, videos duk haka nake yi Mata da wayata, wani kuma muyi tare, mun shaqu sosai,

kuma mun saba, ahaka har sati biyu na tacika, nafara shirin komawa makaranta
Ranar dazan koma, saida aka yiwa baby wayo tatafi school sannan muka tafi kano, nahadu da Zahra muka tafi airport, ina kuka mukai sallama dasu mama da husna dasuka rakoni
Kuka na daya baby, bansan yaya zataji ba idan taga bana nan

Muna sauka kuwa nakira su mama nace musu mun sauka, tacemin ga baby nan tana zazzabi, tun rana take kuka, taga bana nan, ni kaina kuka nasawa mama, tace" to yanzu kukan zakiyi kokuma so kike nima ki karyamin zuciya, ga yarinya babu lafiya", haka mama taita min fada har mukai sallama

** *** **

After 1month, alhmdlh nafara karatuna cikin kwanciyar hankali, kusan kullum sainaji muryar 'yata nakejin dadi,🤣
wani lokacin ina karatu, haka nake bari, sainaji muryar ta sannan zanci Gaba da karatun, Allah Allah nake ingama karatun nan in koma kusa da yata, inde ina missing dinta videos dinta nake kallah kokuma in kalli pictures dinta, haka mukhtar ma, har pictures dinta natura masa

** *** **

I V yake ta rabawa abokansa na office, yana cewa "wallahi wata yata ce, za'a yi bikinta wannan weekend din, Dan Allah ku daure kuje"
Ahmad yafuto cikin sauri yana waya, zai fita daga company, Ammu ya karasa suka gaisa, ya miqa masa iv din shima yace "yallabai ina gayyatarka Zuwa wajan bikin wata yata da za'a yi," ahmad ya karbi iv din yace "hassan ko itace wadda kadauko daga school kwanaki?"

Ammu yace "a a ya'uwarta cede,"
ahmad yace "Toshiknn insha Allah zanyi kokari inzo nima,"

daga haka yayi waje

** *** **

"Izdihar karfa kiyi wani wajan, wanka kawai zanyi inzo mutafi, kinga abbanki yaji ma da shirya wa,"
baby tace "to mama"
Yar babynta ta dauka, tafara yimata kitso, tanata waqa, har mama ta futo, cikin shiri, izdihar ta

kallah duk tabata kwalliyar ta, janyota tayi tagyara Mata, taqara gyara Mata parking din gashin ta, sosai idan ka kalleta zakace yar turawa ce, kwata kwata bazakace tanajin wani yare hausa ba, Riga da wando ne ajikinta ja, tayi kyau sosai yarinyar kamar ka sace ta kagudu
Mama nagama komai, suka dau hanya
Gidan kala suka sauka, anan suka tarda su husna da yan biyunta harda ummi
Anata hidimar biki, husna na wajan amare anata shirya amarya 🤣

Karfe biyu daidai aka daura auren aysha da angonta nasir,akofar gidansu,
izdihar na Zuwa wajansu mama da mima, nan suka fara wasa, Ana wasa rimi rimi, anan ta nuna halin nata na tsokana, 🤣🤣
mama da mima suka biyo ta da gudu, suna saisun Rama
Tafita waje da gudu

Suna tsaye shida abokan ango sunata gaida shi, kasancewar sa sanannan mutum, sai murmushi yake, yaci manyan kaya cikin farin yadi mai tsada

Kawai yaji anbigeshi, kuma anriqe masa kafa anacewa
"boyeni, boyeni," 🤣

juyowar dazaiyi yaganta, gabansa yayi mugun faduwa, tsananin kamar dasuke da itane yasa cikin rawar murya Ahmad yace "MY FEENAH"

Mrs usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dubun godia gareki, yanda kike bibiyar novel dina, nima ina tare dake, kyautar wannan page izuwa Garki
@RESPECTABLE

45

Tahir yaci gaba dacewa, "Amma hakan bawani matsala bane, idan muka dora shi Akan magani

insha Allah za'a samu abinda akeso"
Ahmad shiru kawai yayi yana kallan tahir
Laila nagama Jin wannan batun tasaki tsaki, fuuuu ta tashi tafice daga office din har tana bigewa da kujera Amma ko juyowa batayi ba

Ahmad ya sunkunyar da kansa, tahir yayi shiru,shi kansa ya rasa da wanne kalma zaiyi amfani da ita wajan bawa aminin nasa hakuri, saboda haka yatashi daga kujerar dayake kai, yadawo ya tsaya agefen ahmad yafara bubbuga bayansa alamun rarrashi,

ahmad yadago kansa cike da damuwa yace
"meyasa tahir? Meyasa?" Nan danan qwalla ta cika idonsa

Tahir idansa yakada yayi jajir, yace. "Ahmad kayi hakuri mana,ni dakai duk dayane ahmad, kaga karkasa damuwa aranka, akan abinda yafaru, ni inde haihuwa ce wallahi nahakura ahmad kadauki su mama, nabaka su, inde Akan yara ne zaka daga hankalin ka, nina hakura, banaso ka sake shiga cikin damuwa ahmad, tunda kasan abinda yake damunka, ba'a San kacika tunani "

Ahmad ya kalleshi yace
" tahir tabbas abin da ciwo, Amma Babu komai, damuwa ta daya tahir meyasa baka sanar Dani hakanba tunda farko?"
Tahir yace" ahmad tayaya zan tabbatar da abinda nake tunani bayan bakada aure alokacin? Ni kaina hasashe nake a wancan lokacin
Ashe abinda nake tunani zai zama gaskiya, kaga yanzu tashi muje mu lallaba madam mu bata hakuri "
Ahmad yace" tahir yi zaman ka, kabarta kawai idan nakoma gidan zamu tattauna nida ita,ni fishinta bai wani dameni ba, saboda bana kaunar ta, ni badan kada nayiwa Allah butulci ba, danace gara ma da bazan iya haihuwar ba, dade inhada jini na da laila,saboda banga tarbiya awajanta ba bare yaran dazamu haifa su samu, sannan tahir kabar maganar su mama, kaimafa su kenan awajanka tahir, ummi tanasan yaran Sosai saboda me ni zan dauke muku su,
Tahir inajin kaunar izdihar sosai araina, banajin iyayen dasuka haifeta ma, zasu kaini sonta 🙆🏻 ni idan aka bani itama ta isheni rayuwa
Katayani da adduah tahir Allah yasa iyayenta su amince da buqatata "

Tahir yayi ajiyar zuciya, yace" ahmad karka damu inde Akan wannan ne, idan ma basu yarda ba, nima zan shiga cikin maganar insha Allah zasu bamu ita,"

yaqarashe maganar yana murmushi, ahmad yayi masa wani irin kallo, yace" abamu ko abani? Aiku kun nema anhanaku, yanzu lokaci nane, "
tahir yace

" to hammad baban izdihar, "
ahmad yasaki daria kamar bashida damuwa yace" kai Amma tahir naji dadi wallahi, idan aka

bani izdihar wannan uncle din datake kirana dashi denawa zatayi, takirani da.... "

Cikin sauri Tahir ya katse shi, yace "daddy?"
Ahmad yace "no banasan daddy
Nafisan takirani da Abeey," tahir yace "um kun koma larabawa kenan,"

ahmad yace "ka manta da jikansa kake tare, Dan renin hankali kawai,"

tahir yace " naji,"
Ahmad yaci gaba da fadin " idan kuma na auri my feenah, nasan itama inde taga baby Zata sota, kaga ita kuma saita dinga kiranta da ummi"

Tahir ya harare shi cikin wasa yace "wannan ai sata ce, da gasa" 🤣

Ahmad yace "edin mun sata,"

tahir yazuba masa ido yana kallansa cikin ransa yace Allah yabaka feenah ahmad, wato har yanzu de tana nan aransa, ahmad yace "gaye kallanfa?"
Tahir yace "kawai so nake naga yaushe zaka haihu, bansan wanne irin so zakayi wa yaranka ba, wannan yarinyar izdihar ma kana Mata irin wannan son"

Ahmad yabata fuska yace "oh tahir naroqeka kadena banbanta izdihar da yaran dazan haifa, itama yata ce"

Tahir yazuba masa ido yana ganin karfin Hali, yace "Toshiknn daddyn izdihar, magana yaqare"

Ahmad yayi shiru, sai can yace "tahir nikuwa kunada irin qwayar da aka sakamin nasha?"
Tahir ya kalleshi da mamaki, yace "eh akwai mana me zakai dashi?"

Ahmad yace "nikuwa me zanyi dashi tahir kawai ganinta zanyi"
, waya tahir yadauka, yabada umarni, nan da nan aka kawo masa ita,tahir yace "kaganta nan idan mutum yasha ta wuce guda biyu, shine take yi masa illah,"

ahmad yakarba ya karanta, yace "shikkenan nagani ungo abinka

Nizan wuce gida,"

tahir yace "Amma ahmad bamuyi magana Akan magungunan dazaka dinga shaba,"
Ahmad yace "no karka damu tahir, nafadama nifa izdihar ta isheni, kabar maganin kawai, latter mayi magana,"

tahir yace "ok,"

yafuto domin rakashi wajan mota, anan yajashi yafara nuna masa yanda yakeso ya maida fasalin hospital din

** *** **

"Mom wallahi bazan iyaba, dama nafada miki, ai wannan zaman danayi ma nayi hakuri, kinga kuwa yanzu tunda bazai iya haihuwa ba, mezan zauna inyi agidansa,"

hajiya salaha tace
" gaskya kam tayaya ma zaki zauna da mutum fanko, ai gara kibar masa gidan, wannan jaraba har ina, Allah yabaki wani kawai,"

laila taka she wayar ba tare datace amin ba, mai taxi din tabawa umarni yaqara sauri, tagaji da wannan tafiyar dayake kamar bayaso
Tana Zuwa gida batayi bangaren taba, Part din su mamy tanufa, suna zaune dukansu mabruka, yan biyu Muslim da bukhari, da auta maryam, laila tashigo duk bata hayyacinta
Mamy hakima tace "laila lafiya?"

Laila tace "mamy da momy zanyi magana bada keba" 😳

Mamy hakima najin haka aranta tace babu lafiya, mom tace "inajin ki laila meya faru?"
Laila ta kwashe komai tafada musu, tace
" nikuma bazan iya zama da juya ba, Dan haka ku fada masa yasakeni, bazan iya zama babu yara ba, ashe ma Dan naku Dan shaye shaye ne, inba Dan qwaya ba, meya hadashi da shan qwaya har takai shi ga samun matsala, to nide bazan iyaba,"

tana fadar haka tajuya tayi gaba

Mabruka dayake itace babba maidan hankali, nan da nan tafara kuka, momy tace" innalillahi wa inna ilaihir raju'un"
Mamy hakima kuwa itama kuka tasa, tace
" mun shiga uku, wannan wacce irin masifa ce Zata shigo mana gida, gaskya nikam ban yarda ba"
Mamy tace "hajiya ba'a shedar Dan Yau, Muslim dauko min wayata"
Yana kawo Mata wayar, ta kira ahmad tace
" waladee kazo gida yanzu inasan ganinka,"

ahmad najin haka yace cikin ransa sun samu labari kenan 🤣

** *** **

"Haba Abban husna, wacce irin magana ce wannan? Ahmad fa yayi mana komai, nikam yaron ya kwanta min araina, nayarda da tarbiyar shi, Dan haka inde nice babu damuwa na bashi baby," 🙆🏻

Abba yace "to shikkenan alhmdlh, yanzu zamu fadawa ita nafeesa ne kokuwa?"

Mama tace "haba alhaji ita take iko damu kokuma mune muke iko da ita, idan aka bada baby kamar qarin rufin asirinta ne ai, Akan abin kunyar data janyo mana, Dan haka ni aganina kawai aqyaleta,"

Abba yace "to insha Allah idan tadawo sai nayi Mata bayani dakaina," mama tace "hakan yayi,"

Abba Ammu yakira awaya, yafada masa shawarar dasuka yanke Akan maganar ahmad, Ammu cikin ransa yace gaskya ahmad yasamu karbuwa sosai awajan yaya
Shima kai tsaye yace " ai Babu komai, ahmad kowa yana masa shaidar kirki,"
Mama tace "to ai kaji alhaji, nikam wallahi banji dadi Bama daka bashi sati dayan nan, sai yaga kamar bamu yarda dashi ba, Dan haka kirashi kafada masa gobe yazo yadauke ta su tafi, tunda itama kanta yarinyar tana sanshi,"

Abba yace "hakane, Amma kinsan komai yana buqatar shawara, shiyasa na bashi sati dayan," sake daukar wayar yayi, yakira ahmad, alokacin yana kan hanyar sa ta Zuwa gida, Abba yana fada masa, ahmad ya dinga kwarara godiya, kuma yace insha Allah gobe zaizo gidan, dahaka sukai sallama, parking yayi agefen titi, yafuto daga motar yayi sujud shukur, yanata farin ciki, sannan yakama hanyar gida

** *** **

Yana Zuwa gidan,tun kafin yagama gyara parking din motar sa laila ta taho da sauri tace,
" dama jiran ka nake, ahmad inaso kasani zamana dakai yaqare, kasakeni kawai shine abinda nake buqata,"

ahmad yace " laila kanki daya kuwa? Meya kawo wannan maganar? Kinga kije ciki, ina Zuwa zanzo sai muyi magana,"
tana huci tayi part dinta

mabruka naganin ahmad yashigo falon tahada kan qannanta sukai daki, momy tatashi cikin fishi tace" ahmad mai nakeji? "
Ahmad yace cikin rashin damuwa" momy me yake faruwa naganku haka?"

Momy ta dauke shi da mari, cikin sauri ya riqe kumatunsa, cikin mamaki yace"momy?"
Mamy hakima tace "my son, meya kaika shaye shaye har hakan yahaifar ma da rashin haihuwa?" Ahmad yace "shaye shaye mamy, ni ban taba shaye shaye ba" ,
momy cikin fishi tayi kansa tace "laila karya Zata ma ne?
Kokuma mune zamuyi Maka karya?"
Ahmad zuciyar sa takarye, nan da nan yafara kuka, yace "momy ki yarda Dani mana, wannan bahali na bane,"

mamy hakima tace "munji Ahmad Amma me yake faruwa,"

cikin hawaye ahmad yace "momy, mamy, kuyi hakuri, ni ban taba shan qwaya ba, wannan dalilin ne yasa nakori walaya daga cikin gidan nan, wani yabata magani da kudi Akan ta sakamin acikin lemo nasha, kuma tayi nasara akaina, nasha, nasha momy"

ya qarasa yana kuka 😭

Yace "wannan qwayar datasamun itace dalilin dayasa likita yace bazan iya haihuwa ba, saboda nasha dayawa, sannan... zaici gaba da magana wani irin Baqin ciki yatokare masa maqoshi, har gobe idan yatuna abinda yayiwa feenah abun yana qona masa rai

Momy tayi jagwab ta zauna Akan kujera, mamy hakima tace "mun shiga uku, meyasa baka fadaba ahmad? Aida an tambayeta waye yasa ta aikata hakan"

Ahmad yace "mamy na tambayeta harma tabani number datake magana da mutumin, Amma alokacin ina cikin fishi, saina fasa wayar"

Mamy hakima tace
" innalillahi, kaga tashi kaje kabawa matar ka hakuri, zamuyi magana anjima"
Ahmad ya share hawayen sa, yatashi yafita

Yana Zuwa part din, yaga laila bata nan, Dan haka yabita daki, tura kofar yayi a hankali yashiga, Amma kuma waya take bataji shigowarsa ba, taci Gaba da waya tana fadin

"Wallahi sofy kede bari, ai nake fada miki, qwayar dana bayar asaka masa ne kwanaki, 😳🙆🏻toya zanyi sofy, nakira shi nayi nayi dashi tawaya ina kaunar sa, yabani dama inbaiyana masa son danake masa, Amma yaqi, shiyasa kin sanni ba jira nabawa musa aikin, Naso kawai dana dandani zumar sa in wullar dashi, Amma bansamu hakan ba, Dan haka nayi amfani da yar aikinsu kawai, kuma still shima abun yaci tura, kinga kuwa dana sameshi yanzu sama taka, ai kinga saina kyaleshi kawai, yasakeni kawai, akwai alhazan dasuke jirana "

Idonsa ne ya rufe ruf, yadena gani, kamar makaho haka yajuyo baisan inda yake jefa kafarsa ba, yanabin bango ahaka ya qarasa falo, kan kujera yafada, yana ambaton

" innalillahi wa inna ilaihir raju'un 😭 "

Mrs Usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my lovely sis golden girl

44

Tsugunna wa yayi daidai tsawon ta, yafara kallanta, itama zuba masa ido tayi, tana aikin kallonsa, ahmad yace "ya sunanki? Kuma keda waye kike gudu haka?"

Tace "sunana Baby" , ahmad yace "baby kuma?"

Acan cikin gida kuwa, mama ce tanemi husna tace "yi sauri, naga su baby sun fita da gudu, nasan fada suke jeki kirasu"

Ahmad yace " nace keda waye kike gudu haka?"

Tace "nida qannai nane, gasu can,"
su mima ne suma suka taho da gudu, suka riqe ta suna" mun kamaki,"

mama tace" laaa uncle,"

nan da nan dayake su sun sanshi suka riqe shi, ahmad yace " kunga muje kushiga gida kudena guje guje,"

Ammu ne yahango shi tare da yara, yaqaraso da sauri, yace

"yallabai fada suke ko? Bari nakai su gida,"

cikin sauri ahmad yace "a a hassan bari in kaisu, kasan wannan yarinyar ne?"

Yafada yana nuna baby, Ammu yace "eh nasanta," ahmad yace "ok bari in kaisu,"

nan kuwa yafadi hakanne danya sake samun damar kallan yarinyar

Saida yakawo su har bakin kofar gidan, Amma hankalin sa yanakan wannan yarinyar, nan sukai kicibis da husna, cikin sakin fuska tace
"a a kaga angon lailah,"

ahmad yace "gwauruwa"
Husna aranta tace um Yau kuma yan wasanne akansa,
Gaisawa sukai, yace
" Mata nima nazo daurin aure ne, saikuma naqare arabon fada,"

husna tace "ai inde izdihar ce har ka gaji, haka take bataji, kuma fadan ma da qannanta ,"

ahmad yace "au haka sunan ta?" Tace "eh"

Cikin ransa yace "izdihar"
Suna mai dadi
Sallama ya yiwa husna, yajuya yana kallan baby yatafi

Husna tace "sarakan rigima saiku juya mutafi aiko,"

tayi gaba su mama suna bayanta, juyowa tayi kawai sai ganin baby tayi ta tsaya tanata kallan ahmad dayake tafiya, husna tace "wannan yarinya bataji,"
ta daga murya tace "baby taho mana,"

da gudu izdihar ta taho

** *** **

Gida yakoma cike da gajiya, kasancewar yatsaya gaishe gaishe duk yagaji, dining ya kallah, aransa yace " tofa Yau yaushe"
Daki yashige yayi wanka yafuto da kayan shan iska ajikinsa, afalo ya zauna ya kunna kallo, Amma Gaba daya tunanin sa baya tare dashi, yana tare da yarinyar nan, murmushi yasaki daya tuno ta, aransa yace meyasa nakejinta araina ne haka?
Allah sarki my feenah, bayan rabona dake Yau naga photo copynki,ya Allah!
Meyasa nakasa cire yarinyar araina, laila ce takatse masa tunanin sa, tace " Majnunun lailah, ga abinci a dining fa naga ko budewa bakayi ba,"
ahmad yace "ok aiji nake wani kika hadawa, tunda naga bayi kikeba, sannan laila naroqeki Dan Allah kidena fadamin sunan nan, banajin dadin sa," 🤣

laila ta harzuqa cikin fishi tace "ok bakajin dadin wannan sunan, saide feenah ko?"

Ahmad ya kalleta da mamaki, "ya akai kikasan wannan sunan?"
Laila tace. "ai dole kayimin wannan tambayar, kullum bakada aiki sai Kiran sunanta da daddare, wallahi zan nemi wannan yarinyar sai jikinta yagaya Mata" ,

Ahmad baisan lokacin daya saki daria ba, ya kalleta yace, "da gaske? Amma wallahi Dakin taimaka min, ni kaina nemanta nake, laila da kinyi babban jihadi idan kika shiga duniya kika nemota, ni kaina dana soki" 🤣

Zuciya tazowa laila wuya, cikin takaici tajuya tayi daki, wato Yama maidata mahaukaciya, itace Zataje yawon duniya ta Nemo masa mace, lalle 🤣

** *** **

After 2 months
"Uncle, idan nayi tsokana zaka dinga taremin?"

"To meyasa zakiyi tsokana? Bakya Jin magana ko?"
"To uncle kenan kai baka sona ko? Nikam ina sanka"
Cikin sauri ahmad yace
" izdihar ina sanki mana," turo Dan qaramin bakinta tayi, tace "nide um um, natafi tunda baka sona, bakasan ka taremin tsokana,"
ahmad yace "ina sanki mana, tsaya kiji,"

"a a uncle natafi baka sona,"
kawai tasa gudu, yana "baby! Baby!!"

Amma ina tatafi

Cikin baccinta taji yana fadin "Baby ! Baby!! Baby!!!"
Takaici ya isheta, fillon dayayi matashi dashi tajanye, cikin sauri yafarka daga baccin dayake, yace "laila, lafiya ina bacci zaki tasheni?"

Laila tace "wato abin Naka kullum qara ta'azzara yake,🤣
da kaine feenah, yanzu kuma ka dawo Kiran wata baby
Wacce shegiya ce baby kafadamin?"

Ahmad yace "Allah yabaki lafiya," 😏

yadauki fillonsa yakoma falo
Daga murya tayi yanda zai jiyota, tace "saide yabamu lafiya Gaba daya, bazan iya zaman wannan jarababban auren ba,"
tayi juyi gamida rufe idonta

** *** **

Ita kadai ta qyalqyale da daria, tana zaune afalo, da teddy ahannun ta, mama datake linke kayan Abba tajuyo ta kalleta da mamaki, tace
" izdihar kedawa haka yarinya kamar me aljanu? "

Baby tace" mama rannan na tuno, naqwace abin wasan su mima nagudu, ingaya miki ko mama ina fadawa wani mutum yaqi karbe abin daga wajena, kuma yake ta kallo na, shine nima naketa kallansa, kuma kullum kullum saina tunashi mama "

Mama tace" yaushe kika ce? "🤣

Baby tace" mama nace miki rannan "
Mama tasake kallanta cikin mamaki tace" toko amafarki kika hadu dasu? "🤣

Baby tace" mama rannan fa da mukaje auren anty aysha"
Mama tace "kekiji shirme, Abu kusan wata biyu,amma kicemin rannan"
Izdihar tasa daria, tace "to mama kema zakina taremin idan nayi tsokanar?"
Mama tace "ban fada miki ba, shima kuma bai kyau tamin ba, dabai dakekiba, tunda ke kullum kunnan qashi ne dake"
Mama tana wannan fadan Wayarta tadau qara, feenah ce ta kirata, bayan sun gaisa mama tabawa baby wayar, Ana bata wayar tayi daki da gudu, tana cewa, sabuwar anty, infada miki rannan nahadu da wani ya taremin tsokanar danayi 🤣

Mama aranta tace ai Yau kuma mun shiga uku 🤔😃

** *** **

Wayarsa yadauka yakira hassan, cikin sauri Ammu yasameshi a office dinsa, ahmad yace
" yauwa dama inasan inma wata tambaya ne, yarinyar dana gani kwanaki, shine nace Dan Allah inane gidansu, inaso inje inganta"

Ammu ya kalli ahmad da mamaki, yace "wai izdihar?"

Ahmad yace "eh itafa, wato hassan inajin kaunar yarinyar ne acikin raina, yanda baka zato, tun lokacin dana ganta, naji inasan kasancewa da ita, please a wacce unguwa suke?" 🙆🏻

Ammu yayi murmushi yace "ai yallabai a zaria take,"

gabansa ne yafadi, cikin ransa yace zaria, garinsu feenah fa kenan

Ammu yaci gaba da fadin "ai yarinyar yaya nace, itace qaramar yarsa,"

ahmad yace cikin "mamaki yayanka?kenan kanaso kacemin sister husna ce?"

Ammu yana murmushi yace "hakane yallabai,"

ahmad yace ikon Allah, to bani address din gidansu please, saboda bazan gane ba, rabona da naje Tun bikin su Husna "

Babu bata lokaci Ammu yabashi, ahmad baiyi wata Wataba washe gari yatafi zaria,🤔
da rana ya isa gidan, yafaka motarsa a gefe, manyan kaya ne ajikinsa, yatsaya awaje, yarasa wazai aika ayi masa sallama damai gidan
Kamar anjefota saigata da gudu tazo Zata shiga gida, aransa yace yar halak, wato itade da'iman tana cikin gudu, daga murya yayi yace "baby!!"

Juyowar dazatai ta ganshi, wajanshi ta qaraso da sauri, ahmad yace "daga ina kike da gudu haka ?"

Tace "daga school"
Saida tafadi haka sannan ya lura da uniform din jikinta, da kuma lokaci, yasan yanzu ne ake tashin yara a school, yace "to zo nan"
Matsawa tayi kusa dashi, ahmad ya tsugunna daidai tsawon ta, yace
" kin gane ni?"
Baby tace "emana, kullum saina tunaka, jiyama nabaiwa sabuwar anty labarin ka" 😳

Ahmad cikin ransa yace kullum saita tunani, tome yake shirin faruwa ne? Yace "nazo ne nima naganki,"
washe baki tayi tace
" Allah?"
Kafin yabata amsa tace
" ina sonka,"

tafada jikinsa, ahmad yayi saroro, baiyi wata Wataba shima ya rungume ta 🤣
Tsayuwar motar dasuka jine ya ankarar dasu, baby tatafi da gudu wajan Abba, tace "sannu

Abba,"

Abba yace "sannu izdihar"
Yafada yana kallan ahmad, kamar yasan fuskar
Ahmad yaqarasa suka gaisa, Abba yace "kamar Naso in gane ka"
Ahmad yayi murmushi yace Abba "ahmad ne abokin tahir"
Abba yasaki murmushi yace "yauwa nifa ince,"

nan suka sake sabuwar gaisuwa, Abba yace
" qaraso mana"
Cikin gida suka shiga, mama takawo masa ruwa da lemo, Abba yayi shiru shima ahmad yayi shiru,🤣

shi dama gashi ba damunsa maganar tayi ba, can de yadaure yace
" Abba dama nazo ganin baby ne,

" Abba yace "wai izdihar,? ikon Allah, izdihar mai jama'ah," 🤣

kiranta Abba yayi, tana Zuwa tace "Abba ga wanda nabaka labarin sa rannan nace yataremin tsokana,"
mama da zuwanta kenan tace "au wai dama shine yatare miki tsokanar? Ikon Allah, ai labarin ka babu wanda baiji ba agidan nan," 🤣

ahmad yayi murmushi
Baby wajansa Takoma, tazauna a kusa dashi sosai, tasan idan tazauna ajikinsa Abba dukanta zaiyi
Mama da Abba fita sukai suka barsu
Abba ya kalli mama yace
" ina tasan shine?"😳

Mama tace"to wa yasani ne alhaji, nide cemin tayi awajan auren aysha,"

Abba yace" tofa ikon Allah, Allah mai hada jini "

Sai yamma lis ahmad yace zai tafi, sweet, yar baby, teddy, Babu abinda bai kawo wa baby ba, dazai tafi yanda kasan tashige motar, saida mama ta riqeta 🤣

Awannan dare Baby rasa inda Zata dora ranta tayi saboda wannan kayan wasa
Ammu ne yakira Abba da daddare, suna zaune shida mama a tsakar gida, bayan sun gaisa
Ammu yace "yaya dama yallabai ne yace in bashi address dinka, zaizo yaga izdihar,"

Abba cikin mamaki yace "waye kuma yallabai?"

Ammu yace " wanda nake aiki akamfaninsa,"

Abba yace "wai dama kaine kabashi address din gidan nan?"
Ammu yace "wai yazo ne yaya?" Abba yace "dazu dazu yatafi,"

Ammu yace " jiya jiyafa na bashi, Amma har yazo Yau?" Abba yace "wallahi yazo, nayi mamaki ma dayace ganin izdihar yazo,"
Ammu yace "wallahi yaya nima nayi mamaki, da yacemin yana qaunar baby," Abba yace " Allah kenan mai hada soyaiya
Anan sukai sallama"

** *** **

After 5 months
Abubuwa dadama sun faru,ciki harda shaquwar baby da ahmad, harya kasance ahmad baya sati daya batare daya zo yaga baby ba, ta saba dashi yanda mai karatu baya zato, harya kasance yanada number mama da Abba, kowa yakira acikin su zasu bashi ita awaya suyi ta fira kamar ba kudi yake sakawaba, sosai abin yake daurewa su mama kai 🤔
Sun yarda da ahmad sosai, sun dauki son duniya da yarda sun bashi, har bashida iyaka da gidan, yana Zuwa zai shiga kamar dan gida, saide abinda yake damun ahmad guda daya ne, duk lokacin dayazo idan zai tafi da kuka yake rabuwa da baby,  yariga yayardewa kansa cewa kawai Allah ne yahada jininsa dana yarinyar, kuma yake qara Santa saboda kamar dasuke da feenah

** *** **

Cikin office dinsa yakira Ammu, ahmad yace
" hassan dama wani aiki zan saka,"
Ammu yace "to yallabai,"

check ahmad yarubuta yabawa Ammu yace gashi kaje bank kaciro wannan kudin, ka gyarawa su izdihar gidansu, su Dan koma wani wajan arushe nasun ayi musu sabo, duk abinda babu kayimin bayani, banaso kwandalarka tayi kuka aciki,"😳
Ammu kasa godia yayi, kawai yariqe hannun ahmad yace" bansan Dame zanyi ma godia ba yallabai," ahmad yace
" karka damu, zan iya yiwa baby komai,"

dasu mama sukaji wannan labari kuka tasa, Abba kuwa har kano yazo ya yiwa ahmad godia, haqiqa sun tabbatar izdihar alkhairi ce agaresu, Babu yanda suka iya, gidan Ammu daya tashi suka koma dazama, dayake aikine da kudi, cikin wata biyu aka Gama komai, su mama suka tare agidansu, wannan abun yasa suka qara ganin qimar ahmad da kuma daukarsa da

muhinmnci

** *** **

"Serious baban yan biyu?Gobe goben nan? Wayyo Allah, irin wannan surprise haka, to fadamin mai mijina yake so namasa?"
Tahir yace " duk abinda kikamin yayi,"
husna tace "ka fadawa ummi?" Tahir yace "nafada Mata yanzu,"

tace "Amma ahmad fa?" Tahir yace " ban fada masa ba so nake saide yaganni kawai"
Husna cikin Jin dadi da murna tace "wayyo my heart, to naji yanzu de fadamin abinda zan girka Maka gobe in tashi yanzu nafara shiri"
Tahir yace "aiba saikin wahalar da kanki ba, ke kadai ma kin isheni," husna cikin sauri takashe wayar, tahir yace "zamu gamu ne"

** *** **

Washe gari da yamma ahmad nashirin fita daga office, kansa aqasa yaji yayi Karo da mutum agabansa, yana dagowa yaga tahir, yace " mafarki nake ko gaske?" Tahir ya mintsineshi, aikuwa nan ahmad ya rungume shi, suka saki ihun murna, ahmad yace" tahir kamar kasan inasan ganinka yanzu, wallahi wata muhimmiyar magana nakeso muyi, kuma sai gashi Allah yakawo ka adaidai lokacin daya dace," tahir yace" ina jinka ya akai "
Ahmad bai boye wa tahir komai ba yafada masa, tahir tace" ahmad kayi kokari, gaskya soyaiyar dakake yiwa feenah babba ce, kawai daga ganin kama? Amma guy kana ganin abinda kake shirin aikatawa kuwa zai iyu? Saboda husna tasha fadamin yanda suke kaunar yarinyar, "

ahmad cikin jimami yace
" karka damu tahir zan gwada, "
tahir yace" Toshiknn, yaushe zakaje zarian?" Ahmad yace" yanzu, yanzu zanje tahir, inasan yarinyar sosai, "

tahir yace" toshkn idan ka dawo kayimin waya, sai nazo musha fira," ahmad yace" basai kafada ba tahir, har gidanka zanzo, "
tahir yace" serious ahmad"
, ahmad yace "serious tahir, ka fadawa madam tuwon dare tayi Dani"

Dahaka suka rabu ahmad yadau hanyar zaria

Karfe uku daidai a kofar gidansu izdihar tamasa, kamar kullum suka gaisa da Abba, Abba yace " ahmad shigo mana," ahmad yace "Abba dare yayi, inasan komawa ne da wuri, dama Abba magana nakeso muyi dakai, Dan Allah Abba katemaka kabani izdihar, inaso koda yaushe

inganta kusa Dani, inzame Mata uba da uwa kamar ku Abba," 😳
🙆🏻

Abba ya numfasa yace
" ahmad babu abinda zaka nema awajena karasa, nide ta wajena babu damuwa, Amma kabani sati daya, zanyi magana da maman ta duk yanda mukai zakaji," ahmad yace" toshkn Abba na gode insha Allah zan dawo inji yaya kuka yanke," dahaka sukai sallama

** ** **

After 2days
" Ahmad da kaifa nake, ka tashi ka shirya muje asbitin nan, nagaji da wannan rashin haihuwar," ahmad yace" laila, saunawa zan fada miki haihuwa ta Allah ce idan yanufa zamu samu"

, laila tace "a a nikam nagaji kawai katashi muje,"
Babu yanda ahmad ya iya, dole ya shirya suka tafi, ba suje ko inaba sai asbitin tahir, tahir yana office shida wani doctor suna tattauna yanda zasu sake tsarin asbitin Gaba daya, su ahmad suka shigo, daya doctor din yafita yabasu waje,
Tahir yace" a a kaga amarya da ango," laila Ana yatsina aka amsa, tadau kafa daya ta dora Akan daya, Ahmad ne ya yiwa tahir bayanin komai, tahir yace
" ok Babu damuwa "

Cikin minti arba'in da biyar yagama bincike akansu, duk suna zaune, tahir yadawo yace" gaye kayi hakuri fa", ahmad yace " karka damu dahiru," 🤣

tahir yace " laila kiyiwa angonki magana yadena fadamin wannan sunan," laila tace "kaga tahir kafada mana abinda yakawo mu, ba wannan maganar dakake ta sunace takawo muba,"

Jikin tahir yayi sanyi dajin furucin ta
Ahmad yace "tahir ya ake ciki?"

Tahir yace "kuyi hakuri, musanman ke laila mijin ki bazai iya haihuwa ba, qwayoyin halittarsa basuda qarfin dazasu samarda wata halittar, kuma hakan yafaru ne a dalilin wata qwaya dayasha kwanaki

Mrs Usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

48

Hannu yamiqa masa yace "Nagode sosai yallabai,"
principal ya dubeshi dakyau yace "haba ahmad ai Babu komai, daka aikoma za'a yi Mata komai basai kazo da kanka ba,"
ahmad yace "a a Babu komai, yanzu yaushe kake ganin Zata fara Zuwa school din?"

Yace " aiko gobe ma Zata iya Zuwa, Babu abinda zakuyi mata, duk abinda ake buqata makaranta Zata yi Mata," ahmad yace "ok ngd sosai," principal

yace "ya sunanki?"

Tace "izdihar ahmad muhd"
Ahmad ya kalleta da mamaki ashe bata manta abinda daddy yafada mataba, principal yace "good grl," yamaida kallansa ga ahmad yace
" insha Allah zamu bata kulawar data dace"
Hannu ahmad yaqara bashi sannan suka futo
Baby tace "uncle nan school din aka dawo Dani?"
Ahmad yace "eh gobe zaki fara Zuwa," tace "to kaine zakai dinga kawo ni?"
Ahmad yace "a a baby akwai driver zai dinga kawoki, kinga nima akwai office"
Turo Dan qaramin bakinta tayi gaba, tayi shiru
ya kalleta yace " to menene kuma?" Tsugunna wa yayi, yace
" toyi murmushi mana, zan dinga kawoki shikkenan?
Amma baby banasan rigima ba kullum zan dinga kawoki ba, kinga ne?"
dahaka har suka koma gida

** *** **

"Dad aure nakeso, kuma cikin sauri nake buqata kuyimin,"
alhaji yasaki murmushi dansa dayake ji dashi ne Yau shine dakansa yace yana son aure, lalle kuwa za'a yi bikin da ba'a tabayiba

Yace "A'ina take? Wacce mai sa'ar ce wannan?" Kabeer yace "dad a zaria take, inaso Asa mana rana nida ita da wuri, nafisan namata surprise, kawai saide taji bikinmu" 🤣

Alhaji yasake sakin murmushi, yace

" kungama daidai tawa da ita yarinyar ne?"
Kb yace "sosai ma dad, kawai kayi komai yanda ya dace" ,
Dad yace "karka damu dana, inde kudi na aiki, mulki na aiki kasamu yarinyar kagama"
da murna Kb yatashi yayi dakinsa yana ayyana irin rayuwar dazasuyi da feenah

** ** **

Akwance yake dagashi sai kayan baccinsa, yana sakin murmushi shi kadai, my feenah, ina kika shiga ne inata nemanki? Kinsan yanda hakan yake azabtar da zuciya ta kuwa? Murmushi yasake saki tareda janyo fillo ya rungume shi sosai akirjinsa, yanajin kamar itace atare dashi
Lumshe ido yayi, yaci gaba da tunanin ta, bai tsammani ba yaji anfado kansa da karfi tace
" uncle!!" 🤣

Ahmad yace "baby bakyajin magana ko, nahanaki shigowa ba tare da kinyi sallama ba" 🙊
Tace "sorry uncle"
Yace "naji, banasan uncle din nan, sauya wani sunan," tace "Tome zance uncle" yace "abbey"
Daria tasaki tace "to zanfada"
Tace "Un.... Au namanta tasa hannu abakinta da sauri, abbeey yimin tatsuniya"
Cikin mamaki yace "baby me kika ce?" 🤔
Tace "tatsuniya"
Murmushin dabai shiryaba yasaki, yace "niban tabayiba," 🤣

tace "nima sabuwar anty tataba min"
Yace" toki yimin naji koda dadi "
Tana farawa, auta tashigo Dakin itama tariketa tana cewa" Wana kama? "
Ahmad yace" maryam lafiya?"

Auta tace" yaya kagafa tsokanata tayi tagudo wajanka"🤣

Ahmad yace "toyi hakuri aikinga kece babba," baby tayi kalar tausayi tace "bazan sakeba"
Ahmad yace "kinji ba? Itama tace bazata sakeba, shikkenan zance ya wuce ku tashi ku tafi kuje ku kwanta"
Baby tace "a a uncle nide anan zan kwana," ahmad yace "no ga maryam nan tashi kuje, banaso naji kinsake min magana"

Hakan kuwa akayi, batace komai ba suka fita

** *** **

"Baby na rokeki kibar wannan 'yar babyn agida, inba haka ba kuwa Babu inda zaki bini," 🤣

babyn ta kalla tace "to ai uncle idan nabarta kuka zatayi," 🤣
ahmad yace "a a ga momy nan, Zata rarrashe ta,"

izdihar tace "to momy ga yata nan," 🤣

suka kama hanyar fita, harsun fara tafiya tadawo tayiwa babyn kiss sannan suka tafi
Momy tana zaune kamar gunki tana ganin wannan salo 🤔
, yana fita yakira saudat awaya yace "yaushe zaku shigo ne?"
Tace " yaya meyafaru?" Yace "kizo kiga yata, nayi yarinya"
Saudat tace "yaya kamarya?"
Girgiza kai yayi, kawai ya kashe wayarsa
Wayar ta kallah tana
" hello hello" taji shiru 🤔

Momy takira danta samu qarin bayani, cikin mamaki momy tace "au ashe kema anfada miki, tana nan wata yarinya yaje aka bashi, tana nan kamar yar buzuwa🤣
Tunda aka bashi ita yakasa zaune, yakasa tsaye

Saudat tasaki daria tace" lalle yaya, nima fa yanzu kirana yayi wai inzo naganta", momy tace " aikuwa kizo inba so kike yayi fishi ba"

** *** **

Tariqe hannun sa nadama, haka suka qarasa company, yayi abinda zaiyi, suna zaune a office baby tataba wannan, yayi magana ta janyo wannan yahanata, cikin ransa yace bari de mu tafi, tun kafin narasa wata takardar🤣
Ammu yakira, yashigo office din, baby na ganinsa taje ta rungume shi, Ammu yace "a a izdihar, manyan kasa, yagida?" Tace " lafiya, Ammu ina Abba?"
Ammu yace" Abba yana gida izdihar, ya school kina Zuwa ko?" Tace" eh"
Ahmad yace "Ammu wallahi tafiya takama mu nida baby, zandan kwana biyu ban shigo ba, please inaso ka kula da komai," Ammu yayi murmushi Jin sunan da ahmad yakirashi
Yace "to yallabai babu damuwa Allah ya tsare"

Tare suka futo, kowa sai kallan izdihar yake, wasu kuwa har wajansu suke Zuwa, daga nan wajan passport ya wuce akayi Mata, suka wuce wajan visa suka bada passport din

Daganan sukayi wajan yawo, ya kaita nan ya kaita nan, da sukaje Park ne yaga hankalin ta ya karkata waje daya, yajuyo ya kalleta yace
" baby me kike gani ne?" Tace "nan mukazo da sabuwar anty rannan," murmushi yayi yace

"kede baby bakida dama, abinda akai jiyama saikice rannan"
Kinga taho mu tafi

Tayi wasa sosai sannan suka kama hanyar gida

** *** **

"Wato alhaji abinda yake faruwa, shine, ita wannan yarinyar dakukazo magana Akan ta, ni kwata kwata ma, bata min maganar wannan yaron ba, sannan Bama wannan ba, ai anriga ansa Mata rana itada wani yaro,"
daddy cikin rashin walwala yace" to Mungo de, mun gode sosai," Abba yace" babu damuwa", suka sake musabaha suka tafi

Yana Zuwa gida mahaifinsa yafada masa wannan maganar atake ya haukace musu, shi wallahi yana Santa kuma bazai iya hakura da itaba, dad yace "Kabeer kabi komai asannu mana,"

Kb yace " daddy wallahi idan yarinyar nan bata aure niba sai tayi DANA SANI"

** *** **

Cikin sati biyu aka Gama musu komai, dukansu suna falo anata fira kasancewar saudat tazo ganin baby, tana ganin yarinyar taji tashiga ranta, duk motsin da baby zatayi, idan saudat na kanta, har ahmad yafahinci halin datake ciki
Saida yatafi daki, yana shirya kaya ajaka, saudat tashigo tace" yaya, yanaga kana hada kaya"

, yace "sauda jibi zamu wuce misra ne, zan kai baby wajan tsohon can taganshi yaganta,"
😳saudat tace" yaya wallahi wannan yarinyar kama suke da feenah sosai "
Ahmad ya kalleta da mamaki, yace cikin ransa ashe bashi kadai ne yake wannan tunanin ba, Yace" kama ce kawai saudat "

Dahaka tayi shiru dataga kamar bayasan maganar, tajuya ta fita, yana ganin fitar ta, yagoge qwallar idonsa

Bayan kwana daya sukai
 sallama dakowa, inda suka Lula Egypt shida baby

Kakanninsa sunyi murna sosai da ganin baby, inda marzuk yasake masa fada Akan Dan Allah koda yayi aure yadaure ya riqe matar dakyau kada yasake tunanin rabuwa da mace, koma menene hakuri akeyi da Juna
Ahmad yaji shawarar kakan nasa Sosai, kuma yayi alkawari zai kiyaye Gaba

Tunda sukaje yake kaita wajan yawo kala kala, pictures kuwa harda na banza, duk inda sukaje sai yayi musu pictures, ahaka suka dauki Tsawon sati biyu, har yana shirin dawowarsu Nigeria

Bai cika dora pictures dinsa a Facebook ba, Amma Yau saboda baby yahau danya do rasu, abinda yagani ne yabashi mamaki, pictures din bikinsa shida laila

Babu wanda yafado masa arai sai tahir, yasan shine zai aikata
"zamu hadu ne "
Yafadi haka afili, pictures dinsa yasa shida baby yasauka, duk tarin massages din da aka turo babu wanda ya bude

** *** **

After 4 months
Feenah sun kammala 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

48
Hannu yamiqa masa yace Nagode sosai yallabai, principal ya dubeshi dakyau yace haba ahmad ai Babu komai, daka aikoma za'a yi Mata komai basai kazo da kanka ba, ahmad yace a a Babu komai, yanzu yaushe kake ganin Zata fara Zuwa school din?

Yace aiko gobe ma Zata iya Zuwa, Babu abinda zakuyi mata, duk abinda ake buqata makaranta Zata yi Mata, ahmad yace ok ngd sosai, principal yace ya sunanki?
Tace izdihar ahmad muhd
Ahmad ya kalleta da mamaki ashe bata manta abinda daddy yafada mataba, principal yace good grl, yamaida kallansa ga ahmad yace insha Allah zamu bata kulawar data dace
Hannu ahmad yaqara bashi sannan suka futo
Baby tace uncle nan school din aka dawo Dani? Ahmad yace eh gobe zaki fara Zuwa, tace to kaine zakai dinga kawo ni?
Ahmad yace a a baby akwai driver zai dinga kawoki, kinga nima akwai office
Turo Dan qaramin bakinta tayi gaba, tayi shiru
ya kalleta yace to menene kuma? Tsugunna wa yayi, yace toyi murmushi mana, zan dinga kawoki shikkenan?
Amma baby banasan rigima ba kullum zan dinga kawoki ba, kinga ne?
dahaka har suka koma gida

** *** **

Dad aure nakeso, kuma cikin sauri nake buqata kuyimin, alhaji yasaki murmushi dansa dayake ji dashi ne Yau shine dakansa yace yana son aure, lalle kuwa za'a yi bikin da ba'a tabayiba

Yace A'ina take? Wacce mai sa'ar ce wannan? Kabeer yace dad a zaria take, inaso Asa mana rana nida ita da wuri, nafisan namata surprise, kawai saide taji bikinmu

Alhaji yasake sakin murmushi, yace kungama daidai tawa da ita yarinyar ne? Kb yace sosai ma dad, kawai kayi komai yanda ya dace,
Dad yace karka damu dana, inde kudi na aiki, mulki na aiki kasamu yarinyar kagama
da murna Kb yatashi yayi dakinsa yana ayyana irin rayuwar dazasuyi da feenah

** ** **

Akwance yake dagashi sai kayan baccinsa, yana sakin murmushi shi kadai, my feenah, ina kika shiga ne inata nemanki? Kinsan yanda hakan yake azabtar da zuciya ta kuwa? Murmushi yasake saki tareda janyo fillo ya rungume shi sosai akirjinsa, yanajin kamar itace atare dashi
Lumshe ido yayi, yaci gaba da tunanin ta, bai tsammani ba yaji anfado kansa da karfi tace uncle!!
Ahmad yace baby bakyajin magana ko, nahanaki shigowa ba tare da kinyi sallama ba
Tace sorry uncle
Yace naji, banasan uncle din nan, sauya wani sunan, tace Tome zance uncle yace abbey
Daria tasaki tace to zanfada
Tace Un.... Au namanta tasa hannu abakinta da sauri, abbeey yimin tatsuniya
Cikin mamaki yace baby me kika ce?
Tace tatsuniya
Murmushin dabai shiryaba yasaki, yace niban tabayiba, tace nima sabuwar anty tataba min
Yace toki yimin naji koda dadi
Tana farawa, auta tashigo Dakin itama tariketa tana cewa Wana kama?
Ahmad yace maryam lafiya? Auta tace yaya kagafa tsokanata tayi tagudo wajanka

Ahmad yace toyi hakuri aikinga kece babba, baby tayi kalar tausayi tace bazan sakeba
Ahmad yace kinji ba? Itama tace bazata sakeba, shikkenan zance ya wuce ku tashi ku tafi kuje ku kwanta
Baby tace a a uncle nide anan zan kwana, ahmad yace no ga maryam nan tashi kuje, banaso naji kinsake min magana

Hakan kuwa akayi, batace komai ba suka fita

** *** **

Baby na rokeki kibar wannan babyn agida, inba haka ba kuwa Babu inda zaki bini, babyn ta

kalla tace to ai uncle idan nabarta kuka zatayi, ahmad yace a a ga momy nan, Zata rarrashe ta, izdihar tace to momy ga yata nan, suka kama hanyar fita, harsun fara tafiya tadawo tayiwa babyn kiss sannan suka tafi
Momy tana zaune kamar gunki tana ganin wannan salo
, yana fita yakira saudat awaya yace yaushe zaku shigo ne? Tace yaya meyafaru? Yace kizo kiga yata, nayi yarinya
Saudat tace yaya kamarya?
Girgiza kai yayi, kawai ya kashe wayarsa
Wayar ta kallah tana hello hello taji shiru

Momy takira danta samu qarin bayani, cikin mamaki momy tace au ashe kema anfada miki, tana nan wata yarinya yaje aka bashi, tana nan kamar yar buzuwa
Tunda aka bashi ita yakasa zaune, yakasa tsaye

Saudat tasaki daria tace lalle yaya, nima fa yanzu kirana yayi wai inzo naganta, momy tace aikuwa kizo inba so kike yayi fishi ba

** *** **

Tariqe hannun sa nadama, haka suka qarasa company, yayi abinda zaiyi, suna zaune a office baby tataba wannan, yayi magana ta janyo wannan yahanata, cikin ransa yace bari de mu tafi, tun kafin narasa wata takardar
Ammu yakira, yashigo office din, baby na ganinsa taje ta rungume shi, Ammu yace a a izdihar, manyan kasa, yagida? Tace lafiya, Ammu ina Abba?
Ammu yace Abba yana gida izdihar, ya school kina Zuwa ko? Tace eh
Ahmad yace Ammu wallahi tafiya takama mu nida baby, zandan kwana biyu ban shigo ba, please inaso ka kula da komai, Ammu yayi murmushi Jin sunan da ahmad yakirashi
Yace to yallabai babu damuwa Allah ya tsare

Tare suka futo, kowa sai kallan izdihar yake, wasu kuwa har wajansu suke Zuwa, daga nan wajan passport ya wuce akayi Mata, suka wuce wajan visa suka bada passport din

Daganan sukayi wajan yawo, ya kaita nan ya kaita nan, da sukaje Park ne yaga hankalin ta ya karkata waje daya, yajuyo ya kalleta yace baby me kike gani ne? Tace nan mukazo da sabuwar anty rannan, murmushi yayi yace kede baby bakida dama, abinda akai jiyama saikice rannan Kinga taho mu tafi

Tayi wasa sosai sannan suka kama hanyar gida

** *** **

Wato alhaji abinda yake faruwa, shine, ita wannan yarinyar dakukazo magana Akan ta, ni kwata kwata ma, bata min maganar wannan yaron ba, sannan Bama wannan ba, ai anriga ansa Mata rana itada wani yaro, daddy cikin rashin walwala yace to Mungo de, mun gode sosai, Abba yace

babu damuwa, suka sake musabaha suka tafi

Yana Zuwa gida mahaifinsa yafada masa wannan maganar atake ya haukace musu, shi wallahi yana Santa kuma bazai iya hakura da itaba, dad yace Kabeer kabi komai asannu mana, Kb yace daddy wallahi idan yarinyar nan bata aure niba sai tayi DANA SANI

** *** **

Cikin sati biyu aka Gama musu komai, dukansu suna falo anata fira kasancewar saudat tazo ganin baby, tana ganin yarinyar taji tashiga ranta, duk motsin da baby zatayi, idan saudat na kanta, har ahmad yafahinci halin datake ciki
Saida yatafi daki, yana shirya kaya ajaka, saudat tashigo tace yaya, yanaga kana hada kaya, yace sauda jibi zamu wuce misra ne, zan kai baby wajan tsohon can taganshi yaganta, saudat tace yaya wallahi wannan yarinyar kama suke da feenah sosai
Ahmad ya kalleta da mamaki, yace cikin ransa ashe bashi kadai ne yake wannan tunanin ba, Yace kama ce kawai saudat

Dahaka tayi shiru dataga kamar bayasan maganar, tajuya ta fita, yana ganin fitar ta, yagoge qwallar idonsa

Bayan kwana daya sukai
 sallama dakowa, inda suka Lula Egypt shida baby

Kakanninsa sunyi murna sosai da ganin baby, inda marzuk yasake masa fada Akan Dan Allah koda yayi aure yadaure ya riqe matar dakyau kada yasake tunanin rabuwa da mace, koma menene hakuri akeyi da Juna
Ahmad yaji shawarar kakan nasa Sosai, kuma yayi alkawari zai kiyaye Gaba

Tunda sukaje yake kaita wajan yawo kala kala, pictures kuwa harda na banza, duk inda sukaje sai yayi musu pictures, ahaka suka dauki Tsawon sati biyu, har yana shirin dawowarsu Nigeria

Bai cika dora pictures dinsa a Facebook ba, Amma Yau saboda baby yahau danya do rasu, abinda yagani ne yabashi mamaki, pictures din bikinsa shida laila

Babu wanda yafado masa arai sai tahir, yasan shine zai aikata
"zamu hadu ne "
Yafadi haka afili, pictures dinsa yasa shida baby yasauka, duk tarin massages din da aka turo babu wanda ya bude

** *** **

After 4 months
Feenah sun kammala karatun su itada mukhtar, soyaiyar su kuwa sai qara gaba take yi, sunaji

da junan su sosai, saura wata uku su dawo gida, abinda ya rage Mata yanzu project ne kawai, data gama sai gida, shiyasa tabaro madani, tadawo Khartoum kusa da Zahra, tunda rubutu ne kawai

Itama tagama karatun ta kawai jiran result dinta take, sosai nake rubutu na, danna matsu na dawo gida, baby tana raina, kullum nakira waya nace abata akwai abinda ake fadamin, nasan akwai abinda yake faruwa, Dan haka koda yaushe nake Allah Allah nazo naga halin da yata take ciki,

Muna falo nida Zahra, munacin abinci, su salma suka shigo nan suma suka zauna mukaci Gaba daya,
Muna gamawa aka fara firar duniya, salma ce tahau chting tafara daria ita kadai
Alamar a chting dinne ake bata daria

Tashi nayi nashiga daki danna kwanta in huta, Zahra ma tabiyoni, salma tace "laaa! Ku tsaya kuga pictures din ahmad Dan gidan deputy governor , shida wata yarinya wai yarsa" 🤣

Nide nace "a a kede kigani," 🤣

nayi daki, Zahra ma tace
" salma kyaban labari daga baya," itama tashigo Dakin

Ina shiga na tsaya ni kadai adakin ina tunani, kenan ma har ya haihu, mayaudari kawai

A a feenah, kimanta dashi kawai, kidena zancan yaudara ki barshi da halinsa, juyawa nayi na kalleta sai a sannan nasan maganar danayi ashe afili nayi

Zahra tace " kiyi hakuri, ki rungumi mukhtar dinki, tunda kinga har salma nacewa wai ya haihu,"
Nace "insha Allah zanyi yanda kika ce"

Zahra tace "yauwa kokefa, ni wallahi salma ma tabani haushi, shiyasa nace latter tabani labari" 🤣

Nace "aike kin kulatama ni bazan iya controlling kaina ba, gara nabar wajan,ni yar iska ce zan tsaya kallan pic din wata yarsa ina ruwana da ita" 🙆🏻

Zahra tace "wallahi kuwa" 🤣

Mrs Usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

47

Mama Jin wannan tambayar yasa jikinta yayi sanyi, tace "auta baby tana kano,"

feenah bata kawo komai aranta ba, tunda tasan de baby bazata wuce gidan kaka ko kalatinsu, ko gidan husna ko Ammu ba, Dan haka tace
" Toshiknn, mama wannan satin iyayen mukhtar zasuzo,"

mama cikin farin ciki tace " to alhmdlh, Allah yakawo su lafiya auta, Allah ya nunamin bikin ki,"
feenah cikin murmushi tace "amin mama,"

nan sukai sallama,
Mama falo ta futo taga Abba a zaune tace "Abban husna yanaga Kanata farinciki haka,"

anan ya nuna Mata text din da nafeesa taturo masa, mama tace
" yanzun nan nima take fadamin awaya," Abba yace "to Allah yakawo su lafiya,wannan karon insha Allah bazamuyi DANA SANI ba"

** *** **

momy tazauna jiki asanyaye, mamy hakima itama tazauna tace "hajia me yake faruwa ne naga jikinki yayi sanyi?" Momy tace "hajia yaron nan yasaki yarinyar nan," mamy hakima ta rafka salati, tace "saki hajiya?" momy tace "saki har uku,ahmad bashida hankali," mamy tace "a a hajiya kina ganifa ita dakanta tace bazata iya zama dashi ba," momy tace "Amma kuma sai yayi Mata saki har uku?"
Mamy tace " gaskiya de ahmad bai kyauta ba, kuma ni narasa me yake damunta? Kidubafa kiga abinda take," momy tace
" akwai abinda yake faruwa hajiya, dole akwai abinda yamata, zaizo yasameni," waya ta dauka ta kira ahmad Amma wayar akashe, tajuyo ta cewa mamy "wayar tasa akashe"

mamy tace "bari inkira alhaji hajia, yasan abinda yake faruwa yakira mahaifin yarinyar nan," momy tace "kirashi to," idonta yakada yayi Ja, mamy tace " haba hajia kiyi hakuri mana," momy tace "yanzu ace hajia duk wata matsala datake bullowa agidan nan, shine yake haddasa ta, haba hajia dole nashiga damuwa," mamy tace "kiyi hakuri mana hajiya" tafadi haka muryarta na rawa itama

Mamy takira alhaji tayi masa bayanin komai, yace "gashinan Zuwa gidan"

** *** **

Hajia salaha tana ta zirga zirga agaban office din doctor, wata nurse ce tazo tace doctor yace Zata iya shiga taga yarta, idan ta futo taje ta sameshi a office

Dakin tashiga, laila tana kwance tana bacci, hajia salaha tace cikin ranta duk abinda yasamu yarta, wallahi bashi suka dauka, Dan saita qwatowa yarta yanci, duk ahalin marzuk sai sunyi DANA SANI Akan taba yarta, office din doctor ta nufa

Kujera taja tazauna tana fuskantar shi, doctor yace " wato hajia gaskya sai kinyi hakuri, yarki tasha qwaya, har tayi Mata shan hauka, wannan dalilin ne yasa Tafita ahayyacinta,"
Hajia salaha tace " to yanzu me ake ciki doctor?"

Yadubeta da kyau yace "maganar gaskya yarki bazata iya haihuwa ba, tasamu matsala a mahaifarta dalilin wannan qwayar,
Kuma barin mahaifar haka zaisa ta dinga kumbura
Saide ayi dayan biyu ko adaure mahaifar kokuma acireta" 🙆🏻

Hajia salaha cikin kuka tace "nashiga uku, laila ta kalau take likita, karya kake,"
doctor ya dubeta yace "kinga hajia banasan hayaniya, idan bazaki nutsu kiyimin bayanin abinda za'a Mata ba, to kofa abude take"
File yabude yafara rubuce rubucensa

Hajia salaha kamar mahaukaciya tace
" wallahi bazai iyu ba, bazai iyuba,"
Tafita daga office din tana" bazai iyuba!! "
Bata wuce ko ina ba sai gidansu ahmad
Su momy suna nan, inda suke da, ko sallama hajia salaha batayiba, tafado falon tafara nunasu da hannu," wallahi daya bayan dayanku sai kunyi DANA SANI "

Daddy da shigowarsa kenan yace" hajia me yake faruwa ne? "
Su momy sukai shiru,
Hajia salaha tace" Danku yasaki yata saki uku, sannan ya dirka Mata magani tasha har hakan

yasan mahaifar ta ta lalace, "
salati su momy suka sa, daddy kuwa waje yanema ya zauna yace
" hajia kiyi hakuri zanyi magana da alhajin "
Hajia salaha ba tare datace komai ba tajuya ta fice

Daddy yajuya ya kalli momy tada fara kuka, al'amarin ahmad ma kadai ta isheta, kosu Muslim baza suyi abinda yake ba
Mamy ce tayi karfin halin yimasa bayani, daddy yace" to Allah yarufa asiri, idan yadawo nazauna muyi magana dashi," yatashi yayi sama, mamy ta juya taci Gaba dabawa momy hakuri

Hajia salaha na fita, asbiti Takoma, alokacin laila tafarka, nan tafada Mata abinda likita yace, laila tace" wallahi ahmad ne yabani lemo nasha, tabbas shine yasamin magani aciki "

Hajia salaha tace
" kwantar da hankalin ki, dole alhaji yadau mataki Akan haka, tunda dama can shine ya qulla "

Waya tadauka takira alhaji bukhar, tafada masa abinda yake faruwa, alhaji yace" to Allah yakiyaye hanya "🤣

Hajia tace" kamarya Allah yakiyaye hanya,? Bangane ba "

Yace" kidauketa kiwuce gidanku, karki dawomin gida, tunda kin kashe Mata auren ai shikkenan Amma idan kika kuskura kika dawomin gida abakin auren ki, "

yana Gama fada Mata ya kashe wayarsa
Hajia salaha ta rafka uban tagumi

** *** **

Juyi tayi tabu de idonta, cikin muryar bacci tace
" uncle munzo ko?"

Yace" baby munzo ga gidan can "
Tashi tayi dakyau tafara kalle kalle, har sukazo gidan tace " uncle,"
yace" na'am baby"

Tace "gidanku yanada kyau, yafi namu kyau,"

ahmad yayi murmushi yace "ai yanzu kema kin dawo nan, nan shine gidanku, kowa ya tambayeki inane gidan Abban ki kice masa nan"

, cikin murmushi tace " to uncle"

Parking yagyara, yazo yabudewa baby kofa tafuto, yace " kinga wancan hanyar?"
Ya nuna Mata wani kofa, tace "eh,"
yace "to kije kishiga tanan, gani nan Zuwa, zan dauko kayanki,"

tace "to uncle"
da babyn ta a hannunta tabi hanyar, a hankali taturo tashiga falon, Gaba dayansu suna zaune Ana jiran Ahmad 🤣banda daddy dayake dakinsa

Tana shiga falon taja ta tsaya abakin kofar, su momy suka zuba Mata ido, mamy hakima tace " to ina muka samu baqi kuma? 🤣
Yarinya shigo"

Ahankli baby tashigo, mamy hakima tace
" wakike nema?"
Baby tace "Uncle"
Mamy tace " uncle kuma?" Cike da mamaki

Baby ta daga kai, alamun eh
momy cikin ranta tace
" masha Allah wannan yarinya kamar ba bahaushiya ba,"

Momy tace "zonan, menene sunanki?"

Izdihar tace sunana "baby"

Momy ta juya ta cewa mamy nifa da farko jinake batajin hausa" 🤣

Mamy tayi daria tace
" hajia ai shiyasa nace ina muka samu baqi"

Ahmad suka gani yashigo da jaka ahannun sa, baby tatafi da gudu wajansa
Su mamy da sauran yara suka zama yan kallo

Mamy tace "ahmad baqi mukayi ne?"

Ahmad yana murmushi yace  " mamy yarinya aka bani, kyauta" 🤣

Kallansa suke da mamaki
Yace " mamy serious, bani ita akai, nima nayi 'ya yanzu"

Momy ce tace "kai yimana bayani yanda zamu gane" 🤣

Anan ahmad yafada musu komai
Momy nan da nan taji tana kaunar yarinyar, ta janyo ta tace "zonan baby sannu kinji"
Izdihar tace "yauwa," ta kalli ahmad tace "uncle ina maryam din dazamuna wasa?"

Ahmad yace "baby bakya mantuwa ko?"

Mabaruka tashi kije kibata abinci, kiyi Mata wanka ki kaita Dakin auta, mabaruka cikin murna tace "to zomuje," takama hannun ta suka tafi

Shiru sukai dukansu, sannan daga baya momy tace "ahmad me yake faruwa, tsakanin ka da laila?"
Shi sai sannan ma yatuna da ita, shaf ya manta ta wallahi
Ahmad yace "babu komai momy"
Momy tace "hajia kinji ba, kinji abinda nake fada miki ko? Zurfin cikin tsiya

Bari nakira mahaifin ka, may be shi zaka iya fada masa gaskya,"
bata Dade da hawa saman ba suka sauko tare da daddy

Daddy yace "ahmad me yake faruwa tsakanin da iyalinka"
Ahmad yace "daddy itace tace nasake ta, kuma namata abinda ta nema,"

daddy yace "kuma shine kasaketa har saki uku, haba ahmad kamar qaramin yaro? Ina ka taba gani kai tsaye anyi haka?"
Ahmad yace "daddy kayi hakuri,"
daddy yace "sai maganar magani

Metayima da har zaka dauki mummunan mataki irin haka? Kokuma kai Dan ance bazaka haihu ba, shine itama kace bari ka maida ta haka ku zama daya?"

Maganar ta masa ciwo nan da nan yafara hawaye yace "daddy kayi hakuri"

Daddy yace "a a ni ahmad kafi karfina, tunda nayima aure ka nuna min ban isa dakai ba, shikkenan kaje duniya ce" 🙆🏻

Mamy hakima tace
" haba alhaji, ai ka tsaya kaji abinda yaron nan zai fada ko?
My son yimana bayani me yake faruwa?"
Ahmad yana hawaye yace " daddy Dan Allah kayi hakuri kayafemin, banyi haka Dan inci mutuncinka ba, kayafemin daddy, insha Allah haka bazata sake faruwa ba

Daddy laila itace tasa min magani cikin drinks din dakina Gaba daya, nasha.. Har hakan yasa nayiwa... Kuka yasa yakasa qarasa maganar, yace daddy laila nita zalunta, kawai nima ramawa

nayi, tabawa walaya magani tasamin nasha, tahir shine ya dubani a dalilin maganin ne yasa nima bazan iya haihuwa ba, har sai andorani Akan magani

Idan dukanta nace zanyi bazan huce ba, shiyasa nabi shawarar zuciyata nima nayi Mata abinda tayimin

Wannan dalilin ne yasa nakori walaya daga gidan nan, Amma kayi hakuri daddy, kabawa mahaifin ta hakuri, yayafemin,"

Daddy yasauke numfashi yace" tokai waye yafadama duk wannan abubuwan? "
Ahmad yace" wallahi daddy da kunne na naji tana fadawa qawarta awaya," daddy yace

" shikkenan tashi kaje"
Ahmad kan kujera yakoma ya zauna shima yayi shiru

Daddy yadau waya yakira alhaji bukhar yayi masa bayanin komai, tare da neman yafiyarsa, alhaji bukhar yace "wallahi karka damu, duk mahaifiyar tace take dorata Akan turbar banza, nima nace karsu kuskura suzomin gida, nagaji da halaiyarsu alhaji,"

Daddy yace "a a alhaji ba za'a yi haka ba," nande daddy yayi ta tausarsa sannan sukai sallama

Daddy yafadawa su momy yanda sukai da mahaifin laila, nan momy tace " to alhmdlh tunda an samu an fahinci Juna, kai kuma karka sake irin wannan

Dan anyi ma Abu kace kaima saika Rama, daka barta da halin ta ma, dakanta zatayi DANA SANI
Kaga yanzu ba musan abinda mahaifiyarta zatayi ba, dakayi mana bayani tun farko da tuni an warware matsalar cikin kwanciyar hankali"

Ahmad aransa yace ainagama warware matsala 😂

Cikin sanyin murya yace
" kuyi hakuri,"

wayarsa ya janyo yakira Abba yafada masa sun sauka lafiya, Abba yace a gaida baby

Momy ce tace" alhaji namanta ban fada makaba, munyi jika fa," alhaji yace" ko sauda ce tasamu ciki? "
Momy tace " a a ahmad ne de yayi 'ya, "

Nan suka bashi labarin komai, daddy yace

" a a to akirata mana naganta," ahmad yana murmushin Jin dadi yanda iyayansa suka karbi baby hannu bibiyu, yatashi da kansa yaje Dakin, lokacin har ansa Mata kayan shan iska ya dauko ta akafadarsa kamar wata jaririya, mamy cikin kasa kasa da murya tace "hajia aikuma munga ta kanmu Akan wannan yarinya," 🤣

momy tace "um zamusha kallo kam, kamar akansa aka fara," 🤣

daddy yana jinsu baice musu komai ba, kawai de yayi murmushi

Ahmad har gaban daddy yaje, ya dora masa baby Akan cinyarsa, yace
" daddy ga jikar taka, ina Santa daddy, wallahi ko iyayen ta banajin sunkaini Santa "😳🙆🏻

Gaba daya iyayen nasa suka hada ido cikin mamaki
Momy tace "aikam gashinan nagani, nina rasama ya akai suka baka yarinya, kamar wanda ka musu asiri" 🤣

Ahmad cikin shagwaba yace "kai momy"

Mamy hakima tace "to yanzu my son Naka shagwabar zamuji kona yar taka?" 🤣
Sunkuyar da kansa yayi yana Sosa qeya

Daddy yace" ya sunan jikar tawa,"

baby tace" sunana baby"
Daddy yace "baby sunanki me dadi, Amma fadamin daya sunan, ai baby ba suna bane,"

tace "Izdihar"
Yace "to Allah yamiki albarka kinji,"

tace "to kaima haka" 🤣

Gaba dayansu sukasa daria

Daddy yace "kina Zuwa school ko?" Tace " ina Zuwa a nursery 5 nake,"

Abba yace "a a masha Allah, da wanne suna ake kiranki a school dinku?"

Tace " Izdihar mu'az"

Daddy yace "gaskya ne, Amma daga yau kin koma Izdihar Ahmad muhd marzuk"

Ahmad dayake kallansu dadi yakeji kamar me

** *** **

"Nafeesa tun dazu nake kiranki Amma kinqi daga wayata, meyasa?"

"K'B atunani na, mun riga da mun Gama magana dakai,"
Kb yace " hakane, dama zan tafi Nigeria ne shine nace yakamata inji muryarki kuma inyi miki sallama,"

feenah tace "ah "mabrouk" (congrats )
Allah yakiyaye hanya ya tsare "
Kb yace" nafeesa kinqi ni de, "
Feenah tace" Kb nafadama dalili aiko,"

yace" hakane, saboda ina Dan gidan Dan siyasa bakya sona," feenah tace
" haka yake, kuma Dan Allah kadena kirana, nariga da na zabi mijin da zan aura
Ahalin yanzu ma, cikin satin nan, ake tunanin saka mana rana, "

Kb yace" mukhtar ko? "
Feenah tace" ya akai ka sani? "

Kb yayi murmushi yace
" tayaya kike tunanin bazan San komai nakiba bayan ina kaunar ki "
Feenah tace" ok ngd bye," takashe wayar bata jira amsarsa ba

Kb yace feenah kenan, kina tunanin zan barki ne cikin sauqi haka? Bazai iyu ba!

** *** **

Ranar talata, iyayen mukhtar sukaje gidansu feenah, ba laifi anyi musu karba ta mutunci, inda suka tsaida ranar bikin su bayan sun Gama karatu da wata biyu

Al'amarin ya yiwa wasu dadi, wasu kuma sabanin haka, tahir yaso ace yahadata da abokinsa ahmad, husna ma hakan take

Yayin da kaka tace ita wannan al'amari baiyi Mata ba, saboda akwai tsohon saurayin nafi, wanda ya kwanta Mata arai, shi taso nafi ta aura 😂

Saide bangaren ita feenah, abin yayi Mata dadi, tana ganin hakanne zaisa ta dena tunanin mutumin dayaci amanarta

Amma a bangaren iyayen ta, sunfi kowa murna, suna Allah Allah ranar tazo suyi Mata auren, saboda kada su sake maimaita DANA SANI irin wand sukai abaya

Mrs Usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

46

Salati yaci gaba da maimaita wa cikin ransa Zuwa wani lokaci
Kamar wanda aka tsikara yatashi cikin sauri yashiga mota Yabar gidan
Tashin motar da laila taji ne yasa cikin sauri ta Bude window ta leqa, tace "au shine ina jiran sa zai shanyani yafita, zaizo yasameni ne,"
falo Takoma ta dora kafa daya kan daya

** *** **

"Hajiya yanzu ya zamuyi da yaran nan?"

Momy tace "hakuri zai bata mana hajiya, su sasanta kansu, shikuma zan sanarwa alhaji matsalar ko wata qasar ne saiya shirya yaje su dora shi Akan magani,"

mamy hakima tace
" hakane, Amma wannan yarinya sai tayi DANA SANI
kizo ki tsaya a kanmu Dan cin mutunci kamar bamu haifeki ba,"
Momy tace" toya zamuyi hajiya alhaji nede duk ya janyo wannan matsalar"

**    ***    **

Yana tuqi ya dauko wayarsa yakira tahir, yace " tahir kazo gidanka kasameni inajiranka yanzu akwai matsala,"

yana fadar haka ya kashe wayar
Tahir yace "to akwai matsala kenan duk yanda akai laila taqi hakura" ,
shima yahada yanasa yanasa  yayi hanyar gida

Yana Zuwa gidan tahir maigadi yabude masa, yayi parking ya zauna acikin motar ko budewa baiyi ba, kansa ya dora Akan sitiyari sai a wannan lokacin wani kuka mai ciwo yazo masa, shi kadai yanata kuka, rayuwa kenan shikuma haka tasa rayuwar take, a duniya bazaiji dadin zama da mace ba, ashe duk wannan bala'in daya shiga sanadin laila ne, tasan itace ta sashi a wannan halin Amma itace take cewa bazata iya zama dashi ba, wai shine Dan shaye shaye, hawaye ya share yace "tabbas laila sai kinyi DANA SANI"

qonqwasa glass din motar yayi, ahmad yabude masa, yashigo, ya kalli ahmad da idonsa yayi jajir, yace "nawan me yake faruwa ne?"

Ahmad yace tahir " laila ce"

Sai hawaye
Tahir yace "bangane ba,? Meka ke nufi?"
Ahmad yace " tahir laila ta cuceni, ta azabtar Dani, kuma wallahi yanda ta illa ta ni, saita fadawa aya zaqin ta"
Ahmad yafadawa tahir komai, yaci gaba da fadin  " ashe itace tasa na dawo maci Amana a idon yar mutane, har Yau nafeesa takasa fahimta ta, tahir laila ce tasa nakasa mallakar abinda nakeso, tasa nayiwa rayuwar feenah illa, nasan cewa duk mijin dazata aura ayanxu, bazai ga darajar taba, dole inci Gaba da neman feenah tahir inroqeta tayafemin in kuma aure ta,"

 tahir yace
"innalillahi wa inna ilaihir raju'un
Abu kamar almara
Lailah!"
Yafadi haka cikin mamaki

Ahmad yace "wallahi tahir kaji abinda yake faruwa, yanzu haka batasan ma nabar gidanba," tahir yace
" yanzu menene abin yi? Ahmad kayi hakuri Dan Allah, haka Allah yaqaddaroma Naka rayuwar, karkaje kadaki yar mutane kayi Mata illah"
Ahmad yace "bazan yi Mata komaiba tahir, Amma tabbas nasan sai tayi DANA SANI Akan abinda tamin"

Tahir ya rungume shi, yana aikin rarrashi
Ahmad yace " wallahi ni tsoro ma take bani,🤣🤣 Mata kaidin su yafi karfin tunanin mutum,"

tahir yace "a a to yanzu buya zakayi kenan?"

Ahmad baisan lokacin daya saki daria ba, yace
" ni inbuyawa mace?" Tahir ma daria yayi yace
" Tome zakayi?" Ahmad yace "kawai idan natuna da abubuwan data haddasa a dalilin wannan shan wannan maganin kawai sai inji Gaba daya tsoron mace ma ya shigeni,"

tahir yace "gaskya ne kayi hakuri ahmad hakika laila ta cutar dakai, Amma inama fatan samun mace ta gari,"

ahmad yace "inaaaa, ainida kula wata mace sai ranar da Allah ya nufa,"

tahir yace "har feenah?"

Ahmad yace "kadena saka feenah alayin sauran mata, saboda ita din ta banbanta dasu, Amma hakika zamana da laila yaqare"

Tahir zaiyi magana ahmad yace "please tahir karka cemin komai please, gobe zan tafi zaria in dauko baby"
Tahir cikin mamaki yace
" Dan Allah?,
Wai kana nufin har an wuce wajan?"
Ahmad yace "sa wasa, kaga fitamin a mota, zan wuce gida," 🤣

tahir yace "to masu mota, Babu inda zanje, kafata kafarka, Dan nasan bazakayi wa laila hukunci mai sauqi ba,"

ahmad yace "ka yarda Dani tahir babu abinda zanyi Mata,"

tahir yace "toshkn Allah yakiyaye"

Yafita yashiga gida, aransa yana tunanin qaidi irin na wasu matan

Ahmad bai wuce gidaba, kai tsaye wani chemist ya wuce, yayi musu bayanin irin maganin dayake so, aka bashi, yashiga mota, bai wuce gidanba kawai yawo ya wuce, sai dare yakoma gida

Yana Zuwa gida yaga laila afalo, wata tsanarta tasake shigar sa, wuceta yayi zai shiga daki, tace

" jimana,"
ya juyo ba tare daya tanka mataba, tace
" kasan me nake jira ai
"bani"

tafadi haka gamida miqa masa hannu, ahmad yadawo ya zauna kusa da ita, yace " laila, banasan rigima, kiyi hakuri mana ko?"
Laila tace " inaaaa bazai iyuba, bazan iya zama da juya ba,"

ahmad yace " toshkn naji zan baki takardar ki, Amma kibari sai gobe, yanzu banda nutsuwar dazan iya rubutu kinga ne?" Yana fadar haka yashiga daki, ya kulle, kan kadonsa yafada, ya riqe kansa dayake sara masa, yace" innalillahi, wannan wacce irin qaddara ce, Allah ya baiyanamin feenah "

Washe gari da safe ya shirya, cikin qananun kaya, milk din Riga daga gefenta wajan hannun anyi sirikin baqi, sai baqin wando jeans, agogo ne ahannunsa gucci, sai qamshin turare yake, yayi masifar kyau, yan futowa falo, dining ya kallah, yanda ya Zata kuwa haka yagani, wayam Laila ta futo cikin shiri itama, tace "dama kai nake jira ahmad,"

Ahmad ya kalleta yace "to zauna ina Zuwa,"

Kitchen yashiga ya dauko flask yadau cup ya tsiyaya ruwan zafin, yahada tea mai kyauri, ya zauna afalo yanasha, ya cewa laila " jeki dauko takarda da biro,"

laila cikin sauri ta tashi, ta dauko daga tsaye ta miqa masa yakarba,
Saida yagama shan tea, sannan yajuyo ya fuskance ta, yace " laila, kinga Allah bayasan saki, ya halatta manashi Amma kuma bayaso, kinga yanzu zaria zanje anbani yarinya saboda haka zan dauko ta inkawo miki ita, saiki riqeta," 🤣

laila tace "ahmad me kace?"
Ahmad yace "shikkenan yi hakuri, ina Zuwa, nasan bakici komai ba, kibari kisha ko ruwa ne zuciyarki tayi sanyi saimu qarasa maganar,"

yatashi yashiga dakinsa ba tare daya jira amsar ta ba

Yana tashi laila tace " tab ni zan yima riqon yarinya, lalle, to ai nakama banajin zan riqesu bare na wani"

Yana shiga dakinsa, maganin daya siyo jiya yadauko, yaciro guda hudu,😳🙆 yadauko coca-cola yazuba acikin glass cup, yasa spoon yajuya, sannan yakawo Mata falo
Yace "gashi"

, Babu kunya laila ta karba takafa kai ta shanye, ahmad ya zauna yace "to yanzu me kika yanke

laila?"
Cikin fishi tace "kai nagaji da wannan renin wayon, bazan iya zama dakai ba, kuma bazan iya riqema daba, Dan haka kasakeni cc

Ahmad baiyi wata wata ba, yadau paper yafara rubutu, har zaisa saki daya, cikin ransa yace kai! Ai kuma daddy yanasan auren nan,🤣 zai iya cewa namaidata, Dan haka yarubuta Mata saki uku yabata, ya miqe yace
"to ni zan wuce, yarinyar da akaban ma ta isheni rayuwa, baizama lalle saina haihu ba, kekuma tunda kinaso to kya samu awajan mijin dazaki aura,"

yana fadar haka yayi waje,
Motar sa yashiga yanaji kamar ansauke masa wani nauyi akansa, cikin nishadi yake tuqinsa zaije yaga baby

** *** **

" Mama kisamin da wannan teddy dinma,"

mama tace" baby Amma naga alama so kike ki barni ko? "🤣

Izdihar tace" mama ai uncle dinma yana sona,"

mama girgiza kai tayi, aranta tace" ina miki maganar kanki, kinamin maganar yana sanki,"🤣

baby tace " to mama yaqi Zuwa ma, yaushe zaizo ne?"😳

Mama tace"ai zaizo baby," Izdihar tace

" to mama kirashi awaya," mama tace
" wallahi idan bakimin shiru ba, saina bigeki."🤣 🤣

Dataga de mama Zata iya dukanta nan da nan tayi shiru,

12:26 yashigo Garin, kai tsaye gidan yashiga, da sallamar sa, baby najin sallamar sa ta taho da gudu ta rungume shi, Riga ce ajikinta pink color, marar hannu, sai qasan rigar ansa net yayi hawa hawa, tayi kyau sosai, anyi Mata fakin da gashinta, idan ka kalleta saika sake waigawa

Qansa aqasa ya tsugunna yagaida mama, suka gaisa sosai, mama aranta tace wannan yaro shide akwai kunya 🙈 babu ruwansa, Abba aka kira awaya, yana Zuwa basuyi wata wataba, sukai sallama dakowa suka dau hanyar kano, Izdihar sai bye bye take musu ta window, da yar

babynta ahannun ta,
Sunyi nisa atafia baby tace "uncle, kuma yaushe zan dawo wajansu mama?"

Ahmad cikin ransa yace tofa!
Kallanta yayi yace "baby ba yanzu zaki dawoba, Amma de zan dinga kawoki kina ganinsu kinji?"
Baby tace "to dawa zan dinga wasa? Da anty?"

Ahmad yace "emana, dasu maryam dani,"

baby tace "yeee harda kai uncle? Ashe kaima zakana goyani kamar sabuwar anty?" 😳

Ahmad cikin ko in kula yace "sosai ma,"

tanata zuba masa surutu, har sukai nisa ahanya
Daga nan tayi bacci

** *** **

"Oh me yake damuna ne?"

Cigaba tayi dahada kayanta, saida tagama tas, sannan ta janyo Jakarta ta futo,

"oh ya Allah tafadi haka da karfi,"
ta tsugunna awajan, runtse ido tafara tana lashe lips dinta, maigadi yana hangota yataho da sauri yana tambyarta hajiya lafiya kuwa? Laila ta dago ta kalleshi, tuni ya rikide yakoma Mata ahmad, janyo shi tayi jikinta,🙆🏻
cikin sauri ya fizge tare da fadin "subhanallah"
Yayi part din su hajiya da sauri yasanar musu abinda yake faruwa, dukansu suka futo, ga ma'aikata sunata kallansu
Laila ta tashi dakyar Zata sake ruqo maigadi, duk wajan kamar almara suka hada baki wajan fadin "lahaula wala quwata!!!" 🤣

Mamy hakima tace "laila me yake damunki haka?"

Laila ta nunata da hannu tace "babu ruwan ki,"

tasake yin kan maigadi, mom ce tayi sauri tace
wa driver ya dauko mota akaita asbiti
Mamy hakima bata daddara ba, ta ruqota tace "yi hakuri kawo jakar amaida ciki,"

laila tasake nunata da hannu 👉🏻kamar yar maye tace "nace miki babu ruwan ki,"

mom ce taga takarda ahannun ta, cikin sauri ta karba, budewar dazatayi idonta yagane mata😳

Laila ta cewa momy
" bani takarda ta"

,ta fizge takardar ta, daidai lokacin driver yazo, momy ta bashi umarni akaita asbiti, mamy hakima ce ta kamata suka sakata a motar, daga nan suka kira hajia salaha suka fada Mata abinda yake faruwa

Jikin momy asanyaye sukai cikin gida, mamy na tambayar ta, abinda yake faruwa

** *** **

"Feenah ta, saura wata shida mukoma gida, gaskya nikuma na matsu naga na mallakeki, Dan haka nakeso kibani dama intura gidanku ayi maganar auren mu, kinga damun koma saide asha bikin mu"

Murmushi nasaki nace
" mukhtar irin wannan gaggawa haka?"

Yayimin hararar wasa yace "to saina tsaya kallan ruwa kwado yayimin kafa, Dan haka bani wayar ki"
Kai tsaye nabashi, wajan text yashiga yace "tura a gabana, ki fadawa Abba iyayena zasuzo nemamin auren ki,"
Nace "mukhtar tun yanzu zan fada musu?"
Hannayensa ya hade waje daya yace "please feenah tah"
Babu yanda ta iya dole tatura masa, Abba yana zaune afalo yaga text din aransa yace to alhmdlh, yanata farin ciki

Saida tatura mukhtar ya kalleta, yace "da fatan de feenah ta zatai farin-cikin zuwan magabatana gidansu,"

cikin farin ciki nace "sosai ma"

Agogo ya kallah yace
" yamma tayi, yakamata mu tafi gida ko?"

Nace "tomuje,"

muna tafiya ahanya, nace " mukhtar jinake wani iri wallahi ajikina, kamar wani Abu yana faruwa,"

mukhtar yace "kinga ki kwantar da hankalin ki, insha Allah Babu komai"
Nace "Toshiknn
Amma de bari inkira mama itama saina hadaku ma ku gaisa,"

Kiran ta nayi muka gaisa kalau, nabawa mukhtar ma suka gaisa, saida nasake tambayar ta mama kowa de lafiya ko?
Cikin mamaki mama tace "kalau muke auta," nace "Toshiknn"
Har zan kashe sainace
" mama ina baby? "

Mrs Usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

49

Awannan ranar haka na wuni sukuku, wai ahmad dina ya haihu da wata batare daniba, wata zuciyar ce tace Dani baby fa?
Hawayen idona na share afili nace hakane

Zahra ce mai lallashi na Akan wannan mugun labari dana samu, har zazzabi nafara ji, 🤣daga karshe nasha magani na kwanta

** *** **

"My heart yakamata kayi sauri fa mukam mungama shiryawa kai muke jira,"
tahir ya dubeta cikin tsananin soyaiya yace "to ai kece baki taimaka minba,"
husna tace "naji bani kagani," cikin sauri tagama gyara masa kansa sannan ta bashi kayan da zaisa gamida taimakon ta, tsaf suka futo hannun su maqale cikin na Juna, twins nafalo suna

Zuwa sukafita Gaba dayansu
Basu zarce ko inaba sai wani hadadden super market, shopping suke cike da kulawa da annuri atare dasu , su mama suna binsu abaya, mima ce ta janyo mama tace
" kinga inasan wancan teddy , zamuje mu Dako"

Suka tafi da gudu, sunje dauka suka kasa, wata Mata suka gani agefe, mama tace "aunty please munasan wannan,"
tana ganin yaran taji sun shiga ranta, daga gani kasan twins ne

Dauko musu tayi, tace "toku tafi," maimakon su tafi sai sukai wani wajan,
Acan kuwa tahir da husna sunata neman su
Husna ce tafara hangosu
Tatafi cikin sauri wajansu, sannan shima tahir yaqaraso, baima kula da matar dake gefensa ba, yasa hannu yadauki mama, itama husna ta dauki mima, dagowar dazaiyi idanunsu ya sarke dana Juna, fuska yayi yafara tafiya
Ita kuwa cikin mamaki tace " tahir!"
Juyowa yayi yace "wacece?" 🤣
Tace "iklima cefa tahir, kana nufin baka ganeniba?"
Tahir yace " au iklima ashe kece ai ban ganekiba," 🤣
husna tana tsaye tana kallan ikon Allah,

Iklima tace " Dan Allah ko zaka iya bani number ka?"
Husna najin haka tayi gaba cikin fishi
Itama mama naganin maman ta sun fita da mima, nan itama tafara kokarin sauka daga hannun sa,🤣 ganin de mamanta take son bi yasa shima yasauketa, aikuwa da gudu tabi su husna
Tahir yace " iklima, bazan iya baki number taba, kiyi hakuri"
Yayi Gaba, iklima tace
" haba tahir, kayi hakuri mana, please tahir kayafemin abubuwan dasuka faru abaya, yanzu a shirye nake dannaga na aure ka" 🤣

Tahir yasaki murmushin dabai shiryaba, yace
" aure!
Nine zan aure ki iklima?a misali?
Haba aike ba ajina bace, saide gomnoni, kinga wadda Tafita yanzu? Itace matata, ita nakeso take sona, itace bata qiniba alokacin danake kaunar ta
Wadannan yaran kuwa namu ne nida ita, Dan haka kidena wannan mafarkin "
Yana gama magana yayi waje, iklima ta durqusa awajan tana kukan nadama

Yana fita, yashiga mota yaja suka tafi, tunda suka fara tafiya babu abinda husna tace dashi, ta maida hankalin ta ga window

Suna Zuwa gida, tafi ce tabar motar, ga qaramar leda ahannun ta, tabarta anan tayi cikin gida
Tahir yafuto da sauri yana "my heart!!"

Mama tace "mom kinbar ledar" 🤣

Amma ko kula su batayi ba

Tana Zuwa falo taga ummi a zaune, cikin mamaki ummi tace
" harkun dawo?"
Husna tace "um" 😱

Ummi tace "me yake faruwa ne?"
Husna cikin rawar murya tace "ummi ba komai"
Saikuma tasaki kuka
Alokacin tahir yashigo da kayan nasu ahannun sa, ummi tace " me akayi Mata ne?"
Tahir yace " ummi kawai tana ganin iklima ne shine fa take fishi"

Ummi cikin tsananin mamaki tace "iklima!!!
To ita datake Abuja meya kawo ta kano?"
Tahir yace "nima bansaniba ummi"
Husna taga sunma manta da ita, sun fara zancan wata iklima cikin fishi tayi daki 🤣

Ummi tace "a a kaga bita kabata hakuri, mezakai da wata iklima, Allah ya tsareka, matar data saka ahalin masifa"

Husna na Zuwa daki tafada kan gado tana kuka, suma yaran suka rirriketa, suna kallanta, tahir ne ya shigo yace
" mama kuje ummi nakiranku," da gudu suka fita

Yajanyota jikinsa ya rungume ta yafara aikin rarrashi, yace "kiyi hakuri mana my heart, idan Akan wannan matar kike kuka, ni ba sauraran ta zanyiba," husna cikin kuka tace bagashi nan har tana tambayarka number ba,"

tahir yace" yanzu my hrt daga tambaya number sai fishi?

Kuma idan zan Karo miki kishiya fa, sai yaya?" Husna ta aika masa da harara, yayi murmushi yace" naji, toyi hakuri mana, kinji, yanzu zan baki labarin iklima "

** *** **

After 2 months, yana kwance adakinsa, yafada duniyar tunani, yarasa meyasa mom keyi masa haka, batasan irin yanda yake kaunar feenah bane cikin ransa
Yama za'ai ace ya hakura yabarwa mukhtar ita

Ita kenan batada aiki sai wa'azi inrabu da feenah, bayan tasan abinda bazai iyu bane
Wayarsa yadauka yakira wani yaronsa yabashi kudi mai yawa, yace yaje yayi masa bincike
Akan mukhtar, kawai inda yake yakesan sani da kuma gidansu
Nan take yaron yace angama
Kwanciya yayi ya lumshe idonsa, yanajin wannan hanyar ce kadai zatasa yasamu feenah

** ** **

"Wayyo momy kiyi sauri please,"
momy tace "ahmad nifa kaga wannan tafiya saina fasata, haba tun jiya ka ishi mutane da zancan zaria" 🤣
Kunnansa yakama yace
" sorry momy
Shirya asannu muna jiranki afalo"

Yaja baby suka fita, momy tasaki murmushi tace "kai zamani"

Tsaf ta futo cikin shiri na alfarma, taji sarka ahannun ta da wuyanta, mamy hakima ma tana falo, tace " hajia yaude an samu tafiyar bazata," momy tace "ni hajia dakinbi su kunje ma, ni saina zauna agidan"
Mamy tace "a a kiyi hakuri muje"

Ahmad ne yadawo shima yayi kyau sosai cikin farin yadi mai ratsin milk color
Yakama hannun baby yace "to mamy sai kun futo muna jiran ku"
Momy tace "driver ne zai kaimu ne?"
Ahmad yace "haba momy, tayaya zanbar mutanan dasukafi komai tsada awajena wani yajasu, bayan gani, me amfani na?"

Auta tace "yaya Dan Allah kaje Dani," ahmad yace "auta, kawai yan gidansu baby zamuje mu Gano mu dawo, kiyi hakuri kinji, bazamu dadeba"

Maryam tace" toshkn yaya, Amma saide in zaka dawo kasiyomin ice cream," yace" angama gimbiyata "

Muslim ne yace" baby! "
Tajuyo tace" bye bye na tafi wajan Abba "
Yace" ki tahomin da abin dadi "
Tace" to "
Su momy sunata kallansu
Bukhari ya dubi ahmad yace" yaya Muslim yana San baby, zaka bashi ita? "🙆🏻😳
Cikin tsananin mamaki ahmad yace " Bukhari me kace?

Karna sakejin wannan maganar abakinka kaji ko? "
Yace" sorry yaya, nadena fada "
Yace"ok"
Yaja hannun ta suka fita, su momy ma suka bisu abaya, suna shiga basu tsaya ko inaba sai zaria

Su Abba sunyi mamaki kwarai dasuka ga ahmad yakawo musu iyayen sa sun gaisa, sosai suka qara yarda dashi, sun San konan gaba bazasuyi DANA SANIN bashi baby ba

Kayan abinci sosai momy tasa aka kawo musu, duk da basu rasaba, shima dakyar Abba ya yarda yakarba, Dan yaga wahalar nasu yana nema yayi yawa

Dazasu tafi izdihar sai bye bye take musu, nan suka sake tabbatar wa kansu cewa tana cikin kwanciyar hankali
Mama tace "baby ko kewata ma bakiyi ba?"

Daria kawai tayiwa mama, mama tace
" toshkn Amma ai kinyi kewar sabuwar anty ko?"
Da sauri ta daga kanta, tace mama
"  aitatafi tabarni "
Mama tace "a a bata barki ba baby Zata dawo nanda wata daya kinji"

Ahmad yana jinsu aransa yace zai zauna da baby de ya tambaye ta, wacece wannan sabuwar antyn?
Agidan take?
Yayarta ce?
Menene sunanta?

Dahaka sukai sallama dakowa, su momy sosai sun yaba dasu mama, kuma sunsan baby daga gidan qwarai take

** *** **

Yana zaune Akan motar sa aharabar gidansu, yaronsa yazo, yakawo masa wata takarda, yace " gashi oga, angama komai, wannan shine abinda bincikenmu ya nuna Akan mukhtar"

Kb yace "toshkn ngd, zaka iya tafiya"

** *** **

"Oh feenah, wai kina nufin harkin fara hada kayanki?"

"To Zahra mezan jira, saura 5 days na wuce gida, kede nake bawa shawara ki tsaya kiyi masters" 🤣
Zahra tace "a a feenah bazan iya ba, shekarar mu hudu fa a qasar nan, gara mutafi kawai"
Feenah tace "hakane kam nima wallahi ganinki ne yasa na iya zama
Dakuma mukhtar Amma banda haka da iya degree na ya isheni, zaman duniya de bana qiyamaba,"

Zahra tace "ai shine"

Feenah taci Gaba da cewa, "wallahi wannan zuwan cike nake da darura Zahra, nakasa gane inda su mama suka dosa, kullum nakira waya nace abawa baby basa bata
Zahra anya kuwa baby ba mutuwa tayi ba?" 😭Taqara sa maganar cikin kuka
Zahra tace "haba feenah, haba qawata meyasa kike wannan maganar ne?
Insha Allah Babu komai sai alkhairi, Amma nikuma feenah sainake tunanin anya ba wajan husna ta koma ba, tunda kinga dama tanasan abata baby"
Feenah tace "aiko wajan kaka takoma ina Zuwa zan karbe 'yata,🙆🏻😳nima inasan ta, Zahra wallahi ina qaunar baby
Ban qara tabbatar da hakanba saida naje hutu, shiyasa namatsu nakoma inga halin da yata take ciki"

Zahra tana murmushi tace "ga kuma bikin dayake tunkaro muba,"

Feenah tace "shima kinga yakamata nakoma a fara shirye shiryen yanda abin zai kasance" ,
Zahra tace "eh wlh, to Allah yakaimu lafiya de," nace "amin"

"Zahra zaki rakani afra, da kasuwar sha'abi, gobe inje inyiwa baby siyaiya, daganan ma sai muje top galary musai takalma"
Zahra tace "babu damuwa, naga alama de wannan zuwan siyaiyar baby daban ce"
Nace " eh wallahi Zahra, ai sosai nakeso naje naga sagiraty na, mu kwana muna firar yaushe gamo 🤣
, Zahra bazaki ganeba saikin haihu"

Tace "to Allah yakaimu feenah, Amma yanzu de please tashi muje imtiyaz musai shawarma,"

nace "a a gaskiya muje baiti shami (shami house)"

Zahra tace " to naji muje, dole ai nayi miki abinda kikeso tunda nanda 5 days muna gida ba ganinki zanyi ba"

Nan nadau mayafina muka tafi

Mrs Usman ce ✍️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

50

Washe gari mukaje nayi siyaiya, Zahra ma haka, nasaiwa twins kayan wasa Sosa, da Abban anty maimuna, saikuma baby daduk nata yafi na kowa

Da daddare muna zaune nida Zahra, tace "nikam feenah akwai abinda yake damuna game dake,"

nace "Zahra menene wannan Abu kuwa,?"

Dawowa tayi kusa Dani tace "wallahi wata alfarma nake nema awajanki,"
Nace "inde batafi karfinaba mezai hana nayi miki Zahra, ai kinfi karfin komai awajena," Zahra tace "feenah mezai hana ki fadawa ahmad baby yarsa ce?"

Da sauri na kalleta nace "saboda me?"
Tace "to saboda me bazaki fada masaba? Har sai yaushe feenah? Sai lokacin da yarinya tagane basu Abba ne iyayenta ba?
Kice Mata me alokacin?
Kokuma sai alokacin zaki fara nemansa Akan wannan maganar
Kinsan de duk daran dadewa dole yarinyar nan tasan gaskiya
Aganina gara kifada masa yasan cewa yanada wata yarinyar, tunda gashi harya fara haihuwa da wata, yasan cewa ba 'ya' yanta ne kawai nasaba, akwai wata "

Ajiyar zuciya nasauke nace" hakane Zahra, kinyi gaskya, Amma kinsan de abinda yamin bai kyauta bako?" Zahra ta dora hannun ta Akan kafadata tace" feenah banasan kina tuna baya Idan kikace zakina tuna baya da kuma abinda aka miki, bazaki taba yafe masaba, idan baki fada masaba, ke kadai zaki zame Mata uwa da uba ne? Idan ta girma tace ina mahaifina cemata zakiyi nice mahaifinki? Bazai iyuba! "

Nace" to ai nafadawa su Abba bansan wanda yamin cikin ba,"

Zahra tace" Amma kuma keda shi kunsan kanku ba "

Nace"hakane Zahra, Amma ni gaskya bazan iya kiransa ba," Zahra tahade hannayenta waje daya, tace "please feenah, rabuwa fa zamuyi"

Kallanta nayi nace
" Toshiknn, Amma kinsan de, yanzu baya Nigeria, tunda a Egypt muka ganshi, kuma ni number sa ta Nigeria na riqe"

Zahra tace "toga shawara,"

nace "menene shawarar ki?"
Tace "mezai hana kikira saudat
Kinga ta dalilin ta zaki samu number sa koba hakaba, kokuma in kina ganin bazaki ki rashin ba, kawai sai kiyi Mata bayani ita saita fada masa,"

Murmushi nasaki nace "Zahra uwar yan shawara, Toshiknn zan kirata insha Allah"
Rungume ni tayi tace
" Nagode feenah"

** *** **

After 2 days
Suna zaune tana yanke masa farce, yace "qawar iklima, yaushe zan kaiki wajanta ku gana da Juna ne?"
Husna tace "Allah kacika baki kagani, kafarka ce ahannu na"
Tahir yace "kina yankani babu asbitin da zanje, kece zaki dubani
Kanki kika janyowa aiki, nida nakeda Mata likita," tace "nide kadena yimin zancenta"
Yace "angama my heart"

Husna tace "yaufa saura 3days sister tadawo," tahir yace "manyan yan boko kenan, kice munada manyan baqi, kinga ranar saiki shirya da wuri muje Airport mu dauko ta ko"

Husna tace "abinda nace Mata kenan, tasauka anan idan ta huta, saita tafi, kokuma Washe gari ta wuce
Amma saita cemin, bazata iya Zuwa kano tazauna ba tare dataga mama da baby ba"

Tahir yace "to ai babyn tana nan, basai taje taganta ba," 🤣
husna tace "ai kasan har yanzu batasan an bayar da itaba"

Tahir yace "to menene Dan bata saniba, mu munsan anbada itane?"

Husna tace "saboda yarta ce,"

tahir baisan lokacin dayakai kallansa gareta ba

** *** **

"Baba yarinyar nan inasanta, tana sona, aurawa danka ita hakan yana nufin barazana ne ga rayuwata"

Baba ya kalleshi dakyau yace "yaro ni bangane abinda kake nufi ba,?"
Kb yace "inaso danka mukhtar yarabu da nafeesa yabarmin ita, nizan aure ta, konawa kakeso zan baka, kudi ba matsala bane"

Baba yasaki murmushi yace "yaro kasan kuwa wannan yarinyar dakake magana Akan ta ansa Musu rana?"
Kb yace "to menene Dan ansa musu ranar? Aure aka daura musu?"
Baba yace "to kaje da kudin ka, Bama buqata mu yarinyar mukafi buqata"
Kb yace "Allah tsoho? Haka kace? Toshiknn zakaga abinda kudi zaiyi," yana fadar haka yajuya yatafi, Yabar baba da budadden baki

** *** **

Husna ta share hawayen idonta, tace "nadade da burin infadama wannan maganar Amma ina darurar ta ina zan fara?
Tare muka tashi da ita tun yarinta, bamuda wani Hali na rashin kirki, tarbiya daidai misali anbamu, daga bayane itama wannan qaddarar ta fada Mata

Wani marar imanin ne yayi raping dinta, anan Garin, harta samu ciki, wadda kacemin kun karbi haihuwar ta a sbitin ka, har kace ahmd ne yabata jini, auta ce tahir

Alokacin data haihu lokacin yayi daidai da haihuwar mama, ta haifi namiji, Amma ya rasu, hakan ne yasa Abba ya karbi baby daga wajan auta, yabawa mama ita, saboda rufin asirin ta "

Tahir daya mutu da mamaki yace"yanzu kina nufin baby dama ba 'yar mama bace?" Husna tasake goge hawayen ta, tace "hakane, bamusan yar waye ba, tunda tun lokacin anyi Mata tambayar duniya tace wallahi batasan wanda yayi mataba, inda ace tasanshi, nasan cewa Sai inda karfin Abba yaqare"

Gaban tahir ya dinga faduwa yace "kuma kikace raping akayi Mata?"

Husna tace "eh"
Cikin ransa yace " to ai kuma ita wannan tace batasan waye yayi Mata ba, bare yayi tunanin wani Abu"
Janyota yayi jikinsa yafara rarrashinta, yace
" Allah yasaka Mata, kiyi hakuri kinji,"

kanta ta dora Akan kirjinsa

** *** **

Next day

"Wallahi alhaji gabana har faduwa yake idan na tuna yarinyar nan jibi Zata dawo"

Abba yace "menene abin faduwar Gaba kuma maman nafeesa?
Saikace ba kece kika karfafamin gwiwa Akan abinda mukai ba
Nafeesa de mune muke iko da ita, dan munbada wannan yarinyar ni aganina kamar rufin asirinta ne
Saikiga anyi Abu, kana tunanin babu wanda yasani, Amma daga baya sai kiji maganar awaje

To kinga inde ubane, izdihar tasamu, bana tunanin ko mutumin dayayiwa nafeesa wannan abun yakai ahmad son izdihar
Dan haka ga uba nan tasamu, mamanta kuma nafeesa

Koda tayi aure zaman baby awajan ahmad yafi sauqi
Dan haka tana dawowa zanyi Mata bayani da kaina "
Mama tace" to shikkenan Allah yakaimu alhaji "

** *** **

"Kinga ni kawai kiyimin baqin lallan, banasan Jan"
Zahra tace " meyasa feenah,? Kawai ayi mana, duka, baqi da Jan"

Nace "Zahra Jan lalle yana dadewa ahannu na bai fitaba, Amma baqin baya wuce sati daya"

Zahra tace " ok, kumafa hakane, to kawai ayi mana baqin, kar muje ayi mana Jan yaqi fita da wuri
Kuma ga biki yana matsowa"
Feenah tace "emana, nima shi nagani"

Zahra tace "Amma de ai a kano za'a yi miki dilka dasu qunshi ko, kinga sai Amana Gaba daya"
Nace "emana insha Allah"

Mai qunshi takama hannun Zahra tafara yi Mata, saida aka Gama musu, su kabar unguwar

Da daddare sunyi wanka, kowa yana kwalliya, Zahra takira mukhtar tace "ango, to anjima din zaka turo mana motar dazata kaimu airport ne kokuma kawai mutafi?"

Mukhtar yace "a a ku zauna nima sai nazo gidan naku, daga nan saimu kira Tirhal kawai takaimu Airport din Gaba daya"

Zahra tace "a a yanzun kai kana ina?" Yace "ni ina unguwar Salamah yanzu ina sallama da friends dina, kuma daga nanma
Meenal barri zanje daganan inje hilla soba,"
Zahra tace "am mukhtar naga al'amarin Naka bana qare bane kawai sai kazo anjima din" 🤣

Ta dubi feenah datake kokarin saka Riga doguwa abaya mai kyau, tace "wannan angon naki yacika zirga zirga"

Feenah tace "toya za'ai kinsan shi mutum ne na mutane"

Zahra tace "to waye bana mutanan ba, me kike nufi?"
Feenah tace "ahmad mana, tunda nake dashi bai taba nunamin daya daga cikin abokansa ba, kullum saide yacemin yaso yazo da abokinsa Amma abokin nasa bashida lokaci
Dayake abin nasa bana gaskiya bane, Amma inda ba yaudara ce takawoshi wajenaba mezai hana yanunamin wani nasa"

Zahra tace "aikuwa inkina neman mutum na mutane ma kika samu ahmad kinga ma yarinya
Ke shaida cede, kingani da idonki lokacin da mukaje masar
Kinga yanda mutane suke rububinsa"

Feenah tace "um aikam nagani, zahra'u Ahmad muha marzuk" 🤣

Zahra tace "edin kiyi ta fada
Yauwa kin kira saudat kuwa?" Feenah tace "gara dakika tunamin namanta"

Wayarta ta dauko, tasa number saudat, tasa wayar a handfree
Zahra tadena kwalliyar datake tazauna zataji ya zasuyi

Kiran farko a kace call end, feenah tace "Zahra kode tadena amfani da layinne?"
Zahra tace "sake gwadawa muji"
Sake kira tayi, aikuwa bugu uku Ana hudun aka daga

Feenah tace "sister saudat, yar'uwata takaina, amaryar farouq maman baby"

Har abada bazata taba mantawa da mamallakiyar wannan muryar ba

Saudat tace "Dan Allah mafarki nakeyi ko a gaske ne?
Feenah kece? Sister feenah
Kiyi magana mana,"

Tuni kuka yazomin, nace "nice saudat, kwana dayawa yagida, yayaranki?"
Saudat itama kukan take tace "feenah ina kika shiga? Neman duniya muke tayi miki nida yaya"

Nace "saudat ina nan," tace "to kina wanne qasa, naga number bata Nigeria bace"
Nace "eh ina Sudan saudat
Gobe zan dawo Nigeria, inaso zamuyi wata muhimmiyar magana dake, idan nazo insha Allah inasaka wani layin awayata zan kiraki"

Saudat tace " to feenah Dan Allah kikirani, Allah inasan ganinki sosai,"

nace "saudat zankiraki, ina yaranki, sai tambayarki nake kinyi shiru?"

Saudat tace "ban haihu ba feenah, ina fatan de nasamu cikin"
Nace "Allah sarki yar'uwa, nima to zan dinga yi miki addu'ah Allah yabaki," tace "amin"

"Dan Allah feenah ina kika shiga Tsawon wannan lokacin?"

Nace "saudat zamuyi magana idan na dawo kasar"
Tace "to shikkenan, I miss you sosai"

Nace "wallahi nima haka, sai anjima, sai munyi wayar"

Saudat tace "feenah banji kin tambayeni yaya ba, ko akwai abinda yake faruwa ne?"

Nace "saudat babu komai karki damu"
Tace "To shiknn" , nan mukai sallama

Saudat tace wannan daddadan labari ai dole in fadawa yaya, nan take takirashi, saide baya kusa bai dagaba

Sai wajan 11:30 pm yaga Kiran nata, yace gobe ya kirata yasan yanzu tana tare da mijin ta

Ajiyar zuciya nasauke me nauyi, nakalli Zahra ba tare danace komai ba, Zahra tace " to yanzu

ke bakifijin dadi Bama"

, nace "wallahi naji dadi Zahra,
Nayi missing saudat
Tana sona sosai
Zahra tace mukuma banda mu ba,

nace nina isa nace haka
Aike ce first lady

Karfe uku na dare muka tafi airport, bamuyi awa dayaba muka tashi

Bye bye Sudan

dayake jirgin Ethiopian mukahau

Saida mukayi transit a Adis-ababa, na Tsawon awa biyu, sannan mukahau wani jirgin Zuwa Nigeria, karfe 11 nasafe, cikin Airport din Malam aminu kano tayi mana

Mrs Usman ce 🖊️[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

51

Bayan mun futo, nayi sallama da Zahra Akan sai munyi waya, mukhtar yace "wai yanzu bazaki bari azo daukan naki ba?"
Nace "emana dakaina zanje,"

Dan haka yaje yanemomin taxi
Shiya bashi kudin, nan mukai sallama dashi nikuma na shiga sai zaria

Muna sauka a kofar gida, naga gidan ya canja, na futo da mamaki Akan fuska ta, Abba naganin motar mu ta tsaya yaqara so da sauri, yace
" sannu mamana "
Nace "yauwa Abba,"
Nafadi haka hankali na nakan gidan
Muna qarasawa gate mama tazo ta rungume ni, tana "sannu autata," nace "sannu mama"

Afalo muka zube, nadora kaina Akan cinyar mama inata kallan falon da tsananin mamaki

Mama tace "taso kici abinci kiyi wanka kihuta,"

nace  " kai mama barni nagama Jin duminki tukunna," 🤣

saida nahuta Abba yashigo yanamin sannu
Yace " yarinya ki dage ke kadai zaki taho basai munje ba,"

nace "Abba banaso kusha wahala, ai gashi nazo," yace "hakane to Allah yasa angama a sa'ah" nace

"amin Abba"

Mama na kallah nace
" mama ni banga baby ba, tana ina ne?"
Abba da mama ne suka hada ido lokaci daya

** *** **

Yana juyi Akan kujerar office dinsa, wayarsa na hannun sa yana kallan pictures din baby

Wata folder yabude saida yasa security sannan naga yashiga, pictures dinta ne rututu aciki, wani da saudat wani ita kadai
Murmushi yasaki yace
" my feenah I luv u"

Hada pic din yayi dana baby, yace afili, " narasa banbanci tsakanin su,
Allah kenan mai hada kama
Saikaga mutum bakasan Shiba baisanka ba, Amma kaga suna mugun kama"
Pic din yashafa yace "ina sanku dukanku"
Ganin pictures din saudat ne yatuna masa da kiranta da baiyi ba
Fita yayi daga cikin folder ya kirata
Bugu daya ta dauka tace

" yaya!!!"
Ahmad yace "sauda karki kashemin kunne Dan Allah"
tana daria tace "yi hakuri yaya, munyi waya da feenah jiya
Shine nakiraka zan fadama Amma ban same kaba"
Ahmad daya tsinci zancan kamar a mafarki yace " me kika ce?" Tace
" yaya serious nayi magana da ita jiya"
Yace "please turomin Number,"

tace "yaya bazaka sametaba,"

"Kituromin nace," yakatse Kiran, ita kuwa batayi musu ba, tatura masa, yana ganin number yakira
Taqi shiga, yasake kira taqi shiga, haka yayita gwadawa
Daga karshe de yakira saudat yace "meyasa bata shiga ne?"

"Yaya dama fa nafadama bazaka sametaba
nima jiyan tacemin ne tana Sudan kuma Yau Zata dawo Nigeria, Amma idan tasa sim card din Nigeria Zata kirani"
Cikin mamaki yace
" Sudan kuma?"
Saudat tace "eh haka tacemin, wai tana karatu ne"
Cikin ransa yace "Tome ya kaita Egypt?"

Yace "to shikkenan idan ta kiraki please Kituromin Number,"

sauda tace "wallahi yaya nima na matsu takiranin saboda tacemin wai zamuyi wata muhinmiyar magana," gaban ahmad yayanke yafadi, bade abinda yafaru Zata fadawa sauda ba

Zancan nata ya katse da cewa " Amma bata yi miki magana taba?"
Sauda cikin murmushi tace "a a batamin ba, da zamuyi sallama nede nace bata tambayeni yaya ba ko akwai abinda yake faruwa?
Saitacemin karna damu Babu komai"

Wata nannauyar ajiyar zuciya yasauke, yace
" Toshiknn, Amma de tana kiranki Kituromin number karki manta,"

Tace " insha Allah yaya"
Sallama yayi Mata, yafada duniyar tunani, Sudan, Egypt, tana karatu a Sudan, tome ya kaita Egypt? Duk wannan tambayoyin yana wajan feenah
Muhinmiyar magana, tome Zata fada Mata?
Innalillahi
Gara tunda wuri yadamu saudat Akan tabashi number nan, yabawa feenah hakuri, tayafe masa,

tunma kafin suyi maganar, duk da bashida tabbacin wannan maganar zasuyi

** *** **

"Yanzu mamana menene abun kuka, saboda mun dauki yarinyar nan mun bayar da ita? Nayi tunanin zamu iya iko dake da abinda yake naki ne
Sannan karki manta duk daran dadewa akwai ranar da zatazo wannan yarinyar tagane ba mune iyayanta ba
To wannan bawan Allah yana kaunar yarki kamar shine ya haifeta, nafeesa bana tunanin kema kina Santa kamar yanda yake Santa
Izdihar de tana kano, tana wajan uban gidan ammun ku, idan kinasan ganinta ne kya iya Zuwa ki ganta 🙆🏻
Kokuma ayi masa waya idan yasamu dama yakawo miki ita ki ganta "

Hawayen idonta ta share tace" Toshiknn Abba Nagode Allah yasa hakane yafi alkhairi"

Abba yace "yauwa mamana, haka nakeso naji, yaron yanada hankali, duk mutumin daya nuna yanasan Naka ba qaramin masoyinka bane, to nide abinda nakeso dake shine ko bayan raina, inde ba mahaifin wannan yarinyar ne ya baiyanaba to banaso naji kince ahmad bashine ya haifi Izdihar ba "
Cikin sauri tadago kanta Jin sunan da Abba ya ambata

Ahmad!
Sunan da bazata taba mantawa dashi ba, kuma mutumin dayaci amanarta karshe yaje ya auri wata, me sunansa ne zasu dauki yarta su bashi

Abba yace" mude mun yarda dashi, Dan haka kema inaso kisawa zuciyar ki salama, kinji ko? "
Nace" to shikkenan Abba,"
Yace" yauwa Allah ya miki albarka," nace" amin "

Daki na shiga, ina kuka ni kadai, Amma abayar da yarinya kyauta, aka sa kirana a fadamin, Amma aiko husna yaci ace takirani tafadamin
Wayata nadauko zan kirata, kawai ma nafasa

Wanka na shiga, adakin da aka nunamin a matsayin nawa, duk abubuwana suna ciki

Ina futowa awanka, na kwanta da niyyar hutawa nan bacci ya daukeni

Wayar da mama takeyi ne ya tasheni, tace
" gatanan bacci take,"
juyi nayi, nace "mama wace?"

Wayar tabani tayi waje
Nace " hello,"

tace "Allah sarki sis, kina bacci nasa antasheki ko?
Na matsu naji ya kikazo ne"
Nace " anty husna ai fishi nake dake"
Tace "subhanallah, me yake faruwa,"

nace "yanzu har abada baby Amma koki sanar Dani?"
Husna tace " sister bahaka bane, nasan abin da ciwo, tunda nima inada yaran, nasan yin hakan babu dadi, wallahi shiyasa ma naji tsoron fadamiki"

Nace "to ai shikkenan, Abba yafadamin," tace "kiyi hakuri
, komai mai wucewa ne, kuma hakan shine yafi, idan kikai tunani"
Nace "hakane, aina hakura ma
Ina twins?"

Tace "suna wajan ummi, ga tahir"

Wayar tabashi muka gaisa, yace "irin wannan qin zumunci haka auta, memakon ko kwana biyu ne ki tsaya kiyi mana"

Nace "kuyi hakuri yaya tahir, wallahi na matsu nazo naga mama ne da baby"
Yace "to ai muma gobe zamuzo ko jibi, kar muyi laifi," nace "a a yaya tahir, kawai ku zauna nima zanzo, inaso naje naga baby, this week insha Allah zan shigo,"

tahir yace "to shikkenan, da fatan de Babu matsala ko?
Karfa kisa tunanin abin aranki," murmushi nayi nace "babu komai yaya tahir, sai anjima,"

yace "toshkn ki huta lafiya"

Baccin daban komaba kenan, sai kirana suke ta layin mama suna min sannu da Zuwa, daga karshe ma a cinyar mama na kwanta muka kafa sabuwar fira, sai zance muke munata daria, kamar babu abinda yake damuna,
Nace "mama wai nikam yaushe Abba yasake mana sabon gina ne?"

Mama tace" ba abbanki ne yayi ba, baban Izdihar ne yayi mana "
Cikin raina nace wai baban Izdihar, ga babanta acan wani waje ga nan Ana liqawa wani ita, nace" Allah sarki, Allah yasaka da alkhairi"
Abba ma daya shigo yaga nasaki raina saiyaji dadi

** *** **

Awannan rana saida saudat tayi DANA SANI Akan Kiran ahmad datayi, domin kuwa damunta yayi da jarabar Kiran waya, Ajima kadan yakira ta yace har yanzu bata kiraba?
Saudat tace wlh yaya bata kiraba, nima jira nake, ai tana kira zan turoma insha Allah
Allah Allah yake yasamu number ya kirata, ya matsu yaji muryar ta, lumshe idonsa yayi yace my feenah, please kikira mana

** *** **

"Momy albishir inkin"
", goro sauda, menene?"
Tanada fara'ah tace
" Momy Yau sis takirani," Momy cikin rashin fahimta tace "wacce sister?"
Saudat cikin shagwaba tace "kai Momy sister feenah fa, budurwar yaya"

Momy cikin mamaki tace "wai wannan qawar taki dakukai karatu?"
Saudat tace " emana" , Momy tace " um Amma nayi miki murna, yanda kika shiga damuwa dakika rasa number ta,"
Saudat tace "Momy muka shiga de nida yaya" 🤣

Momy cikin mamaki tace "wai kina nufin itace yarinyar dayake so, yace yanemeta yarasa?"
Sauda tace "emana, itace fa Momy"
Momy tace "to ina tashige kuwa duk dadewar nan?"
Saudat tace" wallahi Momy bata qasar ne, karatu takeyi a Sudan," Momy tace" kai alhmdlh Allah Nagode ma,
Yanzu shi ahmad din yasamu labari? Sunyi magana da ita? "
Saudat tace" ai bamuyi waya da itaba a Nigeria, jiyane fa takirani, tace Yau Zata dawo qasar, idan tazo Zata kirani inga number ta", Momy tace

"Kai Amma naji dadi wallahi, Allah ya karbi addu'armu Yau

Kice mutumin naki, sai murna," saudat tace "ai Momy Yau kadai ma yakirani yakai sau biyar, wai takirani? Nace har yanzu de nima jira nake"
Momy tace "to Allah yasa ta kira" , nan sukai sallama

** *** **

Daddare Ammu yakirani awayar mama, yayimin sannu da Zuwa, yace yakira number ta taqi shiga, nace wallahi ban dora layin bane
Yace to insa zai turo min kati yanzu, godia nayi masa gamida saka sim card din nawa

Aikuwa ya turo katin 1k, nakira shi nayi masa godia

Ina kwance adakina, da daddare, nakira layin Zahra, Allah yatemakeni nasameta, tace shine tun dadewa kikaqi dora sim card dinki, sai nemanki nake, nace "yi hakuri Zahra, wallahi bana cikin kwanciyar hankali nane"
Zahra tace "subhanallah me yake faruwa?"
Nan take nabata labarin abinda yafaru game da baby
Tace "anbada ita, abun kamar almara, Amma nikam banji dadi ba, saide ta wani Fannin kuma sunada gaskya," nace " hakane"
Tace "to kiyi hakuri feenah, haka Allah ya tsara mana, yanzu yaushe zakizo kiga babyn?"
Nace "cikin satin nan zanzo Zahra"
Tace to saikin zo, Allah yakawo ki lafiya, nace "amin Zahra Nagode "

** *** **

Da asuba mama tajira taji shiru shiru bataji motsin tashi naba, aranta tace may be baccin gajia nake, anjima zan tashi

Da aka jima dinma de haka taji shiru, tana Zuwa ta leqa dakina, ta ganni na tuqun qune cikin blanket, tace "auta tashi kiyi sallah mana "

Natashi dakyar, nace mama wallahi sanyi nakeji, tace yanayin ne haka, kinsan sanyi ya matso
Natashi nayi sallah nakoma bacci,
Da gari ya waye ma haka, mama tajira taji shiru ban futo ba, taleqa Dakin, kawai sai ganina tayi ina rawar sanyi, da sauri taqaraso tana tambaya ta lafiya?
Cikin rawar murya nace "zazzabi mama"

Dasauri tayi waje takira Abba, Babu bata lokaci muka tafi asbiti
Ansamin qarin ruwa, sai allurai da aka min, likita yace su kwantar da hankalin su babu abinda yake damuna

Kawai damuwa ce araina, yakamata su kiyaye abinda zaina batamin rai saboda hawan jinin danake tare dashi

Abba da mama lokaci daya suka hada baki wajan fadin "hawan jini doctor?"

** *** **

Tsawon kwana daya dayayi yana jiran Kiran feenah, duk yadamu, saida saudat tayi dana sani yafi aqirga,
wata sabuwar qaunar tace take shiga cikin jini da gangar jikinsa, fatan sa daya feenah takira

waya

** *** **

" Yanzu auta saboda Allah dama baki cire maganar baby aranki ba?
Har hakan yasa doctor yace mana kinada hawan jini, haba nafeesa, kiyi hakuri mana"

"Abba kayi hakuri insha Allah nadena, Amma ku kwantar da hankalin ku, tun lokacin haihuwar baby dama inada hawan jini"

Sanin dasukai idan mutum zai haihu mafi yawan Mata sunada hawan jini, hakan ne yasa suka yarda da maganar ta, Abba yace
" to shikkenan, ga magungunan ki nan kidaure kisha kinji," nace
" to Abba"

Mama ce takawomin abinci naci sannan nasha magani na kwanta

** *** **

After 1week
"kaji Abba Dan Allah kabani, Allah a hankali zan tafi,"

Abba yace "a a mamana tafiya daga zaria Zuwa kano, ke kadai, kuma ni nasan hannun ki bai fada ba da driving din nan,"
Cikin shagwaba nace
" Allah Abba a hankali zanja, kaji Abba
Kaga inada kaya dayawa, ga tsarabar su anty husna da yara,
Amma kaga idan kabani motar shikkenan '
Abba yace "Toshiknn naji, Amma kitafi a hankali banasan gudu," nace" to Abba insha Allah"
Da saurina kuwa nasa duka kayan aboot din motar
Nayiwa su mama sallama tana cewa yaushe zaki dawo nace kawai sai kun ganni mama, tace" na gaida kowa da kowa'

Agidan kaka nasauka saida nawuni agidanta muna abinda muka saba, sannan natafi gidan husna,
Sunyi mamaki sosai dasuka ganni da motar Abba, tahir yace "gaskya nayarda autar ce, tunda Abba yayarda yabaki wannan motar," dukanmu mukasa daria, kamar mun saba dashi dama haka naware mukai ta fira
Sai jana yake da fira, harda cewa ban hadashi da mukhtar ba, nace karya damu gobe zan hadasu su gaisa
Husna ce tace" yaushe zanje inga baby" nace

" gobe da safe insha Allah"

** *** **

Yana gama cike ciken wasu takardu yadawo da hankalinsa ga baby datake game da kayan baccinta ajikinta, yace
" yauwa baby nikam Yama sunan sabuwar anty?"
Baby tasa daria tace
" uncle kawai haka sunanta, nima haka nake kiranta"

Ahmad yace "kai baby, kuma bata taba fada miki sunan taba?"
Tayi shiru alamar tunani sai can tace "yauwa natuna
Tataba cemin sunanta nafeesa"
Gabansa ne yayi muguwar faduwa

Mrs Usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

52

Yace " me kika ce baby?" Tace "nima haka naji mama tana fada Mata, uncle sabuwar anty tana sona, kaima kana sona ko?"
Kamar wani dolo yace
" emana,"

tace "to kamar yaya?"
Yace "kamar cikin duniyar nan"
Daria tasaki tace " to ai itama haka tace,"

ahmad yace " wa?"
Tace "sabuwar anty mana," 🤣

Gaba daya jinta yake kawai Amma azahirin gaskya gabansa mugun faduwa yake, yace "baby tashi kije ki kwanta"
Turo bakinta tayi gaba tace "uncle nifa bangama game dinaba," yace  " bani wayar nan kije ki kwanta,"

tace "to ai Babu school ko"
Yace "saboda babu school bazakije ki kwanta ba, oya tashi,"
Tashi tayi tatafi cikin fishi, yadauke wayarsa jikinsa asanyaye
Ganin tatafi ko sallama babu yace  " baby,"

tajuyo yace "zonan,"

tana Zuwa yanuna Mata kumatunsa,
Tagane abinda yake nufi, Dan haka tayi masa kiss tace "bye bye, uncle," yace "yauwa baby na, bye"

Tana fita yafada duniyar tunani, karfa ace qanwar feenah ce wannan yarinyar
Nafeesa!
Ya maimaita sunan aransa, kai gaskiya da sake, dole gobe da sassafe yashirya yaje zaria
Kawai zai tambayi mama bayan husna da baby batada wasu yaran ne? To kuma bazatayi tunanin wani Abu idan yayi Mata wannan tambayar kai tsaye?
Kai da sake, gaskya de dole gobe yakira mama awaya, kokuma de yaje Garin da kansa yaji gaskyar al'amari

Da wannan tunanin ya kwanta, Amma zuciyar sa Gaba daya banda faduwa babu abinda take

Asuba ta gari hammad

** *** **

"Kawai kisa Mata su acikin wannan jakar nakega ai tafi girma ko?"

Nace  " yauwa anty husna kin kyauta, ai danma wannan teddy's dinne dayawa, da bazasu cika jakar ba"
Tace "hakane, nikam da kinji tawama Dakin sani, dabaki siyo dayawa ba, tunda wannan gidan bana tunanin baby Zata rasa komai," 🤣

Nace "zanje de inga wannan gida, inga me ake bawa baby data manta da maman ta"

Husna tace "ok yanzu kinayin yar da ita kenan,"

nace "dama ina yi, alkunya nake muku," 🤣

cikin daria tace "Allah ya shiryeki feenah" nace "amin"
Ina gamawa nace "bazaki tafi wajan mijin kiba?" Tace "aikuwa kamar kinsani, nasan yana can yana jirana, bari natafi" , ta miqe Zata dauki
Mima nace "sister barsu kawai, barsu mu kwanta"
Tace " ok"
Adduah nayi musu nakashe wutar Dakin na kwanta, ina Allah Allah gari ya waye inje inga baby nah

Asuba ta gari nafisan mukhtar

** *** **

"Mom kudin hannu na fa sun qare, kozan samu ko dubu hamsin ne awajanki?"
Hajia salaha tace "yanzu laila bazakiyi wa kanki fadaba? Kikaga de duk abina nayi hakuri, ina zaune agida lafiya, har Allah yasa hankalin babanki yadawo kanmu yayi hakuri ya maidamu, Amma shine ke koda Yaushe kina cikin yawo?"
Laila ta yatsina fuska, tace "mom
Bazaki ganeba
Tunda nace bazaki ganeba, bazaki gane dinba
Inada party anjima kadan, bazan samu damar dawowa gida ba, sai wajan dare, nina tafi"

Hajia salaha tana " laila, laila tsaya mana,"
dakyar ta tsaya, hajia salaha ta tashi tace
" yanzu ke laila Kodan abinda yafaru a asbiti ba zaisa ki nutsu ba?"
Laila tace "no ba damuwa mom, ni kinsan haihuwar mafa wani lokacin matsala ce
Yaran sun cika damuwa, so ni ban wani damuba
, am mom kina batamin lokaci, ni nayi nan" 🤣

Tana fadar haka tayi waje
Hajia salaha ta rafka uban tagumi tashiga DANA SANI Akan tarbiyar data bawa laila

** *** **

Yana tafiya Akan titi, yana waya sai murmushi yake, daka ganshi kasan yana cikin walwala
"Please feenah ta, kidaure idan kinje ki hadani da baby naji muryarta nima"

Feenah tace "karka damu mukhtar, insha Allah ina Zuwa zan hadaku," yace

" to shikkenan ki kulamin...." Maganar dabai qarasaba kenan yaga anrufe masa fuska da wani baqin qyalle
Wayarsa tafadi aqasa, daya daga cikin mutanan ne, yadauki wayar yashaqewa mukhtar wuya, yace" kana magana wallahi ina aikaka lahira"

Feenah tun tana hello hello, taji shiru saitace may be babu network ne, Dan haka tasaka Wayarta cikin hand back dinta
Baqar abaya nasaka, nayi rolling da Dan kwalin rigar, sai Jan baki danasa pink, nataje girata nagyarata, nayi kyau sosai acikin rigar, inata zuba qamshi na futo falo, naga husna tana hada break fast, naje nakarba ina kaiwa dining
Tace "bade harkin Gama shiryawa ba," nace
" wallahi inasone naje na dawo da wuri, inaso inje wajan Zahra"
, ina Gama kaiwa dining, naje na gaida ummi na dawo

Munfara break kenan tahir ma yafuto cikin shiri, husna tace " Amma de Yau Babu inda zakaje ko?" Yace "babu inda zanje my heart ina gida tare da iyalina"
Murmushi tasaki
Nace " yaya tahir ina kwana," kallo na yayi cikin ransa yace masha Allah, shi kam yanayiwa ahmad sha'awar yarinyar nan, Amma Babu yanda za'ai, tunda ita ansa Mata rana, shikuma ya liqewa wannan jarababbiyar yarinyar

Cikin sakin fuska ya amsa, nan muka ci Gaba da break, nariga su gamawa, husna tace
" aide kya bari ingama ko, sarkin gaggawa," tahir yace "a a banga laifin taba, barta taje taga yarta," nace "yauwa yaya tahir fada Mata de,shekara guda bangan taba"

Husna tashi tayi, taje ta daukomin sweet dayawa tace "gashinan idan kinje saiki kaimata wannan sweet din, nasan halin baby da mugun San alawa"
Nace "anty husna aike ta biyo"
Tace "wa,? Kema kinsan wata biyo"
Tahir yace "towa ta biyo acikin ku kenan?" Husna tace "wallahi ita ta biyo," dukanmu mukasa daria

Tahir yace "to kinsan gidan ne kokuma Asa driver yakaiki?" Nace " a a bansaniba saide inkira Ammu ince masa ya turo min address din gidan, tunda suncemin uban gidansa ne, kaga ai zaisan gidan ko?"
Husna da tahir suka sa daria baki daya, tahir yace " tunda kin sameni ai kingam samun address, abokina ne fa, tun muna yara, aminina ne sosai," nace

" to alhmdlh
Rubutamin,"

takarda yasamu yarubutamin, nakarba nayi musu sallama nafice da kayan baby ahannuna

** *** **

"Uncle Yau zaka kaini wajan wasa?"
Ahmad da gabansa yake faduwa tun jiya, yace
" baby banajin dadi, bazan iya kaiki ba, jekice wa mamy tabawa mabaruka abinci na takawomin daki, banasan sauka,"

Tace " to uncle," bayan ankawo masa break dinne ya zauna adaki yanaci, Amma still gabansa yana faduwa, baby tana gefensa, cikin ransa yace tomeke faruwa ne haka?

** *** **

Tana tuqi taji qara shigowar text, ta duba number taga number mukhtar ce, afili tace
" wannan ina tuqi, banaso na kalli waya, idan naje gidan sai naduba," ta ajiye wayar taci Gaba da tuqinta

** *** **

Suna zaune afalo, husna sai sakin tsaki take, tace
" wannan yarinyar ina takai Wayarta ne, sai kira nake naji ko taje lafiya Amma bata dagawa,"

tahir dayake kwance Akan kujera yace" wacce yarinya kenan?"

Tace" FEENAH mana, ta wani bar waya awani waje "

Kansane yasara lokaci
daya dajin wannan sunan, yace" me kika ce?"🙆🏻 Cikin mamaki husna tace" kamarya?"
Yace"sunan nakeso naji,"

tace "feenah nace,"

yace "wai dama haka sunan ta?"

Husna tace "kajika da wani magana wai kana nufin kacemin bakasan sunan da qawaye da

yan'uwa suke Kiran taba? Ai sunanta feenah"

Gabansa yayanke yafadi, taci Gaba da cewa " idan kace nafeesa aiba kowane yasanta da wannan sunan ba" 🤣

"Dan dakata "

Abinda tahir yace kenan, yadauki wayarsa yakira ahmad
Bugun farko ahmad ya daga, yace tahir yanzu nake shirin kiranka, wallahi tahir gabana faduwa yake tun jiya,tahir cikin ransa yace ai dole,
Amma afili saiyace

" subhanallah to Allah yasa lafiya, nawan dama tambayarka zanyi, nikam Yama sunan budurwar nan taka?"

Ahmad yace "feenah mana,"
tahir yace

" no na gaskya,"

ahmad yace " nafeesa"

, tahir yace "kuma a zaria take ko?"

Ahmad yace "emana,"

"Amma please yaya kammaninta suke?"

Ahmad yace "zaka ganta yar fara, me dimple, yar doguwa kadan, wai meke faruwa ne? Kokuma inturo ma pic dinta?"

Dif tahir yakashe wayar, batare daya bawa ahmad amsaba, yadubi husna yace "Mata, akwai matsala ba yar qarama ba🙆🏻"

** *** **

"Malama kiyi hakuri Akan aikinmu muke dole sai ansanar damasu gidan koke wacece sannan zamu barki kishiga,"

feenah tace "kace musu yayar izdihar ce,"

Baiyi musu ba yashiga gidan, duk yan gidan suna falo Gaba dayansu, dayake weekend ne, ma'aikacin yacewa mamy hakima Hajia kunyi baquwa wai yayar izdihar, mamy da momy kai tsaye sukace suyi sauri su shigo da ita, aikuwa yana komawa, yakarbi jakar hannun feenah, yace "Hajia kawo jakar" 🤣

Babu musu tabashi, gabanta sai faduwa yake
Ta kalli harabar gidan tace cikin ranta masu kudi suna abinda sukai niyya, yanzu anan baby take rayuwa
Mamakinta bai qareba saida suka shigo falon, taga wata sabuwar aljannar duniya, momy tace "sannunki da Zuwa zauna mana, ya hanya?"

feenah ta zauna, nan suka sake sabuwar gaisuwa, mamy hakima tace wa momy Hajia kiduba kiga yanda suke kama da baby, banda shirme irin na ma'aikata aida sunga kamar ma yaci ace sun barta tashigo, ta dubi su mabaruka tace" ku Baku iya gaisuwa bane? "

Nan suka fara gaisheta tana amsawa, mamy tace" bari inkira alhaji yazo ku gaisa,"

tayi sama, momy tasa ma'aikata su kawo Mata abun motsa baki, nan da nan suka cika Mata gabanta da kayan ciye ciye su dangin fruit, daddy ne yasauko feenah tayi sauri tasauka qasa ta gaida shi, daddy sosai yayaba da tarbiyar yarinyar
Itama cikin ranta tana cewa a a wannan sunada mutunci 😃
Momy kaunar yarinyar take har ranta, tace

" baki zuba lemon ba yata, yaya sunan kine?"

, feenah tayi murmushi tace "sunana Nafeesa ," gamida daukar robar ruwa tafara tsiyayawa a glass cup din gabanta

Adaidai wannan lokacin su baby sungama break fast itada Ahmad yariqo hannun ta suna saukowa daga beni, Jin takunsu ne yasa feenah dagowa, aikuwa karaf idonta yahadu dana baby, baby da gudu ta iyo wajan ta tace "yeeeee ga sabuwar anty"
Feenah tatashi da niyyar rungume ta, gabanta yayi mugun faduwa ganin fuskar dabazata taba mantawa ba
Cikin mamaki tace

"Ahmad!!!"

Daskarewa yayi awajan cikin mamaki shima yace

" feenah!!!"

Jin wannan sunan yasa momy tatashi tsaye tace "a a wai feenah ce qawar saudat?"
Ahmad bai kula momy ba yaqaraso wajan ta yace

" feenah kece da gaske ko mafarki nake?"

Murmushin takaici nasaki nace "yanzu ma kayi mamakin ganinako?"

Nan danan kuka ya qwace min
Nace "danasan agidan nan kake wallahi dabanzo ba Ahmad , mayaudari kawai,"

Ahmad yasake matsowa kusa da ita yace "feenah kibari nayi miki bayani"

Tass kakeji ta daukeshi da mari🙆🏻
 tace cikin kuka 😭 "mezanji ahmad? Ka lalata rayuwata, ka zubarmin da mutuncina na ya mace, karshe kaje kayi auren ka, kafadamin meya hadaka da 'yata?"

Cikin mamaki yace "yarki?"

Cikin takaici nace "au baka ganeba kenan shine kake tambayata? To yarka"

Jiri Momy tafara gani, tana daga tsaye, sai luuu tafadi qasa Allah yaso akwai kujera awajan

Feenah kuwa taja hannun baby sukai waje, kotakan kayan data kawo Mata batabi ba 🤣

Ahmad tsugunna wa yayi awajan yana ambaton

" Innalillahi wa inna ilaihir raju'un"

Yayinda sauran yaran sukai kan Momy suna kuka

Mrs Usman ce
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Wannan shafin nakune kyauta, iyalan maman khaleel jama'ar 😍LOVELY FANS😍

53

Daddy ne daya daskare a tsaye, yayi karfin halin cewa adebo masa ruwa, mamy hakima ce tafara kokarin kamata Zata gyara Mata kwanciya, ahmad yatashi zai gyara Mata, cikin fishi daddy yace "karka kuskura"
Mamy hakima cikin kuka tace "haba alhaji, ka barshi mana, Dame zamuji ne?"
Shiru yayi, batare daya tankaba, ganin hakane yasa ahmad yadauke ta cimak, yamaidata kan doguwar kujera, aka kawo ruwa aka yaiyafa mata, ba'a dauki lokaci mai tsawo ba tafarka, Amma banda kuka babu abinda take
Itakam tacire hannun ta a al'amarin ahmad,ace mutum kullum kaine cikin matsala

** *** **

Ina kuka inajan baby muka futo daga gidan, masu gadi sai kallo na suke, sunga nashiga kalau, na futo da kuka, inajin wani yana tambaya "hajia lafiya kuwa?"
Kyaleshi nayi, na fice daga gida
Muna Zuwa wajan mota dayake awaje na barta, baby tafara tirjewa tareda alamun kuka tace

" anty ina zamu? "

Kai tsaye nace Mata
" gida,"

tace" to anty nide ki tsaya uncle "

Nace" baby zaki shiga mutafi kosaina bigeki?"

Tace" nide anty Allah da uncle zan tafi "

Ganin Zata batamin lokaci ne yasa nadauketa nasata agidan baya, sannan nashiga naja motar muka tafi
Ina driving ina goge hawaye

Ashe shiyasa gabana yake ta faduwa, ashe da wannan azzalumin zan hadu shiyasa

Ina parking agidan husna na futo, nacemata "idan kinga dama ki futo, in kuma wajansa zaki koma saiki ja motar kije" 🤣

da sauri ta futo ta riqeni, tace "to anty yaushe zaki mayar dani wajan uncle din?" 🤣

Nace "baby Dan Allah kimin shiru"

Cikin gida kuwa husna tayi tayi yafada Mata wacce matsala yake nufi, yace babu komai, yadauki hannu ya rafka uban tagumi 🙆🏻😳🤣
Shi kansa tausayin kansa yake, bare idan yatuna ahmad, ko yaya zasu qare da feenah? 🤣

Suna wannan halin nashigo falon nida baby ina kuka
Sallama nayi muryata ciki ciki, ina Zuwa nafada jikin husna nasaki wani uban kuka mai ciwo

Tahir kasa magana yayi cikin ransa yace shikkenan tafaru ta qare, 🤣 ruwa yaqarewa Dan kada Dagani har ahmad din Yau babu me wata dabara, kawai inma zagi ne ayi mana, in hakan zaisa a huce

Husna tace "me yake faruwa kika taho da babyn?"
cikin kuka nace  " anty husna shine, wallahi shine azzalumi"
Husna tace "wai menene hakane? Kai kacemin akwai matsala ba yar qarama ba, ita tacemin shine,"

baby ta kalla tace "ke baby me yake faruwa? Me akayi Mata?"

Baby tace "nima bansaniba, nide naga ta mari uncle,"

tahir cikin ransa yace "ai kadan ma kenan, nayi Zatan abin zaifi haka" 🤣

Cikin mamaki husna tace
" mari!"

"Feenah, tahir wai kuyi min bayani mana,"

feenah tace "anty husna ashe mutumin dayaci mutunci na, ya keta min haddi na, shine wanda su Abba suka dauki baby suka bashi"

Husna tace "subhanallah" 🤦🏻‍♀️

Tadubi izdihar tace "baby jeki wajan su mama suna daki kuyi wasa"

Tana tafiya husna tace
" innalillahi, mun shiga uku!" 🙆🏻

Sannan Ta kalli tahir tace

"Tahir!!! "

Tahir yakasa magana, sai can yace "shiyasa nace miki akwai matsala babba, Amma meyasa kika cemin nafeesa batasan baban baby ba?"

Husna tace "haka tace mana ai, gatanan ka tambaye ta" ,

cikin ransa yace wato saboda soyaiyar datake masane yasa takasa tona masa asiri,
afili yace "ai ni yanzu bana buqatar dogon bayani, nasan komai
Itama kuma tasani"

Husna ta dubi feenah tace " hakane?"
Gyada kai nayi kamar kadangaruwa nace
" nasanshi anty husna,"

Husna tasake maida kallanta ga tahir tace "wai kana nufin itace wadda kabani labari kace ahmad yana Santa harma yakasa sauraron kowa saboda ita?" 🤣

Cikin sauri nace "wallahi anty husna karya yake
Mayaudari ne, bayan saida na yarda dashi yaci amanata karshe yaje yayi auren sa" 🤣

Tahir ne yace "am feenah kingane ahmad bashida laifi anan idan kika tsaya kika saurari abinda zai....."

"Ni kadena min maganarsa yaya tahir, wallahi na tsaneshi"

Husna ma tace " to Amma ya ahmad zai Mata haka?"

Tahir yace "kamarya ya zai Mata haka, kin tsaya kinji yayi miki bayani ne?"

Wayar feenah ce ta dauki qara,
New Number tagani, tana dagawa taji ance
" nafeesa"
Cikin nutsuwa ta amsa, yace "mahaifin mukhtar ne,"

cikin ladabi tasake gaida shi, yace "kema sun turo miki saqon ta layin mukhtar dinko?"
Sai alokacin tatuna da saqon da mukhtar ya turo mata, tace " baba, naga anturo de, Amma ban budeba,"

muryarsa na rawa yace
" kayya sun saceshi nafeesa, abinda suka fada kenan, wai bazasu sake Shiba har sai yace

yabarki "
Wani ihun kukan naqara sakawa, bansan yaushe baba yakashe wayarba

. Nace "na shiga uku na, wannan wacce irin masifa ce ne?"
Husna da tahir ne suka hada baki wajan fadin "menene?"
Nace "ansace shi, wai wasune suka sace mukhtar"

Husna tace "Yau munga ta kanmu
Satar ango kacokam" 🙆

** *** **

"Momy Dan Allah kiyi hakuri, kiyafemin, daddy, mamy kuma kuyi hakuri Dan Allah, banyi hakan da niyya ba, nasan duk abinda zan fada muku bazaku fahinceniba"

Daddy kawai kallansa yake, saida yagama bayaninsa, yace
" kagama? To tunda kasan bazamu fahimta ba karma kasake kayimana maganar"

Ahmad yajuya ya kalli Momy yace "Momy Dan....."

itama cikin sauri ta katse shi, tace "karka cemin komai ahmad nikam na zare hannu na acikin al'amarinka," mamy hakima ita kanta wannan al'amari baiyi Mata dadiba, itada take Dan goyon bayansa, shiyasa itama tayi shiru

Rana zafi inuwa quna, Yama rasa ina zaisa ransa, Dame zaiji? Ita waccan taqi kula shi, suma iyayan nasa sun kasa fahimtar sa

Tashi yayi, zuciyarsa nayi masa zafi, idonsa jajir
Kofar fita ya nufa, yana Zuwa bakin Kofar, yaji kirjinsa ya riqe, yakasa numfashi, cak yaja ya tsaya, daga baya su Momy sukaji qara, suna juyawa su kaga ahmad a kwance shame shame babu alamar numfashi

Gaba dayansu sukai kansa da gudu
Daddy yafi kowa shiga cikin rikici, da sauri yace

"adauko mota,"
nan da nan suka tafi asbiti
Kai tsaye asbitin tahir sukaje
, gashi bayanan, Dan haka mamy hakima takirashi awaya tace yazo asbitin sa yanzu ahmad ba lafiya
Cikin sauri yafuto, husna tace "ina zakaje?"

Yace "ahmad ne wai bashida lafiya, kuma nasan hakan baya rasa nasaba da wannan rikicin Zanje asbitin yanzu, ki kula da nafeesa"

Nikuwa ina daki ina kuka, ina hada kayana, husna tashigo tace "mekikeyi hakan?"

Nace "gida zan tafi anty husna, duk Garin yaficemin akai,"
Husna ta rungume ni itama, tana share qwallah, tace " kiyi hakuri, insha Allah, Allah zai bayyanashi kinji, kiyi hakuri"

Nace "to sister"

Tace " shima tahir din yatafi asbiti yanzu wai ahmad din bashida lafiya,"
yatsina fuskata nayi, nace "shiya jiyo"

Ina Gama hada kayana, nacewa anty husna na tafi, gara inje in sanar da Abba abinda yake faruwa dangane da mukhtar, ita kuwa baby daga Yau tadena zama agidan wannan mayaudarin Babu yanda ta iya Dani, dole ta rabu Dani na tafi, baby tana dayan seat din, ina driving mukadau hanyar zaria, munyi nisa ahanya Zahra ta kirani tace " feenah Amma kin fasa Zuwa ko?"
Nace "Zahra ainakoma zaria ma," tace

" subhanallah Allah yasa lafiya," nace "lafiya Amma ba kalau ba, Zahra naje ganin baby Wai ashe ahmad aka bawa baby bansaniba,"

Zahra cikin firgici tace

" wai wanne Ahmad" 🤣

nace "ahmad de nawa"
Zahra tace "innalillahi to tayaya?" Nace "ina nasani Zahra, nikam wallahi nadauko yata nabar musu gidansu,"

Zahra tace "matsala!"
Nace "ina kikaji matsala Zahra, wai ansace mukhtar, dazu dazu babansa yakirani yake fadamin," Zahra tace
" munshiga uku, wata sabuwa," nace "Zahra bana cikin nutsuwa ta yanzu, mayi waya daga baya,"
wayar na ajiye muka ci Gaba da tafiya

** *** **

Yana Gama dubashi yafuto daga Dakin din, yasamu su Momy awaje a tsaye, yace "Momy ku qaraso daga ciki,"
Babu musu dukansu suka shiga office dinsa
Tahir yace "daddy saide kuyi hakuri, Amma ahmad ayanxu kulawar ku yake buqata, yana gab da kamuwa da ciwon zuciya, kuma kunsan hakan, Amma bakwa kiyaye damuwar sa
To maganar gaskya, abin nasa yayi girma dayawa, yakamata a kiyaye abinda zai dinga bata masa rai"
Daddy yace "Amma tahir kasan abinda yaron nan kuwa ya aikata? Zinafa tahir
Ina hankalinsa yake? Har menene zai debeshi yaje ya aikata wannan mummunan aikin,?"

Tahir ya nunfasa yace
" hakane daddy, Amma kuma bakusan menene abinda yasa yaje ya aikata hakanba
Ninasan ahmad, kuma nasan abinda ku Baku saniba nasa
Abinda yake faruwa shine ahmad yanada zurfin ciki, bai futo lokaci daya yayi muku bayani ba, Amma nasan yayi muku bayani Akan maganin da laila tasa masa
To daddy laila bawai tamasa illah bane wajan hanashi haihuwa ba, a a, asanadin wannan maganin dayasha ne yasa yaje yayi raping wannan yarinyar, alokacin shida ita suna soyaiya

Wannan dalilin ne yasa kai tsaye ya yiwa laila saki uku,
Alokacin da abin yafaru ninaje nataho dashi daga asbiti, wanda anan aka tabbatar da qwayar dayasha ne yasa shi aikata haka
Damuka zo gida duk kunyi bacci, auta ce kawai bata kwanta ba, kuma wannan yarinyar itama shaida ce Akan halin dataga ahmad aciki

Haba Momy, daddy, mamy ku yiwa zancena kallan fahimta, anan ina ahmad yake da laifi? Laifinsa daya yaci amanar soyaiyar dasuke da wannan yarinyar, shima kuma idan ya nemi yafiyarta Zata yafe masa,

Maganar yarinyar nan baby kuma, ni kaina danake auran yayar ita nafeesa wallahi bansan yarinyar nan yar ahmad bace, saida suka fadamin dazu

Ita kanta nafeesa batasan agidan su ahmad aka bayar da yarinyar ba, "

Momy taja numfashi dajin wannan zance kamar almara
Tace" eh naji tace datasan agidan yakema da bata zoba
Haba nifa ince, wannan yarinya tunda tazo gidan nan kowa yadauki son duniya ya dora Mata, ashe jinin muce
, Amma yanzu tahir ace wannan babban al'amari yafaru ahmad yakasa Bude baki yayi mana bayani,
Yanzu ba Dan Allah yakawo wannan yarinyar ba, munsan gaskya, aida anyi batacciya, domin kuwa kullum Muslim bashi da aiki sai cewa yake yana San baby"🤣

Tahir yayi murmushi yace

" Momy soyaiyar jini ce kawai"
Mamy hakima tace "kace munkusa kashe danmu batare da munsan gaskiyar magana ba"

Daddy yace "to Allah yarufa asiri," Gaba dayansu sukace " amin"

"Yanzu abinda za'ai, tahir kayi mana jagora gobe muje gidan iyayan ita yarinyar nan mu basu hakuri kuma mu nemi yafiyarta"
Tahir yace "to daddy babu damuwa, yanzu ma zaku iya tafiya insha Allah zan kula da ahmad din"

Saida suka koma suka sake duba jikin ahmad din, daddy ne harda tattaba fuskar sa, aikuwa nan take yafarka, yana dora ido Akan daddy yace, "daddy Dan Allah kayi hakuri"
Daddy yace "karka damu my son, tahir yayi mana bayani, Amma karka sake boye mana komai nan Gaba kaji, Allah ya yafe mana baki daya," Momy tace "Allah yasawaqe mu zamu tafi, tahir yace zai kula dakai,"

yana murmushi yace "to Momy Nagode," mamy hakima ma saida tashafa kansa tayi masa addu'ah sannan suka tafi

Suna fita ahmad ya cewa tahir "kai meka fadawa mutanan nan kuwa? Naga kowa sai nan nan yake Dani,"

tahir yace "ai abinne saida siyasa, cewa nayi ciwon zuciya ne yake gab da kamaka, kana matakin karshe, ingayama nan da nan suka rikice," 🤣

ahmad yasaki daria yace
" kai Amma kai dinnan bakada dama wallahi"

Tahir yace "wallahi saina koma nafada musu gaskya,"

ahmad yace "haba abokina yi hakuri mana,"

tahir yace "har labarin abinda yahadaku da feenah nafada musu, kuma alhmdlh sun fahinceka,"
ahmad yace " babu abinda zance ma tahir saide godia,"
Tahir yace "karka wani damu, ai yiwa kaine, danna yiwa qanina abinda yadace" 🤣 🤣

Ahmad yace "yauwa wai meyasa ka kirani ne dazu kake min tambayoyi Akan feenah"
Anan tahir yabashi labarin komai
Yaci gaba da cewa "yanzu saide muje gidan kabata hakuri"

Ahmad yace "wa? Ni?😳 Wallahi ni tsoron tama nakeji"

Tahir ya kwashe da daria yace "ah haba kamar ba ahmad din dana saniba?"
Ahmad yace "wallahi tsoron ta nakeji, idan tahuce Zuwa gobe naje  nabata hakuri"

Tahir yace "aikuwa su daddy ma sunce zasuje subawa iyayan ta hakuri,"

ahmad yace "shikkenan ma saina bisu nima
Amma yanzu kam

Inaaa wallahi bazan iya Zuwa wajanta ba, yanda naga lokaci daya ta rikide dinnan Takoma wata daban kamar ba my feenah taba"

Tahir yace "ai tunda naji baby tana cewa anty ta mari uncle araina nace ai abinma da sauqi" 🤣

Ahmad yace " infadama ban zataba wallahi kawai naji tasss
Kaga kuwa yanzu idan naje ai saide duka"
Gaba dayansu suka sa daria

** *** **

Ina parking gida nashigo ina kuka, ko motar ban rufe ba, baby ce a bayana tana janyo jakarmu daqyar 🤣
Abba dayake alwala atsakar gida yace
" subhanallah, uwata me yake faruwa haka?"

Ina kuka nace "Abba babu ansace mukhtar
Wai bazasu sake shiba saina rabu dashi
Shikkenan Abba so suke su rabani da mukhtar"

Kamani Abba yayi muka shiga falo, mama tana tambayar abinda yake faruwa

"Abba zoka dau jakar nikam bazan iyaba nakasa" 🤣 🤣

Sukaji muryar baby tana wannan maganar

Abba yace "a a ita kuma wannan daga ina haka?" 🤔
Kukanane yaqaru nakasa yin magana

Baby tace "mama kinga ko anty ce ta wanke uncle da mari, kuma tace masa yaci Amana,
Wai nima yarsa ce" 🤣

Mama ce ta rafka uban salati

Abba yace "innalillahi, uwata kina nufin ahmad...."
Tun kafin Abba ya qarasa cikin kuka nace "hakane, shine Abba"

Nan da nan Abba yacire hularsa yafara firfita da ita

Mrs Usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

54

"Mama zoki janyomin wannan babyn acikin jaka" 🤣

Mama ta kalli izdihar ita ko ajikinta ma, ta abin wasanta take
Dauko Mata tayi, tana karba tayi Dakin mama da gudu
Abba yadubi feenah yace "tashi kishiga ciki"
Ina goge hawayen idona nayi ciki, Abu yahadu yazamemin goma da ashirin, ga haduwa ta da ahmad ga batan mukhtar
Harara na zubawa bangon dakin kai kace ahmad dinne awajan, nace sai wani qiba ma daya qara dakyau kamar bai zalinci yar mutane ba 🤣

Kaina ne yasara, alamun ciwo, Dan haka kawai na kwanta tare da rufe idona

Mama ta janye ta gumin datayi ta dubi Abba tace "alhaji kayi shiru"
Abba yace "Tome zance maman nafeesa, ban taba tunanin yaron nan zai iya aikata wannan abun ba, abin baqin cikinma yanda yazo yashige mana, muka yarda dashi kamar dan'uwa, nine mai cewa ko bayan raina ban yarda akarbi baby daga hannun sa ba, ashe shinema uban yarinyar "🤣

Mama tace" to taya kuwa za'a ce zai aikata alhaji, yaronda saboda tsananin kunya bayama yarda kahada ido dashi
Har garama tahir zai zauna ayi fira dashi, Amma shifa wannan gim yake zaune, bazakace zai aikata wani Abu naqi ba"

Abba yace "ai shikkenan, bamu ya yiwa ba, kansa ya yiwa,"
mama tace "hakane, Amma nikam banda nafeesan tafada da bakinta babu wanda zai fadamin wannan maganar na yarda, wannan yaro bai kyauta mana ba"
Abba yace "jeki ga halinda ita nafeesan take ciki"

Tana Zuwa Dakin taga nayi bacci tajuya, nikuwa batasan idona biyu ba, a wannan halin wanne bacci zan iya

Abba ne yakira Ammu yace "hassan idan kasamu dama kazo gobe da safe inasan magana dakai,"
Babu musu Ammu yace
" insha Allah zai shigo"

** *** **

"Yanzu de damuwa da kuka da tunani duk sun qare tunda kaga feenah"

Ahmad yace "wallahi tahir kalau nake jina yanzu, banajin ciwon komai, kai farin ciki ma nake ciki, Tsawon shekarun dana dauka ina nemanta Yau naganta, tazo har gida tasameni"

Tahir yace " kawai dande haka Ubangiji yatsara ne, Amma ai haduwa kam kun kusa haduwa"
Ahmad yace " kamarya?"
Tahir yace " wai kasan anan asbitin ta haifi baby?"
Cikin mamaki ahmad yace "bangane ba"
Tahir yace "tonima alokacin bansan taba, Dan ko ita husnan banma hadu da itaba alokacin Da'aka kawo ta batada jini, ga kuma haihuwar tazo kusa,kuma anrasa irin jinin ta, in bazaka manta ba, kaine kace adebi naka abata, batare dakai koni munsan itace feenah ba, ni bansan taba, kai kuma bakaje wajanta Bama bare kaganta"
Ahmad yace "wai kana nufin feenah nabawa jini na tahir?
Ashe alokacin aka haifi baby na
Ashe nima na temaka wajan zuwanta duniya"

Tahir yace "abin de kamar almara
Itace fa wadda nake cema nayima budurwa qanwar matata
Kacimin mutunci Akan feenah, ashe ma itance"
Ahmad yace "to aide kaganta, yarinyar tayi tahir, zan iya yin komai saboda ita, har Yau nakasa manta yanayin danajini aciki, lokacin da wannan abin yafaru, yarinyar tanada...."

Gyaran murya tahir yayi yace "wai koka manta qanwata ce ne? Kaini fa yayanka ne yanzu, yaya tahir yakamata kace"

"Allah ko yayan zamani," inji ahmad
Tahir yace "kacika baki, wallahi tsaf zanje in zigata," ahmad yace "haba nawan kaifa na hannun dama nane"

** *** **

Kaina ko dankwali babu sai qananun kalba, mama nasamu afalo ita kadai tayi shiru, kai tsaye cinyarta nadora kaina, mama tace " kai nikam dagake har baby ne zaku qarasani" 🤣
Murmushi nayi nace "kai mama, dande mu biyun"
Wayata na janyo na duba text din da aka turomin ta layin mukhtar

"bazamu sake Shiba har sai kinyi alqawarin zaki rabu dashi, shima yayi wannan alqawarin "

Mama na nunawa tace "Allah yarufa asiri," nace "mama bari nakira naji,"
Ina kira nasa wayar a handsfree
Nace "Dan Allah kuyi hakuri ku sakeshi,"

"Wacece kedin?"
Nace " ni kuka turowa text Akan in rabu dashi
Naji zan rabu dashi, Amma Dan Allah karku taba lafiyarsa, Dan Allah ku rabu dashi, banaso komai yasame shi"

Qit aka kashe wayar batare da ancemin komai ba
Mama na kallah da mamaki tace "wannan yaro ko a wanne Hali yake ciki, nasan iyayansa hankalinsu ba a kwance yake ba"
Nace "hakane mama, Allah yasa suyi hakuri su sake shi," tace "amin"

Batamin zancan ahmad ba, nima banyi mataba

** *** **

Next day, maqota da yan'uwa ne suka cika gidan kowa yana fadar albarkacin bakinsa Akan dawowar mukhtar
Wasu gulma ce take kawo su, wasu kuma jaje
Iyayansa sunfi kowa murna da dawowar dansu lafiya batare da komai ya sameshi ba

Saida suka kebe da iyayansa ne baba yake tambayarsa babu de abinda suka masa ko? Yace babu komai
Ko zaginsa basuyi ba, kawai sude fatansu na rabu da ita, baba yace ikon Allah to ai Allah yafisu
Inna ce tace nikam Malam yaron nan daya hakura da al'amarin nan, tunda Abu yafara Zuwa da matsala

Baba yace "a a haba de zainabu
Yaza'ai mu zama qananan mutane a idan iyayen yarinyar
Bayan kuma suma kansu yaran sunason junan su"

Tace "Toshiknn, Allah yashige mana Gaba"

** *** **

Ina kwance adaki ina waya da mukhtar sai farin ciki nake saboda futowarsa
Nace "wallahi naji dadin yanda ka futo lafiya mukhtar," yace "Allah ne abin godia feenah tah, kinsan yanzu fa baba yahanani fita ko ina
Banda masjid babu inda nake Zuwa, kullum ina gida ina tunanin feenah tah"
Daria nayi nace" wallahi gara haka, tunda ai bazasu zo har gida su daukeka bako, mukhtar abin nan yana dauremin kai, narasa waye yakesan rabani dakai
Basusan cewa duk wani farin ciki na yana tare dakai ba
Fatana da burina shine ka kasance uban 'ya'yana"
Mukhtar yace "me kika ce? Please Dan Allah maimaita"

Kashe wayar nayi ina daria, daga cikin blanket na futo, baby duk ta yaye jikinta anatashan bacci, falo na futo da murna ta nace "mama ansakeshi!"
Turus nayi ganin Ammu da Abba da mama ne afalon, ko yaushe yazo oho

Rissinawa nayi na gaida shi, yace "nafeesa kiyi hakuri fa Akan abinda yafaru, ni nasan ahmad bawai haka kawai yayi ba, dole nasan akwai sanadi, saboda wannan ba halayyarsa bane"
Nide bance komai ba nakoma daki, mama tace "zonan ina zakije kuma"
Dawowa nayi tace "yaushe aka sakeshi," nace cikin murmushi "yacemin de dazu ne da safe"
Abba yace "to alhmdlh, bari nima nakira iyayan nasa"
Ammu yace "eh gaskya kam, Allah yaqara kiyayewa Gaba," cikin murmushi nayi daki na

** *** **

Wandon jeans ne ajikinsa blue, sai baqar Riga body hug, daidai jikinsa
Sai yar sama daya dora kalar jeans din jikinsa mai laushi
Sumarsa tasha gyara
Agogo yasa qirar plaget
Sai zuba qamshi yake

Falo yatafi kai tsaye, yana Zuwa yaga iyayansa suna break
Har qasa yagaida su, mamy hakima tace "yajikin Naka?"
Daddy ne yabata amsa da fadin " kya tambaye shi jiki, mutumin dayayi irin wannan wankan" 🤣

Kansa ya sunkuyar yana Sosa qeya, yace "mamy jiki yayi sauqi"

Tace "alhmdlh ga break fa"
Tasowa yayi, yana zama qannansa suka fara gaida shi, auta ce tajefo masa tambaya
"Yaya yaushe baby Zata dawo?"
Mabruka ce ta doketa
Momy tace "a a Mabruka kya daketa?
Dan tayi tambaya? Ai yanada kyau taji, 😃"

Ahmad ne yahade ransa, ya kalli Mabruka yace "idan kika sake dukanta saina tsinka miki mari"

Momy tace "daga tambaya sai duka? A wanne dalili?"

Shiru kawai yayi, yaga alama Momy so take ta dora masa laifin komai
Maryam yaja, yamaidata cinyarsa yace "kiyi hakuri Zata dawo, kinji?"
Hawayen ta ta share tace "to yaya"

Sun Gama kenan tahir yayi sallama yashigo, yasa yadi fari mai kyau, Amma baisa babbar rigaba, yayi kyau sosai
Yana gaidasu Momy da da daddy, dukansu sukai haramar tafiya

Har sunzo shiga mota, ahmad yace "tahir kawo key din saina kaimu"
Daddy da haushi yacika shi, yace "kakai suwa? 😳

Saide kakai wasu, Amma mukam bazaka bimu da wannan shigar ba, haba kullum mutum cikin qananun kaya," yadubi tahir yace "ka dinga yimasa fada, tunda naga kai ka fishi Dan hankali"

Sunkuyar da kansa yayi yace "daddy "ma'alesh" (kayi hakuri)

Juyawa yayi cikin sauri yaje yasauya kaya, shima farin yadin yasa, tahir sai daria yake masa, mota biyu sukayi suka tafi

Suna Zuwa zaria guards suka Bude musu mota

Tahir ne yakira Abba awaya yace sunyi baqi
, ahmad kuwa kasa futowa yayi daga motar
Daddy ya kalleshi yace tunda mu mukai laifin aimune yakamata mu futo

Sai a sannan yafuto, Gaba daya jikinsa yayi sanyi, yarasa tayaya zai fuskanci wadannan bayin Allah
Haka de yafuto kansa asunkuye
Su Momy kai tsaye cikin gidan suka shiga

da Abba suka hadu suka gaisa ba yabo ba fallasa
Kofar gidan ya qarasa ya yiwa su daddy iso

Abba cikin mamaki yace "haba alhaji, harda kai ake tafe ashe,"

daddy yace "ah babu komai wallahi, ai takamane"

Dukansu Abba yace ku shigo mana, su Momy suna Zuwa suka zauna afalon, nan su Abba da daddy ma suka shigo falon
Gaba dayansu, ahmad da tahir ne aqarshe

Mama tace "nafeesa tashi kikawo musu ruwa mana,"
Dan kwalina nafara lalube
Ina dagowa karaf muka hada ido dashi
Da sauri na janye idona

Cikin ransa yace masha Allah gashin ta de yana Nan da yawanshi
Da kallo yabita kamar zai hadiyeta
Saida tahir yalura, ya mintsineshi, sannan yadawo hayyacinsa 🤣
Kallansa yakai kan Momy, ta balla masa harara

Shi kam Yau yaga ta kansa
Abba ne yace "tahir ku zauna mana"

Kansu aqasa kamar munafukai, suka shigo aqasa suka zauna

Ina kawo ruwan da lemuka, nafara zuba musu

, su kuwa ko kallansu banyi ba, mama ce ta harare ni, afakaice
Aikuwa na matsa nakai musu
Idonsa kyar akaina
Kamar bazan Bude bakiba nace "yaya tahir gashi"
Tahir yace   " yauwa autar mu, mun gode"

Shikuwa Dan qaramin bakinta yake kallah yanda take budeshi kamar bataso

Baby ce ta futo daga daki, tana kallan mutane afalon ta tafi da gudu wajan daddy
Tace "ga daddy"
Daddy yace "izdihar, ashe kina ciki,"
saikuma Takoma wajan su Momy, tana ganin ahmad kuma sai Takoma wajansa da gudu
Saita bawa yan falon daria
Tace "yauwa uncle, ashe kazo tafiya Dani

Anty to kema debo kayanki saimu tafi Gaba daya" 🤣

Nikam ko inda suke ban kallah ba

Daddy ne yayi gyaran murya, anan aka sake sabuwar gaisuwa
Daddy ya dubi Abba yace "alhaji munzo ne Akan abinda yafaru tsakanin yaran nan, Dan Allah Dan annabi kayi hakuri
Kuyafewa yaron nan
Dan Allah alhaji," saukowa daddy yayi yadawo qasa, Abba Da sauri yatashi ya tareshi yace "haba alhaji
Ni danasan zaka zo da kanka ma, dana hanaka wallahi
Babu komai ai Dan Adam baya wuce qaddarar sa"

Daddy yace "hakane
Tahir kayi musu bayanin abinda yake faruwa, kamar yanda muma kayi mana bayani"

Aikuwa tahir tiryan tiryan yabada labarin komai

Abba yace "babu komai, adade nayiwa zancan mummunar fahimta, Amma ayanxu dana gane komai, to alhmdlh nikam komai ya wuce awajena, wallahi har cikin raina, nida mahaifiyar wannan yarinya, mun yafe masa"

Cikin sanyin murya Ahmad yace" Nagode Abba, Allah yasaka da alkhairi"
Abba yace "babu komai ahmad karka damu, Allah yakiyaye Gaba kuma"
Gaba daya falon a kace

" amin"

Abba yace "saide ita, gatanan saika bata hakuri, ku sasanta kanku, tunda Allah yanufa da rabo atsakanin ku, koba komai kudinga gaisawa ma, albarkacin wannan yarinyar Allah yasa mufi karfin zuciyar mu"
Aka sake cewa "amin"

Momy da mamy ma, sun nemi yafiya, kuma anyi musu, anan de aka fahinci Juna

Daddy ne yadubi Abba yace "alhaji ina neman alfarma awajanka, idan bazaka damuba,"

Abba yace " haba alhaji aikafi karfin komai awajena, kasauke mulkin da Allah yadorama kazo nan da kanka saboda abinda yafaru ai kayi komai"

Daddy yace "hakane Nagode sosai, dama inaso ne ka temaka kabawa yarona auren yarka Kaga shikkenan saisu riqe yarsu, batare da kowa yasan halin da ake ciki ba"

Abba ne yace, "wallahi alhaji nafi kowa San wannan al'amari, Kodan izdihar ma, Amma hakan bazai iyuba"

Gaba daya falon akai shiru dajin furucin daddy
Musanman ahmad

Abba yace "saboda anriga anyi Mata miji, yanzu haka saura wata daya da yan kwanaki yarage bikinta"

Kansa ne yaji yasara
Idonsa yakada yayi jajir lokaci daya

Daddy yace "Toshiknn alhaji, ai duk daya, dama haka Allah yatsara"

Mama ce ta cewa su Momy, "hajia ku shigo daga ciki"
Babu musu suka bita, baby ma tabisu

Daddy ma fita sukai tare dasu tahir,

Wajan yarage dagashi sai ita

Mrs Usman ce ✍️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

55

shiru ne yabiyo baya, kanta asunkuye takasa dagowa ma bare ta kalleshi, ada kam yanda zuciyar ta take yi Mata zafi, gani take Zata iya yimasa rashin mutunci
Saide gashi kuma gata gashi, Amma kuma tama kasa dagowa bare ta kalleshi

Shine yayi karfin halin tashi daga inda yake ahankli, cikin nutsuwa yaqarasa dab da ita ya

zauna, duk da yana tsoron yimata magana saboda baisan mai Zata maida masaba, Amma kuma wani bangare na zuciyarsa yana qara qarfafa masa gwiwa

Cikin muryarsa mai dadi da sanyi, yace
 "My feenah"

Har cikin qwaqwalwarta taji sunan, meyasa takeji ahmad yafi kowa iya fadar sunan ta? Meyasa duk lokacin daya ambaci sunan ta take jinta cikin wani yanayi na daban?

Karfin halin dagowa nayi nace, "meyasa zaka fadamin wannan sunan? Alaqar datake tsakanin mu ai ina tunanin tariga data qare
Nasan maganar yafiya ce, zakamin, tona yafema
Shikkenan zaka iya tafiya"

Kansa ya sunkuyar, Yama rasa maizai fada Mata, tsareta yayi da idanunsa dasuke sumar da ma'abocin qaunarsa musanman feenah
Furzar da iska yayi,yace
" Nagode da yafiyarki agareni, duk nasan cewa abune mai wahala hakan, Amma bayanin da tahir yayi muku nasan zai gamsar dake, ni tunda nake babu mutumin dana taba zalinta saide cikin rashin sani, bare kuma abar danafi Santa fiye da kowa aduniya, bayan iyayena, "
Kallansa nayi nace" ok inka Gama nizan shiga ciki "

Miqewa nayi da nufin tafiya, caraf naji ya riqe hannu na, yace "meyasa feenah?
Meyasa koda yaushe kikesan ganinmu cikin tashin hankali ?"

Shima tasowa yayi yaci gaba da fadin

"Yanzu shi wannan lusarin ya zaki dashi? Dan nikam ban taba sawa araina zan rasaki ba, kuma bazan fara yanzu ba,"

Takaici yacikani, wai mukhtar ne lusari
Fizge hannu na nafara, Amma riqon dayamin yasa nakasa qwacewa, kallansa nayi cikin ido, nace "karka sake aibatamin abinda nakeso
, koma abinda yafi lusari ne naji inasan abina, ina qaunarsa haka"
Wani zafi ne yaji ya ziyarci zuciyarsa, kansa ya sunkuyar
Yana dagowa taga idonsa yayi jajir, ita kanta saida ta tsorata
Kallanta yayi babu alamar wasa atare dashi, yace "karki qara cewa kinason wani a gabana
Inba haka ba wallahi zaki gane kurenki"

Kuka ne ya kufcemin, cikin shagwaba nace

 "nafadadin, nima cikani, kuma koda babu mukhtar babu abinda zanyi kai"
Cikin tsawa yace "nace karki sake ambatarsa a gabana ko!!"

Gyaran murya sukaji akansu, atare suka juya, tahir ya kallesu yace

" daddy yace kafuto mutafi," sannan yamaida kallansa ga feenah yace
" auta, ki turo su Momy, kice su futo mutafi"
Sai a sannan ahmad yacikata
Yana sakinta tashige ciki da kuka

Atare suka futo da tahir, kirjinsa banda zafi babu abinda yake, tahir ya fuskanci halinda yake ciki, Dan haka kawai ya bubbuga kafadarsa suka qarasa wajan daddy
Suna Zuwa yashige baya ya zauna, tahir naganin haka aransa yace Yau kuma saita Allah, 😃 shiyasa shima baiyi masa maganar driving ba
Su Momy sosai sukai sallama da mama, inda mama tace izdihar tana Gama hutawa Zata dawo, Dan tasan kawaici suka Mata, suma suna son tafiya da yarinyar

** *** **

Kuka nake Sosai adaki,
" meyasa sai yanzu ahmad ya baiyana agareni? Meyasa saida na mallakawa wani zuciyata sannan ahmad zai bayyana?
Dole ne inyi maganin wannan matsalar tunma kafin ayimin aure in shiga gidan wani da soyaiyar wani a zuciyata, mukhtar yamin komai, bai qiniba alokacin dayaji dukkanin labari na, wanda a wannan zamanin ba kowanne saurayi ne zaiyimin ba"
Share hawayena nayi, nafita falo, nafara tattare kayan da sukai amfani dashi namaida kitchen
Ina kaiwa nakira mukhtar awaya, mukasha firar soyaiyar mu, duk Dan in manta da abinda yake damuna

** *** **

Su Momy sai firarsu suke a mota, suna tuna shirman baby, mamy tace "nikam hajia banji dadin wannan al'amari ba, wallahi Naso wannan yarinyar ta auri ahmad, sun dace da Juna sosai, Naso kasancewar ta cikin family n MARZUQ"

Momy tayi ajiyar zuciya, tace "wallahi hajia nima haka"
Mamy tace "ko yaya ahmad zaiji?"
Momy tace "Ana can de su tahir ne daganin, bacin rai" 😃

Acan daya motar kuwa, daddy ne suke Dan taba hira da tahir, wasu Akan tituna ne, wasu kuma abinda yadanganci siyasa, shikuma gogan yayi gim kai kace babu halittarsa amotar 🤣

Cikin ransa tunani ne fal, wai bata sansa, mukhtar take so, ko waye wannan gaulan?

Yasan de duk tsiya Babu abinda zai fada masa, Amma kome tagani awajan wani dahar ta iya budar baki tace shi Zata aura?
Tsaki yasaki cikin ransa baisan afili yayi ba
Daddy ya kalleshi
Yadubi tahir yace "tahir akwai tsakane acikin motar nan?"
Saurin kallan daddy yayi, anan ya gane abinda yake tunanin azuciyar sa yayi, afili yayi 😃

** *** **

"Mabruka bawa Momy wayar mana, kude kullum aka kira waya sai wani acikinku yadaga"

Daria tasaki tace "to ai basanan masu gidan, yanzu mune masu gidan" 🤣

Saudat tace "kamarya?"

Mabruka tace "wallahi basa nan sunje zaria dukansu"
Cikin mamaki tace
" lafiya? Me akeyi a zaria?"

Tace" wallahi anty sauda bansaniba, Amma de gidansu anty husna suka tafi, matar yaya tahir, wai wata yayar baby ce tazo ganinta
Shine fa tana Zuwa taga yaya, tana ganinsa ta tashi, nan suka fara fada"

Saudat tace "fada kuma? Tome yahadasu?"

Mabruka tace "harfa marinsa tayi anty, wallahi muna tsaye sai tassss kakeji ta mareshi,🤣 ta qwace baby tace yarta ce, shima kuma yarsa ce,Dan haka bata buqatar sake ganinsa arayuwarta, Dan haka yabata yarta,"

Shikuma fa yaqi Rama Marin kawai sai kira yake
" feenah" 🤣

Saudat tace "keeee mekikace?😳 Wai kina nufin feenah ce tazo gidan?"
Mabruka tace "wallahi hakade naji yace, Amma kuma ta cewa su Momy sunanta Nafeesa"

Saudat dafe kanta tayi da hannunta
Takashe wayar kawai,
Subhanallah, me yake shirin faruwa ne? Me sister da yaya suke boyewa atsakanin su?

Babu wanda yasan wannan amsar tambayar sai yaya da feenah da kuma yan gidan, Dan haka Zata jira su dawo taji kan batu

** *** **

Suna Zuwa gida yafuto daga motar baiwa kowa magana ba yayi ciki,
Su Momy ma sukai part dinsu
Suna Zuwa Mabruka tace "anty saudat takiraki Momy, "

tace "ok kiramin ita"

Rufe idonsa yayi ya zauna a kujera, tahir yashigo gamida rufe kofar Dakin
Shima zama yayi, yace
" kayi hakuri ahmad, ni nasan bazakaji dadin wannan labarin ba, shiyasa tun dadewa nakasa fadama, Amma already nasani
Nasan yanda kake Santa
Kayi hakuri kayi addu'ah idan Allah yayi matarka ce Babu wanda zai hana,
Idan kuma ba matarka..."

"Dan Allah tahir karka qarasa, haba tahir
Yanzu kai har kana tunanin feenah ta auri wanina? Bayan kasan irin dunbin wahalar danasha akanta?"
Hannunsa yasa cikin sumar kansa ya yamutsata, yace "meyasa ni a koda yaushe banda sa'ah ne Akan mace?"

Ajiyar zuciya tahir yayi, yace "kayi hakuri mana, insha Allah matarka ce, shikkenan?
Amma kayi addu'ah, nima zan tayaka, Allah ya tabbatar da abinda yake alkhairi,"

ahmad yace "amin
Wai wayema wannan yaron ne? Dan waye?"

Murmushi tahir yayi, yace "kai mukhtar ma yaga takansa, badan kowa bane, kawai de Allah ne yahada soyaiyar su
Kwanaki ma bawan Allah saceshi akayi akanta, wai saiya rabu da ita 🤣
Suma auren nasu ai sai sunyi taka tsantsan Dan may be akwai abinda yake faruwa wanda mu bamu saniba, Amma inba haka ba satar ango guda? "

Ahmad yace" to ai gara asace shin, "😳🙆🏻‍♀️

tahir yace"ahmad kalau kake kuwa?" 🤣
Ahmad yace  " a a totaya zaisa mutane dayawa cikin tunani Akan shi kadai?"
Tahir yace "a a karka ce haka, kasani wanda yasa asaceshin ko shima Santa yake?" 🤣

Ahmad yadagawa tahir hannu yace "tahir please kadena cewa Ana sonta"

Tahir yace "shikkenan nayi shiru"

Acan falo kuwa saudat tace " gaskya Momy abun kamar almara," Momy tace "wallahi sauda, kede al'amarin sai adduah shine fa mukaje bada hakuri d neman yafiya"
Saudat tace hakane, "bari nakira yaya tahir din ince masa ya turomin Number ita feenah Nasan bazai rasaba," Momy tace "eh hakane kikirashi"

** *** **

After one week
"Zahra wallahi de kinji abinda ya faruwa,"

"to feenah yanzu yana Kiran kine?"
Nace "bai kirani ba Zahra kuma nima bana fatan hakan,"
Zahra tace "hakane kam
Gara zauna lafiya,"

Wayarta ce tayi ringing
Tana dubawa ta daga, tace "hello"
Sauda tace "sis feenah kin kirani Nagode"

Daria nasaki nace " sis kiyafemin Dan Allah"

Saudat tace "a a wlh Babu komai karki damu
Sis feenah naji abinda yake faruwa, nima ina qara baki hakuri Akan abinda yaya yayi miki ni nasan ba laifinsa bane, Amma haka kawai bazai miki komai danya cutar dake ba"

Nace "babu komai Saudat
Ai komai ya wuce, saide Allah yayafe mana,"
Tace " amin"
Nace "ina garinkufa, wallahi Yau na shigo," saudat tace "wayyo sis inama ina kano, me akeyi?" nace "wallahi gani na dawo nida baby, zankaita gidanku, sannan kuma..." Sai tayi shiru
Zahra ce ta qwace wayar tace "saudat Zahra ce sabuwar qawar feenah, wallahi tazo gyara ne na bikinta, kinsan yarage saura sati uku"

Saudat tace" bata wayar," saida sauda tayi Mata tatas, wato da saide aji bikin ko, anan de feenah tabata hakuri, tace kuma zatazo bikin insha Allah, nan sukai sallama,
Zahra tajima sannan tayi musu sallama tatafi gida itama

Washe gari da safe, na shirya, nayiwa baby wanka, nace "to sai muje nakaiki wajan uncle ko? Tunda ni bakya sona," nafadi haka cikin bacin fuska, baby tace " to anty kema ki zauna agidan mana ai zai ishemu"

Banza nayi da ita, yaya tahir ne yafuto zaije wajan aiki, yace " wannan bari nakira ahmad yazo yatafi da ita," nace
" wallahi daka hutar Dani yaya tahir"
Wayarsa yadauka yakirashi, aikuwa ahmad yace gashinan Zuwa
Tanaji ance ahmad zaizo tashige daki
Tahir bai Dade da fita ba, ahmad yashigo, husna tana falo itada yara, suka gaisa, baby ta rungume shi, tafara qwalawa feenah kira
"Anty! Anty!! Anty!!"
Da gudu feenah ta futo, tayi zatan wani abinne yafaru da ita, tana Zuwa tayi turus, ganinta tare da ahmad
Juyawa zatayi, husna taja yaran sukai daki tace "ki tsaya ku gaisa mana, ko baki ganshi ba?"
Tsaya wa nayi, batare dana ce masa komai ba, shima ido ya zubamin yayi kyau sosai cikin baqin wando farar Riga, sai yar sama kalar ruwan toka, takowa yake wajena ina matsawa, dahaka har mukaje bangon falon

** *** **

Suna wullar dashi a kofar gidan sukaja motar suka tafi

Dagudu baba yafuto daga gidansa binjimar sa sai tashi take, dakyar aka kama mukhtar da jikinsa yayi jina jina saboda duka

Bayan komai yalafa yana kwance atsakar gida, inna tana masa firfita, baba yace "wato mukhtar abinda nake tunani shine kawai karabu da yarinyar nan"
Dasauri mukhtar ya kalleshi

Mrs Usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

56

"Amma baba ina sonta, ina kaunar zama da ita, Dan Allah baba karka rabani da nafeesa wallahi inasan ta, munyi alqawarin aure nida ita"

Baba da inna suka zubawa mukhtar ido suna kallanshi, wato shi duk wannan dukan da aka masa bai isheshi ba, ahaka yake maganar kar arabasu
Baba cikin ransa yace mukhtar ba a hayyacinsa yake ba,🤣 Dan haka yace masa "Toshiknn, bazan rabaku ba"
Mukhtar yasaki murmushi kamar babu abinda yake masa ciwo, yace "Nagode baba"

** *** **

"Yanzu de alhaji abinda yakawo ni kenan, hajiya salaha taje har gida ta roqeni Akan muzo itada wannan yarinyar, yayi maganar yana kallan lailah
Tace muzo mutaru mu baka hakuri"

Alhaji bukar yace "alhaji musa dande sunje wajanka ne, Amma da tsakanina da wannan matar saide alahira
Gaba daya alhaji musa ta lalatamin tarbiyar yarinya, ban isa inyi magana Akan haka ba saitace min yarinyar datake guda daya jal awajanmu
Toni idan ta shirya zama Dani saide tatsuke bakinta Akan abinda zan yiwa yata, kar inji kar ingani
Sannan ke lailah, daga Yau nakafa miki doka karki sake naqara ganin qafarki awaje
Bake ba fita, ki zauna agida, idan kuma bahaka ba wallahi hukuncin dazan yanke miki bazai miki dadi ba daga ke har uwar taki, "

hajia salaha dataji jiki tace" babu abinda zai faru ma "
Ta dubi alhaji musa abokinsa tace" Mungo de alhaji "
Alhaji bukar yace"kwa iya tafiya,"
hannun laila taja suka yi ciki, laila sai kumburi take ita ala dole anyanke Mata hukuncin dabai mataba

** *** **

Cikin tsoro da faduwar Gaba nake kallansa nace "Malam miye haka?"

Tsareta yayi da ido, kawai yana murmushi yana kallanta, kokarin kaucewa nake in gudu daki, Dan gaskya ba qaramin kwarjini yamin ba
Ganin zan tafi ne yasa shi saka hannunsa yadafe bangon
Cikin qasa qasa da murya kamar mai rada yace "meyasa bazaki kai baby da kanki ba, saide akirani inzo indauketa?"

Cikin takaici nace " naga yarka ce, ai dole kazo ka dauketa,"

murmushin dabai shirya ba yasaki yace "ashe kin yarda yanzu yata ce, da kuwa kika mareni kika ce nabaki yarki,
My feenahhh
Yakirani tare da Jan sunan,
Yaci gaba da fadin" my feenah ina sanki, meyasa kika tsaneni? "
Cikin fishi nace" ahmad Dan Allah matsa na wuce"

Kallo na yayi da mamaki yace "please maimaita sunan Dan Allah"

Bansan ya akai ba kawai naji hawaye yacika idona, kafin in furta masa komai naji duminsu a kumatuna, shikam gogan naku murmushi yake saki yana kallanta, shi kawai koda ace Zata zageshi ne inde zai kasance tare da ita to Babu komai
Yanzu haka wani mugun dadi yakeji kasancewar sa tare shida ita
Banyi aune ba naji tafin hannunsa mai mutukar taushi Akan fuska ta, zaro idona nayi cikin mamaki, wani qarfi naji yazomin na tureshi nayi ciki da gudu,
Shi kuwa murmushi yasaka, cikin ransa yace matsoraciya kawai,
Kujera ya zauna, yana jiran baby

Feenah kuwa tana shida daki husna taganta tana goge hawaye, Tabe baki husna tayi tace "hakade kika iya, ai sai ki dinga yimasa kuka yaji dadin rainaki"
Kama hannun baby tayi suka fita, saida sukaje kofa baby ta juyo tace anty bye bye saikinzo kema"🤣 ,
Dan haushi ko kulata banyi ba

Suna Zuwa falon, ya karbi baby suka tafi, tanata yiwa husna bye bye

Husna na komawa ciki, ta cewa feenah, "idan kina zama kina masa kuka ya dinga miki abinda yagadama kenan, toma menene abin kuka,?
Abinda yafaru fa ya Riga yafaru, kawai ki manta, shima da yarinyar take wajansa ya manta ya fuskanci abinda yake gabansa bare keda kike shirin shiga gidan wani, kawai kema ki manta da komai, kiyi tunanin rayuwar da zaki gina nan Gaba "
Nace" to anty husna"
Janyoni tayi jikinta tace "yauwa kokefa"
Wayar husna ce tadau qara tana dubawa kuwa taga sunan kalatynmu yafuto baro baro, bayan sun gaisa ne, kala tace a turo Mata nafeesa, yanzu yanzu, to husna tace tare da kashe wayar
Ta juyo ta dubeni tace kala tace kije yanzu, dama already a shirye nake, Dan haka kai tsaye na miqe natafi
Ina Zuwa gidan kuwa, bayan mun gaisa, tabani wasu magunguna hadeda madara tace na shanye
Babu bata lokaci nasha, tace to najirata Zuwa anjima, ganin haka yasa na kwanta afalo nida sultan qanin aysha muna ta kallo,
Danaga tashiga kitchen ne naje da niyyar in karbi abinda zatayi inyi Mata, Amma fur tace bazan yi ba

Dole sai falon na dawo nazauna, bata dauki lokaci mai tsawo ba naganta da naman kaza, taji romo, takawomin tace gashinan incinye duka
Tunanina zanji da dinta kamar farfesun kaza, saide ina fara ci nafara yatsina fuska, kala tace kiyi abinki kigama tas saikin cinye
Ina ci ina kawar da fuska ahaka na cinye, sannan tace tonatafi kar dare yayi tunda ni kadai ce Karfe hudu da rabi natafi gida

** *** **

Suna zaune aharabar gidan Akan mota shida tahir
Tahir ya dubeshi yace
" man narasa dalilin wannan ziyara taka, kazo da safe kazo da yamma gida gidan magidanci,🤣"
ahmad yace "to magidanci zageni Akan banda Mata, nima ai nakusa kwana nawane," tahir yace "to gara de kasamu wata ka aura, komaji dadi,"

Jikin ahmad ne yayi sanyi daya tuna matar dayake mutuqar so wani Zata aura
Can ya cewa tahir "aidama ina Zuwa,"

tahir yace "a a kaide fadi gaskya man"

Suna wannan musun nashi go gidan, ina tafiya ta cikin nutsuwa, kaina aqasa nace "yaya tahir barka da hutawa," yace
" yauwa autarmu"
Shi kuwa mutumin basarwa yayi kamar bai ganta ba, tahir ya kalleshi da mamaki yace "man, ga feenah can fa,"

ahmad ya yatsina fuska yace "naganta ai, to menene?
Bahaushe ma yace So mai sonka"
Tahir ya girgiza kai yana kallansa cike da mamaki,
Wayar tahir aka kira yajuya suna magana shida wata nurse datake tambayarsa wasu magunguna
Yana Gama wayar yajuyo zai nunawa ahmad wani Abu awayar, yace
" ahmad kaga abin.... Wayam yaga wajan ba ahmad ba alamarsa
Yana daga kai yaga ahmad yana bin feenah abaya,🤣 tana dauke kafa yana mayarwa

Sai abinma yabawa tahir daria, lalle ma mutumin nan nizai rainawa hankali, lalle ai zai dawo ne

Yana Zuwa wajanta yakama hand back dinta yariqe saboda ya kirata ya kirata ta share shi,
Da tayi niyyar rabuwa dashi, Amma data tuna da shawarar husna saita dake ta juyo tace "cikamin jaka"
Ahmad yace "muje ciki"

Nace  "babu inda zanje, kabani jakata"
Yace "wallahi idan baki jeba cimak zan dagaki"
Yafada yana gyara hannun rigar sa

da mamaki na kalleshi nace "wa? Ai wannan jikin yafi karfin ka wallahi, na adanashi ne ga mukhtar"
Cikin tsawa yace
" nafeesa!!!!"
gabanane yafadi dajin wannan tsawar tashi, Amma nadake nace "to bani jakata," nafada ina miqa masa hannu na
Yace "zan baki, Amma karki sake kikara kiramin sunan wannan mutumin a gabana"
Nace "mijinane fa
Lokacin dakai Naka auren nahakana ne?Kokuma nayima magana lokacin daka dora a Facebook?"

Da mamaki ya kalleta kenan feenah tana bibiyarsa
Nace  " kaga ahmad kana batawa kanka lokaci ba auren ka zanyi ba, koda ace babu mukhtar babu abinda zanyi da sauran wata "
Cikin bacin rai yace
" Amma ai sauran ki ne, kuma insha Allahu saina aure ki innuna miki kece zakiso sauran watan"

Baki kasan abinda zaka fada, bakasan mai za'a maidamaba, maganar sa Gaba daya tasata Jin kunya
Jakarta ta fizge tayi ciki
Ahmad yakama qugunsa yariqe da hannu biyu, ya furzar da iska mai zafi, afili yace "akwai aiki a gabana" 🤣

**   ***   **

"Alhaji ashe kaine, haba shigo daga ciki mana "

Baba ya kalli Abba yace" a a alhaji basai na shiga ciki ba, magana ce zamuyi guda daya
Alhaji ni inaga maganar auren yaran nan akwai matsala, saboda kwanaki yaron wajena, ansace shi, yanzu haka maganar da nakema, jiya jiya aka kamashi akayi masa Dan iskan duka,
Yanzu haka yana kwance agida rai ahannun Allah, to shine naga idan akai aure kuma menene zai biyo baya?
Alhaji kayi hakuri mukhtar shi kadai ne awajena, kuma bana fatan narasa dana
Dan haka maganar auren nan mude mun janye "

Gumi ne ya wanke ilahirin jikin Abba, yadubi baban mukhtar yace
" Amma alhaji duka duka auren baifi sati biyu da kwana biyar ba,"
baba yace "shiyasa natako da kaina alhaji, ban turo wani ba, kayi hakuri Alhaji kayafe mana"

Yana Gama fadar haka yayi Gaba

Abba yajuya cikin gida salalo salalo
Kamar wanda qwai yafashewa

Mrs Usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

57

Yana shiga cikin gida yanemi waje ya zauna, babbar rigar sa yake kokarin cirewa
Mama ta futo daga daki ta zauna tana cewa "wallahi alhaji wannan hidimar bikin duk taqi qarewa, kullum ragewa ake Amma kamar babu abinda ake ragewa" 🤣

Shide Abba shiru yayi yana jinta, mama ta dubeshi tace "haba alhaji yaka naji ina magana Amma kamar ba dakai nake ba kayi shiru"

Abba yace "wallahi maman nafeesa, al'amarin yarinyar nan yafara dauremin kai,"

cikin mamaki mama tace "wacce yarinya kenan alhaji"
Abba yace "nafeesa, wato halin da ake ciki yanzu gidan iyayen yaron nan sunce sun janye maganar auren nan"

nan da nan mama tafara salati, tace "to alhaji kakira mahaifin yaron mana kuyi magana,"

Abba yace "ai shida kansa nema yazo yasameni da maganar"

Mama ta rafka uban tagumi tace "yanzu abinda mutanan sukai sun kyauta kenan? Saida Abu yazo kusa anriga da ansanar da kowa
Yanzu fisabilillahi yaya sukeso muyi?"

Abba kasa magana yayi, wayarsa ya dauko yakira husna, suna gaisawa Abba yace tabawa nafeesa wayar, ina karbar wayar Abba yace"duk abinda kike kibari kikamo hanya kitaho gida

yanzu,"

gabana ne yafadi nace
" Abba lafiya kuwa?"

Yace "babu komai kawai kiyi abinda nace" , jiki asanyaye nace "to Abba"
Husna ce ta kalleni tace "me yace?"

Nace "Abba ne yace intafi gida yanzu yanzu,"

husna tace "to Allah yasa lafiya,"

nace "amin,"

magani ne a kofi ta meqomin tace "gashi kisha wannan din saiki tafi,"

bata fuska nayi nace
" anty husna Dan Allah kidena duramin wadannan abubuwan haka,"

husna tace "yarinya bakida hankali, wannan din shine gatanki, nafisan mukhtar yakasa gane kedin maman baby ce kokuma yayarta" 🤣

Murmushi nayi nakarba nasha
Ina Gama shanyewa na shiga toilet nayi wanka, cikin sauri na shirya, nayi sallama da ummi sannan na dawo part din husna tarakani har gate sannan tadawo gida nikuma natafi
Ina Zuwa gida nafada jikin mama nace "mama wallahi nagaji,"

cikin sanyin jiki mama tace "ke dagani, kede kullum cikin San jiki"

, kallanta nayi nace
" mama kalau kike kuwa?"
Tace "kalau nake auta ta,"

nace "naga duk jikinki yayi sanyi"

Kafin tabani amsa nace "mama nima tun jia gabana yake ta faduwa, kawai de addu'ah nake Allah yasa lafiya"
Mama tace "ai kin kyauta dama hakan akesan bawa," 🤣

Abba ne yashigo da alama daga masallaci yake
Saukowa nayi kasa na gaida shi, ya amsa tare da neman wajan zama, nima komawa nayi kan kujera nazauna kusa da mama, Abba yace
" mamana dawo nan zamuyi magana"

Ina Saukowa Abba yace "nafeesa duk abinda kikaga yasami bawa toya dauka kaddararsa ce tazo masa haka,
Kuma Allah yayi hakanne domin ya jarraba imaninsa,"

nace "hakane Abba, me yake faruwa ne?"

Abba yace "jiya ne mutanan da suka kama mukhtar kwana ki, jiyama suka kamashi sukayi masa duka harda lahani, to...

Cikin kuka natare Abba nace" na shiga uku, shikkenan Abba sun kashe shiko?"

Abba yace" to ai baki bari na qarasa ba uwa ta, basu kashe yaron ba, kawai de sunji masa ciwuka ne, Dan haka nema mahaifinsa yazo har gida yace sun janye maganar auren ku

Dan haka kema inaso kisawa zuciyarki salama, kidauka hakan shine mafi alkhairi "

Kuka nane ya tsananta nace" Abba wallahi ina sanshi "

Abba yace" shima yaron yana sonki, Babu yanda zasuyi ne shiyasa suka dauki wannan hanyar tun kafin abin yakai ga rasa rayuwar sa,
Kowanne iyaye suna San yayansu nafeesa, ni kaina da akanki abin yake faruwa bazan juri ganinki kullum cikin tashin hankali ba, saboda sude mutanan nan ba'a San kosu wayeba, idan kashe shi sukai ma ba'a San suba
Dan haka keda mukhtar dole zakuyi hakuri
Tashi kitafi "

Daki na shige da gudu ina kuka,
Wayata ce tafara kuka, ina dubawa naga husna ce, cikin kuka nayi Mata bayanin komai, husna tasaki salati tace" yanzu yaya zamuyi da mutanan da muka gaiyata?" Nace

" kede bari sister nide inaga banda sa'ah a abangaren maza "

Husna cikin sanyin jiki tace
"Dan bakisan burin danaci Akan wannan auren bane,"
Bamu Gama magana ba takashe wayar, saboda batasan wanne kalma Zatayi amfani da itaba wajan rarrashin yar'uwar tata, wannan yarinya tana ganin rayuwa 😭🤔

Nikuwa ina daga kwance naturawa saudat da Zahra text Akan cewa anfasa bikina da mukhtar, aikuwa ko minti biyu ba'ayi ba, saudat takirani, tace "me nakeji haka feenah babu dadin ji?"

Nace "wallahi sister abinda yafaru kenan"

tace "Tome yasa?"

Nan nabata labarin komai, tace "wallahi infada miki, dazu fa nake fadawa farouq yadaure yabarni inzo bikin ki, harfa su Momy nafadawa ina nan tafe,"

nace "wallahi kiyi zaman ki anfasa saudat,"
Cikin jimami tace "to kiyi hakuri feenah, Allah yasa hakane yafi alkhaairi"

nace "amin, kinga Zahra ma tana kirana bari in daga,"

nan mukai sallama da ita, ina amsa wayar Zahra tace "sister kiyi hakuri, Allah yasa hakane yafi alkhairi"

nace "amin Zahra,"

tace "kinyi magana da mukhtar dinne?"

Nace "ban kira shi ba," tace "toki kirashi kiji, halin dayake ciki,"

nace

" to Zahra sai anjima "

** *** **

"Oga angama komai, nasa yara sungama abinda ka umarceni,"

murmushi yasaki yace "gaskya ne, haka nakeso, zakaji alert din sauran kudinka,"

"to Oga muna jiranka," sake duban yaron yayi yace "kofisto, yanzu yaya suke ciki itada yaron,"

kofisto yace "ai Oga ayanda mukai bincike ma maganar auren tafasaya, Iyayansa sun janye"

Murmushi kb yasaki yace "zaka iya tafiya kofisto,"

Kofi yana tafiya afili yace
" mukhtar kenan, kaida kana tunanin idan bansamu feenah ba kaima zaka sameta ne? Ai bana neman Abu narasa, idan narasa kuwa dole shima wanda yasamu yarasa, kekuma feenah kinyi biyu Babu, Babu nidin babu mukhtar din, Babu Dan Malam babu Dan gidan Dan siyasa, kinga yanzu saiki auri Dan gidan Dan kasuwa,🤣"

yana qarasa fadar haka, ya bushe da daria

** *** **

After 2 days

Karfe sha biyun dare tana dakinta tana waya da mukhtar, tace
" Mukhtar meyasa ka kashe wayarka, tun shekaran jiya nake faman nemanka," mukhtar da idanunsa yayi jajir yace "feenah tah kiyi hakuri, bansan kalmar dazanyi amfani da itaba wajan neman yafiyarki, Amma inaso kimin adalci ke kanki kinsan cewa ina kaunar ki feenah tah, wallahi ki yarda Dani bansan baba zaizo gidanku Akan wannan mgnr ba, dana hanashi, saboda da farko yacemin inhakura, nace bazan iyaba, saiya nunamin maganar ta wuce, ashe shi bai hakura ba, feenah tah ina son ki, zan iya jure komai komin wahalarsa inde akanki ne, ki yarda Dani, "

Ajiyar zuciya nasauke nace"nayarda dakai mukhtar, kuma kokadan bakayimin komai ba,"

yace "Nagode feenah"

Nace "yanzu shikkenan mun rabu mukhtar? Duk soyaiyar damuka Dade muna ginawa taqare kenan? Wallahi mukhtar bazan yafewa duk mutumin dayamin katanga dakai ba,"

yace "kiyi hakuri feenah tah, dole zamu rabu, tunda iyayen mu sun Riga dasun tsaida magana"

,nan yafara kuka shima kamar ba namiji ba yaci gaba cewa "Amma inaso kisa aranki, nimai kaunar kine har gobe feenah," yana Gama fadar haka yakashe wayar
wani kuka ne yazomin mai ciwo, bansan haka zafin rabuwa yake da masoyi kai tsaye ba sai Yau, hakika mukhtar yamin komai, yasoni alokacin dayaji ni wacece, yatemakeni alokacin dana rasa waye zai temakeni, tabbas mukhtar yacika masoyina, bansan ina kaunar saba sai Yau, haqiqa nayi DANA SANI Karo na biyu Akan soyaiya, kuma bazan yi na uku ba insha Allah

** *** **

Yana kishingide Akan kujerar office dinsa, sai juyi yake yana aikin rarrashin matar tasa, dataqi sakin jikinta tadawo normal kamar da, duk saboda abinda yafaru d yar'uwar ta, gaskya zai jima baiga yan'uwa wadanda suke kaunar junan su ba kamar husna da feenah

Yace "kiyi hakuri kinji baby nah, nasan itama autar yanzu ta kwantar da hankalin ta ai"

husna tace "Amma doctor naci buri dayawa Akan wannan auren nata, meyasa Iyayansa zasuyi mana haka?"
Tahir yace "shine abinda nake so kigane, haka kaddararta tazo,

Dole hakuri zamuyi dukanmu"

Turo kofar office din yayi ahankli yashigo, yayi kyau cikin qananan kaya, baqar Riga, baqin wando, yadora rigar yar sama fara, hula fara, sai farin kombos, yayi masifar kyau Sosai
Waje yanema ya zauna, yana jiran tahir yagama wayar,
Shikuwa tahir sai qara kashe murya yake da niyya yana fadin "to baby tunda bazaki hakura ba, kawai zanzo gidan yanzu na lallashi babyna" 🤣

Tsaki yasaki yana daga gefe yace " Malam kaji Dani Dan Allah"

Tahir ya mannawa matarsa kiss ta wayar tare dayi Mata sallama
ya kalli ahmad yace

" kaga saurayi mijin yanmata, wannan wankanfa? Da alama sai zaria"
Ahmad yace " tahir banasan wasa naga alama kai kuma wasa kakeji, ni nasan ba kyau neman aure Akan aure, haramun ne ko a muslinci, Dan haka bazan yi ba, Amma inaso kasani inda ace hakan yanada kyau da tuni na qwace feenah ahannun wannan yaron"

Tahir yasaki murmushi yace "ah ah, kaga na feenah
To ai yanzu ma lokaci bai quremaba,"

cikin mamaki ahmad yace "me kake nufi tahir?"
Cikin jimami tahir yace
" wallahi iyayen mukhtar sunce sun janye maganar auren nan, saboda matsalar nan de ta kwanaki itace tasake faruwa
Kaima kuma....."

Kafin tahir yagama magana, yaji ahmad yakai masa wani wawan rungume cikin ihun murna yace
" yes! yes!! "

Saikuma yasaki tahir ya tsugunna yayi sujud shukr, yana"Allah Nagode ma, alhmdlh gobe gobe azaria zan wuni" 🤣

Tahir daya zama Dan kallo yace "ahmad wannan auran bazai iyuba, bazan baka qanwata ba kaje ka kashe ta, Dan yanda kake wannan rawar kan naga alama ba sauqi" 🤣

Ahmad yace "yaya tahir, yaya tahir nawa"

Cikin murmushi tahir yace " bawani yaya tahir"

Wayarsa ya dauko daga aljihun sa, yana ta faman sakin murmushi

Wajan massage yashiga, nan yafara tura Mata da saqo

"ina miki jaje "

Abinda yafara tura Mata kenan

Saiya sake tura Mata

" ina tayaki murnar dawowar tsohon boyfriend dinki kuma baban yarki gareki "

Mrs Usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

58

(afwan afwan afwan fan's, 🙏🏼🙈banda bakin magana saide in rufe ido saboda kunyarku, Amma ina muku albishir da insha Allah zaku dinga jina kullum kamar da insha Allah, ni kaina inaso nagama nahuta, ga fire na siyan baki🌹🌹😃)

** *** **

Ina zaune afalo ni kadai, abin duniya yataru yamin yawa, kamar wata yar tsana Asa ranar bikina afasa, Kodan kowanne bawa ai baya wuce qaddararsa, dole indauki qaddara ta mai kyau ko akasin haka, qaran text naji yashigo min wayata, ina dubawa naga new Num. Tattara hankali na nayi waje daya, na Bude text din
"ina miki jaje "
Abinda nagani kenan, qaran wani text din nasake ji, bayan na karanta na duba number, number da bazan taba mantawa da itaba arayuwata
Fita nayi daga wajan massage din, ina sakin wani matsiyacin tsaki
Mama data futo daga falo ta kalleni, tasake kallona, ta girgiza kai gamida fadin Allah yabaki lafiya, 🤣inba haka ba mutum yayi ta tsaki shi kadai
Kallanta nayi cikin raina nace mama kenan bazaki ganeba
Nima daki nakoma nazauna agefen gado, naci Gaba da tagumi abina, ni abinda yafi damunama

yanda nake Jin jikina wani iri, saboda magungunan dasu husna sukai ta dirkamin kamar ba gobe, Gaba daya jina nake cikin wani irin yanayi, Babu abinda nake buqata idan ba mijinaba, gashi kuma al'amari ya banje 😃
Oh ya Allah gani gareka kayimin zabi na alkhairi ya ilahi!

** *** **

"Man yanaga Kanata murmushi kana typing ne?"

"Nida matata ne," inji ahmad kenan
Tahir yace "ok au wai tsohuwar matarka laila?"

Ahmad yayi masa kallan tara saura kwata, yace
" inada wata Mata ne data wuce nafeesa?"

Tahir yace "au Yau kuma Babu feenah, sai nafeesa kai tsaye?"
Ahmad yace "a a wai Dan kafi ganewa shiyasa nafadama sunanta na gaskya,
Nafada Mata ne, ta shirya karbar sabon ango, tunda wancan ya kasa"

Tahir yace "ahmad, wallahi de ka kiyaye dakyau, Dan kaima idan aka saceka, Babu ruwanmu"
Ahmad yasaki murmushi yace "sata! Saikace a film, kai nifa yanda nakejina yanzu, gani nake kawai kamar ma andaura, Dan wallahi ina Santa tahir, ina kaunar feenah, shekara da shekaru tamin nisa yanzu tadawo gareni, to saboda me zanyi sanya?"

Tahir yace "hakane, gaskya kunyi kokari dukanku,"

ahmad yace "kamarya dukanmu?"

Tahir yace "kasan abinda yafi bani mamaki Dan gane da yarinyar nan, ace namiji boyfriend dinka yayima haka, Amma saboda tsabar soyaiyar datake ma takasa fadawa iyayen ta, kaine kayi Mata laifi, ai kaima kasan ba duk matane zasuyi wannan jajircewar ba, soyaiyar ma dayaya akeyi, "

ahmad yace" to ai tahir ni feenance yanda take iya tsaya wa ta kalli idona tafadamin magana sai al'amarin nata ya dinga bani tsoro kamar tafi kowa tsana ta wallahi tahir "
Tahir hararar wasa yayi masa yace" to saika tsaya ai ta renaka," ahmad yace
" Allah mutumina,"

tahir yace" to tsaya wasa"

** *** **

Abin duniya ya yiwa laila yawa, kullum tana gida, bata Zuwa ko'ina, bata isa takai qarar dad dinta wajan hajia salaha ba, sai tace tayi hakuri, to hakuri har yaushe zai qare, daganan bata wuce ko'ina ba, kai tsaye sai wajan mahaifinta, inda ta bashi hakuri, Akan abubuwan dasuka faru, takuma nuna tayi DANA SANI Dan haka nan da nan alhaji bukhar yahadata da wani abokinsa, Dan Garin misau, alhaji Bala, yanada Mata biyu, laila Zata je ata uku, a hakanma shine yaga zai iya, yace yaji yagani zai aure ta, saboda shi mutum ne maisan haihuwa ita kuma Babu halin hakan
Allah yakaremu duniya da lahira yarabamu da sharrin zuciya

** *** **

Next day
Tana zaune awani wajan shan iska, ita kadai, tana tunanin rayuwar ta, oh yanzu shekarunta sai qara Gaba suke Amma Babu wani mashin shini
Sallamar da akayi ne yakatse Mata tunanin data Lula, daga kanta tayi tare da amsa masa sallama, babban mutum ne kamili, aqalla shekarun sa zasu kai hamsin da wani abu, yace "sannu fa yanmata," tace "yauwa fa"
Yace "tun dazu nake ta kallanki kina zaune ke kadai, idan Babu damuwa maizai hana inrage miki tunani," murmushi tasaki tace "babu damuwa bissmilla," tafadi hakan tare da nuna masa wajan zama, zama yayi tare da daukan lemon dake gabanta ya tsiyaya a cup yasha, yadubeta yace
" kiyi hakuri fa nasha miki kayanki batare dana nemi izni ba," murmushi tasaki akaro na biyu, tace
" karka damu Babu komai "
Yace "ok, thank you, ni sunana honorable sani Abdul qadir, ni mutumin kano ne, Amma nafi zama a Abuja, inada Mata daya da yarana hudu, yanzu haka nazo nan wajan ne Akan wani taronmu na siyasa

Maganar gaskya tunda na dora idona akanki naji kinyimin idan bazaki damu ba, zan so ki kasance Mata agareni, idan har banyi miki tsufa ba "

Cikin ranta tace" to wanne tsufa ma, nima dana Dade agidanmu ai gara ma amince tun kafin nima na tsufan, Allah sarki rayuwa, ni iklima naga ta kaina, inda ace tun farko na amincewa tahir da tuni na auri yaro kusan sa'a nah, Amma nabi Rudin duniya ninan sai governor, gashi yanzu zan bige a honorable
Nan take tayi DANA SANI yafi cikin carbi, batare da bata lokaci ba ta amince masa

** *** **

Yayi kyau Sosai cikin manyan kaya, yadi ne Dan uban su mai tsadar gaske, kalar golden, sai zuba qamshi yake

Cikin sauri sauri yake saukowa qasa, yana Zuwa falo yaga sauran yan gidan suna break, agurguje yaqarasa suka gaisa
Mamy tace "yauwa my son qaraso ga break dinka nan yana jiranka Yau harda mutumin Naka akai kunun gyada"

Yatsina fuska yayi, gamida dafe cikinsa yace "mamy wallahi inaso Amma kuma ina sauri ne" , Momy ce ta dago babu alamar wasa tace " kai zauna!"
Babu musu ya zauna yana shafa qeyarsa, shikam yanzu Momy bata sansa, tun Akan abinda yafaru shida feenah
Amma aishima bayin kansa bane ko
Kofi daya yasha agurguje, bukhari yace

" yaya zaka qone fa idan kana sha da zafi,"
ko kula shi baiyi ba, yakafa kai babu wani yanga yashanye Gaba daya 🙊

Tissue yaja yagoge bakinsa ya miqe yace

" Momy, mamy, naje zaria saina dawo"

Baby tace "uncle nima zani please"
Kallanta yayi yace "next time zanje dake kinji, Amma banda yanzu,"
Yaci gaba da tafiya

Mamy hakima tayi karaf tace, "zaria kuma? To Allah yasa de lafiya Dan naga Kanata sauri"

Kafin yabata amsa Momy tace "ina kuwa lafiya hajia zaije ya kashewa yar mutane de aure yadawo" 🤣

Cikin sauri yakai kallansa gareta
Baice komai ba ya girgiza kai yafice cikin sauri
(nikuwa cikin raina nace ina ruwan kanku akeji 😃)

Bai Dade da tafiyaba saudat takira su Momy suna gaisawa, kowa saida aka bashi suka gaisa, baby kuwa saida aka qwace wayar,🤣 saboda surutun nata bana qare bane

Zasu yi sallama ne, Momy tace "ya maganar zuwan naki? Zakizo bikin ne da wuri kokuma sai abin ya matso?"

Ajiyar zuciya saudat tayi, tace "hmm wanne biki Momy da anfasa"
Momy tace "bangane ba, kamar yaya?"
Saudat tace "wallahi munyi waya da ita rannan tacemin anfasa bikin nata, daga bangaren angonne aka samu matsala,"
nan de ta basu labarin komai

Momy tasa salati tare da kashe waya

Ta dubi mamy hakima tace "hajia ashe shiyasa danki yake ta rawar kafa zashi zaria" 🤣

Mamy tace "me yake faruwa hajia?"
Momy tace "ashe wai kinji anfasa bikin yarinyar nan ne, shine dagajin labari yadebi kafa yatafi, banda rashin hankali irin na ahmad daga faruwar Abu yadiba kaje musu gida salon suce dama murna kake da hakan?" 🤣

Guda mamy hakima tasaka tace "alhmdlh
A a hajia banga laifinsa ba, gara yaje tun kafin wani Yarigashi"
Murmushi kawai Momy tayi
Dan ita kanta tana yiwa danta fatan samun feenah

** *** **

Yana faka motarsa a kofar gidan, yashiga ciki, batare da tunanin komai ba, saide idan yatunada abinda yafaru abaya sai yaga da wanne ido zai kalli wadannan bayin Allah
Kawai shahada yayi yashiga
Mama tana tsakar gida tanashan hantsi
Sallama yayi, ta amsa masa da mamaki, tace
" a a ahmad ashe kaine atafe"

Kansa aqasa bai yarda sun hada idoba yace " eh wlh mama, dama zan wuce ne nace bari in qaraso mu gaisa daku tukunna" 😉

Mama tace "ahhh aikam ka kyauta, ya wajansu hajia da izdihar din,"

ahmad yace "sunanan kalau, daddy ma yace a gaishe ku, Yama bani saqo yace akawo muku"

Bai jima da rufe bakinsa ba, samarin dayace su taimaka su shigo masa da kaya suka fara shigowa dasu doya ne, taliya, macaroni, jarkokin mai, su indomie,yasan idan yace shine yasiyo fada Zata masa

Mama tacika da mamaki, shida yace Akan hanya yake me kuma yahadashi da kaya?🤣 Tasan sarai aikinsa ne
Dan haka tace "kaide kullum baka gajia ahmad"

Shiru yayi tare da Sosa qeyarsa

Abba ne yafuto daga falo yaci binjimar Riga, saboda yanayin sanyi, nan yagansu a tsakar gida

Mama tace "Abban husna ai yanzu nake shirin kiranka ku gaisa da ahmad"
Abba yace "kice baqi mukayi"
Hannu yamiqawa ahmad, ahmad yaqi bashi hannun yakoma ya tsugunna yagaida shi har qasa
Hakan dayayi saiya birge Abba

Abba yace "kace Yau da safe kake take, kuma ahmad baka gajia da wahala haka"

Murmushi kawai yayi Baice komai ba, dama kuma shima Abban baisa ran Jin amsar sa ba,🤣 saboda yasan Hali
Dan haka yaci gaba da cewa, "wannan nasan ai ko break fast ma bakayi ba

Shigo falon azuba mana abinci"
Babu musu sukai cikin falon dukansu harda mama

Mama ce tafara hada musu,abincin Abba yace "a a kekuma bazaki hutaba, kira yarinyar nan tazo tahada mana"
Daga murya mama tace
"nafeesa!"
Gogan naku cikin ransa yace "alhmdlh" 🤣

Da sauri na futo daga daki kaina ko dankwali babu,kasancewar nasan Babu kowa agidan, dagamu saimu rigar jikina robace, Dan haka shafe dina yabaiyana acikinta, yan madaidaitan breast dina dasuke a tsaye, sai suka qaramin kyau
Ina futowa falon dashi nafara tozali
Cikin sauri najuya daki

Cikin ransa yace "ya Salam
Karfa yarinyar nan tasa yaji kunya agaban surukai"

Shima sunkuyar da kansa yayi qasa cikin sauri

Nadau lokaci kafin na futo cikin dogon hijabi na har qasa ina hada musu shayi
Tsintar muryar Abba nayi yana bashi labarin fasuwar aure na da mukhtar 🙆🏻😃

Cikin tashin hankali ahmad yace "subhanallah Amma Abba Garin yaya,?Tome akayi musu haka mai zafi?" 🤣

Ina zuba musu sukkar (suger) a shayi cikin raina nace lalle mutumin nan Dan renin hankali ne

(nikuwa nace na gaske feenah)

Mrs Usman ce 🖊️
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

59

Abba yace "wallahi matsala aka samu daga shi yaron mukhtar..." Nan Abba yaci gaba da bashi labari harya Gama
Ahmad yayi shiru kamar gaske, can yace "to Abba Allah yarufa asiri, Allah yasa hakane yafi alkhaairi"

Abba da mama suka hada baki wajan fadin
" amin"
Ina Gama zuba musu najuya zan koma daki, Abba yace "uwata kinci abincinne ke?"
Babu abinda naci Amma saboda banasan zama kusa da ahmad yasa nace "eh Abba naci,"

mama ce tace "yaushe kika futo falon ma bare kici abinci?"
Abba ne yakarbe zancan da fadin, "naga alama yarinyar nan tunda abinnan yafaru batasan zama acikin mu ma, bare ta kwantar da hankalin ta, har ta murmure tadawo kamar da
Dan haka babu inda zaki, zauna kici abinci,"

mama ya kalla yace "meyasa kike barinta ita kadai ne, bayan kinsan lalurar datake tare da ita ba'a San ta cika tunani?"

Mama tace "to alhaji ai gatanan agabanka, kai kayi Mata fadan ko kai dabata renaba zataji maganarka"
Kaina a sunkuye, na dawo nazauna, shayi kawai nakesha, sai wainar qwai, shima inaci kamar banaso

Shiru ne yabiyo baya, ahmad cikin ransa yace lalurar menene take damunta? Dole zai tambayeta yaji, Dan shikam bazai juri ganinta cikin damuwa ba, ya gwammace shiya fuskanci matsalar ita kuma ta zauna cikin kwanciyar hankali

Dan yasan tabbas abaya ta fuskanci abubuwa dayawa, wanda bai saniba
Abba ne yace  " ahmad kaima naga bakasan cin abincin, kamar uwata,"

dagowa nayi da nufin kallonsa, adede lokacin da shima yadago kansa
Harara na balla masa, cikin sauri ya sunkuyar da kansa, mama datake kan kujera tana kallansu ta gefen ido

Murmushi ahmad yasaki, yace"Abba inaci"
Hamdala Abba yayi, ya miqe zai fice, mama ma tafara kiransa tabishi suka fita tare
Shiru ne yabiyo baya
Mantawa nayi dashi awajan, naci Gaba da shan tea
Ajiye nasa cup din yayi, yayi tagumi da hannun sa biyu, yazuba Mata ido, yana sakin murmushi
Ina kallansa na share shi
Wainar danake ci yasa hannu ya karyo kadan, ya nufo bakina da ita
Harararsa nayi, yace "koki karba kokuma in miki dura yanzun nan wallahi"
Yatsina fuska ta nayi nace "kamarya, miye hakan Malam?"
Daure fuska yayi yace
" zakici ne kokuma inmiki dole?"
Tashi nayi zan shige daki, yayi saurin riqo hannu nah, yatashi tsaye, cikin Daure fuska yace
"kikarbi wainar nan ko"

Ido nane yacika da hawaye, cikin rawar murya nace "toka rabu Dani mana, dole ne?"

"Zauna"
Yafadi haka babu alamar wasa, zama nayi na sunkuyar da kaina, tausasa muryarsa yayi yace
"my feenahhh"
Har cikin raina naji sunan
Amma ban amsa ba na qyaleshi
Yaci gaba da fadin,
" meyasa bakya sona ne yanzu? Meyasa kika tsaneni feenah?"

Shiru nayi ina ajiyar zuciya
Yace "nide kowanne lokaci kina nan acikin zuciyata, bazan iya cireki daga ciki ba,"

sake tausasa muryar yayi, kamar rada, yace
" my feenah ki yafemin mana, naroqeqi kiyi hakuri feenah"

"Nide ka barni natafi"
Abinda nace kenan, yace
" zan barki Amma idan kin tsaya kinci abinci
Kiyi hakuri kici abincin to,banasan ki zauna da yunwa, kinji? Yi hakuri ci abincin badan halinaba"

Shiru nayi, nasa hannu naci Gaba da cin abinci na, shikuwa yazubamin ido yana kallo na kamar

tv
Tsintar maganarsa nayi yace "me yake damunki?"

Kallansa nayi nace " lafiya nake"
Yace "Amma naji Abba yace bakyajin dadi, menene yake damunki?
Kokuma mu tafi asbiti bayan kin gama?"
Ido nazaro nace "dawa zakaje asbiti? Saide wata Amma bada niba"

Shiru yayi yana aikin kallona, wainar de yasake karya yanufo bakina, nakawar da kaina, yace "please," banza nayi dashi
Yace "naga bakyaci ne dayawa,"
araina nace renin wayo, kamar shi din ci yake
Nace "Dan Allah ahmad karabu Dani nahut..."

shiru nayi Jin ya turamin wainar abakina
Adede lokacin mama tashigo
Tace "ahmad har yanzu tana nan tanacin abincin nata kamar mage ko?"

Nace "mama aina qoshi ma"
Flet din naharhada zanmaida kitchen, natafi zankai, shima ahmad yayi sauri yadauki flask din tea yace "bari intayata mama," 🤣

shima yabiyoni kitchen din, mama murmushi tasaki tabisu da kallo, yaro me kunya, Amma yarinya duk tana nema ta susutar dashi
Nikuwa cikin raina nace Yau naga ta kaina da jaraba
Ina ajiye wa najuyo zan fice daga kitchen din, daidai lokacin shima zai ajiye flask din, aikuwa sai ji kake garam munyi Karo
Nabige agoshi na, hannu na nadora awajan ina shafawa yace "oh sorry, aina biyo kine, kiyi hakuri bansan zaki juyo bane, sannu kinji"
Yafadi hakan da sigar rarrashi, matsowa yayi dab Dani yafara huramin iska awajan, hakan dayayi shiya haifar min dajin wani yanayi atare Dani, shima daga wajansa hakan take
Cikin muryar rada yace "my feenahhh
Ina kaunar ki sosai, please Dan Allah kisoni kema, inaso kibani dama in aure ki, inbaki kulawar data dace"
Dasauri nabar wajan nayi falo, ina Zuwa naga mama bata nan Dan haka nima nayi daki

Ina shiga daki nafada kan gadona ina sakin numfashi, idan banyi da gaske ba tabbas ahmad zai wargazamin tunani na

wuta aka kawo, mama ta futo daga daki zatai kallo, taga ahmad a zaune shi kadai, da mamaki tace "a a ina nafeesan take? Ai nayi Zatan tare kuke,"

ahmad yace "tana daki mama"

Bata ce masa komai ba, ta kunna kallan, ta wuce Dakin danake, tana Zuwa adaidai Ikcin ina saka kaya, kasancewar nayi wanka
Tace "miye hakan kikeyi ne? Mutum yatako yazo har inda kike Amma ki barshi afalo? Dan nasan sarai wajanki yazo, banasan shirme kinji ko?"

Tana Gama fadar haka Takoma Dakin ta
Shima ahmad din danna wayarsa kawai yake

Falon nafuto inata zuba qamshi, nanemi waje nazauna, bance dashi komai ba
Adaidai lokacin wayar ahmad tadau qara, amsawa yay ahankli saikace wani basarake
Tahir yace" man kagama shiryawa ne zaka wuce zarian?"
Ahmad cikin mamaki yace" wanne zaria? Aini 12:00 ma a zaria tayimin
Yanzu ma gani ga matata"
Yafadi hakan yana kallona
Tahir yace "tab, gaskya dole inziga su mama sudena Bude gida da wuri, Dan wataran da asuba zasuji Ana qwanqwasawa"

Ahmad yace "haba de, kaima kasan ai ko cikin dare ne zasu bude min"

Bayan sun Gama wayane yadubeni yace "ki cewa mama zan tafi,"

bance dashi komai ba, naje Dakin ina Zuwa naga tana bacci Dan haka na dawo cikin sanyin murya nace masa "tana bacci"
Yace "ok, to zan tafi, sai yaushe?"

Nace "ka gaida su Momy,"

yace "bakya buqatar qara ganina kenan?"

Ko kunya nace "eh,"

yace "Toshiknn kinsan mu kuma inda ba'a neman mu munfi Zuwa wannan yankin, Dan haka ki saurari ganina a kowanne Ikci,"

yana fadar haka yafice
Harya shiga mota zai tafi sai ga Abba yadawo, futowa yayi sukai sallama, Abba har yajuya zai shiga gida yajuyo yaga ahmad a tsaye awajan, da mamaki yace" ahmad lafiya kuwa?"

Babu kunya ahmad yace" Abba dama inaso zan fadama ne mun dedeta kanmu nida nafeesa dazu "🤣

Cikin mamaki Abba yace

" a a ikon Allah, "

kafin yasake wata maganar kan ahmad a sunkuye yashige mota Yabar wajan cikin kunya, shikuma Abba yayi gida yana fadin yaran zamani kenan

** *** **

Kiran sallar farko ne yayi sanadin farkawarsa daga daddan mafarkin dayake shida feenah, kai aure me dadi, gaskiya yakamata yayi da gaske ayi ayi ayimusu aure, Dan gaskya shikam yagaji da wannan halin dayake ciki
Kallan kansa yayi yaga abinda mafarkin nata ya haddasa masa, Dasauri yadiro daga gadon, yayi toilet, yana fadi cikin ransa dole Yau yaje wajan feenah Susan a inda suka tsaya, wannan boye boyen yafara isarsa, Tsawon sati daya banda wahala babu abinda take bashi, haba Dame zaiji? Da wannan jarababban mafarkin koda fitinar ta,?

Dan haka da safe yana Gama shiryawa ya cewa mabaruka ta shirya baby zasuje zaria, bata dauki Ikci mai tsawo ba, tagama shiryata, bayan sunyi sallama da kowa suka dau hanya

Da azahar sukaje, adaidai wannan lokacin nikuma naje maqota, ina futowa wani saurayi yatareni yana tambayata sunana
Muna tsaye ni dashi a kofar gida, daidai lokacin motar ahmad ta tunkaromu, cikin bacin rai ahmad yace "baby, waye nake gani wancan tare da antynki?"

Izdihar ta ware hannayenta biyu alamar bata saniba tace "to uncle ina zan sani?" 🤣

Dasauri ya qarasa wajansu, feenah kawai ganinsa tayi agabansu kamar an wulloshi, da mamaki take kallansa, ahmad yamiqawa saurayin hannu suka gaisa, daga baya yace
" Dan samari nasan baka saniba shiyasa kake tsaye tare da matar aure ko? "
Saurayin yace
" subhanallah kamarya ina tsaye da matar aure? Me kake San fada bawan Allah?"

Ahmad yadaure fuska yace "qwarai kuwa abinda kunnanka yajiye Maka shi nake nufi, matata ce, duba nan, yayi masa nuni da baby, yace kaga yarmu nan, Dan haka banasan naqara ganin kafarka anan, inba haka ba wallahi hukuma ce Zata rabani dakai"

Yajuyo kan feenah yace
" kekuma wuce mu tafi gida kafin ranmu yabaci anan"

Cikin takaici nace "babu inda zani, tunda ba iko kake daniba" , ahmad yace "ok haka kika ce?"

Nima cikin dakewa nace
" qwarai kuwa haka nac..."

Maganar daban qarasaba kenan ahmad yasa hannu yadaukeni cak, yayi cikin gida Dani, har key din dayake hannun sa yana faduwa, aikuwa baby tasa hannu tadauka itama ta biyo bayanmu

Saurayi dayaga abinda yafaru nan yace astagfirullah, haqiqa wannan mutumi yafini gaskya tunda gashi ya nunamin hakan

Allah ka yafemin, Dan haka shima yadau hanya yayi yamma

(nikuma nayi gabas🏃🏻‍♀️)

Mrs Usman ce 🖊️🌱
[5/6, 3:32 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

60

"Kasaukeni banaso, wannan ai wulakanci ne,"

abinda nake fada kenan, ina zillewa alamar qwatar kaina
Mama tana zaune atsakar gida taga an shigo Dani ahannu, tsintsiyar datake hannun ta ce tafadi, tace
" subhanallah meya faru?"
Kokarin saukowa nake raina yayi mutuqar baci
Kafin insauko ahmad yace "kiyi a hankali mana karki fama ciwon naki"

, yadubi mama yace,
" mama faduwa tayi awaje, shine muka ganta takasa taka kafar, shine ni kuma... Am shine"

Yadubi baby datake tsaye yace "ko baby?"

Aikuwa baby tadaga kai, alamar eh hakane

Mama tace "subhanallah, to Allah yakiyaye, kaita falo, muje, muje"
Mama tariqo hannu na tana min sannu, Gaba dayama mamakin ahmad yacikani, ciwo kuma!

Lalle wannan mutumin Dan duniya ne
Akujera ya ajiyeni, mama tace "bari adauko ruwan zafi saita dunduma wajan"
Tana fita, baby ta tashi tafado kaina, shima ahmad din aqasana ya zauna batare daya hau kan kujerar ba, tace
" antyyyy"
Hararar ta nayi nace "niki dagani, tunda kinfi sansa akaina"
Baby tace "anty kiyi hakuri, kinga tunda safe muke ta murna zamuzo wajanki nida uncle"
Nace "to karku sake Zuwa banaso"

Tace "to ai anty mu muna so, ni inasonki, kuma uncle ma yana sonki, kuma anty tunda dadewa naketa cewa kema ki dawo gidanmu kikaqi, ai dole ace kinji ciwo, tunda bazaki iya tafiya ba" 🤣

Cikin bacin rai, nadaga hannu zan daketa, ahmad daya zuba ido yana kallanmu yayi sauri ya riqe hannu nah, yace
" haba! Haba feenah, yanzu saiki daketa? Kamar wata qanwarki? Yanzu kema ai saiki zama yarinya irinta, kokuma kin manta da matsayin ta ne awajanki?"

Mama ce tashigo falon da ruwan zafi ahannun ta
Tacemin "ungo wannan kidan gasa kafar taki"

Araina nace nikam Yau naga ta kaina, Babu abinda yasameni Ana nema adauramin jinyar qarya
Ruwan nakarba nafara dundumawa a hankali, mama tace "a a wannan ai Bayi kikeba, kawo kigani"
Ahmad dayayi shiru yadan matsa kadan yabasu waje
Mama tana saka Mata ruwan tasaki qara, batasan lokacin datayi jifa da handkerchief dinba
Mama tace "au! dankin samu ma nayi miki shine kikemin wannan abin, to gashinan sai kiyi da kanki, kokuma kafarki tayi tsami, kanki ki kayiwa"
Tatashi Takoma wata kujerar, baby ma tabi bayanta, tace "mama, ina abbana?"
Mama tace "ai munyi fishi izdihar
Kina ganina dazu kika shareni" 🤣

"To mama ai anty nagani"

Mama tace "aikam nagani baby, shine sai yanzu kika lallabo wajena, nasan yanzunma akwai abinda kikeso ne shiyasa"

Handkerchief din yadauka a hankali, yamiqa Mata cikin muryar rada yace "gashi kiyi"
Banza nayi masa

Mama tajuyo tace "ka kyaleta ahmad , ai kanta Zata yiwa"

Baisake magana ba yadauka yadan tsomashi kadan acikin ruwan

Kafar tata yakama ahankli ya zubawa ido, maimakon yayi abinda zaiyi, saiya zubawa Zara zaran yatsun kafarta ido
Ahankli ya ajiye handkerchief din yasa dayan hannun sa yana shafa kafar a hankali, dayake sunbawa mama baya, Babu wanda zai fuskanci wani Abu

hannun sa yamaida tafin kafarta yana shafawa ahankli, wani Abu nakeji yanamin yawo tun daga kaina har tafin kafata

Dasauri nafara kokarin qwace kafata, hakan danayi ne yadawo dashi daga duniyar daya Lula, firgigit yadawo daga tunani, yadauki handkerchief din ko acikin ruwan baisaka Shiba, yafara goge Mata kafarta cikin sauri

Qwace kafata nayi, nafara tafiya ahankli na shige daki, mama ce tabini da kallo

Wajan data tashi ya zubawa ido yana kallo
Ajiyar zuciya yasauke yatashi yadawo kujera,

nan mama tafara tambayarsa mutanan gida, suka sake sabuwar gaisuwa
Baby tace "mama nikam yunwa nakeji," mama tace "af kuyi hakuri, bankawo muku abinci ba," tashi tayi, takawo musu jalof din taliya dataji kifi da ganyaiyaki
Hankalinsu kwance sukaci abincinsu shida baby
Mama ce ma me kokarin jansa da fira, shikum yayi gim babu um bare um um
Mama cikin ranta tace wannan kam bazan iya wannan halin nasaba, bari inturo masa wacce ta iya dashi
Dan haka Tatashi ta wuce dakina, tana Zuwa tace "Toni zanje maqota, yanzun nan zan dawo, kidawo falon ke"

Tana fadar haka bata jira amsataba tayi waje
Inajin fitar ta na futo kalau Dani, naware ina tafiya
Baby tace "anty mu munci abinci kema kizo kizuba kici"
Nace "kude dakukejin yunwa sai kuyi taci"
Waje nanema nazauna, baby tasake dawowa jikina tace "anty muyi wasa, ki rufamin idona ki buya, saina kamoki kema kuma sai arufe naki"

Nace Mata "ni?Saide kiyi da wata,"
bikinta taturo Gaba, tace
" ke anty komai ma bakyaso, laaa anty muga hannun ki,"
da mamaki na miqa Mata hannun kamar wata doluwa, nayi tunanin wani abun tagani
Aikuwa tana kama hannu na, saita cijeni ahankli, ta miqomin nata hannun tace" kema to ki Rama,"

nace" a a ke ni banasan wasan komai baby, ki barni nahuta kinji "

Sake kama hannu na tayi nayi Zatan ahankli zatamin irin na dazu, aikuwa saiji nayi ta gartsamin wani cizo, tayi bayan ahmad Dagudu tana daria
Cikin azabar ciwo nace" auchh!! "

Ina yarfe hannu nah
Baby tana daria tace " anty dazafi? "

Banza nayi Mata, ina yarfe hannu, nakalli wajan har yayi ja kadan, Natashi na kamata, nace" wallahi saina Rama "
Ita kuwa Allah sarki jitake wasan datake sone nake Mata, Dan haka tanata daria tana buya a bayan ahmad
Shi dayake yasan sarai ramawar zanyi, yace" kiyi hakuri mana, kirama anawa"

, yafadi haka yana miqomin hannun sa,
Banza nayi dashi, nakai hannu zan sake damqota, aikuwa dataga da gaske nake nan da nan idan ta yayi qwalqwal alamar kuka
Tace "uncle please kayi Mata irin addu'ar dakamin rannan a ciwo na, Allah nadena bazan sake ba,"
idona yacika da qwalla nace "wallahi idan baki bani narama ba mai rabani dake sai Allah"

Ahmad dayaga abin bana qare bane, Dan haka yace "baby debomin ruwa awaje saina Mata addu'ar kinji"
, aikuwa dama hanyar guduwa take nema, Dan haka tayi wuf tafice

Hannun yakama, yafara murza wajan ahankli, bansan Ikcin da naji hawaye ba, nace cikin kuka "d zafi fa tamin shine zakasa ta gudu"

Da mamaki ya kalleni yace "yanzu ke in a kace ki Rama saiki Rama? Baby cefa!
Ni narasa meyasa dagake har babyn kike biye Mata Kuna Abu kamar wasu yara"

Kafin nasake magana, yatura hannun cikin bakinsa yafara tsotsa ahankli
Lumshe idonsa yayi Jin tattausan hannun ta abakinsa, zubawa Zara zaran gashin idonsa ido nayi ina kallo, na shagala a kallan sa, ahankli yabude idonsa daya fara sauya launi shima yana kallo nah
Juna muka zubawa ido muna kallo, kowa da abinda yake saqawa acikin ransa
Jiyake kamar ya janyo ta jikinsa ya rungume ta, yaji dadin rarrashin ta, yayinda takejin wani irin yanayi atare da ita mai wuyar fassaruwa, meyasa ahmad ya karbi abinda take tattalinsa fiye d komai a duniya? Meyasa bayan ta yafe masa takejin har yanzu zuciyar ta, taqi sake wa dashi kamar da? Meyasa?

Sallama mama ta doka atsakar gidan, hakan ne yafargar dasu daga duniyar dasuka Lula
Cikin sauri yasaki hannun nata ya zauna, yayinda feenah take takawa ahankli Takoma wata kujerar daban nesa dashi tazauna,

Hannun baby yana cikin na mama suka shigo falon, tana ganin feenah tafara buya a bayan mama
, mama tace "kekuma me aka miki kamar hawaye a idonki?"
Murmushi ahmad yasaki, baice komai ba

baby tace "mama wai danna cijeta da wasa shine tace saita Rama"
Mama tace "aikinfita hankali baby, Allah ya miki albarka kinji?" Baby tace "amin mama"
Kiran sallar da aka fara ne yasa ahmad yafita sallah, Ana idar wa kuwa sukaiwa mama sallama zasu tafi inda mama tabasu abubuwan girki dayawa dasu kayan qamshi na girki tace sukaiwa hajia, feenah kuwa daga Allah yakiyaye bata qara cewa komai ba ahmad yaso yasamu Abba agida Amma hakan bai iyuba

** *** **

Next day
"Daddy dama inaso ne ka nema min auren nafeesa awajan abbanta, munriga da mungama dedetawa da ita,"
daddy yasaki murmushi yace "eh naji su hajia sunce anfasa bikin nata ko?"
Ahmad kansa aqasa yace "eh daddy"
Daddy yace "Toshiknn babu damuwa, insha Allah zanje zarian da kaina,"
dahaka ahmad yafice daga falon ransa fari tass, gara ayi auren, koma menene yabata hakuri, Dan yasan zaiyi laifi, tunda shide basu mayi wata maganar kirki shida itaba
Ba'ayi sati dayaba kuwa daddy da tahir da abokan daddy na kusa sukaje zaria, Abba kawai ganinsu yayi, nan yashiga kaikawo wajan yi musu hidima, bayan komai yalafa sunci sunsha ne suke yimasa maganar abinda yakawo su, Abba yace ai ahmad dinma yafadamin sunga ma daidai tawa ajunansu, saboda haka ni ina ganin babu wata damuwa, dama matsalar ai daga wajansu ne kuma sun dedeta, Dan haka nabaku nafeesa, nan take aka sanya ranar biki nanda wata daya cif
Tahir shine yafita yasiyo su alawa da duk abinda ake buqata nasaka rana, suka bawa Abba, nan suka tafi cike da farin-ciki

** *** **

Mama tanata murna, taje har dakina takirani tace inzo abbanmu yana kirana, ina Zuwa nagansu afalo da kayaiyaki
Waya Abban yake Dan haka na nemi waje nazauna, da alama da Ammu yake magana, sai farin ciki yake, Yau de Abba duk yanda akai yana cikin annashuwa inajinsa yana fadawa Ammu yace yanzun nan suka tafi, banyi zatan da wannan maganar zasu zoba, aida kazo tunda safe Dan akarbesu dakyau, eh, eh hakane kam, to Babu damuwa, saika zo din, Allah yakaimu, Allah yakaimu, nan sukai sallama
Yajuyo ya fuskanceni yace "uwa ta ga kayan saka ranar ki nan, ahmad yafadamin kun Gama dedetawa atsakanin ku, harma ya turo I yayansa dazu, mungama magana dasu, Dan haka mun tsaida ranar bikin nanda wata daya insha Allah"

Arazane nadago kaina nakalli su Abba

Mrs Usman ce 🖊️[5/3, 9:56 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🖊️🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

61

Nace "Abba sa ranar me? Ni wallahi bamuyi haka dashiba"
Mama ce ta juyo ta kalleni da mamaki tace
" kina nufin wai duk zuwannan dayake yana zarya awajanki kullum kina nufin har yanzu Baku daidai ta tsakanin kuba?"

Kaina na daga alamar eh
Mama cikin fishi tace
" Tome yake Zuwa yi?"🤔

nayi shiru, tasake cewa
" nace miki me yake Zuwa yi?"
Abba yace "a a maman nafeesa karki Mata fada mana,"

yadubeni yace "ke uwata
Kalleni nan, banasan maganar wasa kinji ko?
Kifada mana gaskiya"

Mama tace "ai Abban husna daka barni da ita ranta yabaci, yarinyar nan nalura wasu ne da ita agefe wanda suke zugata"
Ganin ran mama yabaci akaina, abinda sai mutum yadade bai ganiba, nan da nan nafara kuka
Cikin kuka nace "mama kiyi hakuri, Abba kuyafemin Amma ni wallahi bamuyi maganar komai dashi ba"

Mama ce " tace to yanzu dakika ce bakuyi maganar komai dashi ba, so kike mahaifinki yakoma yafada musu Baku daidaitaba afasa maganar biki, inyaso saiya koma mutumin banza ko?
Ai haka kikeso ko?
Toshiknn tunda haka kikeso kije kiyi tayi, na tabbatar shima ahmad din gajiya yayi da halinki na masifar riqo, yagaji da bibiyar ki shiyasa yayi miki hakan, to wallahi bari kiji babu inda Abban husna zashi, saide ke dayake marar mutunci ce, kije kice musu anqara fasa auranki akaro na

biyu,
Daga nan kuma duk layin dakikabi sai a dinga nunaki Ana zundenki, tashi kiban waje kafin nadora hannu na ajikinki"

Kuka nake Sosai, yanda mai karatu baya zato, bantaba tunanin Akan ahmad mama Zata dauki fishi har haka ba
Tashi nayi zan tafi daki, Abba yace "zonan mamana
Zauna anan,"

ya nunamin waje, nazauna ina sharar hawaye da gefen dankwali na wanda yayi bankwana da kaina tun dazu

Abba yace "meyasa koda yaushe kikeso ki ganmu a hakane nafeesa?"
Dago kai nayi na kalleshi Jin yakira wannan sunan kai tsaye, shida yafi kowa boye sunan, kasancewar sunan mahaifiyarsa ne

Nide narasa bakin magana Dan haka nace
" kayi hakuri Abba"

Yaci gaba da fadin "nafeesa kowanne iyaye na gari burinsu suga sun aurar da yayansu, Babu uban da hankalin sa zai kwanta yanada yaya Mata agabansa
Menene laifin yaron nan?"

Kaina na girgiza cikin kuka nace "babu komai Abba"
Yace "yanzu ke ba rufin asirinki bane dana yarku idan ahmad ya aureki?
Yaron nan yazo nan agaban kowa ya nemi yafiyarki, atake kuma ya nuna yanaso ya aure ki saboda yasan ya lalata miki rayuwa
Alokacin muka nuna masa munyi miki miji, yanzu kuma Babu miji, so kike nakoma nace musu anfasa inyaso insaki agaba ina kallanki? "

Kaina naqara girgizawa
Abba yace" to Dan haka nafeesa, amatsayina na mahaifinki narokeki gafara ki yafewa wannan yaron,"
Dasauri nadago na kalli Abba
Yace" eh, nafeesa banaso naci Gaba da ganinki a gabana, nafiso naganki adakin mijin ki, kamar yar'uwarki, nasan ko bayan raina, nagama daku tunda nacika alkawarin dana daukarwa Allah na kula daku a matsayin yayana

Kiyafe masa, kidena tuna baya koda wasa, yin hakan shine zaisa ki dinga zama cikin bacin rai
Ki dinga addu'ah Allah yasa hakanne yafi alkhairi kinji? "

Hawayen idona nagoge duka nace" to Abba insha Allah nayi muku alkawari ranku bazai qara baci adalili naba

Zanyi abinda kuka umarceni insha Allah "
Abba yace" yauwa haka nakeso uwa ta, Allah yayi miki albarka "
Nace" amin Abba "
Tashi nayi da dankwali na ahannuna nace" mama me za'a dora abinci? "
Shiru tayimin
Abba yace" tana miki magana fa"
Mama tace "najita ai
Taje tayi abinda tayi niyya" 🤣

Kamar wata qaramar yarinya nafara bubbuga kafata akasa nace "Abba kajifa abinda tace"

Murmushi Abba yasaki aransa yace auta kenan har yanzu de a autar take ganin kanta

Mama batasan lokacin data saki murmushi ba tace "naji, jeki dora mana duk abinda kikeso auta"
Jin wannan furucin ne yasa tatafi kitchen din dadan gudunta

** *** **

Yayi kyau Sosai cikin qananun kaya, farar riga, farin wando, Jan takalmi Cambus, sai rigar sama itama ja, yayi mugun kyau, yana ta zagaye falon, yakasa zama, daddy yadawo yayi masa sannu da Zuwa, Amma yayi masa shiru, baiji yaya suka qare da iyayen feenah ba, "Allah sarki ni" 🤣

Yafadi haka afili, yanzu haka Kiran nafeesa akayi tatonamin asiri, tace ni bamu daidai ta da itaba, Dan haka bazata iya aure naba, oh nikam wanne irin so nakewa yarinyar nan ne?
Toni yanxu wajan wa zanje inji yaya sukayi? Idan nakira feenah ma bazata saurareniba, abinda zanyi kawai bari inje in lallaba tahir, inji yaya aka qare

Kamar wani zararre haka yake ta magana shi kadai
Key din motar sa yadauka yafice, su daddy da Momy suna zaune afalo, saijin tashin motar sa sukayi, mamy hakima tace "nikam alhaji ka dawo kayi shiru yaya kukayi da iyayen yarinyar nan ne?"
Daddy yace "ai mun gama magana dasu hajia, harma ansa ranar nanda wata daya"
Gaba dayansu itada Momy suka saki murmushi
Mamy hakima tace "a a alhaji kace babu zama yanzu zamu fara shirye shirye"
Momy tace "gaskya kam"

Daddy ya kalleta yace "au Yau kema harda ke?" Yana murmushi yace to ai shikkenan

Mamy tace "alhaji Amma ahmad baisaniba ko?"

Daddy yace  " ban fada masaba, dazun nan yagama sussunkuyar da kansa yagama yatashi yatafi, yanzu kunji fitar sa may be wajan abokinsa zaije ya tambaye shi"

Mamy tace "um Yau my son babu zaman lafiya agidan nan"

** *** **

"Wash wallahi nagaji sosai, da mukaje ma ban zauna ba nine nan nine can,"

husna tace "to sannu my husband"
Yace "ina yaran nan suke ne?"

"Suna wajan ummi"

"OK sweet hrt bar tausar nan kije kikawo min ruwa"

, bayan tadawo ne ta bashi yasha, tace "ya kamata ka kwanta kahuta ko? Waima meya kaika zaria? Kuma dasu daddyn ahmad"
Tahir yace  "munje ne ansa masa ranar auren sa,"
cikin mamaki husna tace
" ahmad de ahmad namu aka sawa rana?"
Tahir yace  " shide, tare da feenanmu"
Husna tace "wai Dan Allah da gaske?
Wayyo!"

Tahir yace "wallahi, ahmad din yace sungama daidaitawa shida ita, Amma nasan bahaka bane, zanyi magana dashi de latter"

Husna tace "kace akwai daru"
Tahir yace "saje can su qarata, su suka sani"

Husna ce tadauki waya ta kira feenah
Hakan yayi daidai da shigowar ahmad falon
Tahir yace "a a kaga na feenah angon gobe"
Waje ahmad yasamu ya zauna akujera, husna ta katse wayar tadawo suka gaisa, yace "anty husna yayara?"

Murmushi tayi batace masa komaiba, tashige daki, tana so tayi waya da feenah

"Man yagarin, ya hanya? Please tahir ya kukayi? Hankali na yakasa kwanciya"

Da murmushi tahir yajuyo ya dubeshi yace "angama komai mutumina, sauran yaqin yana wajanka"
Ahmad yace "kamar yaya?"

Tahir yace "zaka zama ango nanda wata daya, saide kace bakuyi magana da itaba, saide kadage ka lallabata,"

wata daria yasaki, har tahir yana mamakin wannan daria,yaushe rabon dayaga ahmad yana irin wannan dariyar?

"Shine daddy yayita wahalar Dani bai fadamin Ba? Alhmdlh tun yanzu nafara jina ango tahir, bansan yaya zanyi mataba, tahir nabata hakurin nanemi yafiyar Amma taqi kulani, shiyasa nace kawai mun dedeta kanmu, idan akai auren a hankali Zata ware, wallahi har tausayin kaina nake yanda nake zarya agarin nan, ina kaunar ta, ina Zuwa gidansu zamu zauna gani gata, jikina da jini tahir, bazan iya jurewaba tun kafin tasa inyi abin kunya agaban surukaina gara inmata dole ayi auren koma menene zai faru saiya faru anamu gidan "

Ajiyar zuciya tahir yasauke, yace" hakane kayi gaskya kuma,"

ahmad yace" yanzu mu tsara komai medame kake ganin za'a yi lokacin bikin "
Cikin sauri tahir ya kalleshi yace" haba gaye, haba, yaufa saura kwana talatin "
Ahmad yace" Naka wasa ne, bari kaga in nemi paper a fara tsara komai yanda zai kasance "

** *** **

"Amarsu ta ango, ashe ashe kuma"
Feenah tace "ashe ashe me?
Ni wallahi sister badan Abba yamin fadaba, Babu abinda zanyi dashi"

Husna tace "hakanma de Mungo de, feenah ahmad yana sanki, nima kuma na tabbatar dahaka, tun kafin aure na da tahir, mutum yazama shiru shiru duk a dalilin soyaiya,"

"sister damafa haka yake baya magana, in kinga maganar sa toda mijin ki ne, ni narasa ma ya akayi nakasa mantawa dashi"

Husna tace "tayaya zaki manta dashi kuwa, ai bazai iyuba"
Nace "saboda me?"

Tace "saboda da jininsa kike rayuwa feenah"

Nace "kamar yaya, me kike nufi?"
Tace "tabbas feenah da jikin ahmad ajikinki, lokacin dazaki haifi baby su tahir sun tabbatar

bazaki iya ba saboda bakida isasshan jini ajikinki, alokacin ahmad yana asbitin baisan wacce marar lafiya ce take buqatar jini ba, batare dayaganki ba yace adiba a nasa asaka miki, kuma aka gwada jinin yayi daidai danaki
Ki fadamin tayaya zaki iya mantawa dashi, bnda dunbin soyaiyar da kukayi abaya?

Sister ahmad yamana komai, batare da yasan Ammu qanin mahaifinmu bane yadauke shi aiki a company sa, yabashi manaja

Batare da yasan baby yarsa bace, yasota, yajata ajikinsa, harma yanemi abashi ita aka bashi

Sanadin haka gidan damuke ciki yasauya masa fasali daga tsoho Zuwa sabo

Ahakan duk baisan kinada alaqa da wadannan mutanan ba yayi wannan aikin alkhairin ko tanan yaci ace kin qara gane ahmad mutum ne nagari, mai taimakon mutane, najikinsa da wanda ma bai sansu ba

Kiyi tunani feenah, yakamata ki ajiye duk wani fishi a gefe, ki rungumi ahmad, kuyi rayuwar ku kamar kowa"

Mrs Usman ce ✍️
[5/3, 10:54 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

62

Nace sister kina nufin shine yabani jini?
Husna tace qwarai kuwa haka tahir yafadamin
Kaina na dafe da hannu na, nace Amma de kinsan irin halin daya sanyani aciki, na fuskanci abubuwa dayawa, ciki harda korata da mahaifina yayi, ninaci wahala ta ni kadai, sannan andauki yarinyar anbashi, kuma hakan bai isheshiba saiya hada dani
Husna tace duk wani bawa mumini da yafiya aka sanshi feenah
Jinake keda bakinki ki kace Abba ma da kansa shiyace kiyafewa ahmad din, to kinga shima mutumin daya koreki agidan kenan, zuciyarsa tayi sanyi, harya manta da baya yake so kiyi aure
Menene ribarki idan baki aure Shiba, banasan naga kina zaune agida haka kawai a matsayin ki na yar'uwata, bayan kin Riga da kingama karatun ki, kiyi hakuri feenah, kidauka haka

qaddararki take
Ajiyar zuciya nasauke nace toshkn sister insha Allah komai ya wuce, zamu dawo kamar da
Murmushi tasaki tace yauwa qanwata kokefa

Yanzu abinda nakeso dake kawai kihado kayanki kidawo kano muci Gaba daga inda muka tsaya
Nace kai anty husna ni banasan wannan abin wallahi, wancan gyaran ma ai ya isa, husna tace bakida hankali feenah,ke a tunanin ki yanda yake wannan rawar kafar akanki, ke a tunanin ki qyaleki zaiyi? To wallahi garama ki farka, in kanada kyau toka qara da wanka,gyaraki zanyi tsaf ta yanda zaidinga tambayar kansa cewa anya kuwa nafeesan daya sani ce abaya?
Daria zancan nata yabani, tace Toshiknn tsaya daria, kede kawai kitaho, nace zanzo sister
Amma gaskya agidan kaka zan zauna, tace babu wani gidan kaka, anan zaki zauna, nace to naji shikkenan sai nazo, dahaka muka kashe wayar
Ajiyar zuciya mama tasauke ta tabbatar wannan dadewar da feenah tayi tana waya da husna take magana, alhmdlh ta godewa Allah daya bata yaya masu hadin kai, Allah yasa dukkanin zuri'arta su kasance haka

Husna nafita daga daki, falo Takoma, su ahmad suna nan yanda tabar su, tahir yace my heart irin wannan dadewar haka, kinbarni ni kadai, nasan keda amarya kuke waya, Amma ni kinbarni da yunwa, husna tace toyi hakuri mana, bari akawo muku abinci, ahmad yace ai anty husna ni wucewa ma zanyi, husna tace bazaka tsaya kaci abincin ba? Yace aina qoshi, ina su mama? Tace suna can wajan ummi
Ahmad yace yakamata de Yau kibani su suje wajan baby, husna tace kadauke su acan, Allah yakai ku lafiya
Tahir yace wallahi kuwa
Murmushi husna tayi tajuya tayi kitchen
Ahmad ya kalli tahir yace saboda Xaka zauna daga kai sai itaba, ai dole kace atafi dasu
Tahir yace nabaka suma kyauta, har bayan aure, kai har bayan amarci ma, idan kun Gama amarcin saisu dawo
Kasa magana ahmad yayi kawai ya girgiza kansa yafita, tahir kuwa yabishi da daria
Bai bata lokaci ba awajan ummi yadauke su tareda kayan su suka tafi

** *** **

"Ina kika bar wayar inata kiranki tun dazu zan baki labari mai dadi"

Saudat tace "Momy wallahi munje asbiti ne"

Gaban Momy yayanke yafadi, tace "waye ba lafiya acikin ku?" Daria saudat tayi tace "wallahi Momy Akan rashin haihuwar nan ne de mukaje aka dubamu , Amma likitan yace lafiyar mu kalau, kawai Allah ne bai kawo ba,"

Momy tace" to alhmdlh
Muma ai muna nan muna muku adduah Allah yakawo nagari, shima wannan naga ta auren sa kawai yake kwata kwata babu maganar neman magani agabansa "

" wai yaya?"

Momy tace" shide,"

" to wanne irin aure kuma Momy? "

Momy tace" ai shine labarin danace zanbaki ansa ranar bikin nanda wata daya shida qawarki nafeesa"

"Dan Allah Momy, wayyo dadi"

Momy tace "wallahi ansa rana jiya,"

saudat tace "to Allah yakaimu kice zuwanade bai fasu ba," 🤣

Momy tace "a a Zuwa bai fasu ba, ga qawa da yaya"

"Allah sarki sister ashe sun dedeta"

Momy tace "haka de ahmad din yace sun dedeta, ai yarinyar tayi masa halacci, a wannan lokacin Mata da miji ma suna rabuwa a dalilin rashin haihuwa, Amma ita taji tasan baya haihuwar ta amince Zata aure shi ahaka, ai kinga kuwa tayi kokari,"

saudat tace "gaskya kam Momy hakane, Allah yasaka Mata da alkhairi,"

Momy tace to saikunzo, ki gaida farouq din, sauda tace Momy zasuji ki gaida su mami dahaka sukai sallama sauda sai murna take

** *** **

After one week
"Biki yarage sati uku, wai feenah miye haka kin wani je gida kin maqale, sai nemanki muke, Allah idan kika yarda nazo zaria dake zan taho, kafata kafarki"

Nace "maida wuqar Zahra, kinga yanzun nan nagama hada kayana anjima kadan zan taho, akwai wanda nake jira ne"

"Banganeba feenah wakike jira, keda kike Gab da shiga gidan wani"

Nace "oh Zahra, me kike tunani akaina, kinsan de bazan kula kowa ba"

Tace "to wakike jira da bazaki taho ba, kokuma ahmad dinne yazo ne?"

Ajiyar zuciya nasauke nace " Zahra kenan ni wallahi rabona da ahmad ma nadade, tun lokacin dayazo ya kitsa karya da gaskya, ko gidan nan bai sake Zuwa ba, ke Kiran nawama dayakeyi yadena yanzu🤣"

, Zahra tace" tofa, to Allah yasa lafiya"

nace "amin, yanzu ma Ammu ne yazo suna magana ne shida Abba, to shine yace injirashi saimu tafi tare,"

Zahra tace "Toshiknn Allah yakawo ku lafiya sai kunzo"

nace " to"

** *** **

Direct gidan Ammu muka sauka saida naci abinci nahuta, sannan ya kaini gidan kalatynmu muka gaisa, daga nan yadau hanyar gidan husna, nace
" Ammu ai agidan kaka zan sauka, husna bayau zanje ba,"

Ammu ko magana baimin ba ya wuce gidan kaka, saida yashiga suka Dan taba fira tsakanin su sannan yayi mana sallama yatafi, har wajan mota narakashi ina Ammu Allah yakiyaye, amin kawai yace, araina nace kaji dashi, kaima wani baqin miskilin

Ina dawowa na miqe akujera, nadora kaina acinyar kaka, muka dasa fira, kaka sai nan nan take Dani

** *** **

"Uncle kaga baby ko, ta dakeni banyi Mata komai ba,"
janyo hannun ta yayi yace "mama kiyi hakuri kinji, bazata sakeba,"

Momy dake gefe itada mamy suna kallansa

Da gudu ta taho itama tana hawaye, bata tsaya wajansu Momy ba kai tsaye wajan ahmad ta nufa cikin kuka tace "uncle kaga baby ta shanyemin ice cream dina, kuma ta dakeni,"

goshinsa ya dafe da hannun sa ya janyo ta jikinsa yace "mima, yanzu me kikeso"

tace "Allah saita biyani," 🤣

Yace " to kiyi hakuri nizan biyaki kinji,"
nan da nan ta goge hawayen ta tayi shiru, tace "uncle nicefa mama kake tacemin mima" 🤣

Mima ma datake gefe tasa daria tace "nima haka yacemin mama" 🤣

Ahmad yace "koma de menene ai nace kuyi hakuri ko" 🤣

, Momy ta daga murya tace "oh wato kai bazaka iya Rama musu ba, saide ka dinga aikin bada hakuri
Allah ya shirya, wataran ai kwa tsokano maiyi muku shegen duka"

Murmushi ahmad yayi baice komai ba, mama tace " uncle Yau kace zaka kaimu gida mu tafi kaji,"
Mima ma tace " eh wlh"

, Babu yanda ya iya, dole yasa aka dauko musu kayan su, baby tana musu bye bye, suma sunayi Mata, haka suka rabu da qawar fadan nasu

** *** **

"Mama wai nikam har yanzu basu isobane?"

mama tace "ai Kuwa tun dazu munyi waya tacemin sunje, tana gidan mama,"

husna tace "OK to nasa Tahir yaje yataho da ita, ninakirata wayar Bata shiga," mama tace "Ok"

Falo tafuto dawayar ahannunta, tana Zuwa falon su mama suka taho da gudu suka rungumeta, husna tace
" oyoyo sannunku da Zuwa," tadubi Ahmad tace "sun gajiyar dakai ko,"
Ahmad yace "a a babu komai, yanzu ma sunata rigima ne saina dawo dasu shiyasa muka taho,"

tace "sannunku da Zuwa," Tahir ta duba da zuwansa Kenan tace "my hero ko zaka dauko min auta ne agidan kaka,tazo dazu Kuma nasan bazata zo da wuri ba, nasan halinta, may be tace

Sai gobe, nikuma nayi missing dinta wallahi"

Tahir yace "ok  karki damu yanzun Nan zanje nakawo Miki ita shikkenan?"

Ahmad yace "a a, am kagane Tahir Bari kawai naje na daukota

babu damuwa bani address din gidan dama inasan ganin kaka"

Tahir yasaki murmushi aransa yace "shege Ahmad"

, fada masa address din yayi, shikuma Ahmad yajuya yatafi, Yana sakarwa Tahir wani shu'umin murmushi Wanda su kadai ne suka San ma'anar sa

Mrs usman ce
[5/4, 3:48 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Wannan shafin nakune masoyan wannan novel, Ina yinku sosai👌🏻

63

Magana ta gaskiya gabansa faduwa yake, kawai de daurewa yake Yana driving, nafarko yanaso yaga kaka, ashe dama wannan unguwar tadawo shiyasa naketa haqilon nemanta, sannan ita kanta feenah inasan ganinta saboda inji meda me take tsarawa, idan nayi sa'ah tagama fishin nata saita fadamin
Yana wannan tunanin Har yazo, wasu samari yagani agefe suna zaune, sallama yayi musu yaqara tambayar su, suka tabbatar masa da gidan ne, Dan haka babu Bata lokaci yasa kansa ciki
Abakin kofar falon yatsaya yanata sallama, muryar kaka yajiyo tana amsawa daga nesa, yace " inshigo?"

Kaka tace  " yau naji ikon Allah shigo mana"

Yana shiga, kaka tafuto daga daki, murza idanuwanta tayi da kyau tace "wanake gani Kamar amadu?"
Cikin murmushi yace "nine kaka"

Matsowa tayi takama taba fuskar sa tashafa kansa, tace "yauwa yanzu nasan ba mafarkin dana saba bane, yanzu amadu kana duniyar Nan, muka nemeka muka rasa,"
Sai kuka Kuma
Cikin sauri yace "a a kaka kiyi Hakuri, kiyi shiru," tace "ashe zamu sake ganinka "
Yace "eh wallahi"

kaka,tace aure Kuma yazo kusa
Murmushi yayi baice komai ba

tashi tayi tace "lalle yau inada babban baqo Ina Zuwa" ,

hanyar kitchen ta nufa
Shikuma ya zauna akujera
Yana juyowa hannunsa na dama yaganta akwance tana baccinta Cikin kwanciyar hankali
Gashin kanta yabazo Mata Har fuska, dan qaramin bakinta ya kallah, bazai manta dandanon wannan bakin ba, idonta ya kallah, Gashin idonta daya hadu da dan'uwansa saiya qara yimata kyau, Kamar tasaka gashin ido

Ahankali yatako Yazo Har inda take, agaban kujerar ya tsugunna
Yasa hannunsa yagyara mata gashin kanta
Matso da fuskar sa yayi gab da tata,
Cikin baccinta taji qamshin turaren da bazai Iya gogewa a qwaqwalwarta ba, murmushi tasaki taji baccin yaqara mata dadi, danhaka tasake gyara kwanciyar ta taci gaba da bacci

Murmushin datayi shine yaqara shagalar dashi, baisan lokcin da dayakai hannunsa Kan Dan qaramin lips dinta ba, Ahankali yake shafawa Yana hurawa idanunta iska
Jitake Kamar numfashinta Yana haduwa da wani, kasancewar kusanci da fuskar su tayi, Ahankali ta Bude idonta, aitana ganinsa tatashi tana zare ido
Kenan ba mafarki takeba shine akusa da ita, meya kawoshi gidan Nan? Waye ma yace masa Ina gidan? take tambayar kanta

Murmushin sa Mai tsada yasakar mata, yace
" kinata baccinki nikuma kin barni Sai gadinki nake"

, harararsa tayi tatashi tayi daki, bayanta yabi da kallo yanda hips dinta yake juyawa yayi bala'in tafiya da imaninsa, aransa yace wayyo Allah wannan yarinyar zata kasheni

Toilet tashige tayi brush tasake gyara kanta sannan tafuto falon, Ahankali Kamar bataso tace masa "Ina yini"
Da sauri ya kalleta, saboda baiyi zaton hakanba
Yana Murmushi yace
" lafiya amarya"

Harararsa tayi, tabi kaka kitchen
Kaka tanata kimurtun hada abinci ita kadai, tana ganin feenah tace
" yauwa alhamdulillah dauki wannan kikai masa, Ina Zuwa da lemon Nima"
Babu musu taje ta tsugunna a gabansa ta ajiye abincin, Ahankali Cikin nutsuwa take zuba abincin
Kuskus ne da miya dataji naman sa Sai ganyaiyaki dangin su salat
Tsugunna war datayi ne yabashi damar ganin abinda yake Cikin rigar ta, Cikin ransa yace masha Allah, bulbul dasu farare gwanin sha'awa
Ya shagala a kallan wajan baisan tagama zubawa ba, saijin tashinta yayi
Ba yabo ba fallasa tace
masa "Ga abinci"
Muryarsa ashaqe yace
" bazaki bani ba?"

Shiru tayi masa tana kallan wani wajan

"Ungo"

Abinda yace mata Kenan, takai dubanta gareshi taga yabata hijabi, Shima kawai ganinsa yayi
Akan kujerar baisaniba nata ne kona kaka, shikam koma na Waye
Gara tasaka inba hakanba Kuwa gaskya saide kaka tarufe idonta

Yana Bata hijabin still idonsa ba akanta yake ba, Yana kallan wani wajan, idanunsa tabi da kallo taga ya zubawa kirjinta wani mayan kallo, danhaka Cikin sauri takarbi hijab din tasaka, Cikin ranta tace wannan kallo haka Kamar za'a cinye mutum

Yana cin abinci kaka takawo masa lemon juice
Sai surutu take masa na Bayan saduwa
Haryadanci kadan, tace
" amadu wannan cin abinci Naka Kamar na yar taku"
Shiru yayi Yana Sosa kansa
Daga baya yadinga Bata labarin irin zaryar daya dinga yi atsohon gidanta, kaka tace "wallahi adamu ne yadawo Dani Nan shida ma'azu
Wai sun dawo danine kusa dasu, saboda can din yayi Nisa Kuma ni kadai"
, Ahmad yake "eh gaskya wannan haka yake,

Ashe shiyasa naketa Zuwa bakwa Nan qarshe ma akacemin ansaida gidan,"

kaka tace "eh wallahi Nan na nadawo, ai Ina yawan tambayar ka awajan nafi, tace min katafi masar shiyasa baka Zuwa"

Da sauri ya Kalle ta, wato boye laifinsa tayi, lalle yau yaqara yarda feenah tana sansa
Kaka taci gaba da cewa,

" to itama Kuma adamun yanema mata scholarship tatafi Sudan, saidata dawo ne nakejin labarin komai awajan ta Har abinda yafaru

Nace Toya za'a yi ai haka ubangiji ya qaddara, saide muce Allah mungode Maka daya bamu ikon cin wannan jarabawa amadu

Allah Kuma yayafe mana, yakore shedan azaman auren ku "

Ahmad yace " amin kaka
Yanzu ma naje gidan Tahir ne saiyace min zaizo yadauki nafeesa shine Nace kawai zanzo indauke ta, daga Nan ma naganki, Naga gidan da kike "

Kaka tace" a a ka kyauta babu laifi kayi kokari
Allah yamuku albarka"

Saida muka dade muna fira da kaka, Dan dole na nadauko kayana muka tafi, Ahmad kudi ya ajiye Akan hannun kujerar dayake zaune, aqallah zai Kai dubu hamsin, yace "kaka gashi kyasai goro"

Kaka tanata ruwan godia muka tafi, nikuwa naci hijabi Kamar matar liman

Muna tafiya amota narufe idona Kamar me bacci
Shiru ne yabiyo baya, shi Yana shakkar yimata Magana ita Kuma tanaso tana basarwa
Kamar daga Sama taji yace "Ina tsarabata?"
Still idonta arufe tace
" aibana Bawa irinku, kaga babu amfanin tambaya Kenan"

Cikin ransa yace "dama nasan za'ai haka"

Danhaka yace
" toshikkenan, yasu mama da Abba"
Agajarce tace "lafiya"

Daga haka babu Wanda yasake Magana acikinsu, sunyi tafiya sosai yatsaya awani waje, yace "Ina zuwa,"
Fita yayi yashiga wajan, baidade ba yadawo, suka Ci gaba da tafiya, Shiru Kamar wasu kurame

Sunzo kofar gidan Tahir Ana Kiran sallar magrib, fos dinta tadauka tace
" barshi ananma ya isa," tafara kokarin Fita, tana budewa taji kofa arufe
Juyowa tayi tana kallansa, yace "Amma my feenah Magana nakeso muyi, sannan koba hakaba kema kinsan Bazan barki awaje ba dole saina kaiki Ciki, sonake mugama Magana saimu qarasa Ciki"

Itafa batasan Zaman motor Nan tsakaninta da Ahmad 🤣

Gabana Yana faduwa cikin rawar murya nace
" nide banasan Zaman motor Nan, muje Ciki saimuyi koma wacce irin Magana ce"
Shi maganar tatama saita bashi Daria, yace
" my feenah ki yarda Dani babu abinda zanyi Miki"

Kuka ne yazomin naba gaira babu dalili, nace "ai abayama haka kace"
Yace "OK, OK, naji toyi Shiru banasan kukanki," Bata zataba taji tattausan hannunsa afuskarta, yashare Mata hawayan, yace "Muje"

Atare suka futo, takama kiciniyar daukar jaka

Sunkuyawa yayi, yace
" bani,"

tace "a a barshi zan Iya"

"Allah idan baki baniba zan daukeki daga ke Har jakar"
Sanin zai Iya aikata hakanne yasa tasaki dasauri
Kawai fos ce ahannunta, shikuma yadauki jakar, ahaka sukaje Har falon husna, suna zaune dukansu suna kallo, yaran suka taho da gudu suka rungumesu, Tahir yace "man, sainajika Shiru,"

Ahmad yace "maine yaqare mana ahanya"

Feenah cikin ranta tace
" haka de ka Iya" 🤣

Waje suka samu suka zauna, husna tanata tambayar ta Yan gida, suna firar gida abinsu gwanin sha'awa
Tahir ma Yana wasa dasu mama,
Shikuwa gogan Yana zaune Yana yiwa feenah pictures, Kamar danne danne yake

text ne yashigo wayar Tahir
Anutse yadauko wayar zai duba, yayi tunanin wani abune muhinmi

"Yaya Tahir please please kabani aron qanwarka inaso muyi Magana da ita kafin natafi "

Abinda yagani Kenan, yakai kallansa wajan Ahmad

Tashi yayi yadauki mama da mima afili yace "dole aceda mijin Iya baba" 🤣

Ahmad Sarai yasan dashi yake
Yana Tashi yace "muje nakaiku wajan ummi ko"
Yadubi feenah yace "auta, kaimuku abinci falon baqi mana, kisamu ladan wannan gwauron"

Husna tace "yau Kuma Kaine kake masa,"

Ta kalli yaran tace "mima, mama saida safenku ku gaida ummi,"

taja jakar feenah tayi Ciki

Nima kitchen nanufa, nadauko lemo da kofuna, nace masa muje
Ina gaba Yana bina abaya

Bayan munzauna nazuba masa lemon namiqa masa, maimakon ya karba saiya hada hannun ta da cup din yariqe gaba daya

Kaina na sunkuyar qasa, yace "matsoraciyar Mota"
kawai, inajinsa nayi Shiru
Sakin hannun yayi, ya ajiye lemon batare dayasha ba
Yace "kiyi hakuri feenah, nasan nayi Miki laifi, nafadawa su Abba da daddy Cewa mun daidaita tsakaninmu Bayan bahaka bane, kiyi hakuri Dan Allah kinji?"

Kaina nadaga alamar to
Yace "kin hakura?"
Sake daga Kaina nayi
Nace "Bari in koma Ciki, nagaji dayawa zan kwanta,"
Ina fadar haka namiqe nafara tafiya

Kawai jinayi anfuzgoni, Har munajin hucin numfashin juna, ido nazuba masa, Shima haka, yace "nafeesa meyasa kike San wahalar Dani Wai?
Narasa yanda zanyi Miki bayani ki fahinceni
, feenah inasanki, Ina sanki, Ina sanki feenah"

Abin mamaki hawaye kawai nagani Yana zuba a idonsa
Hannuna yaja yadora Akan kirjinsa saitin zuciyarsa, yace "kinji yanda zuciyata take bugawa a dalilin kaunarki, nafuskanci wahala feenah, a dalilin sonki hawan jini ne yakamani feenah, banda ciwon zuciya Shima dayake gab da kamani
Dan Allah naroqeki kiyi hakuri kiyafemin feenah"

Durqusawa yayi agabana
Tare da kama Hannayena duka biyun yace "please! Please!! My feenah"

Yana Magana hawaye Yana zuba a idanunsa, wani kukane ya kufcemin, dasauri yatashi tsaye Yace
" shikkenan yi hakuri nadena, Bazan sakeba kinji"
Hannu yasa zai sharemin hawayena
Banyi wata wataba nafada jikinsa ina cigaba da kukana
Bayana yafara bugawa alamar rarrashi Yace
" shikkenan yi Shiru banasan kukanki"
Dagowa nayi ga hawaye a fuskata dukan wasa Nakai masa a kirjinsa, nace "kaiko? Meyasa? Meyasa zakasa murabu?"

Shima cikin kukan Yace
" kiyi hakuri kinji nadena Bazan sakeba"
Sake rungumeshi nayi, babu gardama Shima ya rungume abarsa 🤣

Tsawon minti biyar suka dauka ahaka, itace tafara kokarin janye jikinta, cikin rada yaqara rungume ta Yace "please!!!"

Tsayawa tayi, tareda lumshe idonta, Shima Hakan yake awajansa, jinsa yake Kamar ba'a duniyar ba, baiqi ace sun dauwama ahakaba
Dataga Abin nasa ba sarki Sai Allah 🤣Hakan yasa taqwace kanta cikin sauri
Sakinta yayi, Amma still hannunta Yana cikin nasa, Yace "my feenah thank you"
Murmushi nayi masa kawai, yace "mekuke shiryawa ne? Medame kukesanyi Kuma nawa kike ganin zai isheku?" Nace "katambayi Zahra, zansa takiraka," yace "Ok"

Shiru ne yabiyo baya kawai muna kallan junanmu Kamar za'a sace dayanmu, Hakan yasa Nace

"My Ahmad"
na'am "my feenah,"

"kayimin alqawarin bazaka sake gudunaba"

Cikin rada Yace "Har abada
Bazan sake tunanin aikata abinda zai rabamu ba,"
kema kiyimin
Babu kunya nace "nayima"

Hannu na yakama yasanya min zobe Mai kyau da harafin A'N ajiki
Hannun nakalla yayi kyau sosai
Wani zobe yasake bani tareda miqomin hannun sa
Sanya masa nayi, yayi masa kyau sosai, shikuma ansa Harafin N'A ajiki
"Kiyi alqawarin barina acikin zuciyarki, Nima nayi alqawarin haka"

Daga masa Kai nayi alamar nayi masa

Matso da fuskarsa yayi dab da tawa, cikin rada Yace "kinyi alqawari?"
Nace" nayima my Ahmad"

Ahankali yaturo bakinsa daidai nawa ganin abinda yake shirin yi yasa na lumshe idona

Gyaran muryar da mukaji ne yasa cikin sauri muka kalli kofa

Yaya Tahir!!! Nafadi haka cikin zuciyata, aikuwa da gudu nayi cikin gida

Ahmad kuwa Sosa qeyarsa yayi, Yakalli agogon sa qirar Gucci dake daure a tsintsiyar hannunsa yace "ashe Har lokaci yaja haka
Bari intafi"

Tahir yace "Dan renin wayo, kazo kasamin qanwa agaba kana so kakoya Mata rashin kunya, wannan kuwa idan mukai muku auren zamu Iya zuwa gidanku?"

Ahmad yace "besty saida safe"

Tahir yace "ai baka isa ka tankaba, oh ni Tahir qarshan duniya yazo," 🤣

Ahmad yace "Tahir ya isheka haka Dan Allah"

Tahir yace "au Har kanada bakin Magana?"

Sunkuyar da kansa yayi Yana murmushi zai fice, Tahir yace " to Sai yaushe?"

Yace "ba Rana abokina, bazan dawoba, saboda idan nacika zuwa za'a samu matsala,"
Yana fadar haka yayi wuf yafice

Tahir yace "daka tsaya ai"

yanunashi da hannu yace wannan, wannan mutumin Ina tausayawa wannan yarinyar

Ina zuwa dakin danake nafada Kan gado, na lumshe idona, afili Nace "I luv u Ahmad"
Dakin husna naje tana shirin tafiya wajan mijinta Nace mata "saida safe," tace "to Sai Allah yakaimu," futowar dazanyi nahadu da Yaya Tahir, aikuwa kaina aqasa nawuceshi, ban yarda munhada idoba, shine de Yace "amarya saida safe," nikam babu bakin Magana

Har bacci yafara daukana naji qaran wayata, Ina dubawa Naga number Ahmad, cikin muryar bacci nadauka Yace "natasheki kina bacci kiyi hakuri," Nace "babu komai"

"Dama Kira nayi ince Miki I luv u kafin nakwanta," 🤣

Nace "to ngd"
Yace "me kikace? Ai baki isaba saikin fadamin Nima"
Cikin muryar shagwaba Nace "Kai Yaya Dan Allah, kanasani Jin kunya fa, gashi Nan Kasa Sai kunyar Yaya Tahir nakeji,"

Ina jiyo murmushin sa Yace "tokiyi hakuri, shikuma Tahir Ai nayi masa Magana babu abinda zaice Miki kinji?
Amma kiyi hakuri bazan sakeba"

Nace "toshikkenan, saida safe," Yace "um um nide Sai kin fadamin"

Ahankali Nace " I luv u too"
Dif nakashe wayar

** *** **

Gyara sosai nakesha, Ciki da waje, banda magunguna danake amfani dasu, na tsugunno daban na wanka daban, fatata tasauya duka, naqara fari, nayi kyau sosai, jikina banda laushi da tashin qamshi babu abinda yake, gashin Kaina kansa qamshin dayake na dabanne, babu abinda zance da husna Saide Allah yabiyata,

biki yarage saura Kwana hudu muka taho nida husna da Zahra, Amma su anty za maimuna su Kala su kaka sundade Azaria

** *** **
Rana Bata qarya

Ayaune dubban jama'ah suka shaida daurin auren Ahmad muhd marzuq Tare da nafeesa mu'az Akan sadaki nera dubu tamanin lakadan ba ajalan ba, Wanda manya manyan Yan siyasa suka halarta, cikinsu harda gwamnonin wasu jihohin

bakin Ahmad Kamar gonar auduga, yayinda suka hade cikin farar shadda, tareda babbar Riga, agogo fari qirar Rolex, farar hula me sirkin ash, sunyi mugu mugun kyau irin na qarshe din Nan

Kawai pictures suke tayi shida abokansa, banda masu video dasuke nasu, cikin su harda Yan gidan TV, domin sunaso su haska bikin akafafen Yada labarai

Mrs usman ce🖊️
[5/4, 6:08 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Dedicated to my family

Second to the last page

64

Abba gaba daya Yama rasa inda zaisa baqi wasu daga kusa wasu daga nesa
Tahir Yana fama danasa jama'ar Ahmad haka
Ana gama daurin aure, jama'ah suka fara raguwa
Kansa ne yafara sarawa saboda hayaniyar datayi yawa
Nan da Nan yace "muhd yakamata mudau hanya kokuwa?
Ina su wadannan yaran suke?"
Marzuq ne ke wannan maganar, tsoho Mai ran karfe
Daddy yace "to abbey, Bari akirasu"
Awannan lokcin suna cikin gidan tareda abokansu, suna gaida mama da danginta, duk inda sukayi Sai an kallesu, saide idan Kun gaisa ne, zakaji Ana cewa Ina angonne, shikuwa banda waige babu abinda yake Wai kozai danga matar tasa
Suna futowa daddy yahango Tahir

Dan haka yayi masa Magana Akan yakamata su tafi Tahir yace "daddy Bari inkirashi"
Wajan Ahmad yatafi Wanda yatsaya ake tayi musu pictures shida mutane, babbar Riga Sai tashi Sama take,🤣 Tahir yace " Kai to wallahi mutafi, daddy da wancan tsohon suna jira"
Ahmad yace" yaza'ai natafi Tahir Bayan banga matata ba "
Tahir yace" yau munga ta kanmu, daga daura auren,?" Yace" Tahir bafa zan tafi ba saina ganta"

Nikuwa Ina zaune tareda qawayena dasu aysha, Zahra, dawasu daga cikin Yan unguwa, wayata ce tadau qara, Ina dubawa Naga Ahmad ne, Kai tsaye Ina picking cewa yayi zasu tafi infuto mu gaisa
Aikuwa nazaro mayafina nafuto, Ina zuwa kofa muka hadu da husna tace "Ina zakije," nayi Mata bayani, tace babu inda zakije, kikirashi kifada masa yayi hakuri

Nikuwa ba musu najuya, "feenah "
Takira sunana, Ina juyawa tayimin nuni da dakin Abba tace kije can dakin kikirashi
Saida taga nashige dakin sannan tatafi cikin ranta tana fadin badai mutanan su Tahir bane,

tasan Sarai ba hakuri,🤣 musanman ma Ahmad yanda yake wannan rawar kafar
Nikuwa Ina kiranshi yafara fadin, "kina dede Ina?" 🤣

Nace "Yaya anty husna tace bazan zoba, kayi hakuri Yaya tunda ai anjima zamu hadu ko"

, 🤦🏻‍♂️dafe kansa yayi da hannunsa yace " my feenah yanzu kowama haka yake ganina ko?"
Nace "kamarya?"

"To my feenah gashinan Bana Iya boye soyaiyar danake Miki agaban mutane, ai duk laifinki ne kekika maidani haka"

Nace "Yaya kabani Daria" , yace "tobani abata"

"Yaushe zaku tafi?"

"Yanzu zamu tafi tunda anhanani ganinki" , Tahir yaduba yace " muje Tahir"

Tacikin wayar naji Yana masa Magana, Nace "Wai tare kuke,"

Yace "emana, menene?" Nace "kaiiii"
tare da zare Ido, dif nakashe wayar
Wayar ya kallah Yana murmushi yace "su Tahir manya Wai Kai akejin kunya"
Tahir yace "to menene kana mamaki?"
Yace "no bawani mamaki kawai de Naga kunyar marar kunya ai bata lokaci ne" 🤣

"Kacika baki dayawa yaro"
Inji Tahir
Ahmad yace "yaro Kuma? Yaro de? Yanzu nine yaro? Zakayi mamaki na"

Tahir yace "kamarya?" Shima Ahmad din yace " a a abar zancen"

"Ina kuka tsayane tun dazu ku ake jira,"

"kayi hakuri daddy" inji Ahmad
Mota suka shiga inda su daddy suka sake yin sallama da Abba dasu ammu sannan suka tafi

Mukuwa muka ci gaba da hidimar biki, photuna de anyi su selfie kuwa ba'a Magana
Inyi wannan shiga incire asake wannan, ko Ina zani Ina tare da Zahra
Anyi kidan qwarya, inda su Kala suka taka tasu rawar

Da magrib aka fara shirin kaini kano, kuka de Kam nashashi dakyar aka rabani da jikin mama
Shikansa Abba saida yayi qwallah
Ammu ne yadaukemu

Har mukaje kano
Gidansu Ahmad mukaje nide kaina Yana qasa, dazamu shiga yace inshiga da Bismillah haka kuwa a kayi

Saida ammu yakaini Har dakina Wanda yaji furnitures na gasken gaske, sannan yaqaramin fada Shima yatafi

Ina hawaye husna dasu aysha da Zahra ne suketa ban baki
Kala ce tareda wasu Mata tace nataso muje part din su hajia
Aikuwa haka akayi
Muna zuwa su momy suka karbemu hannu biyu, mamy hakima kuwa janyoni tayi jikinta, Sai Nan Nan take Dani
Saudat kuwa takama hannu na tariqe, su kalatynmu suna ganin wannan tarbar da aka mana, sukace tosu zasu tafi, saikuma gobe idan sunzo dinner insha Allah
Dahaka suka tafi gaba dayansu, Ina riqo Zahra tana fizgewa

Dagani saisu momy saikuma baqi Wanda sukazo bikin dasuke ta tururuwar zuwa wajena Dansu ganni
Mamy hakima tace "hajia inaga wannan suje daki ko, Kota samu tahuta"

Momy tace "eh Hakanma yayi," tadubi Saudat tace
" sauda kuje daki tayi wanka taci abinci saita kwanta tahuta"
Saudat tace" to momy "
Kaina aqasa muka tafi, Wai nice a cikin Gidansu Ahmad, amatsayin matarsa, babu nacin da saudat batamin ba, Akan nazo tun muna diploma naqi zuwa, Amma yanzu gashi nazo amatsayin surukarsu

Husna nafita harabar gidan takira Tahir tace
" sweety kazo kadaukeni," alokcin suna tare da Ahmad Yana masa naci su tashi su rakashi wajan matarsa

Tahir yaceda husna "wai harkun gama ne?"

"Eh mungama"

"Amma kina ganin babu damuwa kubarta ita kadai?"
"No ba ita kadai bace, tana wajansu momy," Tahir Yace" eh hakanma yayi, gani nan zuwa "

Yadubi Ahmad Yace" to ango muje nakaika gida, Nima zan dauko maman twins"
Ahmad Yace " yauwa dama namatsu naje wajan matata," Tahir Yace "tome mata, ai tana wajansu momy, saide kabita can,"
Ahmad Yace "kamarya bangane ba? Menene amfanin namu part din?"
Tahir Yace " to saide Nakai ka katambayi su momyn" 🤣

"Dan Allah Tahir Kadena batamin Raina, haba Dame zanji, danaka ko danasu"
Kafadarsa yadafa Yace
" man kayi hakuri
Matarka cefa, nasan cewa koma menene yafaru yanzu tana matsayin matarka ne, kawai idan munje kaje kadauketa saiku koma part dinku ai shikkenan"
Ajiyar zuciya yasauke Yace "shikkenan"

Suna zuwa gidan Tahir yarakashi ciki, daganan yadauki Husna, shikuma yayi part dinsa
Yana zuwa kuwa yanda yazata din hakane, Bata nan, Amma da alamun anshigo part din, koma menene zaije wajansu momyn ai yanzu
Kan gadon yadafa yarufe idonsa, daga bisani yatashi yashige toilet domin watsa ruwa

Saudat tace "sister gaskya wannan kunyar ta isa haka, kunaso Kuna wani noqewa," mayafin kaina nayaye nace
" jarababbiya, Ina ruwanki,"
kaina tafado tace "sister amarya,"

"wash Saudat Zaki karyawa mijina ni"
Tace "lalle amarya, yaude gaki a gidan nan, sister Kinga yanda kika koma kuwa? Wallahi kin qara kyau," nace "kema haka ai, kin girma"

"Eh lalle ma feenah nice nagirma ko "
Nace" Ina farouq," tace
" Yana nan wallahi, ai zaku gaisa kafin mutafi "

Wanka nashiga, nashirya cikin kayan bacci nakwanta, nan da nan bacci yayi awon gaba Dani , Saudat taja bargo tarufeni, sannan itama tafice

Wajan 11:30 yashigo part din, duk baqi sun kwanta, kasancewar sanyin da akeyi
Momy yagani afalo tana bawa ma'aikata umarni, domin su gyara gidan sosai kafin safiya

Da mamaki ta kalleshi tace "bakayi bacci bane dama?" Kansa ya Sosa Yace cam momy dama inajin yunwa ne, ko Zaki sa akawomin abinci? "
Tace" OK,"
Mai aiki ta qwalawa Kira, Yace"a a Barta momy kawai Bari in kwanta," tace "kace yunwa kakeji ka tsaya mana takawoma abincin," 🤣

Yace "to momy Ina Saudat, ko yaran gidan, kokuma...."
Tace "kokuma me? Kaga walady banasan shirme, wuce kaje ka kwanta dare yayi"

cikin shagwaba

Yace "momy Ina nafeesa?"
Kai tsaye tace "tajima da bacci, tace afadama saida safe" 🤣

Babu yanda ya Iya, haka yajuya Yana shafa qeyarsa, Yana waiwayen falon yayi part dinsa
Cikin bacin rai yake fadin mutum da matarsa Amma ahanashi ganinta, wannan wacce irin rayuwa ce
Yana tafiya Yana mita dahaka yaqarasa part dinsa, a wannan dare dakyar bacci barawo yasace Ahmad

** *** **

Yana zaune adakinsa yaharde Yana kallon tashar arewa 24 Kamar wasa yaga photon ta
Tuni yatashi zaune, abin Bai qara daure masa Kai ba saida yaganta tare da mijinta Ahmad muhd marzuq
Mekenan? Meyake shirin faruwa ne? Yaushe haka tafaru? Feenah ta auri Dan gidan Dan siyasa, Kenan dana Rabata da mukhtar masu qasar ta aura
Ato masu qasar mana Dan gidan deputy governor, gobe Kuma ai Dan gidan governor ne, gashi Yaron yaji Ana shi Kansa Mai kudi ne, Bayan babansa, ga kakansa dayake ji dashi

Lalle kuwa Idan hakane ya zalunci mukhtar, gashi yanzu yarabashi da feenah, shi yahanashi aurenta, Shima Kuma Bai same taba
Gashin Kansa ya hargitsa, ya ilahi, yayi zatan tunda yarabata da mukhtar dole zata hakura idan yakoma wajanta ta saurareshi, ashe shi cutarsu yayi gaba daya
Lalle dole yanemi yafiyar mukhtar

** *** **

Washe Gari
Ina tashi Wanka nayi, Ina futowa Naga Mai kwalliya tana jirana, zama nayi aka tsaramin kwalliya tagani tafada, sosai nayi kyau acikin material Mai shegen kyau launin ash color
Mamy hakima ce dakanta tazo tatafi Dani wani falo, tsararre, daddy da momy da marzuq suna zaune kaina aqasa nagaida su, kowa Sai Jana yake da fira, nide cikin kunya nake amsa musu maganarsu

Marzuq Yace "Toya kwanan baqunta" nace
" alhmdlh,"
Yace "kinajin dadi ai babu wata damuwa ko?" Nace "babu komai wallahi"

"Amma baki ganeniba?" Nace "ehh,"
"to nine marzuq" 🤣

Kallansa nayi da mamaki yanda naji hausa radau abakinsa, murmushi nasaki batare danace komai ba
Yace " to alhmdlh, Zaki tashi kuje unguwa yanzu zaku dawo"
Babu musu natashi muka tafi, bamu zame ko inaba Sai wajan passport muna tsaye yafuto aka bamu, wajan visa aka wuce Dani dayake Abu ne nakudi Yace zuwa anjima za'a kawo Har gida

Yayi mamakin lokcin daya dauka Yana bacci, ahanzarce yashirya yafuto yayi kyau cikin manyan Kaya
Sai sauri yake yazo yaga feenah, Yana futowa directly Dakin daddy yayi domin su gaisa, Yana zuwa kuwa yagansu gaba dayansu, suna gaisawa yakoma wajan marzuq
Daddy Yace "my son abeey yasa akai nafeesa wajan passport, yanaso gobe kushirya ku tafi sharil'asal (honeymoon)"

"To daddy itadawa suka tafi,* daddy Yace" itada Saudat da driver "
Cikin ransa Yace" driver"

Wato dawani qato aka hada amaryarsa suka fita, Bayan shi jiya babu yanda baiyi ba aka hanashi ganinta

Baiyi musu maganaba, Har suka qari firarsu suka gama

Da yamma aka shirya kowa yafara haramar tafiya wajan dinner
Nayi kyau sosai cikin yadi Mai tsada launin pink
Nasha kwalliya sosai nayi kyau, Ina Bayan Mota Ina jiran Ahmad yafuto, Yana shigowa driver yaja motor muka tafi, Har mukai Nisa baicemin komai ba, nice nayi qarfin halin cewa
" Yaya Ina yini?"
"lafiya"
Shine kawai abinda Yace
Cikin Raina nace tooo yau abin yazo
Ban daddara ba nasa hannu na naruqo nasa, shiru Yamin Yana Jina,
Taushin hannun ta neyake ingizashi Akan yadan murza hannun
Amma haka ya dake, yaqi kulata
😀
Har sukaje wajan dinner, Prince and Princess dake rijiyar zaki
Sosai an qawata wajan
Duk abinda kake buqata da kanka zakaje kazuba sosai abin ya qayatar da mutant sosai
Washe Gari akayi wata dinner a country mall, Iya qawayan amarya dana ango, daganan Kuma jama'ah suka fara watsewa

** *** **

"Mukhtar kaji de abinda nayima, Amma naroqeka kayafemin," aqasa ya zuba gwiwoyinsa Yace"

kayafemin mukhtar badan halinaba, saidan Allah "
" Kb hakika kacutar Dani, Amma babu komai nayafema, koba komai nasan kayi DANA SANI Akan abinda ka aikata, Amma hakika baka kyau tamin ba, babu komai, komai yawuce"
yasa hannu ya tashi Kb yarungumeshi
Shima Kb rungume mukhtar din yayi Yana kuka
, Kb Yace "mukhtar Dan Allah na roqeka Kasa feenah tayafemin itama," mukhtar Yace "karka damu insha Allah zanyi mata Bayani "

** *** **

"To daddy insha Allah zanyi mata Bayani," Yace "yauwa gobe Shima abeey zai wuce, saiku tafi tare, Bayan Kaga likita yadoraka Akan maganin saikuje ko dubai ne kusha iska, daga nan kuje kuyi umara kayi addu'ah sosai Akan Allah yabaka lafiya
Amma idan kun tashi dawowa kufara biyawa ta masar idan kunyi sallama dasu saiku taho gida ko
Sannan munyi Magana da Saudat tace tanasan tafiya Da baby tayi mata hutu, na Bata damar daukar ta "

Ahmad Yace" to daddy hakanma yayi nagoge "
Daddy Yace" zaka Iya tafiya "

** *** **

Nagama komai nayi Wanka nashafa humra, da turare iri iri
Nasa kayan bacci na Mai kyau black color
Kasancewar da farina saiyayi min kyau sosai

Hijabi na nake nema zansa naji anturo kofar Dakin, kallan kofar nayi, Ahmad ne, ido yazubamin yakasa dauke idonsa akaina
Hakan yasa nasan ya hijab dina
Dakin yaqaraso nace "sannu dazuwa"
Ataqaice Yace "yauwa"

Dakin yayi shiru daga baya Yace "me yasa jiya kikabi driver kuka fita"

Dasauri na kalleshi nace "ai daddy ne..." Katseni yayi Yace " saboda sune suke iko dake ko? Ace matata ahadata dawani qato amota"

Kafin nabashi amsa Yace
" yayi kyau"
Kishirya mana kayanmu gobe zamu wuce masar insha Allah

Nace "to"
Tashi yayi zai fita yaji wayata tana ringing, dubawa yayi
Sunan daya ganine yabashi mamaki
Afili yafurta

"mukhtar "
Ga wayarki Ana kiranki
Yayi wulli da ita Kan gado yafita yabar Dakin😀

Zama nayi aqasa jagab Kamar yar bori nace "nikam yau Naga ta kaina, meyasa mukhtar zai kirani"

Awannan dare masoyan basu rintsa ba kowa da abinda yake saqawa aransa

Washe Gari kuwa sukai sallama da kowa, suka Lula qasar masar, itadashi da tsoho marzuq

kowa Yana basarwa dasun hada ido zai kawar da Kansa

Mrs usman ce 🖊️
[5/4, 7:50 PM] ❣️DANGI DAYA❣️: 🌱DANA SANI 🌱

Writing by Amnah el yaqoub

Last page👌🏻

65

Da tafia tayi tafia Marzuq yatashi yakoma kujerar baya saboda yace yagaji, nikuwa
Har dare yayi idona biyu, Dana juya nakalleshi sainaga idonsa a lumshe, Amma Naga ba bacci yakeba, Hakan Kuma yasamo asali ne da kafarsa danaga Yana karkadawa
Kallan mutane nayi Naga kowa Yana harkar gabansa, daga masu danna wayoyinsu Sai masu bacci
Duk da inajin shayinsa Hakan Bai Hana na matsa kusa dashi nadora kaina akirjinsa ba, wata

wawuyar ajiyar zuciya yasauke, dama ya matsu yajita ajikinsa,🤣 Amma saiya dake ya share ta, dumi yafaraji akirjinsa, dasauri yasa hannu awajan
"hawaye "
Yafurta Hakan aransa, subhanallah, dasauri yasa hannu yasake rungumeta, sunkuyawa yayi daidai kunnanta yarada Mata akunne,"me aka Miki?" cikin shashsheqar kuka nace
" bakaine kaqi kulani ba"
Murmushi yasaki aransa yace "ashe nimade andamu Dani" 🤣
Cikin rada yace Mata "meyasa kikabi driver kuka fita? Sannan me wannan yaron yakira yafada Miki?"
Oh Ahmad kishi, nafadi Hakan araina
Nima cikin rada nafada masa jaddi ne yace muje (kaka kenan)
Shikuma mukhtar Allah baya kirana wannan dinma yakirani ne yafadamin wani Yana neman yafiyata,
" Waye? "
Nace masa" Wanda yasace mukhtar lokacin bikinmu "
Qara rungumeni yayi yace" ai nikam ya kyautamin, kobaki yafe masa Bama nikam nayafe masa "🤣

Daria yabani, Dan haka nayi Murmushi naqara tura kaina akirjinsa, nace
" to kayi hakuri, bazan sakeba kaji my Ahmad?"
Fuskarsa yasa Yana hada mana fuskokinmu waje daya, yace" bazan Iya fishi dakeba my feenah, nahaqura "

Nace"nagode mijina"
Murmushi yasaki yace "sake fada inji"

Nace "miji...."

ban qarasaba yarufemin bakina da nasa
Bakinta yakesha Kamar ba gobe, idonsu a lumshe
Hannunsa yasa asaman rigarta yafara shafa kirjinta
Dasauri tabude idonta tace "Yaya ajirgi fa muke"
Idonsa yabude da qyar baice komai ba yasake rungumeta, dahaka sukai bacci
Suna sauka basu zarce ko'inaba Sai gidan Marzuq, motoci bara'ah taturo aka daukesu, a lokcin biyu da rabi nadare muna zuwa makwanci aka bamu, gaskya tsarin gidan ya birgeni, ban taba tunanin kakan Ahmad Mai mugun kudi bane irin wannan, motoci haka birjik agidan, Kai jama'ah Kamar baza'a mutu ba
Kama hannuna bara'ah tayi muka tafi dakinta, dama nagaji, saboda haka Ina wanka, madara kawai Nasha nakwanta Sai bacci
Shikam Ahmad Yana bangarensa inda yasaba sauqa, Bayan yayi wanka yayi tagumi hannu bibiyu ya zubawa kofin shayi ido🤣
Yarasa meyasa mutanan nan suke masa haka, gaba daya yalura sun maidashi wani dutsi zaice ko gunki

Inba hakaba mutum da matarsa abi atakura masa, haka yahakura yaja fillo yarungume dahaka bacci yadaukeshi

Washe gari,dawuri suka fita asbiti shida Marzuq, a lokacin ko tashi banyi ba daga bacci, wajan wani qwararran likita sukaje, Bayan bincike da komai likita yabashi magungunan dasuka dace Ina kitchen nida bara'ah, Ina tayata girkin abinci, wasu abubuwanma nasu Wanda bansani ba, itace take qaramin bayaninsa
Riga da siket ne ajikina, na atamfa sosai dinkin Yamin kyau, hips dina ya baiyana sosai ajiki, Har muka gama, muna dining munacin abinci suka dawo
, gaba dayanmu muka hadu mukaci abinci, muna gamawa aka fara sabuwar fira, muna kallo muna fira, Ahmad Yana kwance akujera, nikam Ina zaune daga wajan kafafunsa aqasa bara'ah na gefena, inajin kafarsa Yana taboni nayi shiru na kyaleshi
Yamma nayi muka fita yawo, nidashi da bara'ah, Har wajan yan'uwanta takaini mun gaisa dasu, Wanda sukai mamakin Jin larabci abakina
Sai magrib muka dawo gida, abinci mukaci takama hannu na takaini Har dakin Ahmad, wata madara Mai kauri tabani tace nashanye, banyi musu ba nashanye, Bayan tatafi nafara, cire kayana, wanka nashiga inajin yanayi na Yana canjawa, nikam Allah yahadani dawasu irin mutane, a dinga duramin maganin Mata de babu qaqqautawa
Shi wannan dayake na larabawa ne, nan take yafara aiki, 🤣saboda tsabar sun shahara wajan kula da mazajansu
Dakin na sake gyarawa,nayi sallar isha nasaka kayan bacci, nafeshe jikina da turare, nakwanta, wayata na janyo, nafara Kiran Yan gida, daya Bayan daya, saida muka gaisa dasu, Zahra tace " feenah ansamu miji shiru akejinki, to dafatan de komai yawuce oga ya susuce" 🤣
Ajiyar zuciya nayi nace
" babu abinda yafaru, kinsan Yana sona renona yake"
Daria Zahra tasa tace
" kecema jaririya tsabar reno," fira muketa Sha Ina Bata labarin abinda nagani Wanda bamu gani dasuba lokacin da mukazo dasu, Ina waya da husna yashigo dakin, sallama nayi Mata nakashe wayar
Bargo Naja nashige ciki tare dace masa sannu dazuwa
Wani Mayan kallo yabini dashi batare daya amsa ba, toilet yashige yayi wanka, Yana futowa yagyara jikinsa Sai qamshin turare yake, madara ya tsiyayo a cup yasha, sannan yakawomin, blanket din danake ciki yayaye, inajinsa nayi Kamar bacci nake, saide yasan ba bacci nakeba tunda yaga idona Yana motsi, yace" gashi kisha wannan "
Yaji shiru
Aikuwa ajiye cup din yayi yafara min cakulkuli nan muka fara Daria dukanmu
Cikin shagwaba nace" haba Yaya Dan Allah bacci fa nake "
, yace"kidena wannan wasan Dan Allah, ungo Sha," karba nayi Nasha, yace "yauwa oya tashi kije kiyi alwala muyi sallah ko"
Gabanane yafadi, natuna karanmu dashi bawasa, jikina asanyaye naje nayi alwala, muka gabatar da sallah, muna idarwa nasake komawa nakwanta cikin tsoro
Shikuwa waya yadauka inajinsa Yana Magana da wasu daga cikin ma'aikatan companyn sa Saida yagama dasu yakira Tahir, yace "ango kasha qamshi Toya honeymoon din," Ahmad yace

"wanna irin honeymoon Tahir Sai yau aka bani amarya ta" , Tahir yace " yauwa suma Kenan suna tausayin qanwata, Allah sarki,"
Ahmad yace "aikomin wayon amarya... Qarasamin mutumina," Tahir yace "naqi qarasawar wallahi kabi yar mutane ahankali, Inba hakaba mu sakeka," Ahmad yace "a a aiba saki mutu karaba," Tahir yace" takalmin kaza"

Yaya Tahir
Lalle maza basuda kunya, yanzu dashi ake wannan firar, tokode jiyake Bana saurarensu
Nagama maganata acikin Raina nikadai nayi tsilu acikin bargo

Ina jinsa yakashe wutar dakin yakwanta, bargona yajanye yashigo ciki Shima
Ahankali yaradamin akunne na "amaryata, nasan babacci kikeba, idonki biyu"
Nide shiru nayi inajinsa
Juyo Dani yayi, muna fuskantar juna, ahankali cikin rada yace "my feenah!"
Bakinsa yakai Kan idona yafara kissing, Aikuwa nan idona yafara motsi
Murmushi yayi, dama yayi hakanne Dan Yaji baccin take kokuwa

Yace "my feenah," yafadi Hakan Yana shinshinar wuyanta, banda hannunsa dayake yawo ako'ina najikinta, kuka take marar sauti, hawaye kawai take, tana shashshekar kuka, cikin fitar haiyaci yace "kiyi hakuri feenah ahankali zanyi kinji
Bazan Miki da zafi ba kinji"
Kaina nadaga alamar to
Daga nan labari yasha banban, inda ya damqi abinda yafi daukar hankalinsa Yana masa wani irin sha Kamar ba gobe
Tun feenah na daurewa Har tafara kukan wahala, tafara kokarin tureshi, Amma inaaa yamata nauyi bazata iyaba
Cikin kuka tace "my Ahmad dazafi fa Kadena, Allah sunamin zafi"

Ahmad Kam bakinta yahade danasa yahanata Magana, yayinda ya maida hannunsa kirjinta

Feenah babu damar kuka Sai hawaye dayake zarya akumatunta
Yana cire bakinsa daga nata, tafara ihu tana neman temako, Amma inaaa! Ahmad Kam jinsa awata duniya shiya haddasa masa hawayan dadi
Tana kukan wahala Yana na dadi
Kawai babu abinda yake fita daga bakinsa Sai my feenah, my feenah

Daga haka nima nakoma Nigeria domin ingano muku abinda yake wakana

** *** **

"Uncle anty batada lafiya tun dasafe take cikin blanket, Sai amai takeyi"
Cikin tashin hankali farouq yaja hannun baby sukaje dakin saudat
Ahalin daya ganta, yasan daqyar zata Iya tafia, Dan haka baiyi wata wataba yasureta Sai asbiti

Tana kwance agado anyi Mata qarin Ruwa, likita yazo yace masa
" congratulation matarka tana dauke da ciki na sati biyu "
Farouq rungume likitan yayi, yafara ihun murna

** *** **

Nasha kuka na qoshi, idona ya kumbura yayi luhu luhu
Tana rungume a kirjinsa, Yana shafa bayanta, ahankali yace"my feenah, kiyi hakuri kinji bazan sakeba"
Cikin masifa nace "bawani hakuri, bakanaji nace Kadena ba inajin zafi, Amma shine kaqi ji"

Yace"my feenah banajinki, ki yarda Dani, nijinakema Cewa kike naqara yi "
Dukan wasa nakaiwa kirjinsa
Sake rungume ta yayi yanayi Mata ruwan godia

After one week
Soyaiya sosai Ahmad da feenah suke zubawa, zuwa wannan lokcin tafara sabawa dashi, dangane da bangaren auratayyarsu
Suna yawo ko'ina babu inda basu zagaba amasar, wataran sun fita sukazo wucewa ta wani titi
Ahmad yace "kalli can," tana kallah tasa Daria, yace " ai dole kiyi Daria a lokacin kinaji Ina kiranki kika tafi kika barni
Acan wajanfa nasuma"
Ya nuna Mata wani waje
Feenah tace "suma Kuma?" Ahmad yace

" kina wasa da irin soyaiyar danake Miki feenah
Daga nan ne ai likita yace akula Dani sosai Ina gab da kamuwa da ciwon zuciya"
Rungume Shi nayi, nadora kaina Akan kafadarsa
Nace "Allah sarki kayafemin my Ahmad"
Yace " bazan yafe mikiba, saikin fadamin rashin lafiyar datake damunki Har Abba yace likita yace kidena tunani"

Ajiyar zuciya nasauke nace "hawan jini"

Tuqin dayake yadaina yanemi waje ya faka yace "meya haddasa Miki hawan jini my feenah"
Nace "a lokcin damukabar masar muka koma Sudan
Alokcin Zahra tayimin nasiha Akan inyi hakuri muci gaba da Soyaiya dakai
Alokcin naduba account dinka na Facebook da niyyar inyi ma Magana, Naga pictures din aurenka da lailah," kallansa nayi nace
" wannan ne ya haddasa min hawan jini my Ahmad "
Rungume ni yayi yace
" mun fuskanci rayuwa iri iri nidake feenah, asanadin lailah

Kuma nasan insha Allah tayi DANA SANI "

nace" hakane, Allah yabarmu tare my Ahmad "
Yawo muka dannu, mune nan mune can

Satinmu biyu amasar muka wuce dubai, satinmu hudu, muka wuce Saudia, inda mukai sati biyu muke shirin dawowa masar
Ina kwance agadon hotel din da muka kama inata sharar bacci, yazo da Kaya ahannunsa niqi niqi
Tashina yashiga yi, yace
" tashi ki hada mana kayannan, Naga kinfara kin barshi, anya wannan baccin naki kuwa na lafiya ne?"
Shiru nayi masa natashi nahada kayan, Washe gari muka dawo masar

Tunda muka dawo masar naketa faman zazzabi Mai zafi
Marzuq ne yasa aka kirawo likita yadubani, anan yagano inada ciki na sati biyar
Marzuq da kansa yayi farin ciki da wannan labari, lafiya tasamu jikansa Kenan
Ahmad kuwa Kamar qwai haka yake lallaba feenah
Alissafinsa Kenan yakama satinsa uku dafara shan magani tasamu ciki
Daidai da shan Ruwa hanata daukowa yake, Bata aikin komai, Amma Kuma tanashan wahala, Dan dataci abinci yake dawowa, ko Cikin baby batasha wahala hakaba

Yana zaune afalo da system agabansa tazo takwanta ajikinsa Cikin shagwaba tace "Yaya Nide mutafi gida, Allah nagaji da Garin nan"

Ahmad yace "mekikace? Aikinga munkoma gida babyna yaqara girma yafuto, yanda dazaran mutane sun kalleki basai sun tambayeni yajiki ba
Kowa yasan nawarke"

Babu yanda na Iya haka nahakura saida cikina yayi wata uku sannan muka dawo Nigeria, Amma abinda yake bani tsoro shine yanda Cikin yake da uban girma Kamar Cikin wata biyar

Kowa yayi murna da dawowar mu, baby kuwa taga wajan Zama a gidan saudat a Abuja 🤣

Daga hutu tayi zamanta Acan, saudat ta riqeta, inda take reno biyu, baby da babyn cikinta

Watan cikina takwas saudat ta haihu tasamu mace inda aka saka Mata sunan mahaifiyar farouq zainab ake kiranta da Islam

Alokcin cikina yayi nauyi, idan nazauna afalo Bana komawa daki Sai dare, sallah a zaune, komai yimin ake
Ko motsa Cikin da'akace inayi, daqyar nakeyi saboda nauyin cikina

Alokcin ginan Ahmad yayi Nisa inda yake tanfatsa mana gida nagani nafada

Bayan sati uku nafara matsanan ciyar naquda, inda Ahmad ya gigice Yama rasa abinda zaiyi Yanda nake kuka Shima haka yakeyi, Yana Cewa
" bazan sake ba feenah kiyafemin, wallahi bazan sake Bama bare kisamu wani Cikin" 🤣

Ganin Kamar baya haiyacinsa yasa Tahir yajanye Shi Yana rarrashin sa, ita Kuma aka shiga da ita labor room

Husna da mamy hakima ne a asbitin Sai mama damima dasuka qi Zama suka biyo mamansu

Awata biyar Ina naquda Mai zafi sannan nahaifi dana namiji Mai kama da Ahmad sak
Baccin wahala ne yadaukeni, banyi minti talatin da farawaba, nafarka dawani irin ihu
Cikin azaba nafara wata sabuwar naqudar, Nasha wahala sosai daga baya nahaifi wani Yaron Shima de Kamar Ahmad dinne, basuda banbanci dukansu, hadda yatsun su da girar da hancin duk na Ahmad ne, fari ne kawai suka dauko na feenah

Awannan Rana anyi murna sosai, asbiti yacika da Yan dubiya masu ganin twins

Mama da mima kuwa Zama sukai Kowa tadauki daya

Mama tana ga qanina mima ma tana fadar haka da dayan yaron ahannunta

Bayan an sallameta zasu tafi gida, Tahir yagama zuba musu tarkacen kayansu aboot din motor Ahmad
Ta window ya leqo yace
" to sweetheart ki kulamin da kanki"

Yaradawa Ahmad akunnansa yace
" mutumina da fatan de bazaka qara yiba" 🤣

Daria sukasa gaba dayansu

Bayan sati daya akayi suna Yara daya yaci sunan Marzuq daya Kuma yaci sunan Tahir

Ana kiransu da haneef da muneeb

TAMMAT BI HAMDULLAH

anan nakawo qarshen wannan littafin nawa na DANA SANI abinda muka samu daga ciki Mai kyau Allah yabamu ikon yin amfani dashi, marar kyau Allah yabamu ikon watsi dashi

JAN HANKALI
Ataqaice wannan littafi Yana nuni ne Akan mutane sudaina zurfin ciki
Ahmad yayi zurfin ciki baiyiwa iyayensa bayanin abinda faru tsakaninsa da feenah ba, inda ace yafada musu komai da iyayensa bazasuyi fishi dashiba Har suna ganin duk gidan yafi Kowa kawo matsala ba, gashi Kuma shine babba

Saboda haka yakamata yan'uwa mudena zurfin ciki

Nabiyu kadinga Bawa dan'uwanka dama yanama bayani idan Abu yafaru tsakanin ku

Bawai kaqi bashi dama ba Kamar yanda feenah tayi

Shiga motar saurayi Ana fira, ya riqe Miki hannu Kuna Magana Kamar yanda Ahmad yake yiwa feenah duk ba abune Mai kyau ba
Allah yasa mudace amin

GODIA
ga daukacin jama'ar maman Abba novel mussaman Respectable

JINJINA DA GODIA GA
jama'ar

AMNAH EL HAUSA NOVEL

LOVELY FAN'S

HAUSA NOVEL ONE

ZAFAFA

LITTAFIN HAUSA GROUP

SAI MUN HADU ASABON NOVEL DINA NABIYU,, WATA SHEKARAR INSHA ALLAH MAI TAKEN

((BURINAH))

ZAMUGA SOYAIYAR AMAL DA DADDY 💃

MRS USMAN CE😃